🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

Alhmdllh Allah ina godiya da ya bani ikon d'ora alkalamina akan sabon littafina mai suna BAKAN GIZO, Allah ya kareni da sharrin dake cikin wannan littafi, alkhairan dake ciki kuma ya sadani daku makaranta gaba d'aya👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻

labari ne wanda ya k'unshi;
Cin Amana
Tausayi
Yaudara
Daukar fansa
Tawakkali

PAGE 1

****

Abokai ne su biyu d'aya a jikin mota tsaye yayinda d'aya yake tsaye suna magana, a bakin k'ofar wani gida, wanda a duba d'aya zaka gano cewa sabon gida ne, saboda yasha kayan k'arau tareda sabon fenti, gida ne naji da fad'i wanda gaba d'aya unguwar ba wani gida da ya kamo k'afar shi, duk da unguwar ta kasance ta manyan masu, wadda sai kasha gishiri ne kake gini a unguwar.

Salis ya kalli Nasir, a cikin fushi dake kwance a kan fuskarshi, wanda ya kasa b'oyuwa a fuskar shi yace;

"Nasir shin nine dai nace zan auri Amrah ko? to yanzu nafasa, bazan aure ta ba, don haka ni ba ruwana da duk abunda mutane zasu fad'a akan haka, aure dai ne ni wallahi na fasa bazanyi ba"

Nasir yabi salis da kallo, tamkar wani sakarai, saboda tsananin mamakin da ya bashi, ganin rashin hankalin da yake k'ok'arin aikatawa, ace saura kwana biyu aurenshi ya dawo yanzu yace ya fasa, shin me hakan yake nufi?, su zama k'ananan mutane ko yaya?, a cikin damuwa nasir yace;

Wai salis kana cikin hankalinka kuwa?, amrah ce fa yarinyar da ka mato akan k'aunarta,

yarinyar da kace zaka iya salwantar duk abunda ka mallaka , domin ka sameta, shine yanzu ana saura kwana biyu aurenka da ita kace ka fasa, kuma ka fad'a da bakinka ba wani laifi da tayi maka ra'ayinka ne hakan, shin don Allah me ya shiga k'wak'walwarka ne salis?, wanda ya birkice lissafinka kake son kayiwa kanka wannan d'anyen aiki?, kayi tunani fa, yanzu don Allah idan yarinyar nan taji wannan zance, wane hali kakeso ta shiga?, ta sakankance akan kwana biyu ya rage, yanzu kwatsam taji wannan mummunan sak'o?"

A zabure salis ya fara magana tamkar wani tab'ab'b'e yace;

"Nasir ni wad'annan lissafe lissafe naka baya gabana, aure ne na fasa bazan auri amrah ba, koda daga ni sai ita muka rage a duniya, kaje na barmaka ita da duk wani abu da na kaimata, sadaki na lefe na, duk na bar maka kaje a d'aura maka auren da ita, amman nidai wallahi da in auri Amrah gwara ace in mutu yanzu, kaje kawai idan kana buk'atar auren kuyi, nidai kam bazanyi auren ba na fasa"

Nasir zai fara magana, salis ya katse shi da sauri, ta hanyar cewa;

Bana buk'atar duk wata magana da zata fito a bakin ka, dangane da wannan magana, kaje kawai Allah ya baku zaman lafiya.

Yana k'are maganar ya juya ya shige get d'in gidanshi da yasha fenti sai k'yallin sabunta yakeyi, ta hanyar 'yar k'aramar k'ofar, yana shiga ya bugo k'ofar da k'arfi.

Nasir ya bishi da kallon mamaki, ya dad'e tsaye a wajen, yana ta tunanin anya salis ba jinnu akansu?, jiki a sanyaye ya fad'a motar shi yaja, ya bar k'ofar gidan sai tunanin mafita yakeyi, saboda shi har ga Allah baya jin son Amrah a ranshi, amma saboda ya tausayin halin da zata shiga in taji dole ne ya amince ya aureta, don a cewar shi wannan tozarci ne babba salis yake shirin yiwa Amrah.

Tofa d'and'ano daga littafin Bakan gizo....

Akafta 😜

D/Auta 👌

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

PAGE 2

****

Amrah a bayi tana wanka, sai tunanin ango angonta na jibi takeyi, a zuciyarta sai wassafa yanda zasu shinfid'a rayuwar aurensu, mai cike da k'aunar juna takeyi.

K'arar kiran wayarta ne ya katse mata, daddad'an tunanin da takeyi, aguje ta saka zane da kumfa a jikinta ta fito, saboda sautin kid'an da taji ya tabbatar mata da cewa habibinta ne ya kira, saboda caller tone d'in da tasaka masa daban ne dana kowa.

Abokanta dake cike da d'akin, sai tsarguwa suke yimata,tana dariya ba tareda tace dasu komi ba, jikinta yana b'ari ta fisge wayar dake hannun wata k'awarta, a cikin zumud'i ta kasa jiran taji abunda zai fad'a, saboda shauk'in son da yake kwasarta, ta rigashi magana da cewa;

"Habibina! Yanzu nike son inkiraka, ka turo mun mota gasu zee nan sun zo, ni kawai suke jira zamuje gidan lallen"

A d'aya gefe salis ya yamutsa fuskarshi, tamkar yaji sak'on mutuwarshi, a cikin bak'in cikin sunan da ta kirashi dashi, wai habibi, yace da ita;

"Waye habibin naki?, ni bari kiji in fad'a maki, daman na kiraki ne in fad'a maki cewa, na fasa aurenki, lefe da sadakin da na kawo maki, na barwa mijin da duk yazo da nufin zai aureki, na bar masa kyauta halas malas, ina maki fatar alkhairi ke da shi Allah ya baku zaman lafiya, amma kisani koda wasa kada kiyi tunanin zaki k'ara samuna a waya, kuma duk wanda ya kuskura ya nemeni da maganarki, sai na wulak'anta mutum, don haka a kiyaye zuwa gidana ko gidan iyayena"

Yana k'are maganar taji kit! ya kashe wayar, Amrah da tunda ta fara jin lafuzzan da ke fitowa a bakin shi, jikinta ya d'auki rawa, k'afafunta suka kasa d'aukar gangar jikinta, ba shiri ta fad'i zaune sharaf, fuskarta d'auke da wani tashin hankalin da ya ziyarci ta ba shiri, hawaye sai zuba

sukeyi wasu bayan wasu, tana jin k'arshen maganganunshi, masu kama da saukar aradu a kanta, wani k'unci ya ziyarci zuciyarta, wanda yasa zuciyar ta kasa hak'uri har saida tayi sanadin da bakinta ya bud'e ta kwarma wani irin gawurtaccen ihu, tareda buga wayar a k'asa duk ta tarwatse.

Da sauri k'awayenta suka yo kanta, mutanen dake cike da gidansu wad'anda suka zo domin bikin, daga garuruwa mabanbanta suka yo d'akin aguje hankali a tashe, suna tambayar me akayiwa amrah?,.

Amrah dai sai fisge fisge takeyi, tana wani irin kuka na tashin hankali, sai sanbatun kiran ya fasa aurena takeyi, zanen dake d'aure a jikinta sai yakice shi takeyi, ana maida mata saboda tsananin furgicin da ta shiga, batama san a yanayin da take ba, kuka takeyi iya k'arfinta, tana kururuwar fad'in ya fasa aurena.

mahaifiyarta dake rik'e da ita, saboda rud'ewar da tayi, ba shiri ta wankawa Amrah mari tareda katsa mata tsawa tace;

"Amrah k'i dawo a hankalinki kiyi muna bayanin abunda yake faruwa, me akayi ne kika shiga cikin wannan tashin hankali, don kawai kina son ki d'agawa mutane hankali, meke faruwa dake ne waya fasa aurenkin da kike fad'a?"

Amrah tana jin zafin saukar mari a kan fuskarta, ba shiri ta dawo a cikin hankalinta, hawaye na tsiyaya a fuskarta bakinta yana rawa tace;

"Salis ne ya bugo man waya yake sanar dani wai ya fasa aurena, lefe da sadakin da ya kawo, duk ya barwa wanda yazo da nufin aurena, yace kuma duk wanda ya nemeshi akan yaji ba'asin maganar sai ya wulak'anta mutum"

Ga baki d'aya d'akin aka d'au salati, kowa da jimamin abunda yake fad'a, mahaifiyar Amrah ba shiri takai zaune, sabida jikinta yayi mugun sanyi, a cikin muryar kuka tace da Amrah ;

"Me kikayi masa da zafi ne?, da har ya zab'i ya yimuna wannan tozarcin?"

Amrah tana kuka tace ;

"Wallahi mama banyi masa komi ba, yanzu haka jira nikeyi ya turo mota muje wajen lalle, don jiya na fad'a masa yace bazai sami damar zuwa ya kaimu ba, don akwai wasu bak'in abokanshi da zasu zo daga USA, zaije ya dauko su, a filin jirgi"

Aiko dai ko yanzu wata kabbarar mutanen dake d'akin sukeyi, kowa da abunda yake fad'a akan salis, don mamakin wannan abu da yayi, saboda dukansu sunsan yanda Salis yake son Amrah, don ko wannan gidan da suke zaune shine ya basu shi, suka dawo a ciki, b'arin dukiya yake yimasu sosai da sosai.

Daga nan suka dinga baiwa amrar hak'uri, akan tayi imani da k'addara tasa a ranta hakan shine alkhairi, suna cikin wannan maganar ne, wani k'anenta ya shigo yace;

"Amrah kizo ga Nasir nan yazo yana son ganinki"

Jikin Amrah har rawa yakeyi wajen saka zunbulelen hijabinta, har takai k'ofa zata fita, k'anwar mahaifiyarta, ta kirata ta dawo, tace da ita ta saka koda doguwar riga ne kafin ta taje wurin mai kiran nata, sannan hankalinta ya dawo mata ta tuna daga ita sai zane ne, da sauri ta jawo wata doguwar rigar ta ja hijabi ta fita kamar zata tashi a sama saboda sauri.

Nasir tsaye a jingine da motar shi, fuskarshi ba walwala ko kad'an, ganin yanayin da Amrah ta fito, ya tabbatar masa taji abunda yake faruwa, yaji kunyar kallonta, sannan ya tausaya mata matuk'a, asanyaye Amrah ta gaidashi, tareda zubowar wasu sababbin hawaye, shima kanshi yaji saukar hawayen akan fuskarshi, saboda tausayin halin da ta tsinci kanta a ciki na bazato ba tsammani.

A cikin sanyin murya Nasir yace;

"Ki daina kuka, ni a shirye nike zan aureki idan kin amince, rana da lokacin da aka saka duk abarsu yanda suke, idan kinyi shawara kinada number ta sai ki kirani ki sanar dani"

Amrah ta k'ura masa wani kallo, wanda ni kaina bansan taya zan fassara maku irin kallon ba, saboda abun tana kallon shi kamar a mafalki, ko shirin film, ko novel.

Kuyi mata bayani a cikin inane ake wannan kwacagiya🥶

Bazanyi posting buk d'in a ko'ina ba sai a group din D/Auta novel fan's mai bukatar group din tayi man magana zan bata link.

Akafta🦹

D/Auta👌

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

littafin bakan gizo littafi ne wanda zan dinga post a group d'aya wato D/Auta novel fan's duk wadda take buk'atar book d'in zatayi magana sai asaka ta, ban hana a watsa shi a sauran group ba, amman ni dai a group d'aya zan post🥶

PAGE 3

****

Nasir ya gyad'a kai alamar tabbatarwa, sannan ya k'ara da cewa;

"Ki shiga gida kiyi shawara, duk abunda kika yanke sai ki neme ni"

Amrah a cikin tuk'owar wani kuka ta juya, zata shiga gida, ta k'ara juyowa a cikin tantamar abunda yake shirin faruwa, Nasir yana nan a tsaye inda ta barshi, duk'e da kansa a cikin damuwar da shi kad'ai yasan me yakeji, ya d'ago kansa yakai kallonshi gareta, ganin har yanzu kamar bata gasgata abunda yace ba, yayi murmushin k'arfin hali yace da ita;

"Ni nasir na amince zan auri Amrah, budurwar abokina salis da ya fasa aure"

A guje Amrah ta fad'a gida, tana wani kuka a cikin d'imaucewa, saboda yanzu ta k'ara yarda da gaske salis ya gujeta, ba shiri ta zube tsakar gida tana gunjin kuka, sai kace wata 'yar k'aramar yarinya, gaba d'aya akayo kanta da tambaya, amma ita kam bilhak'k'i da gaskiya kukanta takeyi.

A cikin damuwa kowa yayi zugum ana sauraren kukan da take ta rerawa, masu k'aramar zuciya ma, suka fara tayata kukan, masu dauriyar ne suka nace sai bata hak'uri sukeyi, akan tayi imani da duk abunda ya sameta, ta rungumi k'addarar ta.

Bayan tayi kukan ta rage rad'ad'in abunda ke damunta ne ta fara yi masu bayanin kamar haka;

"Nasir ne abokin salis yazo, wai idan na amince shi zai aure ni, a rana da lokacin da duk aka saka na aure nida salis, a shirye yake da a d'aura muna aure ni da shi a ranar"

Gaba d'aya gidan aka d'auki sowar farin ciki, saboda kowa yaji dad'in wannan rufin asiri da Salis zai yiwa Amrah, mahaifiyar amrah tana zubar da hawaye tace;

"Ni mahaifiyar ki, NA amince da ki aure Nasir, kuma na bada goyon bayana d'ari bisa d'ari, saboda haka ki kwantar da hankalin ki, wani hanin ga Allah baiwa ne, Allah ya yiwa wannan yaro albarka, yanda ya rufa muna asiri shima Allah ya rufa masa"

Ga baki d'aya wurin aka amsa kiran; "Ameen".

K'anwar mahaifiyar ta wato aunty Asabe tazo ta tada ita, daga zaman dirshan d'in da tayi, ta kaita har d'akinta tace da ita;

"Kiyi hak'uri amrah, a rayuwa ba duk abunda kake so ne, yake zama alkhairi a gareka ba, wani sa'in abunda baka so shine alkhairin ka, saboda haka ki rungumi wannan aure da zuciya d'aya, ki koyawa kanki son wannan yaron, a hankali zakiji dad'in zaman auren ki, salis kuwa kiyi k'ok'arin fidda shi a ranki, kibar shi da Allah zai yimaki sakayya akanshi, yanzu ki tashi kuje wajen lallen keda k'awayen ki, kici gaba da duk shirye shiryen ki kinji?"

Amrah ta d'aga kanta tareda runtse ido, wasu hawaye suka gangaro mata akan fuska, tasa hannu ta dafe bakinta, dak'yar ta saita kanta ta fara magana, tace da aunty;

"Ni Aunty mamakin da nike tayi shine, shin me nayiwa salis a tsakanin jiya da yau ne?, da ya sauya masa ra'ayi akaina?, saboda nasan salis yana sona, ba ni ba ma, duk wani wanda yake a tare dani ya sani, ina da tabbacin indai har salis yana a cikin hayyacinsa, to inada tabbacin bazai tab'a fasa aurena ba, sai dai in har wani abu ne ya hau kanshi, wanda yayi silar saka shi aikata wannan aringizon tozarci a wurina, amman insha Allahu, zanyi k'ok'arin cire damuwar shi a raina"

Aunty Asabe taji dad'in abunda tace, a cikin daddad'an kalamai, tayi ta kwantar mata da hankali, har ta samu natsuwa tazo wa Amrah, sannan tace da ita, ta d'auko wayarta ta cire sim ta saka a wata wayar, ta kira salis ta fad'a masa ta amince, Amrah tayi k'ok'arin shanye kukan dake son tuk'ak'ota, tace;

"Aunty bazan iya kiran shi ba, wallahi nauyi nikeji "

Aunty Asabe tace ;

"To ki tura masa sak'o yama fi sauk'i"

Amrah jiki a sanyaye ta zare Sim's d'inta a jikin wayarta da ta kwankwatse, ta saka a wata

tsohuwar wayarta, da itama salis ne ya saya mata ita, kafin wannan da ta fashe, jiki a sanyaye ta tura masa text d'in ta amince da aurensa.

Sannan Auntyn tace da ita, ta tashi suje wajan lallen, Amrah bata so zuwa ba sabida ita komi ya fita a kanta yanzu, amma a haka ta daure ta shirya ita da zugar k'awayenta, suka tafi gidan lallen, amma ta zama so silent, don idan son samu ne, tafi son a barta ita kad'ai tayi jinyar zuciyarta, amman saboda ta ragewa kanta damuwa ta biye k'awayen, sai firar k'arfin hali akeyi da ita, sunyi ta bata shawara a kan ta so nasir kawai tayi auren ta, Allah zai saka mata a wajen salis.

**

Biki ya kankama sai hada hada akeyi, duk wani tsari da aka shirya na bikin salis da Amrah ba'a fasa shi ba, duk da zuciyoyin ango da amaryar ba dad'i amma a haka suka b'oye damuwar su akayi hidimar bikin aka k'are lafiya.

An d'aura aure, ankai amarya Amrah d'akinta,a gidan Nasir angonta, tareda rakiyar k'awayenta, 'yan uwa, da abokan arzik'i, sai fatan zaman lafiya ake yi masu.

Bayan kowa ya watse ne, ango ya shigo tareda abokin shi k'waya d'aya da ya rako shi, wanda yayi masu nasiha sosai akan suyi hak'uri da junan su, su baiwa masu cece kuce, da 'yan gutsiri tsoma kunya, saboda abokan Nasir da Salis da yawa basu goyi bayan auren ba, a cewarsu Nasir yaci amanar Salis tunda har ya aure masa budurwa, wasu ma cewa sukeyi saboda ya gano akwai b'oyayyiyar soyayya a tsakanin su ne, yasa salis ya fasa auren amrah, to yanzu koma minene sai dai fatar Allah ya basu zaman lafiya.

Nasir tun da yaje raka abokinshi, amrah bata koma jin d'uriyar sa ba, sai dai taji k'arar rufe k'ofar d'akin shi, tayi ta zuba idanuwa taga ya dawo d'akinta, amma shiru shiru bata ganshi ya dawo ba, ta kalli ledodin daya shigo dasu, wani kuka yazo mata ba shiri, ga wani tsoro da takeji ita kad'ai bata jin motsin komi sai na k'arar Ac'n dake manne a d'akin, a tsorace taje tayi arwallah ta fito ta rama sallolinta, da bata samu tayi ba saboda kacaniyar bikin, bayan ta k'are sallah'r anan ta b'ingire wani bacci mai k'arfi ya fisgeta, tareda wani mafalki mai firgitarwa da tayi.

A zabure ta falka tana ta waige waigen, ta ina zata ga wannan mutumin da ta gani a cikin mafalkin, da yake ta yimata bak'in albishir akan cewa;

"Amrah aurenki zai mutu, aurenki zai mutu!, zai mutu! zai mutu!, nan da sati biyu"

🤷🤷🤷

Akafta🤭

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Jinjinar ban girma a gareki sis Billyn Abdul ki dad'e kiyi lasting👍🏻mutunniyata👍🏻.

PAGE 4.

****

Ta waiga ko'ina bata ga kowa ba, zuciyarta ta tabbatar mata da cewa mafalki ne tayi, da sauri ta dunk'ule a wuri d'aya tana wani irin kuka gwanin ban tausayi, da taga kukan bazai fisheta ba dole tayi shiru ta koma tasbihi a cikin zuciyarta, tareda i tuno irin soyayyar da Salis yake yimata wadda baya shayin nunawa a gaban kowa.

A haka dai ta cenye rabin daren da tunanin tsohon masoyinta Salis, a lokacin ne wata azababbar yunwa ta ziyarci cikinta, ta k'yalla ido ta hango ledodin da Nasir ya shigo dasu, jikinta yana rawa taje ta bud'a ledodin, sai ga wasu kaji bank'ararru sun sha gashi mai kyau sai k'amshi ke tashi, jikinta yana kyarma ta dinga lodawa a cikinta, saboda rabon ta da ta zauna taci abincin kirki tun kafin wannan aringizon tashin hankalin ya rikito mata, sai da taji tayi dam sannan ta jayo fresh milk d'in dake cikin ledodin ta kafa kai har sai dai taji ba komi a cikin gorar sannan ta ajiye, aiko anan take wani bacci ya kawo mata ziyara, ta bingire a nan tana ta sharar baccinta, mai d'auke da mafarkai barkatai.

Bata tashi ba har sai da rana tayi shaa sannan ta falka a firgice, saboda mafalkan da take tayi wad'anda ta rasa gano tantagaryar me tayi mafalki akanshi?, da sauri ta fad'a toilet tayi wanka tareda d'oro arwallah tayi sallah.

Bayan ta k'are ta d'an murza mai da powder sama sama ta fito d'akin, tana shiga falon idanunta suka sauka akan fuskar Nasir dake zaune yana duba wasu takardu, a hankali ta k'araso ta zauna a d'aya daga cikin kujerun dake falon.

Duk da yaji takun zuwanta a palon amma bai d'ago kanshi ya kalleta ba, duba takardunsa kawai yakeyi har sai da ta cire girman kai ta kalle shi tace
"Barka da safiya."

Ko kallo bata ishe sa ba ya kwashi takardunshi ya shigewar shi d'akin shi, Amrah ta bishi da kallo mai cike da mamaki tace "Oh my god wai meke shirin faruwa da rayuwata ne?."

Ba shiri wani sabon kuka yazo mata, a hankali ta fara sharar hawayen da ke ta ambaliya a cikin kwarmin idanunta, wata zuciya tace da ita taje taji meke damunshi, amman taji tsoron zuwa batasan abunda zai biyo baya ba a sanadin zuwan, tana nan a zaune tana ta canki in cankar taje ko kar taje ne, sai gashi ya fito da shigar shi maikyau sai tashin k'amshi yakeyi, yana gyara zaman agogon hannunshi ne ya k'araso falon, ba tareda ya kalleta ba yace "Ni zan fita idan Adam yazo nema na ace ya sameni a majalisa"

Yana kai k'arshen zancen shi ya fara taku zai bar falon, Amrah tayi k'arfin halin bud'a bakinta tace dashi "A dawo lafiya."

K'anzil bai ce da ita ba ya fice abinshi sai k'arar tashin motarshi ta jiyo, tana nan zaune tana tunanin miye mafita?, aure kwana d'aya har ta fara shiga tashin hankali bayan wanda ta shiga na rashin masoyinta?, a cikin ranta tace "Nasir da nasan irin tanadin da kayi man kenan wallahi da ban amince na aureka ba, nafison inyi rayuwata ni kad'ai ba tareda k'arin wata damuwar ba bayan wadda nike aciki"

Tana kuka tace "Salis me nayi maka ka gujeni?, Nasir laifin me nayi maka ka zab'i ka walak'antani a cikin gidanka?, ina tausayin da ka nuna lokacin da ka ganni a cikin k'unci, a hakan kake nufin zaka share man hawayena?,wayyo Allah ka kawo man agaji rayuwa ta juyaman baya."

Tana a cikin wannan hali ne sai ga su zee sun yi sallama fuskokin su cike da annushuwa suka zauna, ganin yanayin da suka tarar da Amrah ne suka kalli juna sukayi wata 'yar shewa irin ta shak'iyanci, zee ta tashi taje ta rungumo Amrah a jikinta tace "Sorry tawan kowa fa da haka ya saba kiyi hakuri kinji.?"

Salma tana dariya tace "Oni salmomon mummy yau naga raguwa yanzu ke duk soyayyar dare d'aya ce ta saka ki zama wata sai a hankali haka?, kinganki kuwa dare d'aya kacal duk wani rafke idanuwa sunyi zuru zuru?, cab da sake yasin."

Amrah ta dallawa Salma harara tace "kefa kunya bata game jikinki gaba d'aya ba."

Zee tana dariya tace "share ta kawai kinsan ita k'urciya ke damunta, kinyi wanka ko kije yanzu ki yi sai mu jiraki?, don mun had'u da angon har mun gaisa nagan shi sai k'ylallin goshi yakeyi."

Amrah ta ture Zee tace "kun dameni da surutu fa ko kuyi man shiru ko yanzu in kora ku kubar gidannan."

Salma da Zee suka fashe da wata dariyar iskanci tareda baiwa juna hannu suka tab'a, Salma ta tashi ta fara rawa tace "Cau cau k'awata naji dad'i da komi ya faru yanzu shikenan sai ki rungumi mai gidanki, insha Allah zakiji dad'in zama da Nasir sabida guy d'in yasan kansa wallahi."

Amrah ta bisu da kallon mamakin yanda suke ta ganin wai zata yi zaman lafiya da Nasir,rashin sani yafi dare duhu, saboda ita ga baki d'aya auren ma ya sure mata ya fita kanta kwata kwata, don hausawa sunce jumu'a mai kyau tun laraba ake ganeta, ta dai yi shiru ne don hud'ubar da Aunty Asabe tayi mata ta shigeta sosai akan ta iya rufe sirrin mijinta, shiyasa tak'i bayyanawa su zee abunda ke faruwa.

Sai da suka tasa ta agaba ta sake wanka zee da kanta tayi mata kwalliya irin ta zamani, ta murza mata d'aurin d'ankwali mai kyau, Amrah ta fito amaryata sharr gwanin sha'awa sai k'amshi ke tashi a jikinta, suka shiga kitchen suka girka mata abinci gida sai tashin k'amshi yakeyi, Salma tace da Amrah
"Zo ki zubawa mai gidanki abinci da hannunki, don kar kice mun masa rowa"

Amrah ta amsa tana dariya ta zuba masa duk da tasan da wuya in har zaici abincin, suna kitchen d'inne ya dawo tareda Adam abokinshi, wanda shi kad'ai ne yayi supporting d'in auren a cikin abokanansu duka.

Suka shigo falon suka zauna suna ta fira a tsakaninsu, Adam yace da Nasir "Allaji wannan k'amshi father ta ina yake fitowa ne?, jar uba wallahi kai ka haye malam ka barmu da kwana a soro."

Nasir yayi murmushin da iya kacinsa leb'en shi, ya share maganar ya janyo wata suka ci gaba da firar su.

Zee tace da Amrah tazo ta kaiwa su Nasir abinci, Amrah ta waske tamkar ba wani Abu ta d'auki

abincin zata fita Salma tayi saurin shan gabanta tace "Haba dai hajjaju taku zakiyi a hankali kina yanga ba kije a haka ba tamkar wadda zata je masallaci."

Dukansu sukayi dariya, Amrah ta fice abinta ta barsu anan kitchen d'in suna ta iya shegen su, jiki a sanyaye ta nufo falon hannunta sai rawa yakeyi saboda jin tsoron abunda zai biyo a baya, aiko tana samu ta ajiye k'aton tiren a saman table d'in dake tsakiyar falon ta juya da sauri, Adam ya bita da kallo yana dariya yace "Sannu da k'ok'ari amarya."

Amrah ta juyo a k'agauce tace "Yawwa Adam ya gida?."

Suka gaisa a tsaitsaye ta koma wurin su Zee da iske sun zuba abincin su sai ci sukeyi suna dariya, saboda Salma da ke ta iskanci kala kala, Amrah tana shigowa zee tace "zo kiji k'urciyar da Salmo take fad'a wallahi dama mummy ta maidaki ciki ta haifo mana wata kawai kowa ya huta."

Amrah ta jawo wata kujerar roba ta zauna tareda cewa bani insha mutuniyata,zee tana dariya tace "Tace ne a fad'a maku idan aka kaita gidan bash bata son taga k'afar kowa a gidanta."

Amrah tana dariya tace "Wai ke salmo ko haihuwar ki akayi ne?."

Salma ta guma abinci a bakinta ta had'iye da k'yar tace "A'a daga sama na fad'o"

Haka dai sukayi ta firar su suna dariya har marece sannan suka tattara suka yi gida. Amrah taji dad'in zuwansu, don sun rage mata damuwar da take a ciki, Nasir kam tunda ya fita da Adam bayan sunci Abinci, bata sake saka shi a ido ba har sai da wata safiya da ta fito neman abunda zatayi break fast dashi, koshi ya shirya tsaf da niyyar fita amma ko kallonta baiyi ba ya ficewar shi, a haka suke zaman ba wata jituwa har tsawon sati biyu.

Ranar da ta cika sati biyun ne tana kwance akan gadonta tana bacci tareda miyagun mafalkan da ta saba, sai jin saukar mari tayi akan fuskarta, a zabure ta falka tana kallon shi a cikin mamaki tace "Nasir me nayi maka kuma da zaka dake ni?."

Nasir ya wurga mata wata jar harara yana fuci yace "Ni zaki ciwa amana?, lalle ma tambaya ma kikeyi me kikayi don kin maida ni wani soko, to bari kiji abunda kikayi tunda kin manta, Adam dake zuwa a gidannan ya kwana akan gadonki shima kin manta ko?, to jira yanzu zan tuna maki."

Aiko ya zaro belt sai saukar duka tayi a jikinta da sauri ta tashi a firgice tana neman hanyar da zata ceci kanta, amma ina ba dama caraf ya damk'o ta dukanta kawai yakeyi da belt tamkar bazai barta da rai ba, sai da ya tabbatar ta daku sannan ya ajiye belt d'in ya fiddo da wata

takarda a aljihun shi yace "Ga takardar ki kije gidanku na sake k'i saki uku."

Wayyo Allah😨😨😨

Akafta😊

D/Auta ce🧐

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Ashe zuma kama takeyi da k'uda bakan gizo shine yake shanye ruwa💃💃💃💃

PAGE 5

****

Yana k'are maganar ya cilla mata takardar ya fice, ranshi a b'ace tamkar wanda aka yiwa mutuwa, ya bar amrah anan tana ta murk'ususun bak'in ciki, saboda gaba d'aya jikinta zafi yake yimata, amman duk da haka lafazin saki da Nasir ya ambata yafi komi d'aga mata hankali, tafi jin zafin shi fiye da dukan da yayi mata, sai da tasha kukanta ta k'oshi sannan ta jawo wata 'yar k'aramar jaka, ta saka kayanta kala biyu a ciki, sabida batada k'arfin d'aukar wasu kaya cen da yawa, sannan ta zumbula hijabinta ta fito falo tayi tsaye tana tuno sati biyu da suka wuce, a lokacin da aka kawota kowa yana cikin farin ciki, yanzu kuwa gashi zata barshi tana a cikin tsananin bak'in ciki, duk da tarin nasihohin da aka ta yimata, gashi komi ya wargaje ba tareda sanin tantagaryar laifin da tayi masa, ta sauke doguwar ajiyar zuciya a fili ta furta cewa "Ya ALLAH kaine gatana kasa mutane su fahimci banida laifin komi akan mutuwar aurena."

Sannan ta janyo jakarta ta fito harabar gidan nufi get, sai gashi nasir d'in ya biyo ta da gudu yana kiran sunanta, a cikin mamaki ta juyo tana tambayar kanta, shin ita Amarah yake kira ko dai wata cen daban mai suna irin nata.?

Abun mamaki sai gashi ya k'araso fuskar shi sharkaf da kuka yace, "Don Allah kar ki tafi kiyi hak'uri ki dawo muci gaba da zaman mu, duk nasan akwai haramci a zaman namu tunda saki uku ne, amma nayi maki alk'awali bazan yi duk wani abin da nasan wata alak'a zata shiga a tsakaninmu ba, ai duk kece kika janyo da yanzu muna zaman mu lafiya, haka kawai ki dinga gayyato Adam yana kwanar man a gida don wulak'anci ma har a kan gadonki, wallahi bazan tab'a yafe masa ba tunda har yasa nayi abunda duniya zata yiman tofin ala tsine."

Amrah ta bishi da wani kallon tuhuma, akan cewa anya kuwa Nasir kanshi d'aya kuwa?, domin idan ba aljanu suka shiga kanshi ba ita rabon da ta saka Adam a ido tun washe garin da tazo gidan ranar da Nasir d'in yazo tare dashi suka ci abinci suka fita, to shine ganin k'arshe da tayiwa Adam, amman wai yanzu don kuturun wulak'anci zai biyota da wannan maganar banza, don kawai yana so ya kare kanshi daga sakin gangancin da yayi mayta, ita kuma yasaka zuciyarta tayi bindiga saboda bak'in ciki.

A hankali ta furta cewa, "Nasir kaje ni na barka da Allah kawai insha ALLAH sai ka girbi abunda ka shuka, k'azafin da ka jefe ni dashi kuma ALLAH zai saka man."

Tana k'are maganar ta zuro kanta a waje zata fito, yayi saurin rik'o jakar yace, "Yanzu idan kinje me zaki fad'a.?"

Amrah ta galla masa wata gwarzuwar harara da jajayen idanuwanta tace,
"Idan hauka ce take damunka to kaje gidan mahaukata a saka maka sark'ar mari"

Ta k'are maganar tareda fisge jakarta ta fito tana takunta a hankali hawaye suna ta zarya akan fuskarta.

A bakin titi ta fito tana neman abun hawa sai ga wata mota mai bala'in kyau ta faka, a hankali aka zuge glass d'in motar sai ga wani dattijo mai kamala ya lek'o yace,

"Ina zuwa ne 'yanmata.?"

Amrah ta kawar da kanta a sanadiyyar wata kekenapep da tazo wucewa da sauri ta tareta ta shige, tareda fad'a masa sunan unguwarsu da zai kaita suka tafi, mai motar nan yabiyo bayansu har sai da yaga gidansu, Amrah ta shiga gida da nufin ta turo masa kud'in, dattijon ya ciro kud'in ya biya sannan yayi saurin barin k'ofar gidan, mai napep d'in yana k'ok'arin gyara zaman, ta sai ga k'anen amrah ya fito da kud'i a hannu ya mik'awa mai napep d'in, shikam yana dariyar jin dad'i yace,

"Ai ni anbiyani kud'i na."

Yana k'are maganar ya cilla napep d'in shi akan titi.

Da kuka wiwi ta shiga gidan, hankalin mamarta ya tashi ba shiri ta fito tana salati, tareda tambayar lafiya? me aka yi mata.?

Amrah ta ciro takardar sakinta a jaka ta mik'awa mahaifiyarta, tun kafin ta amsa ta fara tambayar cewa, " takardar miye ce ne.?"

Amrah ta fashe da wani kuka gwanin ban tausayi tace, "Ya sake ni saki uku."

Ba shiri mamar ta fad'i a k'asa tayi zaman 'yanbori, tareda danna wata irin k'atuwar ashar tace, "Amman wannan yaro yakai shege ana yabonsa sallah ashe ko arwllah ma bai iya ba, amman Allah ya tsinewa wannan yaro,dama ace ba'a yi wannan auren ba yafi sauki fiye da wannan k'addararren aure na sati biyu, an tsunke igiyoyin shi gaba d'aya, har sai da ya gama maida man dake bajawara, sannan ya turo k'eyar ki gida da mummunar takarda."

Aiko inda take shiga ba anan take fita ba fad'a kawai mamar takeyi, Amrah ko taja jikinta ta shige tsohon d'akinta ta kwanta, sai tunanin rayuwar da ta tsinci kanta a ciki takeyi mai kama da almara.

Bayan kwana biyu labari ya bazu a unguwa da gurin k'awayenta da mutanen arzik'i, masu zuwa jaje suna zuwa 'yan gulma ba'a barsu a baya ba, kowa abunda yake fad'a sabida wasu da yawa sun camfa Amrah biyar maza takeyi shiyasa Salis yak'i aurenta, shi kuma Nasir sabida ya kamata turmi da tab'arya da abokinshi shi yasa ya sako ta, aiko mutane suka dinga k'yamarta fita ma ta gagareta daga har mahaifiyarta.

Tana a cikin zaman k'uncin NE ta gama iddah duk da abad'inan ce ba wata idda a kanta, don har tabar gidan Nasir ko hannunta bai tab'a rikawa ba balle takaisu ga saduwar aure.

Ranar Alhamis da marece ranar da tayi wata uku da kwana goma a gida, a k'unshe cikin gida tana jinyar zuciyarta daga mikin da abokai biyu suka shuka mata a zuciya, wani yaro yayi sallama ya shigo yace,

"Wai an ce ana sallama da Amrah"

Mahaifiyarta ta k'walla mata kira, tazo ranta a b'ace don taji abunda d'an duk abunda d'an aiken yace, a cikin nuna ba wasa uwar tace da ita, "Kije ana sallama dake a waje"

Amrah ta k'ara b'ata fuska tace, "Kai jeka kace bani nan."

Kafin ta kai zancenta k'arshe mahaifiyar ta jefo ta da wani kofi dake a kusa da ita, sannan tace, "Wallahi kiyi gaggawar fitowa kije ko yanzu mu kwashi 'yan kallo nida ke, daga ma kinsamu anzo wajenki, tunda kika fito ubanwa kika ga yazo k'ofar gidannan yace ke yazo nema?, zaki zo ki tafi ko sai sab'a ma ki.?"

Amrah ta janyo hijabin dake shanye a saga ta saka, sannan at fita kunbure kunburen fuska, bayan ta fita ne tayi arba da dattijon a cikin motarshi zaune k'afafun shi duka biyu a waje, Amrah tana ganin shi ta zaro ido a waje, saboda tuno lokacin da ta fara ganin shi ranar da Nasir ya sako ta, saboda kwarjinin da yayi mata ba shiri ta gaidashi, ya amsa a cikin sakin fuska yace,

"Kinyi mamakin ganina ko?, ai tun ranar sai da na biyoki naga gidanku"

Amrah tayi murmushi tace, "nagode, amman fa meke tafe da kai ne.?"

Dattijon yayi murmushi yace, "Aure nazo nema a wurin ki."

Amrah ta k'ara girman idonta tace, "Nifa ba budurwa bace na tab'a aure."

Dattijon yayi murmushi har sai da hauren shi na makkah ya fito, sannan yace,

"Nayi bincike akan ki kaf kafin inzo wajenki"

Amrah a cikin dakewa tace, OK kenan kaji zancen ina raba haja ta ga maza kenan.?"

Dattijon yayi murmushi yace, "Ko ma wacece ke ni wannan bai dameni ba naji kuma na gani zan aureki a hakan, koda kuwa kece magajiyar masu rabon hajar, ni ba yaro bane aure ya kawo ni ba wasa ba da zafina na fito ko gobe idan amince a shirye nike da muyi aure."

Amrah k'irjinta ya buga ba shiri, saboda har ga Allah yanzu tsoron maza ma takeyi, amman duba da yanda taga wannan shi ba yaro bane shiyasa ta d'an rage damuwar da takeji, tayi shiru ba tareda tace da shi k'anzil ba, amman fa sai jujjuya zancen takeyi a zuciyarta.

Dattijon yace da ita, "Ni sunana Alhaji Hamza mai akwai, ina da mata biyu da bakwai, shin ko Amrah zata iya auren tsoho?, idan kin amince zan kaiki gidanki daban bazan had'e k'i da matana ba."

Akafta😊

D/Auta 👌

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 6

****

Amrah tayi masa wani kallo, a nan take ta tuno da wata fira da suka tab'a yi da zee, inda take cewa, "kefa ni amrah yanzu nafi son in auri dattijo mai mata, saboda bincike ya nuna sunfi rik'on aure da daraja, sunfi ririta mace su nuna mata soyayya da tattali tamkar yarinyar goye, saboda hak... ."

Kiran sunanta da Alhajin yayi shi ya katse mata tunanin firar su da zee, a firgice ta d'ago fuskarta ta kalleshi a cikin mintunan da basu gaza biyar ba, taji ta amincewa zuciyarta auren shi d'ari bisa d'ari, amman don ta k'ara jawa kanta girma tace,

"Naji maganganunka duk kuma na fahimta, amma ina son ka bani lokaci zanyi shawara."

Alhajin yayi murmushi sannan yace, "Zuwa wane lokaci ne zaki k'are wannan shawarar gobe jibi ko gata?, don bana son aja dogon lokaci batareda an kaiman amaryata ba, ni in anawa ra'ayine nan da sati biyu ma ayi komi a huta."

Amrah tayi murmushin k'arfin hali tace, "Ba damuwa kaje kawai duk hukuncin da na yanke zakaji soon insha Allah."

Ya saka hannu ya b'allo compliment card d'in shi ya mik'a mata, tasaka hannu ta karb'a sukayi sallama ta shige gida.

Shigarta keda wuya mahaiyarta ta taso jikinta yana b'ari tace,

"Ya kukayi dashi ne?, ai na lek'a na hango shi ashe ma babban mutum ne mai kamala, idan har aurenki yazo nema ki amince kawai kije ki rufawa kanki asiri, don yafi maki zaman k'uncin da kike yi a cikin gidannan."

Amrah ta mik'a mata katin da ya bata jiki a sanyaye tace, "Matanshi biyu da yara bakwai, yace in na amince zai ajiye ni a gida daban."

Mahaifiyar ta washe baki tace, "Alhmdllh da man yanzu auren dattijan mutanen ma yafi dad'i, ki amince kawai a gangand'a ayi auren kije ki rufawa kanki asiri."

Amrah jiki ba kuzari ta shige d'akinta ta fad'a kan gado, ta d'aga kanta a sama tana kallon silin, ta shiga zurfin tunanin shi kuma wannan auren idan ta amince wane kalar k'alubale yake tattare dashi?, don jikinta yana bata da wuya in shima zai d'ore, ta tambayi kanta cewa anya kuwa tana

da rabon jin dad'in aure a rayuwarta?, wasu hawaye suka zubo mata a gefen idanuwa, musamman da tuno da rayuwar soyayyarta da salis, ba shiri ta fashe da wani kuka mai sauti, mahaifiyarta ta lek'o tace, "Kuka ba shine maganin matsalarki ba, amincewar ki itace garkuwar da zaki rika domin ki kare kanki daga zargin da ake yimaki."

Amrah ta tashi ta d'auko wayarta ta loda number Alhaji mai akwai, ta tura masa text akan cewa ta amince, shigar text d'in da minti biyu sai ga kiranshi ya biyo baya, a cikin farinciki yake nuna jin dad'insa akan amincewar da tayi, yace da ita ta kwantar da hankalinta matanshi basuda matsala, taji kurum amma ba don ta yarda da hakan ba, domin yanzu sai anyi dak'yar za'a sami macen da bata da zafin kishi, don ko ita ace ta auri salis yace zai yo mata kishiya ba k'aramin tashin hankali zata shiga ba, saboda son da take yimasa tana kishin ace wata mace ta rab'e shi.

A cikin sati biyu Alhaji mai akwai ya kawo sadakin shi har da guzurin lefen shi, aka saka rana sati uku masu zuwa, su zee da 'yan uwanta sun yi mata kara wajen yimata komi tamkar auren farko ne zatayi, don duk gyaran da akewa amarya ba wanda Aunty Asabe batayi mata ba, an ja kunnenta sosai akan tayi hak'uri da mijinta da matan shi duk da ba gida d'aya zasu zauna ba.

Ranar da aka d'aura aure a ranar aka kaita gidan Alhaji mai akwai, mutane sai yimata fatar zama lafiya sukeyi.

A ranar da aka kaita bayan kowa ya watse alhaji ya shigo, bakin shi har kunne saboda cikar burin shi, na mallakar zuk'ek'iyar mace irin Amrah son kowa k'in wanda ya rasa, a cikin farin ciki ya shigo d'akin da sallamar shi a baki,amrah gabanta ya k'ire ya fad'i, saboda tuno da tayi daga ita sai Alhaji a gidan, kuma alamu duk sun nuna Alhaji bazai d'aga mata k'afa ba kamar yanda Nasir yayi a daren farkon su, shikam da zafinshi yake tafe don ta tabbatar ba zai d'aga mata kafa ba a wannan dare.

Da fara'ar shi ya kira sunan ta, jiki a mace amrah ta amsa da murya k'asa k'asa, saboda ita kanta jinta takeyi a cikin yanayin buk'atuwa da a kusanceta, saboda kayan matan da Aunty asabe tayi ta loda mata sun tsimata sosai a jiki.

Alhaji yace da ita, "Alhmdllh ALLAH ya cika mani gurina na auren wannan kyakkyawar halitta, ina rokon Allah ya bani ikon yin adalci a tsakaninki da matana. Allah ya bamu zaman lafiya da zuri'a dayyiba."

Amrah tace "Ameen."

Daga nan ya umurceta da taje ta d'oro arwala suyi sallah, bayan sun yi sallah yayi masu addu'o'in neman zaman lafiya, suka ci suka sha daga nan sai labari ya canza salo.

Alhaji ya shiga yamutsa amrah ta ko'ina yana sambatu, ita kanta taji dad'in kasancewarta a cikin

wannan yanayi, amma abun mamaki yazo gaf da bukatuwa da ya ji ya jefa kwallo a raga, sai kawai yaji shi lagwaf alkalamin shi ya koma tamkar lagwani, yayi iya kokarinshi wajen ganin bukatar shi ta biya amma ina ko alama babu ta cewa hakan zata iya kasancewa.

🙈🙈🙈🙈🙈

Akafta😍

D/Auta ce😊

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 7

****

Dole Alhaji ya hak'ura ba don yaso ba, amman kam zuciyarshi a cike take taf da mamakin faruwar wannan lamarin, saboda shi mutum ne jarumi sosai a wannan fage, haka zalika mutum ne shi mai yawan buk'atar mace, asali ma shine dalilin da ya saka shi k'arin auren, sannan ya sha jik'e jik'e don kawai ya k'ara samun k'arfin da zai gwangwaji angwancinsa shi da amaryarsa,

amman sai gashi wannan lamari yazo masa a bazata, a haka dai ya kwana yana mai jin haushin wannan lamari, kafin safe yayi tsaki yafi dubu saboda bak'in cikin asarar da yayi ta wannan babban dare a wurinsu shi da amaryarsa.

Ita kanta Amrah duk da ba wani sanin kan abun tayi ba, amman taji haushin rashin kusantarta da Alhaji bai yi ba, har sai da ya gama yamutsata ya tada mata da duk wata dad'ad'd'iyar sha'awar dake kunshe a jikinta, sannan ya barta a cikin tsumayin son a kusanceta.

Koda safiya ta waye Alhaji bai canza mata ba, lafiya k'alau suka ci gaba da begen junansu, inda ko a lokacin yaso ace ya gwangwaji amarcinshi, amma kash har lokacin jiya iyau ce, a haka ya lallab'a ya fita domin baya jurar ganinta kuma al'hali baya iya tab'uka wani abun kirki.

Har lokacin kwanakinta suka fita ba wani abu da ya faru a tsakaninsu, dole ya koma gidan sauran matanshi da d'inbin buk'atar shi, amma kash a cen d'inma hakan ce ta kasance, tsawon sati biyu Alhaji ba inda yake rab'awa yaji sanyi, daga wurin amarya Amrah har tsoffin matan shi.

I zuwa lokacin Amrah tayi mul mul gwanin sha'awa, saboda kwanciyar hankalin da ta samu ta ci mai kyau tasha mai kyau ta kwanta and muhalli mai kyau, a kullum ALHAJI sai ririta yakeyi amman fa na karfin hali ne yakeyi, saboda ba k'aramin so yake yiwa Amarah ba, shiyasa bai zargi komi akan cewa matsalar daga wurinta ce ba, amman kam matanshi sun fara zargin akwai wani bak'in k'ullin da Amrah tazo masu dashi, wanda yasaka Alhaji baya iya tab'uka masu komi tunda ya aureta.

Akwai watarana ma da ya kwana a gidan wajen matarshi ta biyu, sun sha artabu ba kad'an ba akan dole sai ya biya mata da buk'atar ta,shi kuma gashi ba yanda ya iya dole hak'uri yayi ta bata, ita ko sanin wanene shi kafin k'arin aurenshi yasa ta k'ara hawa sama, suka yi rikici ba d'an kad'an ba kafin safe, inda take ta zubawa Amrah ALLAH ya isa tafi cikin kwando, saboda a ganin ta duk bak'in k'uli ne Amrah tayi masu, akan kada Alhajin ya koma kusantar su sai ita kawai.

Itama kwanan uwargidan da ya zagayo , haka suka tafka wannan artabun da Alhaji, har tana ik'irarin zata bar masa gidansa, tunda har ya zama mijin tace k'aramar mace ta maida shi lusari.

 A haka dai Alhaji ya k'are kwanakin ba dad'i ya dawo gidan Amrah, i zuwa lokacin shima ya fara damuwa da wannan sabon yanayin da ya tsinci kanshi a ciki, wanda har takai yake fad'awa wani abokinshi, sukaje suka samo wasu magunguna masu k'arfin gaske Alhaji ya fara sha da son ko ALLAH zaisa ya sami lafiya, amman shan magani yakeyi kamar baya sha, suka je suka yiwa wani malamin islamic Center bayani saboda masani ne sosai akan wannan harka, ya had'o masa magunguna yana sha amma a kullum jiya iyau.

Ita kam Amrah tun tana damuwa har ta saki jikinta tana zaman aurenta, bata jin wata doguwar damuwa akan wannan hali da ta riski Alhaji a cikinshi, don ita ko a ka bata kawo cewa itace tsanin matsalar ba, tayi mul mul gwanin sha'awa, k'awayen ta da 'yan uwanta sai murna suke

yimata ganin tana jin dad'in zaman aurenta, don koda wasa bata tab'a furtawa kowa wannan matsalar ba, duk da wani zubin tana sha'awar ace sun kusanci juna da Alhajin, amman saboda yanda take ganin damuwar da yake shiga, a duk lokacin da yaci burin faruwar hakan bai samu ba, shiyasa take had'iye k'walamarta bata so ta nuna masa zalamarta.

Wasa wasa har akayi wata hud'u da auren amma har lokacin ba wani canji, sai k'arin matsaloli da suka kasance a wurin Alhaji, domin a duk lokacin da yayi yunk'urin kusantar Amrah zai kwanta wani zazzab'i mai zafi har na tsawon kwana uku, wanda tun baya kula har ya fara gano akwai matsalar dake tattare da Amrah, domin gano da yayi zazzab'in sa baya zuwa har sai yayi yunk'urin kusantar ta, zuciyarshi ta fara tunanin mafita akan zaman auren shk da Amrah, duk da tsananin sonta da yakeyi.

Matanshi ma ba zama suka YI ba basu wajen wannan malami basu wajen wancen, duk inda suka je magana d'aya ce ake fad'a masu, akan cewa koda mijinsu zai dawo normal to har sai ya rabu da amaryarsa, wani wurin ma idan sunje har cewa akeyi muddin ALHAJI bai rabu da wannan yarinya ba to tabbas rayuwarshi tana k'ila wa k'ala, don haka duk yadda zasuyi suje su raba mijinsu da wannan yarinya, idan ba haka ba su kansu suna cikin matsala.

Aiko hankalinsu ya k'ara tashi suka kwashe komi suka sanar da Alhajin, sannan suka ce da shi muddin bai rabu da Amrah ba to su kam sai dai ya sauwak'e masu.

Oh ni dije🤔

Akafta 😒

D/Auta ce😚

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 8

****

Alhaji ya sauke ajiyar zuciya yace dasu, "kuyi hak'uri zanyi bincike sosai akan maganarku, sabida sakin aure ba abu bane mai kyau da zakuyi ik'irarin ko is sake ta ko ku in rabu daku, komi a sannu ake tafiya dashi ba haka kawai za'a yanke hukunci a cikin gaggawa ba."

Matar shi ta biyu tayi gatsal tace, "Ba wata kwana da zaka yi muna, ni kam idan kaji baza ka iya sakin matar jarabar ba, sai in bar maka gidanka wallahi inaji ina gani bazan tab'a zama honko ba."

Alhaji hankalin shi yayi k'ololuwar tashi yace dasu su, suyi hkr su bashi kwana uku duk abunda ya yanke zasu ji.

Aiko fitar shi gidan keda wuya matarshi ta biyu tace da ta farkon, tazo suje gidan munafukar matar su ci ubanta, aiko ba wani dogon tunani uwargidan ta biye ta suka nufi gidan Amrah, da k'unshin rashin mutuncinsu kwando kwando.

Koda suka je suka tarar da k'ofar shiga gidan a kulle, aiko ba wani jinkiri suka yi ta faman dukan gidan, Amrah tana bacci ba shiri ta falka saboda dukan da suke tayi ba k'ak'k'autawa, da sauri ta zo jikin k'ofar a masifance tace, "wai su waye ne haka da bazaku jira abud'e maku a hankali ba, zaku b'allewa mutane kof..... ."

K'arshen zancenta ya tsaya ne a daida lokacin da ta bud'e k'ofar da karfi, idanunta suka sauka akan fuskokin matan Alhaji mai akwai, saboda tasan fuskokin don lokacin da tana Amarya Alhaji ya kaita gidan ta gaida su, domin SU k'in zuwa gidanta suka yi.

Aiko jikinta ya d'auki rawa saboda bata ji dad'in maganganun da tayi masu ba, duk da a duba d'aya da tayi masu ta gano ba zuwan arzik'i ne suka yo ba, tana k'ok'arin basu hak'uri ne matar ta biyu ta shigo falon tareda bangaje ta har sai da taso fad'uwa, da sauri ta rik'e k'ofar mamaki kwance akan fuskarta, saboda wulak'ancin da suka zo suka yi mata a cikin gidanta, baki a sake

ta bisu da kallo har suka je a tsakiyar falo suka tsaya, matar ta biyu sai wani girgizar jiki takeyi tana hurar hanci, tareda k'arewa falon kallo a yatsine sannan ta dawo da kallonta ga fuskar Amrah tace, "ki k'araso domin kiji sak'on da muka zo maki dashi kafin wanda ya ajiye ki yazo ya baki certificate d'inki ki k'ara gaba, domin wannan wurin yafi k'arfin zamanki, tunda har kika kasance muguwa mai son kanta da yawa."

Gaban Amrah ya k'ire ya fad'i ba shiri tashin hankalinta ya k'aru, ba shiri ta k'araso falon tace dasu, "Don Allah kuyi hak'uri ku zauna sai muyi maganar."

Uwar gidan Alhaji tayi wata shewa tace, "ko bamu haife ki ba to zamuyi k'anwa ta hud'u ko biyar dake, saboda haka ba wani kilbibi da zaki yimuna, bayan kin gama cutar damu kina so ki raba mu da megidanmu, don haka mu tsakaninmu dake kawai sai dai muce Allah isa."

Amrah ta zaro ido acikin mamakin wad'anan lafuzza da suke ta jifarta dasu, wad'anda ita ta rasa gano inda suka dosa, a cikin damuwar da ta bayyana akan fuskarta tace dasu, "Nifa ban fa gane abunda kuke nufi da wad'annan maganganu ba, don Allah ku fito fili ku sanar dani yanda zan fahimta."

Jikin ta biyun har b'ari yake wajen kaiwa Amrah, wani bahagon mari bakinta yana kumfa tace, "Yanzu zaki gane kuwa to farrak'un da kika yi muna akan Alhaji ya guje mu, to yayi aiki sosai kije ki biya bokanki, don tunda kika shigo gidannan ALHAJI ya daina kwanan aure damu, saboda kinyi masa D'ANBAKA kin k'ulle masa wutsiya ta daina aiki a wurinmu sai dai ke d'aya kawai, yanzu kin gane ko sai na kara yi maki yanda zaki gane d'in filla filla?."

Amrah ba shiri ta aza hannu aka tace, "Wallahi ALLAH ni babu hannuna a cikin wannan lamari, kuje cen ku tambayi mijinku ni ba abunda ya had'ani da wannan aikin, don ku kukasan ma yanda ake yin BAKAN ba ni b..... ."

Kafin takai k'arshen zancen suka rufeta da duka ta ko'ina, Amrah sai kuwwa takeyi ba mai ceton ta, har saida suka jibgeta son ransu sannan suka bar gidan, suna ta surfa mata zagi ta uwa ta uba suna tsine mata.

Amrah tayi kuka iya kuka ba mai rarrashinta, dole ta hak'ura don kanta sannan ta jawo wayarta ta kira ALHAJI ta sanar dashi, sai gashi ya dawo gida a firgice saboda jin wannan magana, hankalinshi ya k'ara tashi akan wanda yake a ciki, ganin dukan da matanshi suka yiwa Amrah yaji ranshi ya b'aci sosai, shiyasa ya ajiye k'udurin sakin Amrah da yayi niyya, yayi ta lallashinta yana bata hak'uri.

A cikin kuka Amrah tace dashi, "don ALLAH Alhaji ka sauwak'e mani ko don ka sami zaman lafiya kai da matanka saboda sunce ni nayi maka asiri ka daina kwanciyar aure dasu sai ni kad'ai, kai kafi kowa sanin tunda nazo gidannan ba wani abu da ya shiga tsakaninmu na auratayya, ina hak'uri ne kawai don naga kana shiga damuwa akan rashin faruwar lamarin, amman duk da haka ban wuce zargi a wurin matanka ba, saboda haka na amince zan rungumi

kaddarata, domin ka sami zaman lafiya da iyalinka, bana son ta sanadina,zaman lafiyar gidanka ya wargaje."

😔😔😔

Akafta😍

D/Auta ce😊
🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 9

****

Alhaji jikinshi yayi sanyi k'alau yace, "Kiyi hak'uri Amrah akwai abunda na b'oye maki, don bana son ganin tashin hankalinki, nayi ta k'ok'ari akan in shawo kan matsalar amma abun ya faskara, a zahirin gaskiya koda na aureki lafiyata k'alau, amman tun ranar da aka kawoki na fara shiga matsala, jikina ya kasa aiki yanda kikaga bana iya tsinana maki komi, to suma hakan ce take faruwa a wurinsu, saboda sanin da suka yiman ni mutum ne mabuk'aci, shiyasa suka zargi cewa kece kika yi masu asiri, alhali ni nasan ba haka bane domin idan har kin masu

to kefa zaki cuci kanki ne da kanki?, kinga hakan bazata yiyu ba saboda haka, nayi ta neman magani a b'oye ina sha ba tareda kinsani ba, amman duk abanza ba nasara jiya i yau, sannan idan zaki iya tunawa duk ranar da naso na kusance ki, to aranar ne nike tashi da wannan zazzab'in mai zafi, a majiya mafi tushe an tabbatar man matsalar daga gareki take, idan zaki tuna a kwanakinnnan kaf bana da natsuwa sabida matana sun d'aga man hankali sosai, akan sai na sakesu ni kuma har ga Allah dukanku ba wadda nike son rabuwa da ita acikinku, yanzu dai na yanke shawarar zan nema maki magani, domin matsalar dake a jikinki ta kau koda ALLAH zaisa ayi nasara."

Ba shiri Amrah ta k'ara sautin kukanta a cikin tashin hankali tace,

"Wayyo ni Allah ina zan saka rayuwata ne inji sanyi? daga wannan sai wannan, don ALLAH Alhaji ka taimaki rayuwarka da kwanciyar hankalin gidanka ka sauwak'e man don ALLAH, nayi imanii da kaddara mai kyau ko akasinta, duk abunda ya sameni daga ALLAH ne, kuma nasan baya kwana baya angaje, naji na gani zan rungumi k'addarata, kar kaji komi kayi abunda kaga zai dawo maka da lafiyarka, da kwanciyar hankalin g
Iyalinka."

A cikin damuwa Alhaji yace, "Don ALLAH kiyi hak'uri ba haka na tsara zaman aurena dake ba, wata biyar ace ba wani abu har ga Allah banda niyyar sakin mace idan na aureta, don haka kiyi hak'uri kawai muci gaba da zamanmu zan nema muna magani insha ALLAH za'a dac.... ."

Kafin ya k'arasa maganar yaji anshak'e wuyanshi, ba shiri ya fad'i a k'asa yana birgima hannunshi rik'e da wuyan idanuwa sun ture, azabure Amrah ta mik'e tareda kai kanta a wurinshi tana kuka tana kiran sunan shi, minti biyu a tsakani ALHAJI ya fara dawowa hayyacinshi ya kai kallon shi akanta yace, "Saka hijabinki tashi muje in kaiki gida."

A cikin mamaki Amrah ta daina kukan tana kallonshi da dukkan idanuwanta, a cikin tantamar abunda taji ya fad'a tace, "Gida?, wane gidan kake nufi?."

Alhaji a cikin damuwa ya tashi tsaye ya fara tafiya zai bar falon yace, " gidanku mana ki sameni a waje ina jiranki."

Yana fita Amrah ta aza hannu akai tace, "ALLAH ka kawo man agaji, yanzu shi kuma wannan aure ince dalilin mi nayi aka sako ni."

Tana k'are maganar ta share hawayenta ta tashi tsam ta fad'a d'aki, ta d'auko hijab ta saka tareda d'auko jakar hannunta mai d'auke da yan kayanta masu muhimmanci ta rataya, ta jawo d'akin ta rufe a cikin daskarewar zuciya ta fito tana layi ta shiga motar, inda Alhaji har ya tayar da motar ita kawai yake jira, shigarta keda wuya ya fisgi motar ba wata magana da ta had'asu har ya kai k'ofar gidansu, a cikin zafin nama Amrah ta b'alle murfin motar ta fito, har zata shige gidan Alhaji ya kira sunanta, cak! ta tsaya ba tareda ta waigo ba, a cikin murya mai cike da damuwa Alhajin yace, "Kiyi hak'uri haka Allah ya tsara zamanmu zai kasance, akwai sak'on

da zan turo maki yanzu idan kin shiga gida, Allah ya sake had'a mu zama koda a gidan aljanna ne, nagode da aurena da kika amince sai watarana ALLAH ya had'a fuskokinmu da alkhairi."

A guje Amrah ta fad'a gidan tana wani irin kuka na tashin hankali, a d'ari mahaiyarta ta taryeta tareda tambayarta, "lafiya?, me kuma ya faru yanzu muna murna kinsami wurin zama.?"

Kafin Amrah ta baiwa uwar amsa sai ga k'arar shigowar text a wayarta dake a cikin jaka, ba shiri kirjinta ya buga dam! dam! a cikin hanzari ta ciro wayar tana duba sak'on, a zabure ta tashi tsaye a cikin rawar murya tace,

"Na shiga uku ni Amratu shima ya sakeni."

A cikin d'aga murya uwar tace, "Shi wa?."

Amrah ta fad'i zaune tana kuka kashirb'in ta kasa furta wata kalma daga bakinta, sai ga k'anenta ya shigo uwar tayi saurin fisge wayar ta mik'awa k'anin tace dashi, "karanta man inji."

K'anen Amrah mai suna Aliyu wanda ake yiwa lak'abi da Abba, ya karb'i wayar jikinshi a mace ya fara karantawa kamar haka, "Ni Alhaji mai akwai na saki matata Amrah saki biyu, asanadiyyar rashin lafiyar da take tattare da ita, ga kud'i nan na turo mata dubu hamsin domin ta nemi magani dasu Allah ya bata lafiya."

Ba shiri mahaifiyar ta dafe k'irji tace, "Kan uba don zai sake ki har sai ya janyo muna alkaba'i ya lik'a maki?, to ke wani ciyo ne dake bamuda labari, wanda har yayi sanadin mutuwar aurenki?."

Amrah ta k'ara sautin kukanta tace, "Nima bansani ba wallahi, don nima bansan inada wani ciyo ba."

A cikin d'aga murya mahaifiyar tace da Abba, "Idan akwai kud'i a wayar kira man Asabe, don wallahi har kotu zan iya maka shi akan wannan k'azafi da yayi maki, d'an iskan banza matsiyaci ita dubun hamsin d'in zata isa maganin k'azafin da yayi maki?, da wannan abin kunyar da ya k'ara jawo muna a wurin mutane?, harda wani ik'irarin sunan mai akwai, to mudai bamuga akwai d'in ba har sai tsiya da ta danno muna kai, in banda ma k'addarar aure me Amrah zata yi da irinshi?."

Tana banbamin fad'an ne Abba ya d'aga wayar ya kira Aunty asabe, tana d'auka uwar ta karb'e wayar tace, "Asabe kizo yanzu ga Amrah matsiyacin mijinta ya danna mata saki har biyu, tareda k'azafin wani ciyo da ya lik'a mata na cin amana, wanda ni kaina mahaifiyarta bansan da zaman shi ba."

Amrah taja jikinta ta shige d'akin mahaifiyarta, sabida kalaman mahaifiyarta suna k'ara tunzura zuciyarta, haka zalika cin zarafin Alhaji da takeyi bata jin dad'in hakan, sabida idan zata yi masa adalci tunda ta aureshi, ba wani cin zarafi ko wani cin fuska da ya tab'a yi mata, asali ma ita kanta tun da taga yanayin da Alhaji ya shiga a falo, yaa tabbatar mata da akwai wata matsala a b'oye da ita batasan da ita ba, musamman tuno duk ranar da yazo gwada kusantarta ne yake wannan zazzab'in da yake yi mai zafi.

Tana nan tana ta sak'e sak'e har Asaben tayi sallama ta shigo d'akin, bayan ta k'are jin ta bakin yayarta wato uwar Amrah, a hankali ta k'araso idonta akan Amrah har ta zauna gefen gadon da take kwance akai, ta kira sunan Amrah har sau biyu amman bata ma san tanayi ba, saboda zurfin tunanin da ta fad'a na zaman gidan ALHAJI mai akwai da tayi, a kira na ukun ne ta dawo hankalinta ta kai dubanta ga fuskar Auntyn Asabe, ba shiri ta fashe da wani kuka gwanin ban tausayi.

Aunty Asabe ta fara lallashinta akan tayi shiru tayi mata bayanin abunda yake faruwa, a hankali amrah ta zayyana mata tun ranar da aka kaita har zuwa yanzu, har dukan da matan Alhaji da kalaman da suka fad'a duk sai da ta fayyace mata komi, jikin auntyn Asabe yayi sanyi, domin anan take ta gano akwai wani k'ulli da aka yiwa Amrah, tun akan auren Salis har Nasir har zuwa Alhaji yanzu.

A cikin damuwa ta kira zuwaira mahaifiyar Amrah akan ta shigo, aiko jikinta yana rawa tazo ta zauna, bakinta har rawa yakeyi wajen tambayar Asaben, akan me Amrah'r ta fad'a ne?, aiko a cikin dunk'ule bayanin yanda zata gane ta sanar da ita duk abunda taji daga bakin Amrah, ita kanta uwar jikinta yayi sanyi k'alau tareda fad'uwar gaban da ya kasa tsayawa, zuciyarta sai bugawa takeyi falfal, anan take ta fad'a zurfin tunani bata ma san lokacin da ta furta cewa,

"Allah ya agaje mu idan ba hak'k'in Naziru ne yake bibiyar mu ba."

Ita kanta Amrah sai da taji gabanta yayi dakan lugude, har sai da ta runtse idanunta tareda dafe saitin zuciyarta, a cikin mamaki Asaben tace,

"Hak'k'i kuma?."

Uwar Amrah tayi saurin dawowa a hayyacinta tace,

"Hak'k'i kika ji nace?, eh ina nufin hak'k'in salis."

Asabe tayi mata wani kallon ban yarda dake ba tace, "Me kuka yiwa salis ne da har hak'k'in shi zai kama ku?, ba shi da kanshi yace ya fasa auren ba?, idan dai kinsan da wata matsala kiyi man bayani, don saboda ina son inje wajen wani matashin malamin dake unguwar da nake, na yaba sosai da taimakon da yake yiwa mutane,don haka zanje in kai masa wannan matsala

ta Amrah, duk yanda mukayi zan kiraku a waya na sanar daku."

A haka suka rabu Asabe ta koma gida zuciyarta tana kai da komon me maganar zuwaira take nufi?, anya ba akwai wani abunda ta b'oye mata ba kuwa?, tasa aranta inma akwai su suka sani, ita dai a tsakani da ALLAH take zama tare dasu, haka zalika ta d'auketa a matsayin yaya uwa d'aya uba d'aya, duk da ba uwa d'aya ce ta haife su ba.

Dank'ari akwai fa gumurzu a gaba kuci gaba da biyoni domin kuji shin wane BAKAN GIZO ne yake shanyewa Amrah ruwa idan ta d'ebo 🤔

Akafta🦸‍♀️

D/Auta ce😅
🌈🌈BAKAN GIZO 🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Sai kunyi hkr dani saboda nayi busy da yawa😍

PAGE 10

****

Shin wacece Asabe???

Asabe 'ya ce a wurin k'anwar mahaifiyar zuwaira wato maman Amrah, daga iyayen Asabe har iyayen zuwaira dukan su ba'a garin suke zaune ba.

Kasancewar baban Amrah a cen garin su yaje ya auro ta, yazo da ita a nan garin da suke zaune a yanzu a cikin danginsu, saboda shi haifaffen d'an garin ne, zuwaira bata da kowa a garin sai 'yan uwan mijinta sai abokan arzik'i, to fa sai yanzu da aikin alk'alanci ya kawo mijin asabe a garin, sannan ne ta sami 'yar uwar da suka had'a jini suka rik'i juna tamkar uwa d'aya ce ta haifesu.

Babansu Amrah ya rasu tun Amrah tana 'yar shekara biyar a duniya, amma har yanzu zuwaira albarkacin 'ya'yan da ta haifa bata koma ainahin garinsu ba, tayi zamanta anan tana cin karenta ba babbakar, shiyasa Asabe bata da masaniyar tsiyar da suka shuka kafin mijinta ya kwaso ta su dawo a garin.

**
Koda asabe taje unguwarsu bata zame ko'ina ba sai gidansu wannan matashin malamin da take fad'a, aiko taci sa'a ta sameshi gidansu yana had'in wasu magunguna, tareda wata kanwarshi dake taimakonshi, sabida har a lokacin baiyi aure ba wasu ma suna zargin ko aljana ce take aurenshi shiyasa baya kula kowace mace.

Bayan sun gaisa ne tayi masa bayanin duk abunda yazo da ita, dangane da matsalolin da Amrah take fuskanta, malamin yayi shiru yana nazarin maganganun da ta fad'a masa, sannan a cikin jimami yace da ita, "Tabbas wannan lamari akwai wani k'ulli a cikinshi, amman insha Allahu zamu ga abunda zamu taimaka mata dashi, gobe da safe bayan an tashi makarantar safe sai kuzo tare da ita".

Aunty Asabe tayi masa godiya sannan ta tabbatar masa da goben zata dawo adaidai lokacin da ya fad'a tareda Amrah'r.

Haka ko akayi koda goben tayi tun kafin lokacin ya cika suka isa makarantar islamiyar inda anan ne yake da shagon sayar da magungunan musulunci, bayan ya basu masauki sun zauna ne suka fara gaggaisawa, idonshi a k'asa baya ko son ya had'a idanuwa dasu saboda tsantsar tsantsenenshi da mata, amma yana jin sautin muryar Amrah tana gaidashi yaji jikinshi yayi sanyi, saboda ba k'aramar tafiya dashi muryarta tayi masa ba, yana so ya d'ago ya kalleta yana jin nauyi a haka dai ya daure ya d'ago fuskarshi, tareda kai kallonshi akan kyakkyawar fuskarta ya fesheta da wani guntun murmushi yace, "Amrah ko? insha Allahu zamu taimake k'i da daidai iyarmu, yanzu zan had'a maki wasu magunguna kiyi amfani dasu tsawon sati d'aya, duk yanayin da kika tsinci kanki a ciki sai ki fad'awa Hajiya Asabe ta sanar dani, Allah yasa mu dace."

Dukansu suka ce Ameen, ya tashi ya shiga harhad'o mata magunguna sai da ya cika leda baka, sannan ya mik'a mata ta saka hannu ta karb'a tareda zaro kud'i a cikin jaka ta mik'a masa, yana murmushi yace da ita,

"A'a ki barsu kawai kije ALLAH yasa a dace."

Amrah tayi sororo da kud'in a hannu a cike da mamakin wannan bajinta ta malamin, Aunty Asabe tayi saurin karb'ar kud'in tace, "Allah gafarta malam ba biya mukayi ba tukuici ne muka bada, saboda muna fatar ALLAH ya shiga a cikin lamarin matsalolin su kau."

Matashin malamin yayi murmushi tareda fara jawo shagonshi yana k'ok'arin rufewa yace, "Kuje kawai ALLAH ya bata lafiya."

Aunty Asabe da Amrah suka ji dad'in wannan karamci da malamin yayi masu, suka dinga yimasa godiya ba k'ak'k'autawa tareda yi masa addu'ar gamawa lafiya, har sun fara tafiya zasu bar wajen malamin yace da Aunty, "Ga number ta duk abunda taji bayan tasha maganin sai ta neme ni."

Amrah ta fiddo wayarta yana fad'a tana lodawa har ya k'are tayi saving d'in number'r, sannan suka k'ara yimasa godiya suka wuce.

Malam kam bayan wucewar su yabi bayan Amrah da kallo yana murmushi, saboda har ga ALLAH bai tab'a samun 'yar da ta sace zuciyarshi a farat d'aya ba sai Amrah, duk da matsalalolin da yaji an karanto a kanta yaji baya ko d'ar akan ya fad'a neman aurenta idan ta cika iddah, dik da a bayanan da Aunty tayi masa ya gano ba wata iddah akanta.

**

Kafin su rabu sai da Aunty tayi ta jaddada mata yanda zata yi amfani da magungunan, tayi mata jan kunne sosai akan kada tayi sake da shan maganin koda ALLAH zaisa a samu matsalar ta kau.

Koda Amrah ta dawo gida fillah fillah tayiwa mahaifiyarta bayanin komi, mahaifiyar taji dad'i sosai amma kuma taji tsoron kada ace sonta yakeyi, domin ita kam sam bata son irin wannan zak'ewa, don bata shiri da duk wanda baya da hannu da shuni yace yazo neman aurenta, saboda a acewarta Amrah babbar kadara ce ko dai ta zama matar wani d'an majalisa ko wani Commissioner.

**

Tsawon kwana uku Amrah tana shan magani amman ba wani sauyi da taji a jikinta, illah k'arin miyagun mafalkan da take tayi a duk lokacin da tayi kuskuren kwantawa da sunan bacci.

A rana ta hud'u ne Aunty ta kira ta domin taji wani ci gaba ne aka samu, aiko bakinta a sake ta zayyanewa Aunty komi, jikin Auntyn a sanyaye tace da ita ta kira malamin ta sanar dashi, bayan sun k'are wayar da Aunty ta dannawa lambar malam kira, bugu d'aya biyu ya d'aga yana jin muryarta yaji gabanshi ya fad'i daram! ya gane muryarta anan take, saboda tsawon kwana ukun a kullum tsumayin kiran nata yakeyi, shiyasa yana ganin bak'uwar number yayi caraf ya d'aga, bayan sun gaisa a mutunce tayi masa bayanin miyagun mafalkan da takeyi, a cikin jimami yace da ita taci gaba da sha insha ALLAH ba abunda zai k'ara faruwa,, saboda magungunan duk na tsarin jiki ne sosai, yaci gaba da kwantar mata da hankali har taji natsuwa ta ziyarceta, aiko tun daga ranar Amrah ta dage sai shan magani takeyi, ba laifi taji natsuwa sosai ta ratsa jikinta, don ko miyagun mafalkan duk ta rage yi sai wanda ba'a rasa ba.

Wasa wasa shak'uwa ta fara shiga a tsakanin Amrah da malam Nura, mahaifiyarta a kullum sai kyararta takeyi musamman idan taga suna waya, domin har a lokacin bai zo gidan ba zumuncinsu iya waya ne, amman yawan wayar da suke YI yasa soyayyarshi ta fara ratsa zuciyar Amrah, saboda a kullum da shawarwarin da yake bata wad'anda take amfana dasu, kuma suke k'ara sakata tsantseni da rayuwar duniya, saboda malam nura mutum ne mai kaifin basira da daddad'an lafuzza masu k'ara cusawa mutum tsoron ALLAH a zuciya.

Aunty Asabe kam taji dad'in wannan zumunci nasu, saboda a tunaninta koda Allah yayi aurensu matsalar Amrah zata kau har ta zama tarihi.

Mahaifiyarta kam ina wuta ta jefa Amrah ta huta saboda jin haushin sakewar da taga tana yiwa malam nura, domin acewarta Amrah taci baya sosai matuk'ar ta lalace akan malamin islamiya.

A ranar da malam ya fara zuwa gidan har waje taje tayi masa wankin babban bargo, ran malam a b'ace yabar gidan batareda ya sami damar ganawa da Amrah'r ba.

Tasha kuka sosai saboda cin zarafin da mahaifiyarta tayiwa malam, ta d'aga waya da niyarr ta bashi hak'uri mamar ta k'wace wayar tana ta danna masa asharr.

Zama yak'i dad'i a tsakanin Amrah da mahaifiyarta, saboda a sace watarana take fita taje gidan Aunty su sha firar su da malam hankali a kwance, sai dai idan ta dawo mamar tayita surfa mata zagi ta uwa ta uba duk da batada masaniyar inda take zuwa.

A ranar da mamar ta gano kuwa tattaki tayi har gidan Asaben taci karo da Amrah da malam a farfajiyar gidan Aunty suna fira, aiko tayi cikin Amrah da duka tareda jifarta da miyagun kalamai marasa dad'in ji, ita ko Aunty tatas ta wanketa da soso da sabulu bayan tayi ta jera mata ALLAH ya isa tafi dubu, akan wannan auren tsiya da take so ta had'a tunda ba itace ta haifi Amrah ba.

Duk da Auntyn taji ciyon abunda tayi mata Amma bata biye ta ba har taci fad'anta ta gaji ta bari, sannan taja Amrah sukayi gida tareda k'wace mata waya ta b'oye.

Amrah ta shiga k'unci sosai saboda matsin lambar da mamar take yimata, gashi ta rasa wayar

da zata kira malam ko Aunty taji sanyi, ko k'awayenta suka zo kad'a su takeyi subar gidan bata fita ko'ina daga gida sai gida.

Tana cikin wannan matsin lambar ne wani d'aya daga cikin k'annen baban su Amrah yazo da sadaki tareda goro ya kawowa mamar, a cikin tuhuma take tambayar na miye ne?, a take ya sanar da ita sun d'aura auren Amrah da malam nura.

Kwacagiya wannan aure fa akwai k'atuwar sark'ak'iya a cikinshi ku biyoni domin kuji wace sark'ak'iya ce wannan🙀

Akafta🏃‍♀️

D/Auta ce🤹‍♀️

Anya mamar Arah

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 11

****

A zabure zuwaira ta mik'e tsaye tareda yiwa goron da kud'in kallon k'yama tamkar wadda taga wani k'aton kashi, bakinta yana rawa ta nuna shi da yatsa tace, "Yanzu don kun maidani ba a bakin komi ba, shine kuka yiman rufa rufa kuka daurawa d'iyata aure ba tareda masaniyata ba, ai ko wallahi kaf d'inku sai kunsan dani kuke zance idan har ba kuyi gaggawar raba wannan tsinannen auren ba."

K'anin baban amrah yayi wani murmushi sannan ya fara taku zai bar cikin gidan yace, "Aure kam ya riga da ya d'auru kuma ba wanda ya isa ya kunce shi, matakin da duk kikaga zaki iya d'auka bisimillah muna jiraye dashi."

Aiko yana k'are maganar a zuciye zuwaira tayi cikin Amrah dake tsaye tana saurarensu da duka, a cikin zafin nama k'anin baban ya dawo ya fisge amrah daga wannan dukan mahaukaciya da zuwaira take yimata, yace da ita taje ta sako hijabinta aiko jikinta yana rawa ta fad'a daki ta sako hijab ta fito, yace da ita,

"Zo muje gidana ki zauna kafin gobe mijinki yazo ya tafi dake, don bazan barki anan gidan ba haka kawai ta kassaraki a banza."

Ya saka Amrah a gaba suka fita saboda mamaki zuwaira sakato tayi tana kallon wannan almara da take faruwa, ta maida kallonta akan goron da kud'in da ya ajiye mata atake wani b'acin rai ya mamaye dukkan zuciyarta, ba shiri ta jawo hijabi ta saka a guje ta biyosu wanda fitowarta yayi daidai da tashin mashin d'inshi goye da amrah dake ta sharara kuka, zuwaira itama bata yi kasa a gwiwa ba ta bisu da gudu tana kiran atare atare, da taga ba wanda ya kulata ta fad'i a tsakiyar titin tana wani bajimin kuka, mutane suka taru akanta ana tambayarta lafiya? me ya faru?.

Saboda tsabar bak'in ciki kasa magana tayi sai gurzar kukanta da takeyi bilhak'k'i tamkar wadda akace za'a zarewa rai a lokacin, da taga mutane sai tururuwar zuwa kallonta sukeyi, saboda d'an k'aramin go slow d'in da ta had'a a cikin k'ank'anin lokaci, wanda har mutane sun fara zage zagen tare masu hanya da aka yi, jiki ba kuzari ta yunk'ura ta shige gida tareda jawo wayarta jikinta yana bari ta dannawa Aunty Asabe kira.

Bugu d'aya biyu har ta tsinke batareda Auntyn ta d'aga wayar ba, itama kam bata daina kira ba har sai da taci nasarar da aka d'auki wayar, jikinta yana rawa saboda masifa ta fara magana,

"ALLAH ya isa tsakanina dake asabe wallahi nayi danasanin zuwanki a garinnan, domin idan ba ke ba babu wadda zata yiman irin wannan tozarcin kuma ace in k'yaleta, amman ko ke kisani daga yau na datse duk wata alak'ar da kika sani a tsakanina dake, Amrah ce kije na bar maku ita duniya da lahira keda dangin ubanta, ko mutuwa nayi akayi mata gaisuwata ta karb'a wallahi ban yafe nonona da tasha ba."

Aunty Asabe bata katse ta ba har ta k'are banbamin masifarta, sannan ta sauke k'atuwar ajiyar zuciya tace da ita, "Aunty zuwaira ina guje maki ranar danasani saboda nidai aure na had'a ba zaman banza ba, saboda haka duk wani tsine tsinenki ko d'aya bazai kama Amrah ba ballanta ni da baki haifa ba."

Zuwaira ta k'ara kufula jikinta yana mazari kamar zata kai duka a cikin wayar tace, "Asabe ALLAH ya tsine maki albarka dai gwargwado, CIN amanar da kuka yimani kuma wallahi kuje na barku da ALLAH."

Kif!!!! ta kashe wayar sai huci takeyi tamkar wata kasa, k'anen amrah mai bi mata ya shigo a cikin tashin hankali saboda labari yaje kunnensa, anga mamar a kan titi tana ta risgar kuka shine ya dawo gida a firgice domin yaji meke faruwa, ganin yanayin da ya isketa a ciki ne hankalinshi ya k'ara tashi, a cikin fargaba yace, "Wai mama mike faruwa ne.?"

Mamar kam wasu sababbin hawaye suka zubo mata ta kalleshi da rinannun idanuwanta da suka yi ja tace, "dangin babanku sun d'aura wa amrah aure da matsiyacin malamin cen da na tsana batareda sanina ba."

Abba duk da yaji ba dad'i amman sai ya wayance yace, "Kiyi hak'uri mama tabbas basu kyauta ba yanzu ina ita Amrah.?"

Mamar tayi wani mere murya aciki ciki tace,

"Sun tafi da ita babban gida tunda a ganinsu sun fini iko da ita."

Abba yayi shiru na d'an lokaci sannan yace, "mama fa wannan aure ba haramun bane, kawai dai hukuncin da suka yanke ba tareda saninki bane basu kyauta ba, duk da shima d'in idan aka yi duba da k'arfin da suke dashi a kan hakan ba laifi bane a musulunce, saboda haka kiyi hak'uri ki yafe masu."

Zuwaira tayo cikinsa kamar wata zakanya zata dakeshi, ba shiri ya ja baya yana ta kallon yanda take ciccika, a wurin zuwaira kuwa Abba ya k'ara tono fushinta ta fara amayar da zantuka bakinta yana kunfa tace, "Ai dama ni nasan ba goyon bayana zaka yi ba, sabida daman cen ina sane dakai ai kafi son su dani, to kaima ka tattara yanaka yanaka ka koma wurinsu tunda har sun fini iko da ku."

Abba salun alun ya fita ya barta tana ta zazzaga ruwan bala'i, tareda tsinewa auren akan kada

yayi albarka.

***

Amrah kuwa tana gidan k'anin babanta musa sai cisgar kuka takeyi ana lallashinta, ganin tak'i daina kukan ne iyayen suka had'a baki akan cewa da malam nura yazo gobe ya tafi da matarshi, sannan aka tada gwaggonninta biyu da suje gidan mamarta su kwaso mata kayan d'akinta aje ajero mata gidan malam nura.

Koda aka je tufafinta ma zuwaira hanawa tayi tareda sauke masu da kwandon masifa kala kala, da yake suma a jiraye suke da ita haka suka had'u aka yita jifar juna da miyagun kalamai, aka rabu baram baram suka dawo hannu rabbana ba ko tsinken da suka samu suka d'auko, dole aka baiwa malam nura hak'uri gameda tarewarta akan ya basu sati d'aya, kafinnan sun gangand'a sun saya mata kayan d'aki, shi ma suka ce ya nema mata kayan da zata saka kafin lokacin, aiko a cikin rufin asiri aka tarkato mai taro mai sisi aka sai mata duk wani abunda zata buk'ata a gidan aure, shima malam nura ya had'o mata kala goma daidai karfinshi suka tattarata da kayanta suka mik'a ta gidan Nura, bayan an kaiwa zuwaira ita saboda amrah ta rok'eta gafara, amman saboda miyagun lafuzzan da tayi ta jefawa auren dole ba shiri aka dunk'ulo amrah tana kuka aka kaita d'akin mijinta, tareda yimata addu'ar neman zaman lafiya da jan kunne kalakala akan tayi hak'uri da duk abunda ta gani ta baiwa mara d'a kunya.

Bayan kowa ya watse ne malam ya shigo tareda guzurin ledar shi da ya siyowa amaryarshi kazar ci muyi, aiko bayan sunyi sallah tareda dogayen addu'o'i ga zaman lafiyarsu, suka ci suka k'oshi malam yazo ya fara share fage wasa ta mik'a yana gaf da fara neman hanyar b'ullewa ya fad'i sharaf akan gadon yana wani bacci mai nauyin gaske, abun mamaki kuwa sai ga malam wutsiya a mik'e sai sambatu yakeyi yana kiran sunan amrah tamkar wanda yake kwanciyar aure da ita.

A cikin mamaki amrah ta k'ura masa kallo ganin yanda yake bacci sharkaf amma bakinshi ya haukace da sambatun dad'i, bata kawo komi a ranta ba ita a lokacin har dariya ma ya bata ganin yanda ya rud'e yana kiran sunanta, a cikin ranta tace,

"Watak'ila jiganiyar biki ce tasa ya tara bacci har yaci k'arfinshi haka."

Koda safiya ta waye malam sai jerawa Amrah albarka yakeyi yana godiya, mamaki ya kama amrah saboda ita dai tasan ba wani abu da ya shiga tsakaninsu, a ranta ta sak'a kodai mafalkin da yayi ne da ita yake ganin kamar da gaske ne?.

Bayan sun karya ne yace zaije makaranta a cikin farinciki ta raka shi har k'ofar gida, yace da ita zai aiko da cefane don bazai dawo ba sai k'arfe biyu, sannan ya fara tsokanarta suna yiwa juna barkwanci sukayi sallama ya fita ta dawo gida, bayan kamar minti talatin da fitar shi sai gashi ya dawo hannunshi da cefane, da murnarta ta tareshi shima a cike da begenta ya shigo gidan ba tareda b'ata lokaci ba, ya mamayeta da soyayyarshi mai zafi suka fad'a d'aki ba shiri

daman ita d'okance take da ganin wannan rana, a d'imauce ta saki akala malam ya dinga sarrafata ta yanda yakeso, amrah tun tana farinciki har ta koma jin zafi ta fara neman ceto a hannun malam, saboda ya saki jiki ya gwangwaje angoncinshi dakyau sannan ya tsallaketa ya barta tana ta kuka, bayan yaje ya watso ruwa ne yazo yana yimata sallama akan zai koma, yace da ita tayi sauri ta tashi ta kimtsa jikinta ga ruwan zafi cen ya aza mata ta gaggasa ko'ina ,sannan yace da ita akwai cefanen da ya bada asiyo a kawo mata yana nan zuwa, a cikin jin jiki tace dashi, "Wanda ka shigo dashi yanzunnan fa.?"

Yayi murmushi yace da ita, "Eh wancen na fara badawa a siyo da naga zanzo gidan, to shine naje na siyo wannan kawai don bana son ayi delay d'in kawo wancen ki dad'e baki d'ora sanwar ba."

Daga nan kwance Amrah tayi masa a dawo lafiya, ya fice yana wani munafukin murmushin, da shikad'ai yasan ma'anar shi tareda yin wata k'ofa mai sauti.

Babbar buta cike da ruwan zafi🤔🤔🤔jama'a wasar fa yanzu ta fara anya anya dai nayi shiru nidai kada aji mutuwar sarki a bakina ku ci gaba da biyoni domin jin yanda wannan cab'a zata ci gaba da kasancewa😔

Akafta😒
🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Ashe zuma kama takeyi k'uda BAKAN GIZO shine yake shanye ruwa😢

BAKON YANAYI shine sabon book dina da ke tafe ba da jimawa ba LITTAFI ne mai k'unshe da hargitsi rungutsumi tareda nishadantarwa sannan ga fadakarwa kada ku bari a baku labari BAKON YANAYI takunshi daban yake dana saura 💃💃💃💃

PAGE 12

****

Tana nan a kwance tana jinyar jikinta saboda ba k'aramin jin jiki tayi ba, asanadiyyar wannan sukuwar dokin da malam yayi akanta tamkar da k'eta a cikin lamarin nashi, aikuwa sai zancen zuci takeyi saboda a ganinta malam huce haushin tuzurantakarsa ne yakeyi akanta, amman duk da haka ta jinjinawa k'ok'arinsa sosai saboda ya tabbatar mata da cewa, tabbas shi cikakken namiji ne wanda a ko'ina za'a nunashi a fad'in duniyar nan, shiyasa a lokaci d'aya ta k'ara jin k'aunarshi ta mamaye lungu da sak'o na zuciyarta.

Tana nan a kwance tana ta wannan tunanin zucin sai ga wani yaro ya shigo gidan, rik'e da cefane a hannunshi sai rafka sallama yakeyi Amrah tana jin wannan sallama wadda tak'i k'arewa, a daddafe ta yunk'ura ta tashi zaune ba shiri ta cije baki tareda runtse idanuwa, a dalilin wani irin zugi da ya ziyarci k'asanta ta saka hannu ta dafe gado, sannan ta lallab'awa a hankali ta mik'e tsaye ta fara taku bakinta a cije tamkar wata mai koyon tafiya, dak'yar ta samu ta bud'e murya ta amsa sallamar saboda yawan nanata sallamar da yaron yakeyi.

A cikin dubara ta saita tafiyar taje ta karb'o cefanen tazo ajiyewa ne idonta yakai inda ta bar d'ayan cefanen da malam yazo dashi tayi murmushi, saboda tuno lokacin da dukansu suka fita a hayyacinsu suna neman hanyar da zasu gamsar da junansu.

A cike da nishadi a zuciyarta taje ta d'ebo ruwan zafin da har sun fara tafasa taje tayi wanka bayan ta gasa jikinta sosai sannan taji k'arfin jikinta, a gurguje ta fara d'ora sanwa kala biyu saboda cefanen da aka kawo mabanbanta, d'aya tayi shinkafa da miya da salad yayinda d'ayan cefanen tayi tuwo da miyar taushe,tareda taimakon k'anwar malam da tazo wurinta mai suna jamila, bayan sun k'are taje ta feso wankanta ta cab'a kwalliyarta gwanin burgewa, k'anwar malam sai satar kallonta takeyi saboda ganin tsananin kyawon da tayi.

Amra kyakkyawa ce son kowa k'in wanda bai samu ba, suna nan suna fira da jamila bayan sunci abincinsu sun k'oshi, sai ga malam ya shigo da sallamar shi fuskarshi cike da annuri saboda ganin kwalliyar da amaryarsa tayi masa, bayan sun gaisa da jamila ne ta fara shire shiren barin gidan amrah tace da ita ta wuce da abincin da za'a kaiwa mahaifiyar malam,aiko ta d'auki kular tayi masu sallama ta fice, malam ya kai dubanshi ga amrah da take ta jin kunyar

had'a idanuwanta dashi, don ko sannu da zuwan da tayi masa bata bari idanuwansu suka had'u ba, saboda tsananin kunyarshi da take ji musamman idan ta tuno abunda ya faru a tsakaninsu dazu.

Malam dai sai kallonta yakeyi tana jera masa abinci a gabansa yana jin dad'in sa'ar da yayi na aure kyakkyawar mace irinta, uwa uba ga hankali da sanin yakamata tareda sanyin zuciyar da take dashi, amrah ta k'are jera masa kulolin abincin tareda janyo plate ta zuzzuba masa abincin duka kala biyu d'in, sannan tace dashi, "bisimillah."

Malam kam da idanuwanshi suna kan Amrah'r bai masan me takeyi ba, saboda ya riga ya shagaltu da ganin amaryarshi kyakkyawa maganar da tayi ce ta dawo dashi daga santin ta da yakeyi a zuciya, anan take k'amshin abincin ya daki hancinshi ba shiri ya kai kallonshi akan abincin da ta zuzzuba masa, da sauri ya zaro idanuwa a waje yace,

"Lalle ni Nura d'an gata ne abinci har kala biyu duk ni kad'ai?, cab lalle kafin nan da wata d'aya ma ni na fara ajiye tumbi, amman ke kam kodai yaron da na aiko ne bai kawo cefanen da wuri bane shiyasa kika aika aka siyo wani.?"

Amrah da sauri ta d'ago fuskarta tayi mashi kallon ido cikin ido, zuciyarta a cike da mamakin wannan magana ta malam nura ta ma kasa magana saboda jin wannan maganar da tafito a bakinshi, a cikin d'inbin mamaki tace dashi, kana nufin bakasan lokacin da ka shigo gidan ka kawo shi ba.?"

Ta k'are maganar a cikin dariya saboda tuno a yanayin da ya shigo tamkar wanda aka koro da d'inbin shaawarshi a cikin k'wayar idanuwanshi, malam yayi murmushi yace, "Eh nine ko" ba tareda ya k'ara tofa wata magana ba sannan ya fara cin abincin a hankali, amma a cikin zuciyarshi sai tunani yakeyi yana so ya tuno lokacin da hakan ta faru amma ya kasa, shiyasa ya bar abun a ranshi domin shi a tsammaninshi ko ita amrah'r ce ta bada aka siyo cefanen shiyasa takeso ta zolayeshi.

Yace da ita ta saka hannunta suci a tare da tak'i ya d'ebo ya kai mata a baki dole ta bud'e bakinta ya saka mata lomar daga nan suka dinga ciyar da junansu, malam yana cin abincin sai zuba santi yakeyi amrah tayi masa waigi da wani plate tana yi masa dariya.

Koda suka k'are cin abincin malam ya fara jagulata lungu da sak'o, har sai da ya tabbatar ya kamata a hannu sannan yayi k'ok'arin jefa k'wallonshi a raga, aikuwa sai ga malam ya tafi luu yana ta sharar bacci bindi mik'e yana sambatun,amrah kam shirun da taji ne yasa ta bud'e idanuwa a hankali, domin taga wace wainar ce ta tsayar da malam daga wannan d'imaucewar da yayi akan son biyan buk'atarshi, aikuwa caraf idanuwanta suka kai akan wutsiyar malam da take tsaye tsam yana zuba sambatu irin na jiya, aikuwa a zabure ta mik'e zaune tana mamakin faruwar wannan lamari, domin idan bata manta ba ko ajiya hakan ce ta faru dashi da yayi k'udurin yi mata tsome, aranta tace, " anya dai ba aljanu suke damun malam ba? To kuma idan har sune ya akayi yau ya sami lafiyar gwangwajewa da ita.?"

Shiyasa tayi saurin k'aryata hakan jiki a sanyaye ta saka gefen zanen gadon ta rufe masa al'aurarshi, sannan ta sauko gadon ta mayar da kayanta da yayi cilli dasu d'aya d'aya a cikin d'akin, sannan ta fara tattara kayan abincin taje takai kitchen, ta fara wanke wanke a makwararar gidan tana k'arewa ta k'ara gyara gidan ko'ina tas ta feshe da turaren wuta, amma har izuwa lokacin malam bai tashi daga baccin ba gashi yamma ta gabato, har sai da ta shiga d'akin ta tarar dashi ya gyara kwanciyarshi kuma ya daina sambatun, sannan ta zauna a gefen gadon ta cira hannu ta fara shafo fuskarshi tana hura masa iska a idanuwa.

Sannan malam yayi firgigit ya tashi zaune yana kallonta da wani tsadadden murmushi akan fuskarshi, yace da ita, "Nagode sosai zaujatu Nura 'yar aljannah ina godiya da farincikin da kike sakani nagode nagode amaryata nikam nafi kowa dace da mata a kaf fad'in duniyarnan fatana kawai ALLAH ya barmu tare har aljannah."

Amrah taji dad'in wannan yabo da yayi mata tayi fari da ido tana murmushi sannan tace, "kayi hak'uri na tada kai daga bacci sabida naga marece har yayi shiyasa gashi kuma kasha fad'a mani ba kyau baccin marece."

Malam ya kai mata sumba yace, "Ai ni kin gama mani komai tunda kike bani abunda yake sakani manta ina nake."

Amrah tayi saurin rufe fuskarta tana murmushi, a tare suka fito ta raka shi bayi ta taimaka masa yayi wanka sannan ya shirya ya fita zuwa islamiya, domin yana so yaga abunda yake gudana acen kasancewar shi malamin da ragamar makarantar take a hannunshi.

Koda dare yayi abincin da ta dafa da rana shi suka Ci har suka kyautar da saura ga wani almajiri da yayi bara, sannan suka dinga firarsu ta ma'aurata mai cike da tsokanar juna a tsakaninsu, inda labarin yasha bambam lokacin da malam nura ya nemi ya k'ara komawa a filin daga, aikuwa 'yar gidan jiya ce ta k'ara kasancewa ya bige yana ta shan barcinshi mai cike da sambatun kiran sunan amrah'r.

Amrah kam izuwa lokacin abun ya fara bata tsoro saboda ganin wannan hali da mijinta yake kasancewa, da tunani fal aranta tayi bacci har da mafalkai kala kala wad'anda ta kasa gano kansu ballantana ma'anar su.

Koda safiya ta waye bayan sun karya tayiwa malam rakiya kamar jiya ya fita, sannan ta fara 'yan aikace aikacenta aiko sai ga malam ya dawo afujajan yana neman hak'k'inshi, ba musu ta amince masa duk da a zuciyarta tana ta jin tsoron abunda zai faru, aikuwa abun mamaki sai gashi yayi mata bazata domin kuwa har sai da tayi ta rok'arshi akan yayi hak'uri, saboda ya gajiyar da ita sosai sannan ya k'yaleta yaje yayi wanka ya mayar da kayanshi, yayi mata sallama daga kwancen ya fitawar shi.

Yazo k'ofar gidan kenan yana sauri yayi kicib'is da aunty asabe zata shigo gidan, ba shiri

gabanta ya fad'i taja baya ta bashi hanya ya fice tana mai jin nauyin wannan gaf da gaf d'in da tayi da surukinta, amma abun mamaki ko waiwayo aunty baiyi ba ballantana ya tsaya su gaisa, aunty ta bishi da kallo a cike da mamakin faruwar hakan domin tasan yanda malam yake girmamata ba kad'an ba, tun kafin ya auri Amrah muddin ya ganta koda bata kula dashi ba sai ya tsaya ya gaidata.

🤔🤔🤔🤔

Akafta🦹

D/Auta ce😝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI🔥

KAR KU MANTA LITTAFAN HADIZA D/AUTA

Tartsatsi
Ruwa da kanra
Bakan Gizo
Sai
🔥BAKON YANAYI🔥 mai take da nashi kalar salo kar ku bari a baku labari sayen nagari maida kud'i gida🤝

PAGE 13

****

Aunty da k'aton mamakinta a zuciya ta shiga gidan tareda sallamarta abaki, Amrah tana jin sallama tayi saurin tashi zaune ta kimtsa jikinta, sallamar da aunty ta k'ara yi ne yasa ta gano muryarta aikuwa da sauri ta tako a hankali ta fito d'akin, saboda k'afafuwanta da suka yimata sanyi saboda ba k'aramar jigatata malam yayi ba, tana k'yalla idanuwa ta hango aunty da sauri taje ta rungumeta tana murna, auntyn ma taji dad'in ganinta musamman yanayin da taga tafiyarta, sannan da abunda taji yana tashi a jikin amrah , zuciyarta ta tabbatar mata da lalle Amrah ta sami lafiya, ta jawo hannunta suka shiga d'akin tana kai dubanta akan gadon ta k'ara tabbatar da lalle komi yayi zam kasancewar d'aki guda ne k'ato ba falo, a cikin farinciki ta zauna a kan d'aya daga cikin kujerun dake d'akin tana murmushi tace, "to ya gidan dafatar dai komi yayi normal.?"

Amrah ta sunne kai tana murmushi aunty ta k'ara tabbatar da lalle zarginta ya zama gaskiya, a cikin farin ciki suka fara fira a cikin dabara ta tambayeta ko akwai wani laifi da tayiwa malam shiyasa ya fita yana fushi?, Amrah ta tabbatar mata da lafiya lau suka rabu aunty ta k'ara jin dad'i a ranta, saboda ganin kwanciyar hankali a tattare da amrah amma zuciyarta bata daina yimata mamakin akan abunda malam yayi mata ba, ta tsayu akan magana d'aya da cewa bai kula da ita ba ne , saboda ko a jiya har gida yaje yana ta yimata godiya shiyasa tayi matuk'ar mamakin abun.

Daga nan suka ci gaba da firarsu a nan ne Amrah take tambayar aunty ko tana da labarin mamarta?, a cikin damuwa aunty ta fara bata hak'uri saboda tuno zuwan da zuwaira tayi har gidanta, taci mata mutunci ta uwa ta uba bayan had'a tan da iyayensu da tayi acen garinsu, Amrah ganin yana yin aunty yasa ta fara kuka saboda jikinta ya bata akwai abunda mamar ta k'ara yiwa aunty wanda ya b'ata mata rai bayan aurensu, a cikin dauriya Aunty ta saki jiki tayi ta yiwa amrah bayanan yanda zatayi ta k'ara cafko zuciyar malam, tareda dubaru irin na kamo kan miji a rik'e jabau har asa shi ya manta sunanshi, daga nan tayi mata sallama ta tafi suka rabu a cikin kewar juna.

Sannan taje ta k'arasa 'yan ayukanta tayi wanka ta d'ora sanwar rana, zuwan jamila k'anwar malam yasa ta saki jiki ta cire damuwar dake damunta dangane da matsalar mamarta, suka yi ta firarsu har malam ya dawo ta tafi gida da kular abincinsu.

Koda safiya ta k'ara wayewa malam ya fita ya k'ara dawowa ya k'ule da amrah a d'aki yana kwasar gara, bayan ya gama yaje yayi wanka yayi amrah sallama ya fito yana saka talkaminshi zai fita, sai ga jamila ta shigo gidan da kuzarinta domin tasan malam baya gidan a lokacin, kawai sai fashi tayi kicib'is dashi a gidan, ba shiri ta zaro idanuwa tana nunashi tace, "ba yanzu na baro ka makaranta ba yaushe ka shigo gidan ban ganka a gabana ba.?"

Malam ya shak'o wuyanta ya matse ga gini da jajayen idanuwanshi yace da ita, "Kika kuskura kika fad'awa wani wannan maganar wallahi a ranar zaki bar duniya."

Yana k'are maganar ya wurgata kanta ya bugu da gini ya fice abinshi, to tun daga ranar malam bai k'ara dawowa a gidan da wannan lokacin ba.

A haka dai zaman nasu yaci gaba da kasancewa har tsawon sati biyu, wanda a 'yan kwanakin amrah take jin wani canjin yanayin da bata saba dashi ba a jikinta,saboda a kullum da zazzab'i take kwana sai safiya tayi ta tashi garau, shiyasa bata maida abun wani abu ba duk da malam yayi ta zancen suje asibiti tana dojewa, don batason ace za'a yimata allura saboda a rayuwarta sam ta tsani ace za'a yimata allura, tafison tayi ta shan magani har ALLAH ya kawo mata sauk'i, don ko a gida ba k'aramar tarzoma akeyi da ita ba idan batada lafiya aka zo za'a yimata allura.

Wasa wasa har tsawon wata d'aya tana fama da ciyon kai da dare kuma ta kwana da zazzab'i, shiyasa malam ma ya daina matsa mata sabida ganin yanda take fama da kanta,a wani dare da ta kwana tana wani zazzab'i mai zafi tana ta kelaya amai, tun da sassafe Nura yaje ya fad'owa aunty suka kwasheta sai asibiti saboda ta jigata sosai aman yaci k'arfinta, koda suka je a binciken farko aka gano tana d'auke da juna biyu na wata d'aya, daga malam har aunty babu wanda baiyi murna da wannan samuwar cikin ba, saboda a ganinsu shine k'arshen duk wata matsala, aka baiwa Amrah gado tareda manna mata k'arin ruwa bayan anyi mata allurai tana ta kuwwa.

Koda auntyn taga bacci ya d'auki amrah tace da malam zataje gidansu Amrah ta sanar da mahaifiyarta abunda yake faruwa domin abata hak'k'inta, duk da malam yaji tsoron abinda zaije ya dawo amma yayi mata adawo lafiya, aunty ta fita ta tari napep sai gidansu Amrah zuciyarta sai fargabar yanda zasu kwashe da zuwaira takeyi.

Wannan cikin fa da amrah tayi shine silar bankade duk wani sirri dake lullub'e shin to tayaya????ku biyoni domin kuji komi🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️

Akafta🏃‍♀️

D/Auta ce🤝
🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐

(We entertain and educate according to our religion and
ethnics)

PAGE 14

****

Da fara'arta ta rafka sallama Zuwaira dake tsakar gida tana tsintar shinkafa, tana d'ago fuskarta suka yi ido biyu da Aunty Asabe ta had'e fuskarta tamau, sannan ta mayar da kanta taci gaba da aikin da take yi, Aunty tayi kamar bata ji zafi ba ta jawo kujerar robar dake ajiye tsakar gidan ta zauna, sannan tace da ita, "Aunty wajenki nazo."

Zuwaira TAYI banza da ita tareda tashi tsam ta kwashe robar shinkafar da tiren da take tsintar tayi kitchen ta ajiye, sannan ta dawo ta cire d'ankwalin da ke kanta tasha d'amara, fuskar a murtuk'e tace da Asabe, "Sawunki a likkafa ki tashi ki fita gidanna tun kafin in nad'a maki shegen duka wallahi, in yaso sai akaini gidan yari a rufe ace d'an mabud'in ya b'ace."

Aunty ta Mik'e tsaye tareda gyara tsayuwarta ta fara murmushi mai cike takaici tace, "Ni ba wannan ne ya kawoni gidanki ba, daman nazo ne na sanar dake Amrah ta sami juna biyu yanzu haka tana asibiti an kwantar da ita."

Zuwaira duk da jikinta yayi sanyi jin Amrah ta sami lafiya wai har da ciki, amman bata fasa aibata Amrah da malam Nura ba har da tayin cikin dake kwance cikin mararta, wajen fad'in, "To ni miye nawa a ciki da zaki zo ki sanar dani, ai na riga da na bar maku ita ko mutuwa tayi bana k'aunar ganin gawarta balle don tana asibiti ki kwaso k'afafuwa kizo ki fad'a man"

Aunty ranta a b'ace tace, "Hak'k'inki ne shiyasa har nazo na sanar dake, wai don kisan rabo idan ya rantse sai ya fito to wajibi ne ya fiton ko ta hanyar halas d'in ko kuma ta hanyar da ba'a so, saboda haka rabo ajali ne ki godewa ALLAH da bai kashe ki ba kuma anyi sa'a ya fito ta hanyar halass, ni kinga tafiyata idan kinga da hali kizo kiga 'YARKI."

Aunty ta fara tafiya zata fita Zuwaira tayi saurin jawo hijabinta bakinta yana kumfa saboda bala'i tace, "Da Amrah'r da Matsiyacin malamin da yayi cikin, da cikin kanshi sannan dake duka ALLAH ya tsine maku gaba d'ayanku, Wallahi na k'ara ganin k'afarki a cikin gidannan sai na yaga maki rigar mutunci, bak'ar munafuka ai wallahi duk bak'in kullin da kuka k'ulla sai kun warware shi da hannunku, don kuwa indai ni na haifi Amrah bazata tab'a jin dad'in wannan tsiyataccen auren ba don kuwa har abada ba zai tab'a yin albarka ba, ta dinga had'uwa da musibu kenan matuk'ar ba kashe wannan bak'in k'addararren auren tayi ba."

Aunty jikinta ya d'auki rawa da sassarfa ta fito gidan saboda Jim miyagun alkaba'in da Zuwaira take ta jifar 'yarta dasu, taji tsoron lafuzzan da take furzarwa a bakinta wai kuma ga tilon 'yarta mace da ALLAH ya bata, zufa sai karye mata take yi a jiki saboda tsananin tashin hankalin da ta shiga, tayi da tasanin zuwa wurin Zuwaira don a ganinta duk itace ta jawo komi,tunda tun farko sai da taja kunnensu akan bata ba Amrah, amman idan tayi duba da hak'k'in da take dashi ga 'yarta sai taga ba wani abu bane don taje ta sanar da ita halin da 'yarta take ciki, koda mai Napep ya ajiyeta bakin asibitin kai tsaye d'akin da aka kwantar da ita ta shiga, koda taje ta tararda ita ta falka tana shan lemun fatar da Malam ya siyo mata, saboda bakinta da baya yimata dad'i gaba d'aya ta rasa appetite, Aunty ta k'araso jikin gadon idonta akan Amrah tace, "Masha ALLAH ashe ta tashi."

Malam yayi saurin tashi daga kan kujerar da yake zaune a cikin girmamawa ya ce "Eh Aunty yanzu ta tashi."

Aunty tace dashi, "Ka kira Jamila tazo ta zauna da ita kafin inje gida in yi abinci in dawo."

Malam Nura yace "to yayi Aunty bari in kirata tazo sai kin dawo ALLAH ya tsare hanya."

Aunty taje kusa da Amrah ta ri'ko hannunta tace, "Ya jikin me kike so inje in dafo maki?."

Amrah ta yamutsa fuska a cikin rashin jin son cin komi tace, "Alale"

Aunty tace, "To yayi jirani zan kawo maki bada jimawa ba, ALLAH ya baki lafiya."

Ta k'are maganar tareda shafa kanta sannan ta yi sallama da Nura ta fice, zuciyarta cike da tausayin Amrah saboda rashin dace da Mahaifiya da bata yi ba.

Malam ya jawo kujerar kusa da gadon ya zauna idonshi akanta yace "sannu" ta d'aga masa kai saboda yawun da ya cika mata baki, ya yago tissue ya mik'a mata ta zubar da yawun ya amsa yaje ya zuba a dustbin ya dawo, ta langab'e masa tace, "Da zan sami Abu mai bauri in

sha don bana son tara yawunnan da nike."

Malam ya yi saurin cewa, "Kamar me fa?" ta b'ata fuska sannan tace "ko d'anyen dabino haka"

Yace, "OK jirani minti biyu inje in ga me zan samo maki" ta lumshe ido ta bishi da kallo har ya fice sannan ta mayar da dubanta ga matan da ke cikin d'akin, masu jinya da majinyatan ta natsu sosai cikin tunanin Mahaifiyarta Zuwaira da taji tana da cikin me tace, saboda ta mance shaf bata tambayi Aunty yanda suka yi ba har ta tafi gida, don lokacin da ta farfad'o ne Malam yake sanar da ita inda Auntyn taje.

Minti biyar a tsakani sai ga Malam ya dawo hannunshi rik'e da ledodi masu kunshe da kankana da lemu ayaba gwaba gwanda da abarba,, sai lemuka na gora kala kala ya sami gefen gadon ya ajiye ledodin sannan ya rik'o hannunta a cikin tausayawa yace, "ya jikin?" ta k'ura masa kallo zuciyarta cinkushe da damuwa bata ce komi ba, ya tsargu da kallon yaga tana yi masa shiyasa ya duk'a ya d'auko ayaba d'aya ya b'are ya mik'a mata, ta saka hannu ta karb'a duk da zuciyarta bata son cin komi, ta kai bakinta ta d'an gutsura aikuwa sai gashi taji dad'inta a baki, nan take ta canye ayabar ya k'ara b'allo mata wata ta cenye kasancewar cikinta ba komi duk ta amaye, sai da taci uku sannan ya d'auko plate ya zuzzuba mata sauran kayan yanka yanka ya d'ora mata akan cinya, sannan yace shi zai je ya dawo tayi masa murmushi mai cike da jin dad'in bajintar da yayi, aiko da sauri ya Mik'e yazo fita d'akin ne yaci karo da Jamila da bak'ar leda a hannunta, suna had'a ido ta zaro ido saboda tsananin Mamakin da tayi, don ko minti biyu bata yi da rabuwa da Malam d'in ba, shine ma ya bata ledar da ke hannunta ta kawo wa Amrah yace mata ya tafi ganin likitan da ke kula da Amrah, saboda ganinsa da yayi lokacin da ya shigo asibitin yace yazo ya karb'i magungunan da za'a siyo mata.

Shi kam ko bi ta kanta bai yi ba ya fice jamila ta bishi da kallo har ta daina ganinshi, sannan ta k'araso jikin gadon Amrah tana dariyar yak'e saboda fargaba da tsoron da ya cika mata zuciya.

Aikuwa minti sha biyar a tsakani sai ga Malam ya dawo hannunshi d'auke da ledar magungunan da ya siyo, ganin plate cike da kayan fruits a saman cinyarta tana sha, yayi murmushin jin dad'i yace, "Masha ALLAH waye yayi muna wannan k'ok'ari?"

Amrah ta bishi da kallo cike da mamakin tambayar da taji yayi a cikin tantama ta ajiye yankan gwandar da take sha tace, "Bangane abunda kake nufi ba."

Malam yana murmushi ya matso jikin gadon ya tsaya idonshi akan plate d'in yace, "Wadannan kayan lambun waye ya kawo muna su halan bayan na fita?"

To fa ku baiwa malam amsa😳nidai yasin nayi nan 🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️.

Akafta 😂

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

PAGE 15

****

Amrah kam ba shiri k'irjinta ya buga dam! Dam! Tareda zaro ido a waje tace, "Yau ma ka k'ara kwata 'yar ranar ko?, nifa WALLAHI kar kasa in fara jin tsoronka, sai kayi abu ka dawo kace baka san kayi ba."

Kanshi a d'aure yace, "in har haka ne kema ya kamata a bincike ki a gabanki fa na fita kuma wannan ce dawowata, da tareda jamila zamu shigo sai ga likita yayi kirana shine ledar sak'on da kika ce a siyo maki na bata takawo maki na wuce office d'in likitan, ya bani takardar magungunanki kin gasu ma sai da naje na siyo sannan na zo."

Amrah ta k'ara gwalalo idanuwa a cikin tsoro tace, "Na shige su ni Amratu to idan ba kai bane wanene?."

Ganin yanda hankalinta ya tashi ne yasa yace, "To miye na d'aga hankali kuma? Naji nine d'in shikenan komi ya wuce."

Ya fad'a ne kawai don ya kwantar mata da hankali, Jamila dai in ta kalli Malam Nura ta kalli Amrah saboda maganar dake cinta a rai amman ba halin fad'a, saboda tana jin tsoron ta rasa

ranta kamar yanda aka garfad'eta, ba shiri ta zauna gefen gadon Amrah tayi tagumi saboda ita kanta wani tsoro ne ya shigeta, saboda yanzu ta k'ara tabbatar da zarginta akwai aljanin dake bibiyar rayuwar aurensu.

Amrah kam duk yanda malam yaso ta kwantar da hankalinta abun yaci tura, domin kuwa k'urawa Malam kallo take yi a wautarta tana so ta gano a hayyacinshi yake ko kuwa, sai gashi ta kasa gano wata alama da zata tabbatar mata da hakan, saboda ita duk zarginta Malam shaye shaye yake yi a b'oye baya son a sani, Musamman da taga Jamila tayi shiru bata ce komi ba, dukansu kowa da abunda yake sak'awa a ranshi.

Shigowar Aunty shi ya yasa dukansu suka dawo daga zuzzurfan tunanin da suka lula, Musamman Malam da ya k'urawa ledodin kallo yana son ya tuno lokacin da ya siyo kayan fruits d'in, amman ya kasa tunowa, shine ya zargi ko dai bacci ya d'ebeta wani ya kawo ta zaci shine.

Aunty ta k'araso ta ajiye kulolin ta na Murmushin ganin yanda Amrah ta ware, tana ajiye kulolin ta fara kiciniyar fiddo plate ta zuba mata alelen gwangwanin da tayo mata, tareda manja da yaji sai da ta zuba mata kusan shida sannan ta saka mata yaji da manja ta mik'a mata, aiko miyon Amrah har tsinkewa suke yi saboda sha'awar cin alalen da take yi, Aunty ta saka mata spoon tana 'yar dariya tace, "Sha kuruminki gata kici har sai kince ta isa, don kinga sauranta nan a cooler."

Amrah ta karb'i plate d'in tana dariyar jin dad'i ta fara ci, Aunty ta Kalli Malam a cikin jin nauyin surukuta tace, Ga abincinka kai kuma sai ka sami inda zaka d'an rab'a kaci jamila d'auki kular ki kai masa ki dawo ga alalen kema."

Jamila ta sunkuya ta karb'i Kular da plate da spoon d'in da Auntyn take mik'a mata sannan ta fita, Malam ya fita Aunty ta jawo kujerar ta zauna idonta a kan Amrah da ke ta auna alalenta tana lodawa a baki, sai da ta kusan cenye alalen sannan ta fara jin amai, aiko ta fara yamutsa fuska Aunty tace, "lafiya?"
Bakinta a dantse tace
"Amai."

Aunty ta fara bud'a ledodin ta ciro d'anyen dabinon da Malam ya siyo ta mik'a mata tace, "Yi k'ok'ari ki ci insha ALLAH zai tsaya."

Da sauri ta gutsura TANA tauna a hankali aiko sai ga aman da take ji ya fad'a, sannan nutsuwa ta ziyarceta ta jingina bayanta a pilo ta lumshe idanuwanta tana tuno Mahaifiyarta Zuwaira, saboda yanda take ji a jikinta yasa ta k'ara girmama matsayin Uwa, a hankali ta lula tunanin rikicin da aka yi da tata Uwar kafin ta aure Malam Nura, Aunty cikin jin dad'i tace, "Shi ko Malam da hidima yake wannan uwar siyayya duk a lokaci d'aya?"

Amrah ta kai kallonta ga ledodin sannan ta b'ata fuska tace, "Aikam dai kin ganshi nan yayi amman ya dawo yace ba shi bane."

Aunty tayi saurin fad'in, "kamar ya ni ban gane wannan hausar taki ba, yace ba ba shi bane kamar yaya?"

Amrah ta k'ara kai kallonta ga ledodin tace, "Shifa ya kawo amman da ya dawo sai gashi yana tambayar wa ya kawo kayan, haka fa ranar ya yi cefane biyu yace baisan yayi ba guda d'aya ya sani."

Aiko Aunty ta fashe da dariya tace, "Lalle Malam d'alibanshi sun fara rud'a shi"

Itama Amrah tayi dariya tace, "Da alama kam tunda sai ya yi abu ya dawo yace sam ba shine ba"

Suna tsaka da dariyar ne Jamila ta shigo da yake ta tsinkayo maganar da Amrah take yi, aiko ta bisu da kallo mai cike da bakusan dawan garin ba, Musamman Amrah da a take ta fara bata tausayi duk da k'arancin shekarunta ta gano akwai lauje a cikin nad'i, dangane da zaman aurenta da d'an uwanta, alalen ma kad'an ta tsakura tace ta k'oshi.

Amrah dai kwananta Uku Asibitin sannan aka sallameta suka koma gida, amman ko d'an sak'o Zuwaira bata aiko ya duba mata jikinta ba, shiyasa da Amrah ta tambayi auntyn yanda suka yi bata sanar da ita gaskiya ba, don bata son ta k'ara d'aga mata hankali da d'an tayin cikinta, duk ko da nacin da tayi akan tana son tasan abunda ya faru.

Sannu a hankali Amrah tana jinyar cikinta yau lafiya gobe ciyo, a kullum zuciyarta tana d'okin taje taga Mahaifiyarta da 'yan k'annenta amman Aunty tayi mata gargad'iin kada taje ta d'an jira lokacin da zata je baiyi ba, ita Aunty tsoron da take ji taje Zuwaira ta illatata tareda d'an cikinta, saboda a yanda taga ta hau da yawa komai zata iya aikatawa,saboda ta d'ebe takaicin fin k'arfin da aka yimata, don ko k'annen Amrah'r zuwaira ta gargadesu idan suka kuskura suka je gidan Amrah, koda a sace ne to fa bata yafe masu ba, daga dangin Babanta sai aunty sune kawai suke fad'i tashi da ita ta b'angare kula da wani abu idan tayi sha'awa.

Kwanci tashi asarar mai rai don kuwa gashi cikin Amrah har ya kai wata biyar, duk wasu k'ananun matsala da take ji sun kau sai d'an abunda ba'a rasa ba, kuma har lokacin suna nan a yanda suke da Malam zai yi ta mafalkinshi yana sambatu, da safe ya tashi yayi wankanshi ita kam a kullum k'ara tsulewa take yi da lamarinshi, saboda ita kanta a matse take da buk'ata don tunda ta sami ciki Malam bai koma kusantarta ba, saboda da sunfara wasa yazo gangar jik'a alkalaminshi sai kawai yayi ta baccinshi yana abunda ya saba, tun bata damuwa da lamarin har abun yazo yana damunta, don ma tun da ta sami cikin ba ta jin wata sha'awa sosai sai dai fa duk da hak'urinta tana buk'atar ta kusanci mijinta, amman ba damar hakan gashi kuma tana jin kunyar ta fad'awa Aunty abunda yake faruwa, dole ta rungume hak'uri ba don taso ba sai dai kullum idan taga Malam a yanayin da yake shiga tayi ta sharb'ar hawaye, saboda tausayin kanta da shi kanshi da take ganin kamar da gaske aljanar ce ta aureshi, don daman cen an riga da an canfa hakan, a cewar Mutane ma itace ta hana shi aure da wuri.

Cikin Amrah yana wata bakwai ta rame sosai saboda damuwowin da tasawa kanta, ga tunanin Mahaiyarta da 'yan uwanta, haka ma ga tunanin halinda take ciki na matsuwa da son mijinta ya kusanceta, sannan ga Matsalar Malam da kullum ci gaba take yi, ko fitar da yakeyi ya dawo ya kusanceta a matse komi ya daina, sai dai idan ya fita tayi ta kukanta saboda bata san ta hanyar da zata sanar dashi abunda yake faruwa dashi ba, aiko sai gashi Kwatsam bayan fitarshi Aunty tazo ta tarar da ita tana ta Kuka, a cikin Mamaki tareda tashin hankali ta rik'ota tana tambayarta abunda yake faruwa, Amrah tak'i fad'a mata gaskiya ta dai ce da ita tana son taje taga Mahaifiyarta ta bata hak'uri, aiko a take Aunty ta kira mijinta ta sanar dashi zata kai Amrah wajen Mahaifiyarta, sannan ta kira Number Malam tace dashi yazo, aiko minti goma a tsakanin ko sai gashi ya shigo gidan Aunty tayi masa bayanin halin da ta tarar da Amrah, idan ba damuwa ya barta taje ta gano Mahaifiyarta ta nemi yafiyarta,a cikin jimamin abun Malam yace ba damuwa shima zai so suje tare su nemi yafiyarta duka, aiko a take Amrah ta shirya tareda saka zunbulelen Hijabi Malam ya taro masu Napep suka shiga,dukansu zuciyoyinsu sai bugawa suke yi saboda tsoron abunda zasu je su tarar, sai gashi sunyi rashin sa'a domin kuwa Zuwaira bata nan sai k'annenta biyu da ta iske, sunji dad'in ganin juna sai dai sunji tausayin ramar da suka ga 'yar uwarsu tayi, duk da daman cen ba wani jiki ne da ita ba sai dai sun ta'allaka hakan da cikin da suka gani a jikinta,wanda ya fito sosai a kallo d'aya za'a gano shi saboda girman da yayi, bayan sun d'an huta ne suka tashi zasu tafi Amrah ta fara kuka tana rok'on su Aunty su tafi ita su barta sai Mamarta ta dawo ta nemi yafiyarta, tsoron abunda zai je ya dawo sanin sanin halin Zuwairar yasa ta ce bazasu barta ba, dole ba don taso ba suka fita sai kuka take yi gwanin ban tausayi, ganin Hakan yasa Aunty ta rok'i Malam akan zata tafi da ita gidanta ba musu ya amince aka ajiyeshi makaranta su suka wuce gidan auntyn.

Da lallami da ban baki Aunty ta samu Amrah ta daina kukan sannan ta tashi taje ta dafo mata abunda tace tana so, ta kawo mata suna fira tana ci har ta cenye, sai bayan Magriba sannan Malam yazo suka tafi gida, shima ya dosa inda Aunty ta tsaya sai lallashinta yake yi tareda ban baki akan tayi hak'uri komi zai gyaru insha ALLAH, shigarsu gida keda wuya suka tarar da wata envelope a k'ofar d'akinta ajiye, a cikin Mamaki suka yi turus dukansu tareda k'urawa envelope d'in idanuwa, Malam ne yayi jarumtar isa wajen ya duk'a tareda bismillah a bakinshi ya d'aukota ya shiga jujjuyata da zaton ko akwai rubutu a wani gu,amman ba wani rubutu sai nauyi da envelope d'in take da, sai da Malam ya tofe ta da addu'a sannan ya d'an yage gefe ya lek'a aiko sai ga Kud'i ya hango tareda takarda, a cikin tsananin Mamaki ya k'ara yage ta gaba d'aya, sai ga kud'i 'yan dubu dubu sababbi k'al tareda wata farar takarda, ya zaro takardar ya bud'e kasancewar akwai nefa ya fara karantawa ba shiri ya zaro ido a waje, tareda sakin takardar da kud'in ak'asa ya fara tafiya da baya baya idonshi akan Amrah ya kai zaune dirshan ba shiri, a cikin tsananin fargaba Amrah ta taka inda takardar take a yashe ta sunkuya ta d'auka jikinta sai rawa yake yi ta bud'a takardar aikuwa sai gashi taga abunda ya firgita Malam wanda itama idan ba'a yi wasa ba zai kaita lahira bata tantance ba saboda bak'in ciki, don kuwa tana k'are karanta abunda takarda ta k'unsa ba shiri tayi zaman 'yan bori tareda aza hannu aka ta kurma ihu sannan ta yi luuu ta sume.

Malam kam yana zaune inda yake sai jib'i ke kwararo masa saboda tsananin tashin hankalin da

ya shiga, duk da a gabanshi ta sume amman baiyi yunk'urin tashi ya tallafa mata ba, saboda mamakinta da tsananin tsanarta da yaji sun dirar masa a lokaci d'aya.

 ina tsaye ina kallon ikon ALLAH na kasa hak'uri naje na d'auko takardar domin ina son inga me ya d'aga masu hankali har haka, saboda a tarihin aurensu fad'a ko na d'ai rana basu tab'a yi ba, sai dai d'an sab'ani na yau da gobe na zaman tare wanda ba za'a rasa ba, amman wai gata a sume shi ko a jikinshi sai kallon tsana da yake yimata, a cikin tsananin mamaki na fara karanta takardar kamar haka,

Aslm
Amrah nine uban cikinki ba Nura ba saboda yau cikin watanshi bakwai da kwana shida don haka ki sani da kin haife cikin a ranar zan zo in karb'i d'ana ko 'yata ga kud'i nan a baiwa masu karb'ar haihuwa.

Rigiji gafji😱😱😱😱😱

Akafta 😹

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

PAGE 16

****

Malam dake zaune ko d'an yatsanshi ya kasa d'agawa saboda tsananin tashin hankalin da yake a ciki, amman kallon Amrah da yakeyi a gabanshi sume, yasa yayi yunk'urin tashi tsaye dak'yar yana layi yaje ya d'ebo ruwa cike da bokiti yana zuwa ya antaya mata su da k'arfi, ba shiri ta tashi a razane tareda firgici ta kai kallonta gareshi tuno abunda yake faruwa ne yasa ta k'ara fashewa da Kuka, Malam ya bita da kallo a cikin tsananin tsana, sannan ya shige d'aki ya kira wayar Aunty a cikin zumud'i ta d'auka tace, "Yanzu fa nike son in kiraku inji ya kuka sauka, da fatar dai kun isa gida lafiya."

Kai tsaye Nura yace, "Ba lafiya ba."

Aunty ta dafe k'irji tareda zaro ido a waje tace, "Na shigesu Nura me ya faru kuma?"

Nura ya b'ata fuska a cikin damuwa yace, "ba maganar waya bace kizo dai ki gani kawai."

Anty kam tashin hankalinta ya k'aru a cikin rawar murya tace, "Eh naji zanzo amman don ALLAH kayi man bayani kafin inzo, don WALLAHI ka d'aga man hankali"

Kai tsaye yace da ita, "Ki dai zo kawai saboda maganar bata waya bace." kitt ya kashe wayar jikinta yana rawa ta iske maigidanta tana sanar dashi abunda yake faruwa ranshi ab'ace yace , "Nifa Asabe na rasa gano kanki tunda aka yi aurennan kin hana kanki zama lafiya nima kin hanani, shikenan ke a matsalar wannan aure zaki dawwama, nifa wallahi na fara gajiya inda ma wadda kike yi donta tasan kinayi banda tsine maki a kullum ba abunda take yi, to kiyiwa kanki karatun ta nutsu gaskiya don ni bana son kina hana ni sukuni saboda rayuwar wasu."
Yana k'are maganar ya tashi ya d'auko key d'in motarshi ya fice, ganin haka yasa taji dad'i ta jawo hijabinta ta saka sannan ta rufo gidan, ta tarar da shi inda yake jiranta bayan ya gyara parking, sannan suka mik'i hanyar gidan Malam Nura, ganin yanda ranshi yake a b'ace yasa Aunty ta rik'o hannunshi tace,

"Don ALLAH kayi hak'uri ni yarinyar tausayi take bani, saboda yanda mahaifiyarta ta wofintar da ita bata da kowa sai ALLAH sai ni da dangin Mahaifinta, shin idan nima na zare hannuna ai kaga damuwar zata yimata yawa, har ga ALLAH ni ina yine don ALLAH amman zumunci nike yi mawa, saboda ko Zuwaira ta yanke zumuncinmu ai ALLAH bai yanke muna ba, don ALLAH kayi hak'uri mu ci gaba da aikin ladar da muke yi, kayi hak'uri kaji?ALLAH zai bamu lada akan abunda muke yi." Sannan yayi murmushi a cikin kwantar da murya yace, "ALLAH yasa mu dace." cikin jin dad'i tace "Ameeñ"

Suna kaiwa k'ofar gidan ta fito jikinta sai tsuma yake yi akan tashiga taga meke faruwa, aiko Sallamarta ta mak'ale ne saboda kukan Amrah da ya tarbeta, da sassarfa ta isa wurinta don har lokacin tana tsakar gidan sai kuka take yi gwanin ban tausayi, Aunty ta ri'kota cikin tashin

hankalin da ya bayyana akan fuskarta tace, "Na shigesu Meke faruwa ne?ko wani abu yana maki ciyo ne?" Amrah ta girgiza kai tareda k'ara sautin Kukanta, Aunty ta k'ara rud'ewa hankali tashe tace, "Don ALLAH kiyiman bayani meke faruwa wai!" Amrah tayi mata nuni da inda takardar take a yashe, a cikin kad'uwa Aunty ta nufi takardar zuciyarta sai bugawa take yi da sauri da sauri, saboda zargin da take yi akan cewa takardar saki ce Nura ya bata, to akan wane dalili?me yayi zafi, tunaninta ya katse ne lokacin da ta fara karanta abunda takardar ta k'unsa, aiko da sauri ta dafe k'irji cikin wani sabon tashin hankali tace, "Me nike shirin gani ni Asabe, wannan bala'i da me yayi kama?" jikinta har tsuma yake wajen kwad'awa Amrah mari a cikin d'aga murya tace, "Miye had'inki da wanda ya rubuto takardar?me kika yi masa da zafi wanda har ya zab'i ya saka maki da wannan masifa ta bak'in k'azafi."

Amrah ta dafe gefen da Autyn ta mareta tareda k'ara sautin kukanta tace, "Wallahi Aunty nima bansan komai akan takardar ba."

Aunty ta maka mata wata k'atuwar harara sannan tace, "Kada ki renawa mutane wayo, taya zaki ce baki sani ba ga sunanki a rubuce?" Amrah ta fara rantse rantse sai ga Malam ya fito daga ban d'aki,saboda zawon da ya je ya tsiyaye na tashin hankali duk da dai kaso mafi rinjaye yana tabbatar masa da ciki nasa ne, to anman in babu rami me ya kawo zancenshi?, dole ne ayi bincike don wannan al'amari da d'aure kai yake.

Aunty tana ganinshi tace "yawwa Malam don ALLAH zo ka warware man wannan k'ulli, shin ya aka yi wannan takarda ta shigo hannunku?" kai tsaye yayi mata bayanin komi ranshi a jagule, Aunty ta kalli Amrah da zungureren cikinta sannan ga idanuwanta har sun kunbure saboda kukan da tasha, kanta gaba d'aya ya k'ulle ta rasa me ma zata fad'a kai tsaye ta nufi k'ofar gida, jiri yana kwasarta saboda tsananin firgici da ta shiga, jiki ba kuzari taje wurin mai gidanta ba tareda bayanin komi ba ta mik'a masa takardar, ya saka hannu ya karb'a a cikin mamakin takardar miye, shima a take ranshi ya bashi sakin Amrah Nura yayi, sai gashi yana gama karantawa yayi saurin d'ago fuskarshi yace, "Wasik'ar waye?" A cikin zubowar wasu hawaye Aunty tace, "Ta Amrah ce" da firgici akan fuskarshi yace, "Garin yaya hakan ta faru to?" Aunty ta share hawayenta tace "Nima bansani ba,kuma itama wai bata san komi ba yanzu haka ma tana cen tana kuka na tashin hankali, ina zamu kai wannan Masifa da darennan?"

Mijinta yayi shiru sannan yace, " ina shi maigidan nata?" Aunty tace "Yana ciki" yace "Kiyi man sallama dashi don wannan abu akwai d'aure kai sosai, amman kuma fa ruwa basu tsami a banza kira shi dai muji ta bakinshi."

Aunty ta koma gidan minti biyu a tsakani sai ga Nura ya fito, Mijin Auntyn ya fito daga motar ya mik'a masa hannu suka gaisa, sannan yace dashi "Me ka sani dangane da wannan takarda?. "

Yace sam shi baisan komi ba shi hasali ma shi zuciyarshi bata yarda da cewa hakan zai faru ba, mijin Aunty yaji dad'in maganganun da yaji ga Nura, yayi ta kwantar masa da hankali tareda

k'ara nusar dashi akan ya zama ido sosai akan gidanshi ko don ya kare martabar iyalinshi.

A cen cikin gida kuwa Aunty ce take ta yiwa Amrah fad'a akan sai ta fad'a mata wanda yayo takardar, amma ta kafe kai da fata akan ita batasan komi ba, dole aunty ta ajiye tambayoyinta ta koma lallashin Amrah, Amrah da jajayen idanuwanta da suka kumbure saboda kuka, ta d'aga kai ta kalli Aunty tace, "Don ALLAH Aunty ki tafi dani a gidanki WALLAHI tsoron gidannan nike yi, saboda bansan wani kalar sharri za'a k'ara biyo man da shi ba."

Aunty tayi jimmm na minti biyu sannan ta ri'ko hannunta, ta taimaka mata ta mik'e tsaye suka fito k'ofar gidan inda suka tarar da su NURA sai firarsu suke yi, Aunty ta kalli Nura tace, "Amrah ta rok'i alfarmar mu tafi da ita idan ka amince sai in wuce da ita in yaso gobe sai kaje ka d'aukota."

Yace,, "Ba damuwa"

Amrah ta shiga motar ta zauna sannan suka yi sallama da shi suka tafi, Amrah dai har suka je gidan aunty bata sani ba, saboda zuzzurfan tunanin da ta fad'a sai dai jin tayi aunty tace, " ki fito muje ko" sannan ta muskuta ta lallab'a ta fito jikinta gaba d'aya ba kuzari suka shiga cikin gidan sai jiri ke kwasarta, saboda kanta da yake ta sara mata har wani dushi dushi take gani dasu, tana zuwa d'akin Aunty tayi tsinke ta fad'a kan gado ta kwanta tareda k'udundunewa a bargo saboda wani zazzab'i da take ji, aikuwa kafin minti biyar sai gata tana kyarmar rawar d'ari saboda sanyin da take ji yana ratsa k'assan jikinta, hak'oranta sai had'uwa suke yi da juna suna kuka kaf! kaf!, Aunty ta shigo d'akin ta isketa a wannan hali jikinta yana rawa ta d'auko mata magunguna ta matsa mata dole sai da tasha sannan ta koma ta kwanta, yayin da wani Bacci yayi awon gaba da ita mai cike da mafalkai barkatai.

Aunty ta kashe fitilar d'akin sannan ta ja mata k'ofar ta nufi d'akin maigidanta, domin tana son su k'ara tattaunawa akan matsalar.
Amrah kam tsakar dare tana baccinta sharkaf sai gashi tayi zumbur ta mik'e zaune tareda dafe kunnuwanta ta k'walla k'ara tana fad'in, _WALLAHI Nazir bazan baka d'ana ba haka kawai da rana tsaka kazo kace sai na baka yarona wallahi bazan bayar ba._

Aunty da mijinta da gudu suka shigo d'akin suka yi cirko curko suna kallonta, suna k'are mata kallo a cikin Mamaki Aunty ta zauna tareda dafota da hannunta biyu ta girgizata sannan ta fara kiran sunanta tana tambayarta lafiya, sai a lokacin Amrah ta dawo a hayyacinta tana ganin Auntyn tayi saurin fad'awa jikinta tana Kuka, Aunty ta rungumeta tsantsan tana bubbuga bayanta tana lallashinta, bayan ta d'an lafa sannan Aunty tace da ita tayi addu'a ta koma ta kwantawarta ba abunda zai samunta, Amrah tace sam ita ba zata iya bacci ba saboda tana jin tsoron miyagun mafalkan da take yi, Aunty tace to taje ta d'oro arwallah sai tayi salloli kafin asuba, aiko tsam ta mik'e taje tayi arwallar Aunty ta shimfid'a mata carpet, sai da ta tada sallahr sannan ta fito d'akin zuciyarta sai tunani take yi akan wanene Nazir d'in da taji Amrah ta fad'a, anya ko wai wannan abu babu k'amshin gaskiya a ciki?taci alwashin idan safiya ta waye zata tambayeta wanene shi, don idan bata manta ba ko Zuwaira sai da taji sunan Naziri a bakinta

tana fad'ar cewa, _kada dai ace hak'k'inshi ne yake bibiyarsu_ Shin shi Nazir d'in wanene? Miye alak'arsu dashi ne? Da har hak'k'inshi zai bisu? Shin to ta yaya ma wai to?haka Aunty ta kwana tana tunanin sunan Nazir da taji Amrah ta ambata tana ta Alla Alla akan safiya ta waye suyi maganar don saboda a gano ta inda kan zaren yake.

Amrah kam bayan tayi ta jera sallolinta ne tareda addu'o'inta, wata azababbar yunwa ta ziyarceta dole ta had'a tea mai shegen kauri ta shanye da guntun biredin da tagani a d'akin sannan hankalinta ya dawo jikinta, ana yin sallar asuba ta samu ta gabatar da ita, ta d'an kishingida a gefen gadon sai bacci.

Koda safiya ta waye har k'arfe takwas Amrah tana ta baccinta, Aunty mayarta biyu tana dubawa bata tashi ba sai a ta uku ce da ta shigo taji motsinta toilet, ta sami gefen gadon ta zauna tana jiran fitowarta, aiko sai gata ta fito da alama wanka ma tayi tana ganin Auntyn ta k'araso da sauri tace, "Aunty ina kwana?" tace "Lafiya lau." Sannan ta bita da kallo mai cike da tausayin yanda ta k'ara zabgewa har k'ashin wuyanta ana gani, Amrah da duk da bata da wani jiki amman wuyanta a cike yake,saboda tsanannen jiki ne da ita kibarta tayi dai dai da jikinta, Aunty tace da ita idan ta k'are ta fito falo ta yi breakfast, taje ta fiddo mata wata doguwar riga bubu a cikin kayanta ta bata ta saka, sannan ta fice zuciyarta cike da sak'e sak'e.

Amrah ta bita da kallo sannan ta d'an shafa mai sama sama ta zura rigar ta fito, kai tsaye falon ta nufa ta zauna inda Aunty ke zaune tana kallon tashar Arewa 24 itama tazo ta zauna Aunty tace, "Yawwa kin fito?" tace. "Eh" Aunty ta mik'e tsaye taje ta kawo mata abun karin sannan ta zauna, Amrah ta sauko jiki ba kuzari ta fara karyawa kamar bata so, cusawa kawai take yi amman ba don zuciyarta tana so ba sai don kawai abin cikinta dake ta damunta da motsi, da alama neman abinci yake yi, bayan ta k'are ne ta kalli Aunty tace, "Auncle fa ko har ya fita?" Aunty tace "Eh ya fita saboda akwai shari'ar da za'a yi yanzu da k'arfe tara."

Tace "OK " sannan taja bakinta ta tsuke saboda daman maganar ta k'arfin hali ce take yi, Aunty ta kalleta ta gyara zama sannan ta kira sunanta a hankali, Amrah tayi saurin d'ago kanta ta kalleta hawaye suka gangaro mata tareda wata fad'uwar gaba da ta diro mata ba shiri, a hankali tace, "N'aam Aunty"

Aunty ta sake kiran sunanta tace, "Wanene Nazir da naji kina ta fad'a jiya akan bazaki bashi yaronki ba?"

Amrah ta zaro ido a waje tace, "Nazir kuma?" Aunty ta had'e fuska sannan tace, "Eh shifa sannan ko Aunty Zuwaira ma naji ta fadeshi lokacin da kika fito gidan ALHAJI mai akwai, tana fad'ar kada ace Hak'k'inshi ne yake bibiyarku, ko dai da gaske shine Uban cikinki?don gaskiya na fara zargin kamar akwai lauje cikin nad'i a cikin lamarinki, saboda jiya banyi baccin kirki ba ina ta sak'awa da kwancewa akan wannan hargitsi da ya ratso cikin rayuwarki."

Amrah ta sauke k'atuwar ajiyar zuciya sannan tace, "Aunty tun ina budurwa na kame kaina ga kowane namiji, ballantana yanzu da nayi aure nikam me zai jani da har zanje in zubar da

mutuncina a waje, WALLAHI ni ba wani d'a namiji da ya tab'a sanina 'ya mace a duniya sai Malam, don ko Salis da muka yi soyayya sosai dashi WALLAHI ban tab'a bashi damar da zai kai jikina ba balle wani cen don ALLAH Aunty ki yarda dani WALLAHI ni bansan komai ba akan wannan bak'in k'azafi da ake so ajefe ni dashi." ta fashe da kuka gwanin ban tausayi Aunty tayi shiru tana kallonta sai cen ta nisa tace, "To Nazir d'in fa miye had'inki dashi?."

Amrah zata yi magana kenan Text ya shigo wayarta, ta kai kallonta ga wayar dake gefenta ajiye ba shiri ta zaro ido da sauri ta d'auko ta k'ara duba text d'in, ba shiri tace, " na shiga Uku Aunty nikam meke shirin faruwa da rayuwata ne?" Ta fashe da wani kuka mai tsanani Aunty ta d'auko wayar ta duba itama sai gashi ta zaro ido saboda ganin abunda aka rubuta,

A ranar da kika haifu a ranar zan zo karb'ar yarona

Aunty tayi saurin dealing d'in numbar aiko har ta tsinke ba'a d'auka ba, bata hak'ura ba ta sake kira aikuwa sai gashi an d'aga, kafin ma Aunty tayi magana sai ya rigata da cewa, "Ki shiryawa zuwana a duk ranar da kika haifu don bana buk'atar shayarwarki ga yarona." kit ya kashe wayar a cikin tashin hankali Auntyn ta sake kiranshi sai gashi taji wayar a switch up, ba shiri ta aza hannu aka tace

"Wannan wane irin kalar bala'i ne yake so ya ruguzo muna ni Asabe?"

Itama sai ga hawaye shaaaa a cikin kuka kalli Amrah tace, "Ki fad'a mani gaskiya Amrah bana son shiga cikin lamarin da ba gaskiya."

Amrah zata yi magana sai ga Muryar Malam Nura yana sallama a waje, da sauri Aunty taja hijabinta ta fita yanayin da taganshi yasa gabanta ya fad'i, da sauri tace "Kayi hak'uri malam Nura Insha Allahu za'a yi bincike komai zai zo da sauk'i."

Malam Nura ba tareda yace da ita k'anzil ba ya mik'a mata wata envelope babba ta zura hannu ta karb'a a cikin mamaki ta bud'a envelope d'in domin taga abunda ke ciki, ta zaro photunan da tagani da yawansu zai kai guda goma, dubawar farko da zata yi idanuwanta suka yi tozali da Amrah zigidir rungume da wani wanda fuskarshi bata fito ba amman shi da guntun wandonshi, Aunty bata k'ara tsayawa duba sauran ba jikinta yana rawa ta koma cikin gidan gadangada tayi kan Amrah da duka tana kuka ta watsa mata photunan duka a jiki.

K'irnjin Amrah ya buda dam! dam! Don ita dukan ma bata jinshi saboda bak'in cikin da ke cikin zuciyarta yafi dukan zafi, tabi photunan da kallo d'aya bayan d'aya da suka tarwatse a tsakiyar falon, ta zura hannu ta d'auki wani dake saman cinyarta tana kai idanuwanta ba shiri ta tashi tsaye, saboda abunda ta gani wanda yake so ya saka zuciyarta barazanar tarwatsewa, photonta ne tareda wani hannuwanshi rik'e da breast d'inta duka biyu.

Akafta😢

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

PAGE 17

****

Ba shiri ta fasa wata k'atuwar k'ara tace,

"ALLAH ka d'auki raina in huta da wad'annan musibu da suka dabaibaye rayuwa, ko'ina na dafa ba sauk'i sai tarin k'alubale mai hana kwakwalwa da ruhi zama lafiya."

Aunty Asabe ta je ta shigo da Malam Nura da yake tsaye inda ta barshi har lokacin, saboda gaba d'aya jikinshi ya mutu murus ya kasa motsa ko d'an yatsanshi, musamman da yaji kalaman da Amrah take furzowa,daga inda yake yana jin sautinta zuciyarshi ta tabbatar masa da akwai wani k'ulli a cikin rayuwar Amrah, wadda itace yanzu ta bibiye aurensu domin cikar bak'in nufin da tun farko ake ta so a cika akanta.

Idonshi akan Amrah har ya zauna zuciyarsh cike da tausayinta, saboda izuwa yanzu ya tabbatarwa zuciyarshi Amrah bata da masaniya akan lamarin, saboda kalaman da yaji suna fita abakinta.

Aunty ta zauna tareda yin tagumi daga ita har Malam kallon Amrah sukeyi gwanin ban tausayi,

hankali a tashe suka yo kanta saboda dukan cikin da ta fara yi a haukace, tana sanbatun bata son cikin gara ma ta mutu kowa ma ya huta, daga Auntyn har malam hankalinsu ya k'ara tashi sosai saboda yanda suka ga ta rikice masu, Aunty ta rik'ota tareda mik'ar da ita tsaye da nufin ta hau kan kujera, aiko sai ga wani jini sun gani da yake biyar k'afafunta, Aunty ta fasa k'ara tace

"Wayyo ALLAH ka kawo muna agaji."

Malam a rud'e ya rungumota jikinshi ya rasa ma me ya dace yayi, Aunty dake rik'e da hannunta tace dashi, "Je yi sauri kazo muna da abun hawa mu kaita asibiti."

Aiko a d'ari ya fice har hularshi ta fad'i amman ko waiwayowa baiyi ba, Amrah ko sai murd'e murd'e take yi saboda azababben ciyon da mararta yake yi, Aunty sai faman sannu take mata, minti biyar a tsakani sai ga Malam ya dawo da Napep d'in, cikin azama Aunty ta d'auko hijabi ta sakawa Amrah itama ta saka nata suka rik'ata suka fito da ita, har sai da suka shiga napep d'in Aunty ta tuno bata d'auko kud'i ba, dole ta fito ta koma cikin gidan ta d'auko sannan suka tafi.

Koda suka je asibitin basu sha wata wahalar jira ba saboda jinin da ke ta zuba jikinta ya tsorata mutane da yawa, direct aka wuce da ita emergency tareda yimata taimakon gaggawa, sannan wani likita ya fito da sauri ya cewa su Aunty, ana buk'atar jini gora biyu da za'a saka mata da gaggawa saboda ceto ranta da abunda ke cikinta, hankalinsu ya k'ara tashi daga Malam har Aunty suka ce agwada jininsu aga in zai yi, aiko koda aka gwada gaba d'aya ba wanda yayi daidai da nata, kasancewar ita amrah jininta Group O nagetive ne ba kowane jini ne ke yi mata ba, hankali a tashe Malam da Aunty suka rok'i alfarmar zasu je su samo mutane a gwada aga in za'a dace, Malam ya nufi makaranta Aunty tayi gidansu Amrah wurin Zuwaira.

Yanayin da Zuwaira taga Aunty ta shigo ne yasa ta adana makaman rashin mutuncinta, saboda hankalinta ya tashi sosai taji tsoron ace mata Amrah ce ta mutu, don tun lokacin da aka ce mata Amrah tazo bata nan, k'annen Amrah'r suke fad'a mata yanda ta rame ta lalace taji jikinta yayi sanyi, kullum tana son tasa 'yarta a ido amman tuno yanda aka nuna mata fin k'arfi akanta aka nuna mata bata isa da ita ba, shiyasa ta k'i zuwa kuma tak'i barin k'annenta su tafi.

Aunty hankali a tashe take sanar da Zuwaira Amrah tana asibiti jini ya tsinke mata ana neman jinin da za'a saka mata da gaggawa, Zuwaira ta aza hannu aka tace

"Wayyo ALLAH Nazir ga ranarka tazo gashi kuma kayi muna nisa."

Aunty ta k'urawa Zuwaira ido saboda duk da tashin hankalin da take ciki, sunan Nazir da, zuwaira ta fad'a yasa ta tuno da abunda yake faruwa da Amrah sannan tareda mafalikin da tayi tana ta kiran sunan Nazir, a cikin rawar baki Auntyn tace "Wanene Nazir?" Zuwaira ta fashe da wani irin kuka ta jawo hijabi cikin rud'u har ta kai bakin k'ofar fita Aunty cike da mamaki tace da ita , "Ina zaki je kuma?" Hawaye suna zuba akan fuskar Zuwaira tace, "Zanje in taho da Nazir don shine kad'ai wanda zai iya bata jini wanda zai yi daidai da nata, don in za'a

tara mutane ashirin dak'yar za'a sami mai daidai da jininta."

Aunty jikinta yana rawa tace, "Muje to ai daga cen sai mu wuce." suka fita hankali tashe suka tari Napep kai tsaye tsohuwar unguwar da su Zuwaira suka taso suka nufa, basu zame ko'ina ba sai k'ofar wani gida wanda tun kafin su k'arasa suka hango k'aton kwadon dake sagale a kofar gidan, Zuwaira ta d'ora hannu aka tareda fashewa da wani sabon kuka tace

"Na shiga Uku ni Zuwaira ina suka shiga?"

Suna nan tsaye suna nazarin mafita Aunty tace, " Ko mu shiga wannan gidan muji inda suka tafi" Zuwaira ta kalli gidan tayi mere tareda yamutsa fuska tace, "Munafukai ne a gidan bana shiga kizo dai mu tafi muga yanda za'ayi asami jinin tunda basa nan."

Aunty ta kalleta ta kalli gidan zuciyarta ta bata ta shiga kawai akwai wani abu ak'asa, kai tsaye ta tunkari gidan da zuciya d'aya don bata yarda da maganar Zuwaira ba, aiko da sallamarta ta shiga gidan wata 'yar dattijuwa zaune akan kujera 'yar tsugunno gindin murhu tana suyar kosai, sai da ta gyara itacen da suke ta hayaki sannan ta d'ago kanta ta kalli Aunty tareda amsa mata sallamarta, Aunty ta k'araso tace

"Sannu Inna" dattijuwar tace "Yawwa 'yarnan k'osan kika zo siya na nawa za'a baki?" Aunty tayi D'an murmushi sannan tace, "A'a inna tambaya nike yi gidansu Nazir nazo naga kuma gidan dantse da kwad'o, shine nace b'ari na shigo nan na tambaya ko kinsan inda suka je, saboda Nazir d'in nike nema afujajan don ALLAH kinsan inda zanje in same shi?"

'yar tsohuwa tayi sagale tana kallon Auntyn baki a sake tace, "Cabd'i jam ai tsawon shekara d'aya gidan ba kowa a ciki, Nazir kam tun ranar da yazo da dillalai aka siye gidan ko labarinshi bamu sake ji ba."

Aunty tayi shiru na minti biyu sannan tace

"To yayi Inna nagode" har ta juya zata fara tafiya ne innar tace,

"Tsaya 'yarnan ga k'osan kisa man albarka"

Aunty ta juyo tace

"A'a nagode Inna ALLAH ya bada lada ya k'ara bud'a kasuwa"

Cikin jin dad'i inna tace "Ameen Amee 'yarnan ki sauka lafiya"

Aunty ta fito zuciyarta sai maida zancen 'yar tsohuwar take aranta, koda tazo Zuwaira ta fara masifa akan taje tayi zamanta, Aunty cikin sanyin jiki tace

"Shekara d'aya gidansu Nazir a rufe ba kowa asali ma yanzu ba gidansu bane sun sayar da shi."

Zuwaira ta zaro ido tareda yin fifita da hijabinta sannan ta fara rafka salati tana nanatawa, Aunty tace "Yanzu miye mafita? saboda WALLAHI buk'ace ake da asaka mata jinin."

Zuwaira ta k'ara rud'ewa tace, "Eh muje asibitin ai baza'a rasa na siyarwa ba sai mu saya."

Aunty tayi shiru bata ce komi ba har suka je asibitin, koda suka je har Malam ya rigasu isa tareda manyan dalibanshi su biyar da yazo da su da nufin agwada aga in jininsi zai yi,suna nan tsaye cirko cirko sai ga likitan ya fito ya kalli su Malam yace, "Alhmdllh jinin Mijinta yayi daidai an diba har an mak'ala mata."

A cikin rashin fahimtar zancenshi Aunty tace,

"An sami jinin kenan?"

Likitan yace "Eh an samu ku kwantar da hankalinku, saboda yana zuwa aka d'auki jinin ba b'ata lokaci muka saka mata."

Malam cikin tantama yace, "Wanene ya bada jinin"

Likitan cikin kaguwa da tambaye tambayensu yace

"Mijinta mana ko baka Ji nace shi ya bada jinin ba?"

Dukansu suka zaro ido, Malam bakinshi yana rawa yace, "Nine fa Mijinta likita kuma ai ka gwada nawa jinin kace ba zai ba." Likitan ya maka masa harara yace.

"To bayan tafiyarku kai da wannan matar da kuka kawota tare, sai ga wani yazo yace muna shine mijinta a gwada jininshi aga in zaiyi, aka yi sa'a ana gwadawa yayi muka dibi gora d'aya a jikinshi aka saka mata"

Malam cikin rud'ewa ya cakumo wuyan likitan yace, "Sai ka gaya man Jinin wa ka d'iba ka sakawa matata?"

Tofa 🤔🤔🤔

Akafta😣

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

ASHE ZUMA KAMA TAKE YI DA K'UDA 🤔BAKAN GIZO shine yake shanye ruwa😳

PAGE 18

****

Aiko ganin hakan yasa D'aliban Malam suka yo kanshi suna bashi hak'uri tareda b'anb'are hannunshi daga cakumar da yayiwa Likitan, a cikin fushi likitan yace

"WALLAHI da nasan abunda zakuyi man kenan da ban saka hannuna cikin lamarinku ba, amman bakomai ko yanzu sai ku nemi wanda zai tsaya maku akan case d'inta."

Aiko da sauri ya bar wurin ranshi a b'ace Aunty tabi shi cikin tsananin rud'u tana bashi hak'uri, tafiya yake yi amman bata daina biyar shi tana magiya da bashi hak'uri ba, har sai da ya tsaya tareda waigowa lokaci d'aya saboda raunin da zuciyarshi tayi da magiyar da yaga Auntyn tana yi masa, saboda maganganun da take fad'a wad'anda suka karya masa zuciya, inda take kuka tana cewa,

"Don girman ALLAH kada ka zare hannunka akan matsalarta kayi hak'uri kayi don ALLAH WALLAHI yarinyar tana cikin gararin rayuwa mai cike da tarin k'alubale wanda ita kanta da za'a barta ta mutu d'in da tafi kowa farin ciki da hakan, amman kuma mutuwarta ba shine maslahar kalubalen dake tattare da rayuwarta ba, kayi don ALLAH ka ceto rayuwar marainiya ALLAH zai baka lada, saboda ko mijinta da kaga yayi ma hakan baya cikin hayyacinshi shiyasa, ka auna

akanka ace hakan ta faru dakai ka kawo matarka asibiti kaje nemo wanda zai bada jini a saka mata koda ka dawo ace maka mijinta yazo an d'ibi nashi wani hali zaka tsintsi kanka?, saboda haka ina nemarwa Malam yafiya a wurinka saboda ya shiga rud'u ne bada gangan yayi ba."

Jikin likitan yayi sanyi zuciyarshi ta sauko daga dokin fushin da ya hau, cikin tausayawa Patient d'in yace, "OK badamuwa komi ya wuce yanzu mun samu an tsayar da jinin haka ma abunda ke cikin yana lafiya, kada ku damu wannan jinin da ake saka mata kuwa ya wadatar, sai dai zamu rubuta mata wasu magunguna da zata CI gaba da sha kafin lokacin haihuwarta, wad'anda zasu k'ara mata jinin da zai wadaci jikinta"

Cikin jin dad'i Aunty tace, "Mun gode likita ALLAH ya biyaka da gidan Aljannah."

Cikin jin dad'in adduarta yace "Ameen"

Har ya fara tafiya Aunty tace, "Zamu iya shiga mu ganta?"

Ya juyo yace, "Zaku shiga ga amman don ALLAH kada ku dameta da hayaniya."

Aunty tace. "Mungode sosai"

Sannan ta dawo inda su Malam suke zaune suna jiran suji yanda suka yi, kowanensu ido zuru zuru, Musamman Malam da a lokaci d'aya shima duk ya zabge saboda tashin hankali, koda tazo tayi masu bayani d'ii suka bi bayanta zuwa d'akin da ake kwantar da masu lalurar ciki, Zuwaira kam biye kawai take dasu zuciyarta cike da tsanar Malam,saboda kallon kaskancin da take masa wai ace shine mijin kyakkyawar 'yarta Amrah, ji take kamar ta shak'oshi tayi ta jibga, gefe d'aya kuma na zuciyarta tana ta sak'e sak'e akan cewar da aka YI mijinta ya bada jini, saboda atake yanke zuciyarta ta tabbatar mata da kowaye da wannan d'anyen aikin.

Koda suka shiga sun tarar da ita kwance sambal da tsinin cikinta, sai sharar bacci take yi sharkaf tana maida numfashi da sauri da sauri, saboda jinin da ake zuk'a mata yana bata reaction sosai.
Zuwaira tazo gefen kanta ta shafo fuskarta hawaye suna kwaranya a idonta, saboda tsananin tausayin 'yarta da rabon tasa ta a ido tun kafin aurenta, wanda yake cikin wata na takwas dai dai da watannin cikinta, amman tabi duk ta rame ta fita hayyacinta kamar wadda TAYI shekara tana jinya.

Malam kan tsaye kawai yake amman gaba d'aya zuciyarshi cike take da tunani kala kala, musamman abu biyu photunan da yagani sannan da zancen da likita yayi a yanzu, wai mijinta ya bada jini shin to wanene mijin bayan shi?, kodai cikin tsoffin mazanta ne da ta aura? in ko haka ne tabbas WALLAHI bazai tab'a zura ido aci masa dunduniya ba, dole ne ta zab'a ko shi ko kuma su don bazai tab'a zama da ita ba alhali tana kula mazan da ta aura baisani ba, yasa aranshi da taji sauk'i za'ayi wadda za'ayi don baza'a maida shi lusari ba.

Kukan Zuwaira gaba d'aya ya karad'e d'akin har sai da wasu nurse's suka shigo suka kora mutanen dake d'akin, sannan ta fito tana ta sharb'ar kuka Aunty tana lalashinta.

Kwanan Amrah uku asibitin ta d'an ji sauk'i amman kallo d'aya idan anyi mata za'a gano tsantsar tashin hankalin da take ciki, saboda tsawon wad'annan kwanakin gaba d'aya tayi su ne a cikin kuka da tunani, wanda har aka k'ara auna jininta aka ga ya hau sosai, duk da fad'an da aka yi mata da jan kunne amman hakan bai hanata sake dilmiya a tunanin ba, don ita lafiya da rayuwar gaba d'aya sun fita kanta, Zuwaira ce ke kwana da ita amman Aunty kullum tare dasu take yini sai da dare maigidanta yazo ya d'auketa, dangin Babanta ma a kullum suna kan hanyar zuwa dubata, sati d'aya da tayi asibiti aka sallameta amman da sharad'in a daina d'aga mata hankali, saboda takatsantsan da lafiyarta da lafiyar abunda ke cikinta.

Ana sallamota kai tsaye Zuwaira ta wuce da ita gida lokacin Aunty da Malam basu riga suka tafi asibitin ba, saboda da safe ne aka yi sallamar amman abun mamaki koda taje tambayar bill d'insu aka ce da Zuwaira Mijinta ya biya kud'in, ba tareda dogon bincike ba suka tattaro kayansu suka yo gida.

Ita kanta Amrah bata da wani zab'i da ya wuce zuwa gidannasu, saboda yanda zuciyarta take a hirgitse sannan yanayin kallon da taga MALAM yana mata, zuciyarta ta tabbatar mata da cewa zarginta ya shiga zuciyarsh ya zauna, shiyasa bata ji ko d'ar ba da tafiyarta gidansu asali ma taimakonta aka yi, don ita gaba d'aya komai ma ya fita zuciyarta in son samu ne ta sami kad'aici tayi jinyar zuciyarta, shigarsu gidan keda wuya sai ga Aunty ta diro da kulolin abincinta, don taje asibitin aka ce mata an sallamosu kuma tana da tabbacin Zuwaira bazata kai Amrah gidan Malam ba, saboda kallon tsanar da tagani da idonta Zuwaira tana yiwa Malam, Zuwaira ta tarbeta ba yabo ba fallasa saboda fad'i tashin da Auntyn tayi dasu Asibitin yasa ta rage jin zafin Auntyn, akan abunda ya faru baya, Aunty tace da Zuwaira, "Ashe an sallamota daga asibitin cen na fito ai ake sanar dani anbata sallama."

Zuwaira tace "Eh yanzu muka shigo gidan muma" Aunty tayi murmushi tareda fad'ar "Alhmdllh." sannan ta ajiye kulolin tace, "Ina Amrah'r?" Zuwaira ta nuna tsohon d'akinta tace "tana ciki" Aunty ta nufi d'akin da sallamarta d'akin fess kamar lokacin da Amrah tana gidan, saboda Zuwaira tana kula dashi sosai don wani zubin ma a d'akin take kwana, shiyasa d'akin yake tsab tsab dashi ba abunda ya sauya.

Sallamar Aunty da Amrah tajiyo ne yasa tayi saurin share hawayenta, tayi k'ok'arin saita natsuwarta saboda fad'an da Autyn ke yimata akan yawan tunanin da take yi, saboda kariyar lafiyarta don an tabbatar masu da jininta ya hau sosai.

Aunty ta zauna idanunta akan Amrah atake ta gano kukan da tayi cikin damuwa ta kira sunanta, Amrah ta d'ago fuskarta ta kalleta nan take wasu sababbin hawaye suka gangaro mata, Aunty ranta ya k'ara jagulewa tayi saurin rik'o hannunta tareda share mata hawayen, a cikin wata murya mai cike da tausayi tace, "Ki natsu ki ajiye komi ki fuskanceni muyi magana ta fahimta, ada naso mu ajiye maganar har sai kin sauka amman ganin yanda kika d'aga hankalinki yasa

dole ne aci maganin matsalar, saboda tsoron abunda zai je ya dawo dangane da matsalolin da suke ta kunno kai, yanzu ina son ki sanar dani wanene Nazir? Miye alak'arki dashi?sannan wace dangantaka ce tsakaninku dashi a baya? Saboda ta wannan hanyar ce kawai zamu kamo kan matsalar" Amrah ta share hawayenta sannan tace, "Nazir mak'ocinmu ne acen unguwar da muka taso, akwai shak'uwa sosai tsakanina dashi, sai daga baya ne da idan yaga ina kula samari muka yi ta samun matsaloli dashi, saboda baya son ya ga ina fira da wani ko wani ya ganni yace yana sona idan muna tare dashi kasancewarshi abokina na kud da kud." Aunty tayi shiru na d'an lokaci sannan tace, "Saurayinki NE kenan shima?" Amrah tayi saurin girgiza KAI sannan tace "A'a gaskiya ba wata alak'ar soyayya da ta had'a ni dashi, sai dai shak'uwar da kika ji na fad'a kawai itace tsakaninmu" Aunty cikin mamaki tace da ita "kina nufin kice bai tab'a cewa yana sonki ba." ta d'aga kai tareda fad'in "Eh gaskiya sai dai yana tsananin kishina, don yasha fad'a da samari masu zuwa fira wurina,saboda ko Salis sunyi ta gwabzawa dashi kafin mu baro unguwar." cikin tsananin firgici Aunty tace, "Ko shakka babu lalle nazir shine BAKAN GIZOnki wanda yake ta shanye maki ruwa ba wani aljani da yake tare dake sai shi."

Sai ga Zuwaira ta fad'o d'akin kamar anjefota saboda daman cen kunnuwanta kaf ta baje su ne wajen sauraren firar tasu jikinta yana rawa tace,

"Yanzu kina nufin duk wannan bala'in da muka shiga Nazir ne sanadi?."

Aunty ta girgiza kai tareda cewa, "ban fa tabbatar ba amman zuciyata shi take zargi, zargi kuma ba gaskiya bane, abu d'aya ya dace muyi yanzu shine mu binciko duk inda Nazir d'in yake, saboda akwai abunda muka b'oye maki bamu sanar dake ba, wanda ya zama dole sai mun nemo Nazir koda ALLAH zai sa hakan ya zamo SILAR samun maslahar matsalolin"

Zuwaira takai zaune ba shiri tareda cewa "Meke faruwa sabo kuma bayan abunda na riga nasani abaya?"

Amrah ta fashe da kuka Aunty ta kalleta cikin tausayi tareda sauke ajiyar zuciya tace, "Wannan cikin dake jikin Amrah wani yayi ik'irarin cewa ba cikin Malam Nura bane nasa ne?"

A zabure Zuwairar ta Mik'e tareda dafe k'irji tace, "Kan Uba wato NI Nazir zai ciwa Amana, waton duk gargad'iin da nayi masa akan Amrah baiji ba har saida ya k'unsa muna bak'in ciki akan wani banzan tunaninshi na k'arya?wallahi sai yasan dani yake zance matuk'ar bai fita sha'anin 'yata ba."
A cikin Mamaki Aunty tabi Zuwaira da kallo hanci da baki, saboda kalamanta sun tabbatar mata da lalle zarginta yazama gaskiya cewa Nazir ne BAKAN GIZOn Amrah, sannan kalaman zuwaira sun tabbatar da cewa akwai wata ak'asa tsakaninsu da Nazir, wanda Zuwairar ce kad'ai zata iya warware masu komi.

Shiyasa ta kalli Zuwairar tace, "Aunty ki fad'a mani gaskiyar abunda ke tsakaninku da Nazir."

Zuwaira ta zauna tareda fashewa da kuka, tana fad'in

"Nazir haka zaka yimuna? ina soyayayr da kace kana yiwa Amrah?haka ake so WALLAHI ALLAH ya isa tsakaninmu da kai kuma idan har hakan ta kasance da gaske kai kayiwa Amrah cikin WALLAHI sai mun durk'usa da kai agaban kuliya."

Aunty tace. "Bayani zakiyi domin musan inda zamu dosa"
Zuwaira tana kuka tace, "Me zan fad'a maki bayan wanda Amrah ta fad'a yanzu? abu d'aya ne nasani wanda naji bata fad'a ba shine tabbas Nazir yana sonta tun tana 'yar k'arama, sannan yayi ta burgar cewa wai ita d'in matarsa ce, to yaya ta zamo matar bayan nida mahaifinta duk bamu sani ba?haka nashi uwayen ba wanda yasan da wannan zance, ita kanta ma bata da masaniya akan hakan, to taya zamu yarda da renin Hankalinshi?."

Ruguntsumi🤔

Akafta 👌

D/Auta ce👍

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

****

Aunty Asabe jikinta yayi sanyi k'alau sannan tayi jarumtar fad'in, " anya ko Nazir Mutum ne kuwa? Nifa wannan lamarin ya rikice man kwakwalwa."

Zuwaira ta sauke ajiyar zuciya sannan tace, "Mutum ne kamar kowa nasan Mamarshi da babanshi da kanwarshi duk, saboda munyi makotaka dasu haka ma munyi zaman lafiya dasu kafin rashin jituwa ta kunno kai tsakanimmu"

Aunty tayi saurin fad'in "Rashin jituwa kamar yaya? Fad'a kuka yi dasu halan?"

Zuwaira tace, "Ba wani fad'a kawai dai rashin fahimta ce ta shiga shiyasa mutanen unguwar suka sako ni agaba, sai gashi ALLAH ya kawo muna Salis ya bamu wannan gidan muka dawo, tun daga lokacin ban koma jin labarinsu ba, saboda ban koma zuwa unguwar ba sai ranar da muka je dake"

Aunty ta kalli Amrah tace, "To ke kina nufin duk zaman da kukayi dashi baki san yana sonki ba?"
Amrah tana sharar hawaye tace. "Nidai WALLAHI bai tab'a cewa dani yana sona ba, sai dai kullum yayita fad'a da samarina, yana cewa wai ni matarshi ce"

Suna cikin firar ne sai ga Abba k'anen Amrah ya shigo yace ga Malam Nura cen k'ofar gida, nan take Zuwaira tayi kicin kucin da rai tareda mik'ewa tsaye ta bar masu d'akin, Aunty Asabe tace, "ka shigo dashi" ya fice d'an lokaci tsakani sai gashi ya shigo tareda Malam d'in, kai tsaye d'akin Amrah ya shiga suka fara gaisawa da Aunty tareda tambayar jikin Amrah, sannan Aunty ta fice ta barsu Malam ya kalli Amrah fuska ba walwala yace,

"Nazo ne domin inji abunda yake tsakaninki da wanda ya baki jini, saboda ni gaskiya bana lamuntar abunda ake so ayiman, ke matata ce aurenki nike banga abunda zai had'aki huld'a da wani mijin da kika fito gidanshi ba, wannan ya zama na farko ya zama na k'arshe idan hakan ta koma faruwa gaskiya zan d'auki mataki."

Amrah tun lokacin da ya fara magana ta fara kuka, saboda daman cen Kukan a kusa yake shiyasa yana kai k'arshen zancenshi ta fashe da wani kuka mai sauti tana fad'in,

"ALLAH ka amshi raina in huta nagaji da wannan bak'in ciki da kullum safiya da sabon salon da yake zo man" aiko sai ga Zuwaira tsidik kamar an jefota jikinta yana rawa ta kalli Malam tace, "Kayi gaggawar bata takardar sakinta don WALLAHI kaji na rantse bazata koma gidanka ba."

Ta k'are maganar a cikin d'aga murya Aunty ta shigo d'akin ranta a b'ace tace

"Haba Aunty Zuwaira wannan fa ba shine maslaha ba, ki bari abi abun a hankali har aga wannan matsalar ta kau, don wannan k'alubale da muke ciki har yanzu babu wanda yasan matsayin auren, har sai komi ya bayyana gaskiya ta fito sannan ne za'a san matakin da za'a d'auka, don haka kima bar zancen wani saki don ba shine agabanmu ba yanzu" Zuwaira tana

hararar Malam tace,

"Nidai yanzu shine agabana idan ya sauwak'e mata zanfi jin dad'in tunkarar matsalar dake gabanmu." Malam ya mik'e ranshi a b'ace ya fito d'akin, Aunty tace dashi "Kayi hak'uri don ALLAH kayiwa Amrah Uzuri saboda ita kanta bata san komi akai ba, don haka mu ajiye komi zuwa lokacin da ta sauka, insha ALLAH komi zai fito kuma gaskiya zata yi halinta"

Dak'yar ya bud'a baki yace, " Bakomi ta zauna gidan har zuwa lokacin da zata haihun" yana k'are maganar ya saka kai ya fice, Zuwaira ta bishi da cewa. "Ko k'arshen rayuwarta kace ta zauna ai gidansu ne kuma mallakinta, huta da hurar hanci ba uban da zaisa ta koma wannan tsinannen gidan naka." cikin b'acin rai Aunty tace

"Gaskiya abunda kikeyi kwatakwata bakya kyautawa Aunty Zuwaira, haba ina laifinshi WALLAHI Malam ya ma yi k'ok'ari da ya tsaya iya haka, wanda na tabbata son da yake yiwa Amrah'r ne yasa bai d'auki wani kwakkwaran mataki akan hakan ba, saboda ba kowa ne zai iya jurar wannan kayan takaicin ba, yanzu abu d'aya ya rage mu gano inda Nazir d'in yake koda ta hanyar abokansh ne."

Zuwaira tana kallonta tana mere har ta k'are maganar sannan tace

"Don ALLAH kice yayi mata saki dubu in anayi." Aunty Asabe ta janyo hijabinta ta saka sannan tace da Amrah, "Ni zan tafi sai kuma na koma dawowa, duk abunda kikaji kina sha'awa ki kirani a waya ki sanar dani, koda banzo ba zan aiko maki ALLAH ya baki lafiya."

Amrah tace Ameeñ cikin zuciya saboda kukan da take yi, Aunty taje ta had'o kan kulolinta ta jibga a wata k'atuwar leda sannan tace da Zuwaira, "Ni na tafi sai kuma na sake juyowa" har ta kai k'ofa sannan Zuwaira tace, "Sauka lafiya" ba tareda tace da ita k'anzil ba ta fice zuciyarta cike da haushin Zuwaira, a gefe d'aya kuma tausayin Amrah da Malam tareda d'an tayin cikinta da zai fad'o duniya cikin ruguntsumin rayuwa.

Bayan fitar Aunty Zuwaira inda take shiga ba anan take fita ba, sai ruwan bala'i take saukewa Malam da Aurenshi, Amrah dai sai sharb'ar hawaye take yi saboda izuwa lokacin zuciyarta har ta saba da bak'in ciki.

Bayan kwana uku da wannan rikici Aunty ta bazama neman Nazir ruwa k'ok'o, koda ALLAH zaisa ta sami wanda zai san inda zata sameshi, don ko gidan Dattijuwar nan mai kosai tayi maya biyu, domin kawai taji wani information game da Nazir amma ba wata nasara, dole ta hak'ura ta zubawa sarautar ALLAH ido, saboda Numbar ma da ya kira Amrah da ita tayi ta kira kullum magana d'aya ce ake cewa waton a kashe take.

Watan cikin Amrah tara cikin na goma ta fara nak'uda, ba shiri Zuwaira ta kinkimeta zuwa Asibiti, tasha wuya sosai kafin ta sanbalo yaronta k'atoto fari jajir masha ALLAH, son kowa k'in wanda ya rasa mai kama da Amrah sak, Zuwaira duk da bata son Malam amman wannan

yaron taji k'aunarshi har cikin ranta, Aunty ko hana kowa ya d'auke shi tayi tana nanuke dashi, Amrah kam duk da taji dad'in ganin yaron, amman kasanceawar ruguntsumin da rayuwarta take a ciki yasa bata wani farin ciki.

Kasancewar haihuwar dare ce tayi akace sai da safe za'a sallameta saboda ta jigatu sosai kafin ta haihu, Aunty Asabe tayi gida Zuwaira ta kwana da Amrah, cikin dare yaron yana ta kuka likitoci suka ce Amrah ta bashi Nono, tana kukan bak'in cikin shayar da yaron da ba'a san wanene tantagaryar ubanshi ba, ta ciro nono ta fara bashi aiko ya karb'e kamar daman cen ya saba sha, zumui zumui yana tsotsa Amrah da zugin bak'in ciki ke ratsa zuciyarta, ta fashe da kuka tareda janye nonon aiko yaro ya k'ara fasa k'ara, Zuwaira ta rufeta da fad'a dole ta maida masa yayi ta tsotso har yayi bacci, sannan aka ajiye mata shi akan gadon, itama ta kwanta, sannan ne kowa hankalinshi ya kwanta Zuwaira ma ta d'an kishingida akan kujera, Amrah kam daman wani masifaffen kwana ne a idonta tana kwantawa sai bacci.

Da misalin k'arfe hud'u na asuba kukan jaririn ya tayar dasu, a firgice dukansu suka falka tareda waigen ta ina kukan jaririn yake fita, abun mamaki ashe wani jaririn ne da ke kusa da gadonsu, wanda shima sabuwar haihuwa ne amman basu ga nasu jaririn ba, cikin fad'uwar gaba Amrah tace

"Mama ina yaron?"

Zuwaira ta zabura da k'arfi cikin tsananin gigita tace, "Nan fa yake kwance kusa dake, kina bacci ma ya falko NA bashi ruwa ya koma baccin, sannan nima na k'ara gincirawa, kodai Nurses sun tafi dashi suyi masa allura ko wani abun?"

Ba shiri Amrah ta fashe da KUKA jikinta yana tsuma saboda tashin hankali tace.

"WALLAHI d'aukesa aka YI Mama daman yace ranar da na haifu a ranar zai karb'i danshi."

To fa wata sabuwa 😱

Akafta😆

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

Kuyi hkr dani don ALLAH WALLAHI nayi busy da yawa kwanan nan am very sorry my fan's 🙏🏻

PAGE 20

****

A cikin fad'uwar gaba Zuwaira tace, "Wanene?" Amrah ta k'ara fashewa da wani kukan tace, "Wanda yace cikin nasa ne."

Ta k'are maganar cikin tsananin kuka, a zabure Zuwaira ta fito d'akin tana kururuwar an sace mata jika, kafin kace me asibitin gaba d'aya ta d'auka anyi satar jariri sabuwar Haifuwa, aka bazama bincike lungu da sak'on na asibiti amman ba wani alamu da zai nuna ma akwai wani mara gaskiya a cikin asibitin balle asami b'arawon jarirai.

Ganin yanda hankulan Amrah da Zuwaira ya tashi yasa wata mata da itama haihuwar tayi, ta zo jikin gadon Amrah cike da tausayi tace, "WALLAHI ni naga fuskar wanda ya d'auki yaronnan da idanuwana, saboda lokacin kwanciyata kenan bayan na k'are baiwa jaririyata nono, sai gashi ya shigo d'akin ganin mutum a gadonki yasa na dallare masa fitilar dake hannuna a fuska, bai damu da hasken fitilar ba haka ma bai fasa d'aukar yaron ba, na yunk'uro da k'arfi da nufin in zo in hanashi d'aukar yaron ne tawa jaririyar ta falko tana ta kuka, dole na d'aukota sannan na nufo shi yana gaf da fita d'akin rungume da jaririn, na ciyo kwalarshi ta baya ba shiri ya k'wace daga rik'on da nayi masa, sannan ya juyo muna kallon juna ido cikin ido yace dani, kada in koma yin gangancin tab'a shi ko inyi kuwwa, don zai iya halakar dani da 'yar jinjirata akan a hanashi d'aukar danshi,na bishi da kallo cike da tsoro tareda k'ara mak'ale 'yata a jikina, har yasa kai zai fita sannan ya juyo yace dani idan an tambayi ina yaron ince daku Babanshi ne yazo ya tafi dashi, idan kun tambayi sunanshi in ce maku NAZIR."

Ba shiri Amrah ta cakumo matar cikin zafin nama, ta d'aga murya kamar wata zararra tace,

"WALLAHI sai kin biyani yarona, kije ki karb'o man yarona."

Dak'yar aka b'anb'ari hannun Amrah daga shak'ar da tayiwa matar, ta haukace mata sosai akan sai ta nemo mata yaronta,
tana maganar cikin k'araji sannan ta zube k'asa a some, da gudu likitoci suka yo kanta zuciyoyinsu cike da tausayinta, tareda fargabar kada ace zuciyarta ta buga saboda bak'in cikin rasa yaronta, don daman cen bincikensu ya gano zuciyar tana gaf da bugawa, saboda jininta ya haye sosai da sosai komai zai iya faruwa da ita matuk'ar ba'a daina b'ata mata rai ba.

Da gudu aka fara bata taimakon gaggawa Zuwaira kam tana cen ana bulayin neman jariri, bata ma san abunda yake faruwa ba saboda an baza 'yan sanda a asibitin sai bincike ake yi, dak'yar aka yi nasarar dawo da numfashinta dake tafiya da sauri da sauri, sannan likitocin suka rage fargaban da suke yi don rayuwarta tana cikin k'ila wa Kala, bayan anyi mata alluran bacci ne sannan likitocin suka watse, sai wanda ke kula da komi nata ne ya tsaya yana k'are mata kallo cike da tausayi, saboda ganin yarinya k'arama da ita ta shiga gararin rayuwa irin haka, yana k'ok'arin barin wajen ne yaga wata farar takarda a k'asa ya duk'a ya d'auko tareda bud'ewa a lokaci d'aya, aikuwa sai gashi yaga abunda ya shalle tunaninshi, domin kuwa abunda ke cikin takardar ya nuna lalle wanda ya d'auki yaron na gida ne, domin kuwa ga abunda ya fad'a,

"Na d'auki yarona idan har kuna son na maido shi taci gaba da shayar dashi sai in kun bani matata, kun walwale aure kan auren da kuka yi mata ko don ragewa kanku girman zunubin da kuke d'aukarwa kanku."
NAZIR

Cikin d'aurewar kai likitan ya k'ara jujjuya takaradar kamar wanda yake neman wani k'arin bayani daga takardar, cikin sanyin jiki ya saka takardar aljihu sannan yakai kallonshi ga kyakkyawar fuskarta, da ta rame tayi fari fayau saboda ciyo damuwa ga kuma fargaba tareda jigatuwar haihuwa, haka kawai yaji yana buk'atar jin ainahin labarinta da abunda ke faruwa ga rayuwarta, cike da tausayinta ya fito d'akin ya nufi Office d'inshi, sai maimaita zancen dake cikin takardar yake yi a ranshi.

Zuwaira kam har gari yayi haske tana cen tareda 'yan sandan suna bincike, sai ga Likitan nan yazo ya jawo wani d'an sanda d'aya tareda yi masa bayanin cewa case d'in na gida ne, saboda uban yaron ne ya d'auki danshi za'a bi abun a hankali a karb'o yaron, amman idan har hakan bata samu ba dole ne a nemo su su shigo cikin lamarin, sannan suka tafi ya juyo kan Zuwaira ya fara bata hak'uri saboda yanda yaga duk ta firgice kamar wata sabuwar Mahaukaciya saboda b'atan jikanta.

Zuwaira kam bata ma gane abunda yake fad'a saboda firgicin da take ciki, don Zuciyarta tana ta canki in cankar waye wanda yayi wannan k'arfin halin raba yaro da mamanshi?.

Dak'yar ya shawo kanta ta hak'ura ta koma inda Amrah'r take domin taga a wane hali take, aiko

ganinta kwance sambal tareda oxygen d'in dake taimakonta wajen zuko numfashi, ba shiri ta fashe da kukan tausayin 'yarta mutane sai lallashinta suke yi suna bata hak'uri.

K'arfe takwas dam Aunty ta shigo d'akin fuskarta cike da fara'a ganin halin da ta tarar da Amrah a ciki yasa tayi turus, sannan ga Zuwaira zaune a gefenta tanata kuka gwanin ban tausayi, Aunty takarasa wurinsu jiki ba kuzari tace, "Ina yaron?"

Zuwaira tana ganin Auntyn taji wani sabon kuka yazo mata cikin muryar kuka tace, "Asabe an sace jaririn." ba shiri Aunty gabanta ya k'ire ya fad'i jiki ba kuzari ta dafa k'arfen gadon tace, "Ta yaya hakan ta faru?"

Daga nan Zuwairar ta fara yimata bayani cikin kuka,tana cikin fad'a mata sai ga likitan ya shigo d'akin yace dasu su zo akwai maganar da zai yi da su, suka biyo bayanshi har office d'inshi suka zazzauna, sannan ya kalli Aunty yace

"Wanene Nazir?"

Dukansu suka zaro ido cike da mamaki suka had'a baki wajen fad'in "kasan shi ne?" yayi d'an murmushi don rage masu firgicin da ya gani kwance ga fuskokinsu sannan yace, "bansanshi ba hasali ma ni tambayarku ce nike yi saboda yaronku yana hannunshi, gaba d'aya suka zabura Zuwaira tayi hanyar fita office d'in kamar wata mahaukaciya, Likitan yayi saurin shawo gabanta yace, "Banso shiga cikin lamarin ba amman duba da yanda yarinyar rayuwarta take cikin had'ari, sannan ku gaku hankalinku yayi tsananin tashi shiyasa na shiga, da zummar ALLAH yasa shiga ta cikin lamarin koda za'a sami sassaucin matsalolin da yarinyar take fuskanta." Zuwaira jikinta sai tsuma yake akan ta fita taje ta d'ebowa Nazir 'yan sanda akawo mata jikanta, Aunty tayi k'arfin halin rik'ota a rikice tareda tambayar Likitan ya aka yi yasan shine ya d'auke yaron?, kai tsaye ya fiddo takardar ya mik'a mata sannan yayi masu bayanin yanda aka yi ya sameta, jikinta yana rawa ta karb'a ta karanta sannan ta d'ago cikin tsananin firgici ta kalli likitan tace, "Ko zaka iya gane wanda yazo ka d'ibi jininshi ka saka mata watannin baya har yace ita d'in matarshi ce?" Likitan yayi shiru na d'an lokaci sannan yace a gaskiya idan har na ganshi zan gane shi, sai dai kai tsaye bazan kawo fuskarshi ba, waton dai a takaice shine Nazir kenan?"

Aunty tace "Eh shine don ALLAH taimako d'aya muke so kayi muna" likitan yace "kamar me fa?"

Tace "ka kula muna da Amrah mu zamu je mu binciko duk inda Nazir d'in yake" yayi saurin fad'in "kada ki damu wannan ba damuwa bane sai dai naso in baku wata 'yar shawara dafatar baza ku ga nayi maku katsalandan ba?" Zuwaira cike jin zafin da zuciyarta take yi tace, "Fad'i kanka a tsaye Likita don na matsu inga inda zan sami wannan d'an tsinannen Nazir d'in, WALLAHI idona idonshi koni ko shi tunda har rashin mutuncinshi yayi k'amari har haka."

Likitan ya sauke ajiyar zuciya sannan yace, "Idan har da gaske matarshi ce kamar yanda ya

fad'a don ALLAH ku bashi matarshi, ko don ragewa wannan yarinyar kaso mafi rinjaye na damuwarta, saboda WALLAHI rayuwarta unconscious take matuk'ar ba'a rage mata lodin bak'in cikin dake damun Zuciyarta ba, komi kuke ji kuyi hak'uri ku maidata gidan Mijinta don ALLAH ." ya k'are maganar cike da tausayin Amrah Kai tsaye Zuwaira tace, "Iskanci ne kawai da ya cika masa ciki don ubanshi sai yasan dani yake zancen."

Fuu ta fice office d'in bayan ta gama maganganunta masu k'arawa zuciyarta zafi, saboda tsananin renin hankalin da Nazir d'in yayi masu, Aunty ma ta biyota a baya da sauri bayan ta k'ara jaddadawa Likitan ya kula masu da Amrah'r kafin su dawo, sannan ta tarar da Zuwaira dake ta sauri kamar ta kifa, suka sami Napep suka shiga kai tsaye Zuwaira tace suje police station, Aunty tayi saurin fad'in "A'a Aunty muje dai Unguwar tasu koda ALLAH zaisa mu sami wanda yasan inda zamu sameshi, saboda koda mun d'ebo 'yansandan ai bamu san inda zamu je su kamoshi ba" Zuwaira tayi shiru tana nazirin irin hukuncin da zata d'auka mummuna ga Nazir d'in, wanda zai ji tsoron k'ara kusantosu ma balle ya sake shiga rayuwar 'yarta.

Har suka kai Unguwar ba wanda yace k'anzil kafin su kai gidan sai ga kira ya shigo wayar Aunty da wata bak'uwar Number, har taso ta share sai kuma ta canza tunani ta d'aga ba tareda tace komi ba taji ance,

"Nazir ne"

A zabure tace da mai Napep tsaya tsaya malam sannan tace,
"Nazir kace?" yace "Eh shine dafatar kunga sak'on da na ajiye maku saboda bana son kusha wahalar neman wanda ya d'auki yaro, to yaro yana hannuna saboda nine Ubanshi, idan har kuna son in maido dashi to sai kun amince kun bani Matata, saboda WALLAHI matuk'ar ina raye babu wani wanda ya isa ya rabeta kuma zanyi ta d'irka mata ciki tana haifeman tunda har haka kuka zab'a" jikin Aunty ya d'auki kyarma bakinta yana rawa tace, "Mun amince ina zamu je mu karb'i yaron WALLAHI rayuwar Amrah tana cikin had'ari don ALLAH bata yaronta, daga baya zamuyi magana ta fahimta da kai, nayi maka alk'awali zan tsaya kai da fata har sai an maido maka matarka kamar yanda kace."

Nazir d'in yace, "Zan bada yaro amman ku sani inma kuna ganin wayo ne zaku yiman to WALLAHI zan bi duk hanyar da zanbi domin ganin yarona ya dawo hannuna" bakin Aunty yana rawa tace, "Ba ma za'ayi haka ba fad'a muna yanzu muzo mu karb'e shi." yayi mata kwatancen inda zasu sameshi jiki yana rawa suka yiwa mai Napep d'in kwatance ya mik'i titi da gudu, Aunty sai zufar tashin hankali ke tsiyoyo mata, Zuwaira kam a k'age take da yaron yazo hannunta tayi masa abunda sai yayi danasanin saninsu ma a rayuwa.

Suna kaiwa inda ya kwatanta masu sai ga kiranshi ya sake shigowa yace dasu su k'araso inda wata mota bak'a da take ajiye bakin titin, Suka firfito Napep d'in aiko sai ga motar sun hango jikinsu yana rawa suka isa wurin motar,Zuwaira tayi tsaye tana shirin aiwatar da nufinta da zarar ya bada yaron, Aunty ko ta fara kwankwasa glass d'in motar sabosa tinted ne ba'a ganin wanda ke ciki, aiko sai gashi ya fara sauke glass d'in motar a hankali sai ga wani had'ad'd'en gay

nagani masha ALLAH, sai dai shi ba fari bane kuma ba bak'i ba wankan tarwada ne atak'aice, yana da faffad'ar fuska da dogon hancinshi ba sosai ba,ga sajenshi da d'an k'aramin gemunshi, a gaskiya ba laifi yana da kyaunshi dai dai gwargwado, sannan ga alamun hutu kwance akan fuskarshi da fatar jikinshi, yana had'a ido da Zuwaira dake tsaye rungume da hannuwa fuska cure, kai tsaye yaji gabanshi ya fad'i saboda bala'in tsananin tsanarta da yayi, shima ya d'aure fuska tamau sannan ya bud'e murfin motar ya fito, ya bud'e seat d'in baya ya d'auko jaririn dake ta baccinshi hankali kwance ya mik'awa Aunty, batareda yace dasu k'anzil ba ya juya da nufin shiga motarshi, Zuwaira ta cakumoshi ta baya ta fara kuwwa tana kururuwar akawo mata agaji ga b'arawon jarirai, kafin kace me wuri ya fara cika batareda dogon ba'asi ba aka fara jibgar Nazir, duk da bayanin da yake yi akan cewa shi ba b'arawon bane danshi ne shi ya haifi yaron, sai da suka yi masa lilis tareda farfasa masa jiki ta ko'ina jini ke zuba, sannan suka dawo kan motarshi suka yi mata kwatsakwatsa, dak'yar wasu masu ragowar tausayin suka hana a sake dukanshi,saboda ganin yanda aka ji masa rauni da yawa, ana cikin haka sai ga wani ya kutso cikin taron mutanen yana had'a ido dashi ya ganeshi da k'arfi yace, "Nazir!!!!!!!" jikinshi yana rawa ya kinkimeshi ya sakashi motarshi aguje ya bar wurin, Zuwaira kam tuni tayi gaba da Jaririn Aunty kam tsaye take tana hawayen tausayin Nazir, saboda Zuciyarta ta k'ara tabbatar mata Zuwaira bata da gaskiya, kuma akwai abunda ta b'oye mata wanda bata sanar da ita ba, duba da yanda shi Nazir d'in ko d'ar baiyi ba lokacin da ya ganta, dako ace baida gaskiya da alamu sun nuna akan fuskarshi dacikin k'wayar idonshi.

Kwacagiya🤔to shin wai miye mafarin wannan ruguntsumin😆.

Akafta😅

D/Auta ce👍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

Gghttps://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

PAGE 21

****

Jiki ba kuzari Aunty taja k'afafunta ta isa inda napep d'in ke jiranta, ba tareda tace da Zuwaira k'anzil ba ta shiga suka bar unguwar, Zuwaira sai k'ara rungume yaron take ajiki zuciyarta cike da jin dad'in abunda tayiwa Nazir, ko ba komi dai ta tauna tsakuwa don aya taji tsoro, don ko ba shakka sai ya ji tsoron k'ara zuwa kusa dasu balle ya k'ara kawo masu wani iya shegen, Aunty dai sai kallonta take zuciyarta cike da jin haushin abunda tasa aka yiwa Nazir, har suka kai Asibitin ba wanda ya tankawa wani, koda suka je d'akin da Amrah take suka yi sa'a idonta biyu sai dai har lokacin bata daina kukan zuci da tunanin ina zata ga yaronta ba.

Koda suka shigo idanuwanta akansu farin ciki ya mamaye zuciyarta saboda ganin yaron da tayi rungume da Zuwaira, cike da murna tayi k'ok'arin tashi zaune tana zura hannu da nufin abata shi, ba musu Zuwaira ta mik'a mata shi zuciyarta cike da tausayin 'yar tata, yaro kam kamar yasan hannun mamarshi ya canyara kuka tareda zura hannu a baki yana tsotso, Amrah ta k'ura masa kallo zuciyarta cike da jin dad'in ganinshi, Aunty tayi saurin fad'in "ki bashi nononshi yasha mana" Amrah taji kunyar yanda zata fito da nonon, ganin yanayinta yasa Zuwaira zuwa ta d'aga mata riga ta k'asa ta saita mata yaron yanda zata ji dad'in shayar dashi, aiko yaro yanan nono a bakinshi ya karb'e da dauri ya fara tsotso zumui zumui, Amrah ta runtse ido tareda cije leb'e Aunty tana 'yar dariya tace, "Banda raki fa Amrahtu" Amrah tayi d'an murmushi sannan ta kai kallonta ga yaron tace, "WALLAHI Aunty da k'arfi yake sha fa"

Zuwaira tayi saurin fad'in, "Ai Uwa tafi k'arfin wasa kema yanzu zaki gano ina da daraja a wurinki, don ko ba komi yanzu kin d'and'ani zafin nak'uda kinsan wahalar haifuwa, ya zamar maki iznah akan kiyi man biyayya ki rabu da wannan tsinannen mijin naki, ko ki sab'a man kici gaba da zama tareda la'antar Ubangiji, don WALLAHI wannan karon ba uban da ya isa ya maida k'i gidanshi matuk'ar ina numfashi" Amrah ta kai kallonta ga Aunty idonta cike da hawaye, Auntyn tayi mata alama da ido akan kada tayi kuka, Amrah kam duk da k'ok'arinta na son ta shanye kukan Amman ta kasa, sai da hawayen suka gangaro saman fuskarta, tayi saurin saka hannu ta share saboda shigowar Likitan Malam na biye dashi a baya, don tun fitarsu Asibitin ya shigo shi kuma, yana tareda Amrar har ta falko, da kanshi ya had'a mata tea mai zafi ya bata sannan likitan ya shigo da takardar magungunan da za'a siyo nata da na jaririnta, don bai sanar dashi abunda yake faruwa ba, amman Malam ya jiyo labarin ga wasu makotan gadonta suna zancen wai ansace yaron, lokacin tana bacci bata falko ba a cikin kokwanto ya tambayesu wane yaro aka sace?, a take wannan matar da taga Nazir tayi masa bayanin duk abunda yake faruwa, shiyasa ranshi ya k'ara b'aci kai tsaye ya yankewa zuciyarshi rabuwa da

Amrah ya fiye masa ALKHAIRI, musamman da ya tuno kalaman da Jamila tayi masa a asibitin tun lokacin da Amrah take laulayin cikin, ma'ana dai ranar da ta had'u da Wani Malam zai fitowa d'akin, bayan ko minti biyu batayi da rabuwa da Malam d'in ba wanda ta kasa hak'uri sai da tayi masa wanka da jirwaye akan lamarin a ranar inda take cewa,

"A gaskiya yaya sai ka dage da addu'a saboda nidai ina ganin kamar akwai wani k'ulli a cikin aurenku, wanda kwanceshi a tsakaninku sai in ka jajirce da addu'a"

Cikin sanyin jiki yaje siyo maganin zai shigo d'akin ya had'u da likitan shima zai zo ya k'ara duba Amrah'r, sai gashi sun taradda Zuwaira da Aunty Asaben sun dawo, idonshi akan Amrah da take baiwa yaron nono ganin yaron yasa yaji gabanshi ya fad'i, amman ya waske ya duk'a yana gayar da su Auntyn, tana k'ok'arin amsa masa ne Zuwaira tayi masa wani kallo sannan tace, "Inda mutuwa tayi shikenan kai baka da asara, ace tun jiya yarinya tana asibiti amman sai yanzu kaga damar zuwa."

Amrah tayi saurin fad'in "tun d'azu fa yana asibitinnan Mama, ya dad'e da zuwa har tea ya bani nasha" Zuwaira cikin fushi tace, "Kamfanin madara ya baki kika shanye ba tea ba, WALLAHI kika sake jin ina magana dashi kika saka baki sai na ci maki mutunci." Malam Nura ya sunkuyar da kai yace, "Ayi hak'uri nayi ta nemanta a waya tun jiya tana ringing ba'a d'auka ba, sai yau da safe ne Abbati ya d'auka yake sanar dani kuna Asibiti" Aunty tayi saurin fad'in "Kayi hak'uri anyi maka laifi nima na rud'e da zanzo jiya ban kiraka na sanar da kai ba, sai bayan ta sauka da na koma nayi ta neman wayarka a kashe."

Yace "Ba komi ai tunda ta sauka lafiya."

Aunty ta amso yaron wurin Amrah ta mik'a masa, ya saka hannu ya karb'a zuciyarshi sai fad'uwa take yi saboda shakku da yake YI akan danshi ne ko na d'aya daga cikin mazajen da ta aura?, ba tareda ya bada k'ofar da za'a gano abunda ke Zuciyarshi ba yayi wa yaron hud'uba da sunan Abbakar, sannan ya mik'awa Aunty shi ya sanar da ita sunan da ya sawa yaron, sannan ya mik'a mata ledar magungunan da ya siyo masu, cikin rashin walwala yace dasu zai je ya dawo har ya kai k'ofa likitan da ke tsaye yana karantar yanayinsu duka yace dashi, "Da ka jira a sallemeta ku tafi gaba d'aya sai dai don ALLAH a kula da lafiyarta sosai." Malam ya dawo yana dariyar yak'e yace, "Alhmdllh fatanmu kenan ALLAH ya bata lafiya."

Sannan aka sallamesu suka tattaro komai nasu suka yo gida, inda Likitan da kanshi ya d'aukosu da motarshi ya kaisu har gida sannan ya juyo, Zuciyarshi cike da tunanin wannan ruguntsumi na wannan ahali.

Bayan dawowarsu gidansu Amrah Malam yayi sallama dasu yayi gida da nufin zaije ya dawo, Aunty taje ta d'orawa Amrah ruwan zafi tayi wanka aka yiwa jariri, sannan suka fara tarbon mak'otan da suke shigowa yi masu barka da Arzik'i har dare Aunty tana gidan sannan mijinta yazo ya d'auketa bayan yaga yaron.

Malam ya aiko da kayan jarirai kala biyar na Amrah kala Uku tareda sauran abun buk'ata na mai jego da sabon jaririnta, Zuwaira ta karb'a a wulakance tareda habaice habaice tana tsinewa auren talaka irin Malam, Amrah dai kallone nata amman zuciyarta cike take da sak'e sak'en makomar wannan yaron, da har lokacin dukansu basu san takamammen wanene ubanshi ba, tsakanin Malam Nura da shi Nazir d'in mai ik'irarin kiran cewa danshi ne.

**

Kwana uku da Haifuwar ne sai ga wannan wanda ya taimakawa Nazir lokacin da aka bubbugeshi, yazo da kaya himili guda yace abaiwa Amrah da yaronshi, sannan a sanar dasu sunan yaronshi Umar, aiko Zuwaira ta taso masa da ruwan bala'i tana k'ok'arin dukan mutumin har sai da aka shiga tsakaninsu, Amrah kam kuka ne kawai nata don izuwa lokacin ta kai k'ololuwar gajiya da wannan badak'alar, cikin fushi ta d'auko yaron zata fita aka tambayeta ina zata je?, tana kuka gwanin ban tausayi tace,

"WALLAHI nagaji nikam gidan marayu zan kai yaron kowa ya huta, duk mai so yaje ya karb'o bazan iya da wannan tashin hankali ba"

Dak'yar aka karb'e yaron a hannunta sai gunjin kuka take yi, d'an sak'on dai ana tsaka da lallashin Amrah ya sulale ya bar kayan anan, koda aka samu Amrah ta sauko ba'a ganshi ba ya tafiyarshi, dole aka shigo da kayan gidan sannan mutane suka watse kowa da tsegumin dake cin zuciyarshi, Malam kam dake tsaye yana kallon abunda ke faruwa, cike k'unar rai ya fasa shiga gidan ya koma gida, zuciyarshi kamar ta fashe saboda bak'in cikin dake cikinta, a matsayinshi na malami ace wai wani yana tarayya da matarshi a waje kuma don tsabar renin hankali ya fito fili ya nuna cewa shine yayi mata cikin abashi danshi, lalle anzo masa da renin hankali da yawa musamman da ita Amrah'r take nuna cewa bata da masaniya akan faruwar komi, kai tsaye ya yanke shawarar kawai yabi ra'ayin zuciyarshi ya sauwak'e mata kawai ya huta da takaici.

**

Ana cikin wannan yanayin ne har satin haihuwar ya zagayo ranar suna aka rad'awa yaro suna Abbakar, saboda abi zab'in Malam ba wai don Zuwaira taso sunan ba, don dai kawai suna ganin shine da danshi tunda sunan ya zab'a dole abi, amman inda kansu ya k'ara d'aurewar bayan k'aton ragon Malam sai ga sa da rago daga hannun Nazir, abun ya zamo tsegumi cikin mutanen dake gidan da unguwar duka, labari ya watsu ko'ina Amrah ba'a san uban cikinta ba, har dangin babansu Amrah sai da suka shigo cikin lamarin, don saboda abun yana so ya shalle tunanin kowa, dole aka bada shawarar a yanka duka saboda ba'a san ta inda rana zata fad'i ba akan wannan badak'alar.

Kwana d'aya da suna dangin baban Amrah suka shirya zaman meeting gidan Zuwaira, da nufin aji shin minene mafarin wannan rikici, gida ya had'u da babanin Amrah da Malam da Aunty da mijinta haka ma da wani baban Malam na 'yan uwa da yayi masa waliccin auren,

suna cikin tattauna abubuwan ne sai ga sallamar wani d'an sanda a k'ofar gida, da gudu Abba ya shigo hankali a tashe yake sanar dasu, dukansu suka yo k'ofar gidan d'an sandan ya mik'awa wani Yayan baban Amrah hannu suka gaisa, sannan ya zura hannu aljihu ya d'auko wata takarda ya mik'a masa, tareda yi masu bayanin cewa takardar Sammaci ce daga kotu ana neman Zuwaira saboda Nazir yayi k'ararta akan ta bashi matarshi da danshi.

Tofa anzo wurin 😳😳😳😳😳 yanzu ne balli zai tashi, to amman dawa shin da Nazir ko da Zuwaira 🤔 .

Akafta😸

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Am back my fan's zan dinga yimaku typing duk lokacin da na jini free insha ALLAH ko ba kullum ba maimakon ku jini d'if😅

PAGE 22

*Waiwaye adon tafiya.*

Wani matashin d'an saurayi ne wanda a kwatance zai kai shekara goma sha biyar, na hango d'akinshi tun da sassafe sai shirin zuwa makaranta yake yi, acikin wasu uniform d'inshi da aduba d'aya zaka gano ba k'aramin mai tsafta bane,saboda kayanshi sunsha karin guga har wani k'yalli sukeyi, bayan ya k'are shiryawa ne tsaf ya d'auko k'atuwar jakarshi ya rataya a kafad'a, tareda fiddo wani d'an karamin mashaci ya k'ara shato sumar kanshi da itama kanta tasha mai har wani k'yalli take yi, KAI tsaye ya fito d'an k'aramin d'akinshi tareda rufoshi har ya kai bakin k'ofar gida zai fita ne, na jiyo sautin wata mata dake zaune gindin murhu tana dama kullun koko tace, "Yau ma tafiyar zakayi ba tareda ka jira k'anwarka ba?" ya waigo ranshi a b'ace yace, "Haba Inna kinfa san Jamila bak'ar Nawa (ganda) ce da ita haka kawai tasa mutum yayi latti a dake shi a banza." ya k'are maganar cikin had'e fuska, Mahaifiyarshi wadda naji ya kira da suna Inna ta k'ura masa kallo cike da takaici tace,

"Ai in baka jirata anan ba sai kaje inda kaine zaka jira har ma a saka ka aikin da zai janyo makka lattin."

Nazir ranshi a b'ace ya kalli kanwarshi da ba zata wuce shekara shidda ba, dake ta cin d'imamen tuwonta yace, "WALLAHI kika yarda na isa gidansu Amrah baki shirya ba, ni ba jiranki zanyi ba don ma ki sani." yana k'are fad'ar maganar ya tusa kanshi zai fita NE Babanshi ya fito daga d'akinshi yace, "Saboda saurin kaje gidan Malam bukar yau har kud'in taran ka manta kenan?" ya k'are maganar yana 'yar dariya sannan ya kalli Jamila dake ta guma lomar tuwonta yace, "Ke kuma kiyi sauri ki k'arasa kar kuje kuyi latti." Jamila ta mik'e tsam ta wanko hannunta tace, "Ni nama k'oshi ai" Innar tasu ta tsiyaya mata kunu a wata gora ta mik'a mata Baban ya basu kud'in taransu, kasancewar Nazir ne ya fara karb'ar kud'in ana bashi yace dasu "ya wuce" suka bishi da addu'ar "a dawo lafiya" Jamila kam sai da ta tsaya saka sucks da sandal d'inta sannan ta rataya jakarta ta bishi da gudunta, koda ta fito har ya shige gidansu Amrah, da sallamarshi a baki ya shiga gidan, inda ya taradda lokacin ma aka k'are yiwa Amrah wanka, ta fito da gudu zuwa d'akin Mamarta tana yarfa hannu, Nazir ya kalleta yana 'yar dariya yace, "Lalle ma to kiyi sauri dai kada muyi latti yarinya" sai ga Zuwaira ta fito daga bayin tana ajiye bokiti tace, "A'a Nazir har an fito to bari inyi sauri in k'arasa shiryata sai ku tafi" ya d'an sosa kanshi yace, "Ba damuwa Mama ina kwana?" Tana amsa masa ta shige d'akinta da sauri tana shiryawa Amrah,Sai dai Zuwaira daga cen cikin d'akin tace dashi "Don ALLAH Nazir zubar man da sharar nan kafin in k'arasa shiryata." Aiko ya ajiye jakarshi ya sungumi sharar yaje zubarwa ne sai ga jamila ta fito daga gidansu, tana hangoshi yana zubar da shara ta rufe bakinta tana dariya, yayi kamar bai ganta ba ya dawo ya ajiye abun sharar yana kakkab'e jikinshi da wani k'aramin hankacif d'in dake hannunshi, ta shigo gidan da sallamarta ta tsaya tsakar gidan tana jiran Amrah'r ta fito su wuce.

Sai ga Amrah ta fito d'akinsu da hijab a hannunta tana saka sandal d'inta da sauri sai rawar jiki takeyi, Nazir ya kalleta yayi dariya yace, "Kiyi a hankali fa kar kije ki fad'i kawo hijabin in saka maki." ta mik'a masa bayan ta k'are saka sandal d'in yana cikin saka mata tana 'yar dariya, sannan Zuwaira ta fito da jakarta ta mik'a masa tareda kular abincin Amrah duka, idonta yakai kan Jamila dake rakub'e jikin gini tana kallonsu, tana 'yar dariya tace. "A'a D'iyar Inna an fito?"

tace "Eh ina kwana?" tace "Lafiya k'alau" ta k'arasa maganar da kallon Nazir tace, "Yau ma dai kam Amrah bata da kud'in tara, GA dai abincinta nan sai ta ci in an tashi break " Nazir ya ri'ko hannun Amrah yace, "Ba komi ai sai in bata nawa zo muje kar muyi latti, mun tafi sai mun dawo" Zuwaira ta bisu tana yi masu ALLAH ya tsare hanya har k'ofar gida, sannan ta juyo tana 'yar dariya tace, "Ai tunda kana bata ni nawa sun huta sai in k'ara a dashena da nike zubawa d'an kullum."

Nazir kam goye yake da tashi jakar a baya sannan ya rik'o kular Amrah da hannu d'aya, ya rik'e hannunta da d'ayan hannun suna tafiya Jamila tana biye dasu a baya, sai sunyi mata nisa ta biyosu da gudu tana fad'in, "Dob ALLAH yaya Nazir ku jirani" Nazir ya juyo ya maka mata wata k'atuwar harara yace, "Idan bazakiyi sauri ba WALLAHI bazamu jiraki ba, raguwa kawai sai shegen son jikin tsiya, amman in wajen CIN abinci ne lomarki tafi ta kowa auki."

Amrah ta juyo tana yimata dariya haka suke tafiyar har su kai makarantar, kasancewar ba wata tazara ce dasu sosai ba, don da sun fito kwararon gidansu Titi kawai zasu tsallewa sai makarantar.

kasancewar Makarantar had'e take da Primary da secondary, shiyasa idan ya kai Amrah ajinsu ya mik'a mata kularta sai shi ya wuce sashensu na 'yan secondary, da kuma an tada su Amrah break indai ya manta bai bata kud'in tarar ba, to duk dabarar da zaiyi sai ya fito ya kai mata kud'in koda ko ace da malami a ajinsu.

Shi kuma ba ya fitowa ma break saboda yasan baida kud'in da zai kashe, haka zaiyi ta zama a class har sai an dawo aci gaba da karatu, sai dai wani zubin idan abokanshi sun ja shi dole ya fito in har sunada kud'in su bashi ya siye abunda yake so.

Idan aka tashi kuwa don su Amrah ake riga tashi kasancewar akwai yara da yawa 'yan unguwarsu, sai su had'u su tafi tare gida gaba d'aya, amman fa duk wadda tayi gangancin tab'a Amrah da ya dawo makarantar sai ya biya gidansu ya tambayeta, dawa dawa suka daketa ita ko tayita lissafo masa su ko d'aya bayan d'aya, duk sai ya rama mata dukanta koda ko da Jamila a ciki, shiyasa da yawa ma basa tab'ata don sun san sauran, don da a daki Amrah gara adaki Jamila sai goma yafi son haka da a tab'i lafiyar 'yar gaban goshinshi.

Shiyasa wani zubin Inna take yi masa fad'a kamar ta dake shi, duk ko da take mace mai sanyin hali amman watarana Nazir sai ya janyo tayi ta fad'a kamar taci babu, Musamman idan yazo dukan Jamila akan ta daki Amrah, har sai dattijuwar nan mai kosai taji ta zagayo tana bata hak'uri, saboda katangarsu a had'e take indai ka d'aga murya dole ne a jiyo sautin juna.

Nazir kam ranar ma hakan ce takasance ya manta shaf bai bata kud'in ba sai da yaji an tada su break, sannan yace da malaminsu dake ta rubutu a allo, yana son yaje ya kaiwa kanwarshi kud'in taranta, Ba tareda ya waigo ba yace dashi minti biyu ya bashi idan ya wucesu jikinshi zai gaya nasa, aiko da sauri ya fito yana ta rabon idon ta ina zai hangota, sai cen ya ganta rakub'e jikin k'arfe k'ofar ajikinsu tana kuka, da sauri ya k'araso ya kira sunanta yace, "Wa ya dake

ki?" Amrah ta fara goge hawayenta da hijabinta tace, "Kowa da kud'inshi yana ta kashewa ni kad'aice ba'a bani ba"

Ya dafe goshinshi yace, "Kash kiyi hak'uri kingansu nan mantawa nayi ban baki ba, karb'i kije ki sayi duk abunda kike so kar ki baiwa kowa kinji?" ta d'aga kanta cikin murna ta karb'e kud'in ta ruga da gudu wurin masu sai da kayan k'walam, ya bita da kallo zuciyarshi cike da tausayinta sannan ya koma class, shigarshi ajin keda wuya Malamin ya katsa masa tsawa akan ya fita waje ya durk'usa, ranshi ya b'aci sosai yak'i bashi hak'uri ya dawo k'ofar ajin ya duk'a, saboda Nazir ba dai Zuciya ba ko kad'an baya da hak'uri matuk'ar ba akan Amrah bane, haka yayita zama wurin har malamin ya gama karatun, ya fito da bulalarshi ta dorina yayita jibgarshi har sai da yayi masa bulala goma sannan yace dashi ya tashi ya biyoshi Office, Nazir kan duk da yaji zafin bulolin amman saboda kafaffiyar zuciya yak'i yin kuka, ya biyoshi Office d'in ya duk'a yana jin rad'ad'in bulolin a jikinshi, Malamin ya ajiye littafan dake hannunshi saman benci, sannan ya zauna yana kallonshi ido cikin ido yace dashi, "Nazir me yasa kake son wasa da karatu ne duk da k'ok'arin da kake dashi?, na fahimceka a duk lokacin da nike yi maku karatu sai kayi dabarar fita ka dad'e baka dawo ba, shin karatun ne nawa baka buk'ata ko kuwa dai a'a da gangan kakeyi karatunne gaba d'aya baka buk'ata ?" Nazir ya duk'e ba tareda yace dashi k'anzil ba saboda zuciyarshi ta kawo wuya, duk maganar da zai fad'a a lokacin ba mai dad'i bace, har sai da Malamin ya k'ara cewa, "Kana da zuciya sosai na fahimta, amman kuma sam baka gudun b'acin ranta, shin dolene sai kai za'a baiwa kud'in tarar k'anwarka?me yasa ita baza'a bata abunta a hannunta ba sai kai dole?, da za'a ce a kullum sai ka shigo aji sannan ka fita zuwa kai mata kud'i" sai a lokacin Nazir yayi jarumtar magana yace

"Mantawa nayi" Malamin yayi saurin fad'in, "To daga yau na tuna maka wajibi ne ka bata kud'inta tun kafin ka shigo class, don matuk'ar ka sake na ji kace fita zakayi sai jikinka ya gaya maka tashi kaje amman ka sani wannan shine last warning da zanyi maka"

Nazir ya mik'e ya fito yana gunguni aranshi yana fad'in, _"WALLAHI sai dai akasheni bazan fasa fitowa na bata kud'in ba matuk'ar dai na manta ban bata ba, haka kawai sai in barta tayita kuka abanza wallahi bazai yiyu ba sai dai ku tanadi wuk'ar yanka ni. "_

Haka ya dinga zancen zucinshi har zuwa class d'insu, inda suma abokanshi suka yo masa caaa akai suna fad'a masa gaskiyar abunda yakeyi ya daina, dukansu ba wanda ya kula don idan ya biyesu damben tsiya ne zai rabashi dasu, ya janyo littafinshi ya CI gaba da cofe rubutun dake allon, Wani abokinshi mai suna Jamilu da tunda aka fara dukanshi ranshi ya b'aci yaji ba dad'i, yayi tagumi yana kallonshi kasancewar kujerarsu d'aya da Nazir, haka ma unguwarsu d'aya dashi sai dai akwai gidaje a tsakaninsu sosai, cikin sanyin Murya yace dashi

"Yanzu shikenan Nazir haka ka zab'arwa kanka?, baka da aiki sai na bautawa Zuwaira da 'yarta? WALLAHI kayiwa kanka karatun tanutsu shikenan kai ka zama bawansu, har kud'in taranma don mugunta bazasu bata ba kaine zaka dinga bata wanda ake baka daga gida?" cikin fushi Nazir ya d'ago daga rubutun da yake yi yace, "Shin wai kai Jamilu meye naka a ciki ne?, ina ga kud'ina ne ko kuma duk abunda nikeyi ba damuwar kowa bace, idan ba zaku iya

zura ido kuyi kallo ba to don Allah ku daina tankani aduk abunda kuka ga nayiwa Zuwaira ko 'yarta, ni naji na gani ku bari dani don ALLAH ba ruwan kowa, ya kukeso inyi da rayuwata ne? yanzu fa koda na fita na tarar da ita tanata kuka fa, to don kawai in farantawa wani zan barta tayi kuka akan abunda banfi karfinshi ba?to WALLAHI bazai yiyu ba kaji na fad'a maka, da Amrah tayi kuka gara duk mutanen garinnan gaba d'aya suyi tayi WALLAHI." yana k'are fad'ar maganar ya fisgi littafinshi yaje wata kujera ya zauna yana ci gaba da rubutushi, Zuciyarshi sai zafi take masa saboda ganin yafi kowa sanin abunda ya dace.

Tofa🤔🤔🤔🤔kuci gaba da biyoni sannu a hankali har muje inda muke son kaiwa😅

Akafta 😸

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

I love you all my fan's👍🏻👍🏻👍🏻

PAGE 23

Koda aka tashi School Sai da Nazir ya biya ta gidansu Amrah, Zuwaira ta bashi kayan miya

yayo mata markad'e sannan yayi gida, inda shigarshi gidansu keda wuya yaci karo da Inna a bakin k'ofar d'akinta tana sanya hijab, aiko tana jin sallamarshi cike da jin dad'in ganinshi tace

" Yawwa daman yaron da zai siyoman man k'uli nike nema, tun d'azu na k'are abincin ina jiranka ka dawo ka siyo a soya muci abinci" Nazir ya b'ata fuska yace, "Haba Inna daga dawowata kofa SALLAH banyi ba gashi itama Mamar Amrah yanzu na dawo kai mata markad'e" Inna tayi sakato tana kallonshi rik'e da kud'i a hannu tace, "Eh lalle tunda Mamar Amrah ta fini ai dole ita kaje nata aiken ni kuma nawa da zai amfane mu duka ka nuna baka son zuwa, to WALLAHI idan baka siyo shi ba yau bazaka ci abincin gidannan ba." ya karb'i kud'in fuska a had'e ya bud'a d'akinshi ya ajiye jakarshi tareda cire kayanshi ya sauya wasu, sannan ya fito fuu ya fice gidan Inna tana nan inda take har lokacin cike da jimamin wannan hali na Nazir, ace shi indai ba abunda ya shafi gidansu Amrah bane ko ma menene sai rayuka sun b'aci kafin yayi abu a gidansu, ko da ko abunnan wanda zai amfaneshi ne ko, 'yan mintuna a tsakani sai gashi ya dawo ya ajiye mata man ya d'auki buta yayi arwallah ya nufi k'aramin masallacin dake unguwar tasu.

Bayan INNA ta soya man ta zuzzubawa kowa sannan ta zauna suna cin abincin ita da Jamila, sai ga Amrah ta shigo gidan ganinta yasa Inna ta k'aro abincin suka zauna duka su uku suna cin abincin a kwano d'aya, suna tsaka da cin abincin ne Inna ta Mik'e domin kawo masu ruwan sha, abu ga k'urciya Amrah ta d'ebo loma jamila zata kai bakinta Jamila ta k'wace da k'arfi tace bazata ci shi ba, sai gashi aka yi dace wajen kwacewar akaifar Jamila ta yanki Amrah kad'an a hannu, aiko tana k'yalla ido taga wurin yad'an fasa kad'an har sawun jini ya fito, aiko ta k'walla k'ara tana kallon hannun, wadda yayi dai dai da shigowar Nazir gidan da 'yar guntuwar sallamarshi.

Inna tace "Haba Jamila me kika yi mata daga tashina yanzunnan?" Nazir ko yana zuwa bai yi wani jinkiri ba ya fallawa Jamila Mari, da sauri Inna ta k'araso wurinsu tace, "Kai kuma me tayi maka daga shigowarka?nifa bana son cin zalin" Nazir yana rik'e da hannun Amrah inda take nuna masa yace da Inna,

"Ji fa don ALLAH Inna yanda ta ji mata ciyo a hannu" ya kalli Jamila yace, "WALLAHI kika sake ji mata sai na rama mata kema kiji inda dad'i, bak'ar muguwa kawai haka kawai baki da aiki a kullum sai zaluntar yarinya." yana k'are fad'ar maganar ya janwo hannun Amrah suka fita k'ofar gida suka zauna a kan dakalin k'ofar gidansu yana lallashinta, sannan yaja hannunta suka tafi wani shagon dake unguwar tasu, ya fiddo kud'in da Jamilu abokinshi ya bashi yayi break baiyi ba, ya siyo mata minti da biscuit suka dawo yace ta shiga gidansu, sannan shi ya koma gida inda ya tarar da Inna zaune tana lallashin Jamila, don bashida kunya ya nufi madafi ya d'auko kwanon abincinshi, zai shige d'akinshi ne Inna ta kira sunanshi fuskarta a had'e alamun ba wasa, jin yanayin sautin muryarta yasa yayi saurin juyowa, don duk abunshi baya son ganin damuwa akan fuskarta, shiyasa ya dawo ya janyo kujerar tsugunno ya zauna sannan ya ajiye kwanon agabanshi ya ce "don ALLAH Inna kiyi hak'uri WALLAHI kema kinsan Jamila bata jin magana, haka kawai tayita dukan 'yar mutane ko bata yi mata komi ba"

Inna tayi masa wani kallo sannan tace, "To me yasa bazaka dinga yin adalci a tsakaninsu ba, ai watarana agaban idona Amrah take tsokalar Jamilar, sai dai inji kace tayi hak'uri don nikam ban tab'a ganin ka doketa kan tayiwa Jamila wani abu ba." yayi 'yar dariyar rashin gaskiya yace, "Ni dai Inna don ALLAH yanzu kiyi hak'uri, nayi laifi ki yafemani ai kin yafe man ko Jamila." Jamila dake kan cinyar Inna tana sharar hawaye ta yi saurin girgiza kai alamun bata yafe ba, gaba d'aya suka saka dariya sannan ya d'auko spoon ya fara cin abincin, Inna tana ta nusar dashi abunda yake bai dace ba, yayita bata hak'uri abu ga d'a da uwa atake suka shirya suka koma firar duniya, har ya k'are cin abincin yasha ruwa yace da Inna shi zai fita ya d'an lek'a gidansu Jamilu suje Kasuwa wurin Babanshi, in akwai wani aikin da zasuyi su sami d'an na kashewa a kasuwar, tayi masa addu'ar Nasara da fatan adawo lafiya ya shafi kan Jamila yace, "D'iyar Inna na tafi in kin yafe man in siyo maki agwalima." tana 'yar dariyar jin dad'i tace, "Na yafe Yaya Amman don ALLAH kada ka siyowa Amrah ." Yana 'yar dariya ya fice gidan a zuciyarshi yace,

"Ai sai ma ta rigaki shanta yasin."

Aiko aka YI dace yana zuwa suka had'u da Jamilu shima ya fito da nufin zuwa wurinshi suka rankaya Kasuwa, kasancewar Nazir mai k'arfin hali ne da k'arfin Zuciya yasa baya jin kiuyar(gandar) aiki ko wane iri ne, shiyasa idan dai yaje Kasuwa to wajibi ne sai ya samo 'yan kud'inshi, komi k'urarren lokacin da yaje ko, Musamman idan ranar da ba'a zuwa boko ne, don makarantar allonsu tunda ya sauke ya koma zuwa ta dare, idan anyi magriba da isha sai ya wuce wurin malamin sai k'arfe goma ya dawo gida ya kwanta.

Aiko koda suka dawo ya samo 'yan kud'inshi ya siyo agwalimar da su yalo da tsami gaye ya raba biyu ya kaiwa Amrah rabi sannan ya shigowa da Jamila rabi.

**

Haka rayuwa taci gaba da shurawa har Baban Amrah ya kwanta ciyon ajali, ganin yanda Nazir yaketa fad'i tashi da 'yarshi yasa ya sanar da Baban Nazir agaban Zuwaira akan cewa idan har ya mutu ko baya da rai to ya bar wasiyyar a aurawa Nazir Amrah, Baban Nazir yaji dad'in wannan kyauta da yayi masu, kasancewar Baban Amrah mutum ne shi mai dattako da sanin halin yakamata, don yasha zaunar da Nazir yayita yi masa fad'a akan ya rage d'awainiyar da yake yi da ita har zuwa lokacin girmanta, amman da yake shi ya riga da yayi zurfin da baya ji baya gani shiyasa ko kad'an bai fasa abunda yake yimata ba.

Sab'anin Zuwaira da a kullum gurinta dai abata abata, shiyasa jikinta har rawa yakeyi ta karb'e abu idan Nazir ya kawowa Amrah , don ko kud'in taran ma a kullum Baban Amrah sai ya bata ta ba Amrah, amman ganin Nazir yana bata yasa ta ke k'in bata tace masa batada dasu, don tasan yanda yake ji da ita bazai barta hakanan ba.

Bayan baban Amrah ya rasu ne sai gaba d'aya hidimar Amrah da k'annenta biyu maza duka Babansu Nazir ne yake YI masu, duk ko da akwai dangin Babansu kuma gwargwado suna yi

masu duk abunda baifi karfinsu ba, amman dai saboda Amanar da Baban Amrah ya barwa babansu NAZIR d'in shiyasa baya jin dad'in yiwa yayanshi biyu da ALLAH ya bashi wani abu ba tareda yayiwa d'iyan Zuwaira ba.

Amman duk da haka Zuwaira bata fasa d'orawa Nazir nauyin Amrah ba, saboda acewarta shine Mijinta idan har bai yimata ba to waye zai mata, shiyasa ta siyo masa asusu ta ajiye hannunta a kullum idan yaje kasuwa ya samo kud'i ita yake kaiwa tana saka masa asusu, da nufin da lalurorin Amrah sun taso sai dai a d'auka kawai ba tareda anjira komi ba, aiko baya ma sani sai dai ta sanar dashi tayiwa Amrah kaza cikin kud'in asusunshi, sai dai yace mata ai daman donta kawai yake fita neman kud'in.

****

Sannu a hankali rayuwa tana shurawa shekara da kwanaki sunata wucewa har Nazir ya k'are secondary inda Amrah da Jamila suka k'are Primary zasu shiga secondary aji d'aya ne Babansu Nazir shima ya kwanta ciyo na kwana uku ALLAH ya karb'i abinshi, a lokacin ne nauyi yayiwa Nazir yawa sosai, ga nauyin gidansu ga na gidansu Amrah, gashi ba wata kwakwarar sana'a ce dashi ba sai biyar Jamilu da yakeyi shagon Babanshi yana rik'a masu aiki, wanda akullum dubu d'aya ce kud'in aikinshi, haka yake gangand'awa ya raba kud'in biyu ya baiwa Mamarshi d'ari biyar Mamar Amrah d'ari biyar, ganin wahalar da Nazir d'in yake sha ne yasa Inna tace a siyar da gonar Baban Nazir d'in, sai ya fara kasuwancin tunda ya fara sanin kan kasuwar, aiko aka d'aga gona kasuwa aka siyar Inna har gidansu Jamilu taje tayiwa Babanshi magana akan gurinsu na son Nazir ya fara harkar kasuwanci, aiko kasancewarshi mutum ne mai amana yasa aka bashi kud'in ya siyo masa kaya ya saka a shagonshi, sannu a hankali kud'i suna albarka har aka ware masa shagonshi na kanshi, da hakan ne ya maida hankalinshi a kasuwar sosai ba tareda yayi tunanin komawa makaranta ba, d'awainiyar Amrah da ta k'annenta duka shine mai yi da jikinshi da aljihunshi, a kullum da sabuwar lalurar da Zuwaira take d'ora masa wadda daga ita sai ALLAH ba wanda yasani yake d'aukar kud'i tsaba ya bata, ko Inna bata sanin yayi balle wani don ko abokinshi Jamilu ma baya sani, bancin abinci da sutura da hidimar karatunsu da duk shi ya d'auke nauyin yimasu duka.

To da yake hausawa sunce yau da gobe sai ALLAH, to hakan ce ta kasance ga kasuwar Nazir domin kuwa sannu a hankali Kasuwar ta fara yin baya, saboda kud'in da Zuwaira take tasa yana bata ta k'ark'ashin k'asa, wad'anda itama take ta gina kanta dasu har sana'o'in takeyi su turame zanen gado dasu talkama, tana badawa bashi wasu su biya wasu su rik'e kud'in k'arshe dai sana'ar tazo ta durk'ushe, amman kuma haka zaiyita lodo mata wasu kayan baya gajiya har ta k'ara farfadowa.

Ana cikin haka su Amrah suka fara zama 'yanmata ita da jamila, don lokacin suna aji biyar a secondary kasancewar unguwar kowa yasan yanda Nazir yake dawainiya da ita yasa idan anganta aketa fad'in *Matar Nazir* ita dai iyakacinta dariya don tasan fiye da hakan ma idan

ance Nazir ya cancanci hakan, sai dai idan ta tuna bai tab'a cewa da ita yana sonta ba yasa take jin kawai had'uwar jini ne kawai tsakaninta dashi da 'yan gidansu duka, da kuma zaman mak'otaka da suke yi ganin yanda har makarantar k'annenta shine ke kula da dawainiyarsu.

Amrah tana aji shida Samari suka yo mata caa ganin hakan a kullum suke rikici da Nazir, Musamman idan ya tarar da ita tana fira da wani a k'ofar gida.

Gashi a lokacin kasuwar taja baya sosai ba kamar baya ba, a kullum Baban Jamilu yana nusar dashi akan ya koma makaranta yayi koda diploma ce, amman ganin d'awainiyar dake kanshi yasa yak'i baiwa maganar Muhimmanci, har lokacin da su Amrah suka k'are secondary wanda a lokacin ne komi na halittarta ya k'ara fitowa, kasancewarta farar mace son kowa k'in wanda ya rasa yasa mutane suka yo mata caa suna sonta, itama a lokacinne Zuwaira ta fara canza shawararta ganin yanda 'yarta take yasa ta fara jin cewa sai wani hamshak'in mai kud'i ko mai ilimin gaske wanda yake ci da gumin biro ne zai iya auren Amrah ba irin Nazir ba, shiyasa da Nazir yazo mata da zancen auren tace dashi, ya jira Amrah ta k'ara wayo don ko anyi auren shirme ne kawai zataje tayi masa, saboda a lokacin tana da shekara sha bakwai a duniya, shine ta bashi shawarar ya fara neman Muhallin da zasu zauna kafin nan sai ita Amrah ta fara jami'a, koda tana cikin karatun ne ya kammala sai ayi auren, duk da baiji dad'in maganar ba amman ya amince da zai samo mata admission saboda ganin yanda ita kanta Amrah'r take bala'in son karatun, yaje wa da Inna Maganar cewa zai saka Amrah Jami'a kafin ya kammala gininshi, Inna tayi masa wani kallon kai yaro ne ranta a b'ace tace dashi, "Wai meyasa a kullum kai Naziru in dai akan abunda ya shafi Amrah ne kwakwalwarka take toshewa ne?, yanzu don an maida ka shashasha za'a tsiro maka da zancen wani zuwanta karatu jami'a?, to WALLAHI bari kaji ni ba abunda ya dameni idan dai kace zaka d'aukarwa kanka wata sabuwar wahala, KAI ba kana buk'atar karatun ba me hana kaje kayi?, sai itace zaka dafe wa kan maciji taje tayi wasa bindi ko? K'arshe ma daga 'yar har uwar su buga k'irji suce su basu tab'a saninka ba ko?, to kaje gaka ga Zuwaira nan don WALLAHI ba baki nayi maka ba Zuwaira tunda kaji ta tsiro da haka, to ba 'yar zata baka ba don jikina ya bani da wuya in har Amratu zata zamo matarka"

Nazir yayi 'yar dariya yace, "WALLAHI Inna NI Amrah matata ce lokacin tarewarta gidana kawai nike jira."

Inna tayi masa wani kallon tashi sakarai sannan ta mik'e ta bar masa wurin ta shigewarta d'akinta, kai tsaye ta fito da hijabinta zata fita Yayi saurin kallonta yace,

"Ina zaki je kuma Inna?" tayi masa wani kallo tace,

"Wurin Zuwaira zanje inji da bakina da nata in kai ta maidaka wani samna aini tasan a girme na girmeta a shekaru ma nesa ba kusa ba"

Tana k'are fad'ar maganar ta fice fuu Nazir ya d'ora hannunshi akai yace,

"Na shigesu Inna kar ki b'ata man budget fa"

Jamila dake fitowa d'aki ta kalleshi tayi mere tace, "WALLAHI Yaya dama ka fita iskanta ka nemo wata don Amrah a kullum sababbin samari takeyi, in nayi mata magana tayo cikina da cin zarafi wai ita WALLAHI ba wanda ya isa ya hanata kula wanda take so"

Nazir ya maka mata harara sannan yace

"To Munafuka waya tambayeki ke kuma?daman ai nasan ba son tarayyata da ita kikeyi ba, to bari kiji Amrah tuni Matatace duk wani mai haukar cewa yana sonta abanza yakeyi,haka ma irinku wad'anda bakwa son aurena da ita kuma kunayi ne abanza don ni tuni nasan na rik'e igiyoyin aure a hannuna, don haka matsa daga nan tun ban sauke fushina akanki ba WALLAHI."

Akafta😝

D/AUTA Ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Jamila ta d'auki buta abunta ta shige toilet tana gunguni aranta, don tasan muddin ya jiyota mai tabarta a hannunshi ma sai yasha wuya, gashi Inna bata nan ballantana tayi masa rantsuwar kada ya sake dukanta, Nazir kam fita yayi k'ofar gidansu ya zauna yana jiran dawowar INNA.

Inna kam da fara'arta wadda iya kacinta kan fuska ta shiga gidansu Amrah, Zuwaira tana ganinta taji k'irjinta ya buga gaba d'aya ta diririce, don zuciyarta ta bata akan zancen su Nazir ne ya kawota, aiko cikin rawar jiki ta jawo tabarma ta shinfid'a mata da wata fara'arta ta munafucci, Bayan Inna ta zauna suka fara gaisawa a gajarce sannan Inna ta gyara zama tace, "Yanzu Naziru yazo man da wata magana wadda na kasa yarda da ita nace bari in zo inji daga bakinki, shin da gaske ne da naji yace wai kince Amrah zata fara jami'a kafin ya kammala ginin gidanshi?" Zuwaira ta fara susar kai na rashin gaskiya sannan tace, "Eh Innar Jamila ganin nayi gara ace ta koma makarantar kafin ya kammala komi hankali a kwance, saboda gaggawa aikin shed'an ne, tunda ai tuwo na maina ne damu daku duka abu d'aya ne" Inna bakinta kawai take kallo cike da mamakinta tace, "To ni dai Zuwaira idan har ni na haifi Nazir to ban amince da Amrah ta tafi wata jami'a cen ba, idan har da gaske don ya kammala aikin nashi ne zatayi karatun, to ta zauna gida kawai ta jira har ya kammala ayi auren, tunda ai tana zuwa islamiya ko yanzu ba zaune take a banza ba" Zuwaira ta yi dariyar yak'e tace

" To ai shikenan tunda haka kikace amman don ai ko wucewa karatun tayi ba wani aibi bane, don dani dake da kowa a unguwarnan yasan cewa Amrah Matar Nazir ce, ina ga ai wannan ba matsala bace da za'a hanata karatun" Inna ta mik'e tana gyara zaman hijabinta tace,

"Zancen karatunta kam ama barshi har idan sunyi auren, don ke kanki kinsan yanda Nazir yake sonta in yana ra'ayi da kanshi zai kaita makarantar, insha ALLAHU nan da wata biyu zaa k'ok'arta a kammala gyaran ko gefen inda zasu zauna ne kawai, kafin daga baya sannu a hankali ya k'arasa gyaran gidan duka, ko yanzu in banda kasuwa taja baya da yanzu ai tuni ya k'are ginin." ta k'are maganar cike da jin haushi, Zuwaira tayi mata wata hararar gefen ido tace, "Wata biyu two ALLAH ya nuna muna" Inna ta saka talkaminta tace da Zuwaira., " Ameen Ni na tafi insha ALLAHU ALLAH zai iya muna." zuwaira ta biyota tana fad'in, "To ALLAH ya shige muna gaba" Inna ta fice Zuwair tabi bayanta da harara tace, "Kwaji da Munafuccinku don WALLAHI bazan tab'a fara kudurina ba, dole ne sai 'yata tayi jami'a shikenan yanda ya lalace a kasuwa yak'i ci gaba da karatun, haka itama kukeso ta zauna batayi karatun ba, don kawai kuna takamar yana yi mana komi sai afara nuna man izza? Ai WALLAHI dole ne sai taje jami'a sai nagani in ku kuka haifa man ita." haka Zuwaira tayi ta banbamin fad'a har Amrah ta dawo daga makarantar islamiya ita da k'annenta, ganin mamarta tana cisgar fad'a yasa ta tambayeta abunda yake faruwa, kai tsaye ta sanar da ita cewa,

"Wai Nazir ne yake son ya hanaki ci gaba da karatunki, ala dole wai sai anyi aurenki dashi ." Amrah ta zaro ido waje tace,

"Aure Mama wani irin aure kuma da rana tsaka haka?" Zuwaira ta mayar da kai gefe tace "Kema dai kya fad'a haka kawai don yana d'awainiya damu sai ya hanamu yin abunda zai zama

ci gabanmu?" Amrah kam jikinta yayi sanyi sosai taja k'afafunta ta shige d'aki ta ajiye jakarta, sannan ta fito ta zauna kusa da mamarta tace, "Mama nidai tunda har yaya Nazir bai amince ba gara kawai abar zancen karatun"

Zuwaira ta mangareta ga kai cikin fushi tace,

"tunda shi yake mulkinmu ai dole mu bi ra'ayinshi, iya kacinshi dai yace bazai biya maki kud'in makarantar ba, to tafi nono fari don sai in had'a kan d'an jarina kije tunda kina so, Wallahi ba uban da ya isa ya hanaki karatunki" Amrah ta share hawayenta saboda ita dai har ga ALLAH tana son tayi jami'a, suna cikin maganar ne sai ga Nazir yayi sallama, sai da suka amsa sannan ya shigo, ganin hawaye akan fuskar Amrah yasa yayi saurin jawo kujerar robar dake ajiye gefe ya zauna idonsh akan Amrah yace, "ALLAH yasa ba akan makarantar ne kike kukan ba?" Zuwaira tayi caraf tace, "Akanshi ne kam don ta riga da ta k'wallafa ranta akan son karatun, shiyasa har kaga na damu akan tayi makarantar don WALLAHI bacci takeyi tana mafalkin jami'a."

Nazir yayi shiru na d'an lokaci saboda tuno yanda suka YI da INNA a yanzu kafin ya shigo gidan, akan ta kafe kai da fata Amrah baza taje makarantar ba, ya sauke k'atuwar ajiyar zuciya sannan yace, "Idan haka ne ni dai na amince taje tayi karatunta, amman da sharad'in duk lokacin da na kammala ginina za'a yi auren." Amrah tayi saurin kallonshi saboda fad'uwar gaban da ta ziyarceta ba shiri, saboda ita fa mamaki ake bata idan taji ana wani zancen aurenta dashi, ko ace mata Matar NAZIR saboda ita kam da rana d'aya bai tab'a furta cewa yana sonta ba, haka ma wani zancen soyayya cen bai tab'a had'asu ba, ita dai abunda ta sani yana kula da komi nata, baya son ganin b'acin ranta haka ma a kullum gurinshi yayi abunda yasan zai faranta mata rai, duk ta d'auki hakan da yake yimata a matsayin Yayanta da yake ji da ita, amman ita kam sam bata wani jin son aurenshi aranta, sai dai so irin na shak'uwa da zaman tare haka a kullum take kallonshi.

Amman jin abunda ya fito a bakinshi yasa ta shiga rud'u domin ta mik'e tsaye da gudu ta shige d'akinsu tana kuka, Zuwaira da Nazir suka bita da kallo Zuwaira ranta a b'ace tace, "Zan had'a kan jarina kakaf tayi makaranta gaskiya, duk lokacin da ka shirya sai AYI auren kawai." Nazir kam ya shiga rud'u sosai saboda jin sautin Kukan Amrah, kai tsaye ba tareda yayi dogon Nazari ba yace, "Zan nemo muna admission ni da ita sai muje karantar a tare, nasan Insha ALLAH Inna zata amince da hakan" Sannan Zuwaira ta saki fuskarta ta fara fara'a tace, "Ko kaifa yanzu naji zance ALLAH ya k'ara rufa asiri, Amrah fito kiji tare ma zakuyi karatun shikenan hankalin kowa sai ya kwanta."

***

Ko da Inna taji zancen ba k'aramar rigima akayi da Inna ba akan rashin amincewarta da karatun Amrah ba, da dad'in baki da siyasa da nuna mata ALLAH kusa Nazir ya samu ya shawo kanta ta amince, duk da har cikin ranta bata so wannan wauta da Nazir yayi ba, ta dai hak'ura ne don kada a zargi kamar ci gaban Amrah ne bata so, koko ace don hidimar da Nazir zaiyi da ita ne

take k'yashi.
Aiko tun daga ranar ya fara shige da ficen had'a kan kud'inshi na shago, ya nemo masu makarantar suka fara zuwa sannan ya ci gaba da aikin ginin gidanshi, wanda dole badon yaso ba ginin ya dakata tunda babu kud'in, shago ya tsiyace ba komi shiyasa ma ya kwashe sauran abunda ke ciki ya bada shagon haya, ya maida hankalinshi kacokam akan karatun nasu,

Hmmmmm Nazir manyan luv🤔

Akafta 😝

D/Auta ce 👌

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 25

Shigar Amrah jami'a ya k'ara rura wutar rikici tsakaninta da Nazir, domin kuwa samari NE suka

yo mata caaa ba d'aliban kawai BA har da wasu lecturer's d'insu, hankalin Nazir ya tashi sosai kullum safiya da sabon fad'an da zai yi da ita ko da masu cewa suna son nata, don yana cin nasara a wurin wasu masu sauk'in hali ne kawai, wajen sanar dasu cewa ita d'in matarshi ce, amman wasu kam ko k'adan basa yarda da tatsuniyar tashi, amaimakon sasanci sai abun ya koma fad'a a tsakaninsu, idan ya had'u da wasu masu ido tsakar ka ma cewa zasuyi dukanshi zasuyi, akan hakan Nazir yabi ya tada hankalinshi sosai baya da aiki kullum sai k'unci, tun INNA tana damuwa har ta zuba masa nagani saboda jin dalilin shigarshi a damuwar, saboda a cewarta "Wanda yak'i ji ai bazai k'i gani ba lokacin da nace da kai duk runtsi kada ka amince da zuwanta jami'a ai baka ji ba, amman da yake kai ka d'auki zancen Zuwaira kamar wani wahayi, shiyasa kaki yarda ka b'atawa Amrah rai ka sab'a maganar uwarta Zuwaira, ka zab'i maganarta fiye da tawa a ganinka tasu ce dai dai to ai ga irinta nan, tun kafin aje ko'ina ka fara cin karo da abunda nike ta tsinkayo maka tun kafin yazo." cikin fushi Nazir ya fito gidan ya nufi gidansu Amrah inda yaci karo da ita a k'ofar gida tsaye tana fira da wani sabon saurayinta mai mota, ranshi a jagule ya shige gidan ko kallonsu bai yi ba, don yasan muddin yayi magana a wannan lokacin ba k'aramar matsala zasu samu da ita ba har da saurayin nata, yanayin da Zuwaira ta ganshi ya shigo gidan ya kayar mata da gaba, amman da yake ta riga da ta shirya zuwan irin wannan ranar ta mazge itama tana wani shan k'amshi, kai tsaye Nazir ya kira sunanta yace, "Maman Amrah wurinki fa nazo." Zuwaira dake wanke wankenta hankali a kwance tace, "Ina saurarenka" Nazir ya gyara tsayuwarsh yace, "Zancen Aurena da Amrah ne nike son in tabbatar maki da cewa, Amrah fa matata ce tun tsawon shekara takwas da suka wuce, tun tana da shekara tara a duniya aka d'aura mani aure ni da ita." Zuwaira ta jefar da kofin dake hannunta ta mik'e tsaye jikinta yana ta rawa k'irjinta yana bugawa, ta dafe gaba bakinta yana rawa tace, "Yaushe aka yi hakan alhali ni bansani ba? To WALLAHI ni ba za'a yi wannan zalunci dani ba, wannan ai keta hukuncin shari'ar musulunci ne, don ni ban tab'a jin inda aka yi irin wannan auren kwamacala ba, ba tareda masaniyar iyayen Yarinya ba sannan ita kanta bata da masaniyar komi akan hakan." Nazir ya gyara tsayuwarshi sannan ya saka hannunshi a Aljihu yace, "Kinsan dai bazan yi maki k'arya ba ko? kin kuma san don biyan buk'atar kaina bazan shirya hakan da gangan ba, don nayi karatu tun daga bakara har zuwa nasi duk na sauke, haka ma nayi littattafai masu dama wad'anda ko iya su kad'ai na tsaya sun wadatar dani zaman duniya, bazan tab'a halasta haram ba haka ma bazan tab'a haramta halas ba, saboda haka ki sani Amrah Matata ce kuma yanzu haka a shirye nike da ta tare gidanmu d'akina kafin in kammala ginin mu koma, nayi shiru ne kawai tun tuni saboda cika alk'awalin Mahaifina, amman yanzu tunda har ta mallaki hankalinta a shirye nike da abani matata."

Zuwaira ta rufe ido ta dinga surfa ma Nazir rashin Mutunci, inda take shiga ba anan take fita ba duk Kawaicin Nazir sai da tasa ya biyeta suka dinga sa'insa, ya fito gidan ta biyoshi har waje tana ta bala'i kafin kace me mutanen unguwa suka fara taruwa, suna kallon yanda take ta masifa don shi kam Nazir mashin ya haye yabar unguwar gaba d'aya.

Dije 'yar tsohuwa mai sai da kosai dake mak'otaka da gidansu Nazir, ta k'araso wurin Zuwaira cikin Mamakin jin lafuzzan da take ta jifar Nazir dasu, saboda kafatanin Unguwar kowa yasan

yanda yake d'awainiya da ita da yaranta, Tsohuwar ranta ab'ace tace da ita, "A gaskiya Zuwaira ko kad'an bakiyi halacci ba, a ganina ko me ma Nazir yayi maki bai kamata ace ki dinga jifarshi da wad'annan miyagun kalamai ba, don Nazir yayi maki gata da bautar da ko uwarshi bai yiwa irinta ba, haka ma yayiwa d'iyanki gata tamkar k'asa bata shafe idon ubansu ba, ita wannan yarinya da kike ganinta matar Nazir ce halas malas, don kuwa ubanta tun yana raye ya riga da ya bada ita ga Nazir, amman da yake ke butulu ce sai kika manta duk alkhairin da Nazir yayi maku kika zab'i ki watsa masa k'asa a ido, to kisani WALLAHI muddin kika hana masa wannan yarinya hak'k'inshi bazai tab'a barinku ku zauna lafiya kuji dad'i ba." ta k'are maganar a cikin zubowar hawayen Tausayin Nazir, Zuwaira dake tsaye bakin k'ofar gida ko hijabi babu, lafuzzan Tsohuwar yasa jikinta yayi sanyi k'alau, amman don gudun ta bada damar da za'a ganin ta kasa ta bud'a baki tace, "Au kice ashe daman cen zaman gulmata ake yi a cikin unguwar?, to ai bani nace dole sai yayiman bauta nida diyana ba, shi yaji ya gani kuma yayi don kanshi ba matsarshi akayi akace sai yayi muna abu dolenshi ba, don haka banga abunda zai sa afara yiman d'an gungu a unguwa ba ana zagina, haka kawai asani abakin duniya nida yarana bamuji ba bamu gani ba, to WALLAHI duk matar da tayi da ni a unguwar nan ban yafe mata hak'k'ina ba." tana k'are maganar matasan yaran dake unguwar suka fara yi mata sowa, wasu matan Unguwar kam har ciki suka taradda ita suna ta zaginta don sunji haushin zagin kud'in goro da tayiwa mutanen Unguwar duka.

Salis dake tsaye da Amrah ganin abunda yake faruwa ga kuma Amrah tana ta kuka, yasa yayi sallama da ita akan sai gobe zai dawo, tayi masa ALLAH ya kiyaye tana tsaye har ya tada motarshi yabar unguwar, sannan taja k'afafunta zata shiga gida ne ta jiyo sautin Jamila a bayanta, da sauri ta juya ido cikin ido ta kalli Jamila da k'iris take jira ta kai mata duka saboda haushinta da take ji, ganin duk itace ta jazawa d'an uwata shiga matsalolin da ya shiga, cikin tsananin b'acin rai tace,

"WALLAHI Amrah kinji kunya kuma kinyiwa son da Yaya Nazir yake yimaki butulci, kuma ki sani kinci amanarshi ya d'auki son duniya ya d'ora maki, amman ke sakayyar da zaki yimasa kenan ki cutar dashi keda Mahaifiyarki, WALLAHI tunda kuka ci Amanarshi bamu yafe maku ba"

Amrah ta k'ara yawan zubar hawayenta cikin kuka ta rik'o hannun Jamila tace, "Yaya Nazir fa ni bai tab'a cewa dani yana sona ba, haka ma ni ban tab'a d'aukarshi a matsayin saurayina ba, a kullum ganinshi nike yi tamkar yayana da muka fito ciki d'aya tamkar ke dashi, don ALLAH Jamila ki fahimceni WALLAHI ba nufina in yiwa Yaya Nazir butulci ba, ni kawai ko a mafalki idan inayi ban tab'a hasasoshi a cikin jerin wad'anda zan iya aura ba, saboda ina yimashi kallon mutum mai darajja a wurina"

Ba shiri Jamila ta k'wace hannunta daga cikin na Amrah, tareda zubowar wasu sababbin hawaye masu zafi ta nuna Amrah hannunta yana rawa tace,, " Ke jakar ina ce da bazaki banbance so ko a ido ba?, wa ya fad'a maki cewa baki ne kawai yake isa ya isar da so a wajen wanda kake son? Yanzu duk irin fifitakin da ya dinga yi akaina shima duk ba son bane? Taya zai fifita son wata akan KANwarshi uwa d'aya uba d'aya matuk'ar ba sonta yake yi ba?, Yaya Nazir ya sadaukar da komai nashi akan soyayyarki, farin cikinki nashi ne kukan ki nashi ne, Ya bada

rayuwarshi sukutum saboda taki rayuwa ta inganta, jininshi da yayita kwantawa ana diba ana saka maki aduk lokacin da ciyonki na typhoid ya tashi, shi ma duk a wofi kika d'auki hakan? To bari kiji idan har da gaske ne zancen da kika fad'a to kin tabbata katanyar lusara wawuya dabbanya tunda har bazaki iya banbace aya da tsakuwa ba, kuma kusani daga ke har ita Mamar taki ALLAH ya isa tsakaninmu daku WALLAHI, duk abunda ya sami yayana WALLAHI daku zamuyi kuka."

Da gudu ta shige gida inda ta bar Inna a tsaye k'ofar gidan Itama tana share nata hawayen, masu cike da takaici da tsantsar tausayin Nazir d'inta, saboda tafi kowa sanin yanda ya k'wallafa ranshi akanta, ashe ita ko k'adan ma bata tab'a jin sonshi aranta ba.

**

Tun daga ranar zaman lafiya yayi k'aranci a unguwar saboda ko k'annen Amrah suka fita an dinga hantararsu kenan, ita kanta Amrah sai da fita taso ta gagareta sai dai fahimtar hakan yasa, Saurayinta Salis ya dinga turo mota ana kaita School ana dawo da ita, saboda ganin Salis d'in da zafinshi ya shigo yanata yi masu b'arin kud'i yasa Zuwaira kanta ya k'ara kumbura sosai, rashin mutuncinta ya k'ara hauhawa.

Inna har gida taje ta sanar da Baban Jamilu abunda yake faruwa, saboda Nazir ciyo ya kwantar dashi sosai kuma yak'i bari akaishi asibiti, a cewarshi abarshi kawai ya mutu yafison mutuwa da ace ya rayu yana gani Amrah ta auri wani ba shi ba.

Baban Jamilu Abokin Nazir har family house d'insu Baban Amrah yayi tattaki yaje akan maganar auren, suka zowa Zuwaira da zancen ta rufe ido ruf ta girba masu rashin mutunci, tareda yi masu kashedi akan kada shegen da ya koma shiga sabgarta da yaranta, suka YI kaca kaca da ita daga nan suka yi zuciya suka zare hannunsu akan lamarinta da yaranta, don sun san duk wani iskanci nata bata isa ta auradda Amrah ba tareda masaniyarsu ba.

Mutane Unguwa suka hana Salis d'in zuwa unguwar, don duk lokacin da yazo matasan unguwar da abin duka suke korarshi a unguwar, sunsha fasa masa glasses d'in mota ko sace masa tayoyin mota amman bazai hanashi dawowa wajen Amrah ba, saboda ALLAH ya jarrabeshi da tsananin sonta, shiyasa yayita sakar masu kud'i yana yimasu wacaka da nera.

Salis mai kud'in gaske ne shiyasa kai tsaye ya siya wa su Amrah wani sabon gida, cikin dare suka yi ta kwasar kayansu tsawon kwana uku har suka kwashe, wata safiya sai dai aka wayi gari gidansu datse da kwad'o sun bar unguwar ba tareda sunyiwa kowa sallama ba, wanda jin hakan ya k'ara saka Nazir cikin wani sabon tashin hankali, don sai da yayi wata biyu asibiti ana fama dashi sannan yaji sauk'i, tareda shawarwarin Abokinshi Jamilu da yake ta karfafa masa gwiwa akan cewa, "Rasa Amrah ba shine rasa komai nashi a rayuwa ba, ya zama dole ya cire ta aranshi ya dawo a kasuwarshi ya tallafi kanshi da mahaifiyarshi da kanwarshi."

Aiko aka ci Nasara Nazir ya fara saka dangana aranshi har ma ya koma kasuwarshi shagon Jamilu kuma yana zuwa makarantarshi, amman fa aranshi yaci alwashin duk hanyar da zaibi sai ya bita ya dasa masu bak'in ciki dai dai da yanda suka yi masa koma fiye.

Amrah kam soyayya tayi tsanani ita da Salis d'inta, kasancewarta sabuwa a fagen so yasa ta dulmiya sosai akan son Salis, da kanta taje dangin Babanta ta basu hak'uri akan abunda Zuwaira tayi masu, kasancewar ance hannunka baya rubewa ka yanke ka yar yasa suka hak'ura suka karb'i Salis a matsayin mijin da zai aurenta, aka shiga shirin biki gadan gadan sai gashi ana saura 'yan kwanki yace ya fasa, daganan aka ci gaba da abunda yayita faruwa ga rayuwar Amrah.

To kunji waiwayen da muka yi wanda muke tsammanin zai haska muna tafiyarmu har ma yayi mata adon 👌 .

Gareku fan's Nazir da su Zuwaira wa yafi yiwa wani mugunta??????

Ku fito afafata 💃

Team Nazir
Team Amrah
Team Zuwaira
Team Malam Nura😂

Akafta🕺

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 26

Mun dawo gundarin labarinmu.

Zuwaira ta k'araso gaban d'an sandan mai kawo sammacin cikin firgici tace, "Wa kace yake k'arar?" kai tsaye yace da ita "Nazir ne yake k'arar Zuwaira a kotu don haka ranar ashirin da Uku ga wannan wata da muke ciki, kotu tana nemanta waton gobe kenan, rashin halartarta tamkar cin karo da sab'a dokokin shari'a ne, don haka za'a d'auki mummunan mataki akan hakan na barku lafiya."

Ya haye d'an acabar da yazo da shi suka bar k'ofar gidan, Zuwaira ta d'ora hannu akai tace, "Na shiga Uku ni Zuwaira har abada bazan tab'a manta Wannan bak'ar rana ba, yanzu ni Nazir zai kai k'ara kotu? To da na masa me kuma? in banda cin zarafi." ta k'are maganar cikin kuka ta yi cikin gida jikinta sai rawa yake saboda tashin hankali.

Gaba d'aya jikin kowa yayi sanyi k'alau musamman Aunty da kuma shi kanshi Malam d'in, dangin Baban Amrah kam da suka tuno lokacin da Baban Jamilu yazo masu da zancen Auren Nazir da Amrah,basu sha mamakin jin hakan ba musamman da suka tunkari Zuwaira da zancen irin tozarcin da tayi masu, kai tsaye suka biyota a baya suka zazzauna kowa yayi jugum jugum, wani daga cikin dangin Baban Amrah'r yayi gyaran murya yace, "To Zuwaira kinga irin ranar da muke gudar maki tazo kin ganta da idonki, kin tuno cin zarafin da kika yi muna akan munje maki da zancen Auren Yaronnan da Amrah? To in kin mance mu bazamu mance cin mutuncin da kika yimuna ba a kan hakan, saboda haka ni dai WALLAHI babu ruwana banci nanin ba Nanin bazata cini ba, ke da kika ji kika jiyo gaki ga wannan yaron sai ki kwaci wuyanki a hannunshi da kanki don ni dai kam WALLAHI na zare hannuna kinga ma tafiyata." ya mik'e tareda saka talkaminshi zai fita wani daga cikin dangin nashi shima ya mik'e yace, "Jirani muje don nima kam na fidda wuyan hannuna." haka suka fice ko sallama basuyi da kowa ba, Zuwaira ta k'ara rushewa da wani sabon kuka, Aunty Asabe dake goye da jaririn Amra ta kai kallonta ga Amrah'r tana karantar yanayinta da na Zuwaira, saboda a take zuciyarta ta k'ara tabbatar mata da zarginta, na cewa Zuwaira bata da gaskiya duba da yanda ta bi duk ta rud'e gaba d'aya.

Wani yayan Baban Amrah da yake sunkuye da kanshi tun bayan fitar 'yan uwanshi yana tunani, ya d'ago fuskarshi cikin sanyin jiki yace

"Zuwaira ki adana hawayenki ko don gaba suyi maki amfani, don ni kaina abunda yasa ban bi sauran 'yan uwana ba saboda kawai ita Amrah'r, don bazamu rungume hannuwanmu dukanmu ba mu barki da matsalarta, musamman saboda wannan auren nata da mu muka yi jagaba wurin aurar da ita ga wannan Yaro Nura, saboda haka idan kinsan akwai wata kullalliya da kika aikata ki sanar damu gaskiya tun kafin akai ga shiga kotun, saboda a nemi yaronnan Naziru ayi sulhu cikin gida ba tareda an shiga kotu duniya ta yi muna tofin ala tsine ba, don WALLAHI in don ta halinki NI bazan tab'a saka kaina a matsala ba, don haka kiyi bayani agaban kowa miye gaskiyar wannan badak'alar?"

Zuwaira ta k'ara sautin kukanta tace, "WALLAHI ALLAH k'arya yake yi ba matarshi bace, shi dai kawai yayi hakan ne don ya rama abunda nasa aka yi mashi."

Kai tsaye Wan Baban Amrah yace, "Me kika sa aka yi masa?"

Zuwaira ta sassafta kukanta tace "Saboda ya sace yaron da Amrah ta haifa ne muka kamashi nayi kururuwa mutane suka dira akanshi suka yita jibarshi, to shine yake so ya rama ya biyo ta wannan hanyar, ai WALLAHI sai ALLAH ya isar muna akan mutuncin gidanmu da yake so ya zubar."

Ta k'are maganar tareda fyace majina da gefen hijabinta, wan Baban Amrah ya mik'e yana saka talkaminshi yace,

"To ni zan wuce sai goben insha ALLAH zanyi k'ok'ari in halarci kotun, tunda dai kin tabbatar da ba wani abu da kika b'oye ALLAH ya kaimu goben lafiya." gaba d'aya aka ce Ameeñ yayi sallama dasu ya fice gidan, Mijin Anty ya kai kallonshi ga Zuwaira yace,

"Ku kwantar da hankalinka Insha ALLAH zanyi k'ok'arin bin case d'in saboda ayi sulhu ba sai anyi zaman shari'a ba" Aunty tayi caraf tace, "Ni ko sai naga kada a katse masa hanzarinshi, gara abari kawai ayi shari'ar, saboda gaskiya ta fito ko don a fitar da wannan yarinya a tsaka mai wuyar da take ciki, tunda ai gashi Aunty ta tabbatar da cewa sharri ne yake biyarsu dashi, gara kawai ayi fito na fiton tunda haka yake so don idan ba kotun ce ta shiga tsakani ba, WALLAHI bazai tab'a barin Amrah ta ji dad'in zaman aurenta ba"

Zuwaira ta fashe da wani kukan tace, "Da za'a yi sulhun ni dai WALLAHI da nafi jin dad'i, don zuwa kotunnan ayi shari'a ba k'aramar bankad'a bace a garemu."

Malam Nura cike da jin haushinta ya mik'e tsaye yace, "Ni zan tafi sai goben idan ALLAH ya kaimu."

Shima wanda yake matsayin waliyyinshi ya mik'e yace, "ALLAH ya kawo muna k'arshen wannan rigima lafiya."

Aunty tace "Ameeñ" suma suka yi sallama da kowa suka fice, Mijin Auntyn ya mik'e tsaye shima yace, "Bari inje kotun inji me ake ciki saboda anyi dace kotun da nake aiki ce za'ayi shari'ar" Zuwaira tana share hawaye tace, "Don ALLAH kayi mani k'ok'ari kada ka bari ayi shari'arnan" Yayi 'yar dariya yace

"Kada ki damu Insha ALLAH komi zai yi settling" sannan ya fice Aunty ta biyoshi har suka kai bakin motarshi, ta kalleshi da kyau tace

"Ina ga abari kawai ashiga shari'ar don a gaskiya matuk'ar ba hakan aka yi ba, to har yanzu tana k'asa tana dabo, domin kuwa rayuwar yarinyar ce abun tausayi yakamata a walwale komi abaiwa mai gaskiya gaskiyarshi, don Zuciyata tana ta bani cewa Aunty Zuwaira bata da gaskiya, to kaga gara a fallasa duk wani abunda ke b'oye ko don asan makomar auren Nura da ita Amrah, uwa uba ga wannan yaron da ya zama wajibi asan wanene Ubanshi na gaskiya."

Megidanta yayi shiru na d'an lokaci sannan yace, "Maganarki gaskiya ce kuma abun dubawa ce, saboda haka Insha ALLAH zan tsayu sosai akan goyon bayan gaskiya a duk inda take, fatanmu kawai ALLAH ya shige muna a gaba." tace "Ameen" sannan suka yi sallama yaja motarshi ya wuce ta koma cikin gidan, bayan sun yi dashi akan idan ya k'are zai zo ya d'auketa su tafi gida.

Aunty ta koma gidan da sauri saboda mutsuniyar da yaron yakeyi a bayanta yana k'ok'arin yin kuka, tana shiga gidan ta saukeshi ta mik'awa Amrah da nufin ta bashi Nono, Amrah tana sharar hawaye tace, "Aunty ki barshi a hannunki ni WALLAHI bana son yaron, tunda duk akan zuwanshi duniya ne muke cikin wannan tashin hankali, da bashi ai da duk hakan bazata faru ba." Autyn ta kalleta sakato tace, "Bana son sakarci ni karb'i yaronki ki bashi nono dashi da bashi duk tunda ALLAH ya kaddaro sai anyi hakan, don haka kima daina d'ora masa laifin tun kafin k'i d'aukar wa kanki zunubi abanza, don lokacin da kuka yi abunku shi bai ma san zai zo duniya ba" Amrah ta karbeshi kamar wadda aka ba kashi ta fara bashi Nonon tana sharb'ar hawaye, Aunty ta zo kusa da Zuwaira ta zauna sannan tace, "Aunty ki daina d'aga hankalinki tunda dai ai da gaskiyarku, don shi ALLAH ba azzalumin sarki bane zai sakawa duk wanda aka zalunta, har ma ya biwa mai hak'k'i hak'k'inshi akan cutar da aka yi masa" maganganu Aunty Asabe tamkar dukan guduma Zuwaira take jinsu a zuciyarta, shiyasa ta k'ara sautin Kukanta k'arshe ma shigewa d'akinta tayi tana ta gunjin kukanta, wanda ya k'ara d'agawa Amrah hankali itama sai kukan take, Aunty ta d'aga murya tace,

"WALLAHI Aunty ki daina wannan kuka da kike kina wahalar da kanki abanza, don Megida yace zai tsayu sosai akan ya baiwa mai gaskiya gaskiyarshi tsakanin ku da Nazir" aiko da gudu Zuwaira ta fito ta kinkimi buta tayi bayi da aguje, saboda cikinta da ya murda ba shiri don tasan ita kam watan tonon asirinta ne ya kama.

Haka tayi ta zaryar zuwa bayi har lokacin da mijin Auntyn ya dawo ya tafi da ita, Amrah kam k'ulewa tayi d'aki tana ta ci gaba da kukanta, musamman idan ta tuno kalaman da Jamila k'anwar Nazir TAYI mata, aranta tace

"waton dai da gaske Yaya Nazir sona yake yi shine bai sanar dani ba, idan aka ce wannan yaron nashi ne to nikam ina zan saka kaina don kunya?"

Ta k'ara fashewa da sabon kuka a fili ta furta, "WALLAHI idan har da gaske kai ne kayi man ciki WALLAHI bazan tab'a yafe maka ba, ai inda Jamila ce bazaka so ayi mata hakan ba"

Haka dai suka kwana gidan cikin faduwar gaba da fargabar zuwan goben, wadda Zuwaira ta kira da sunan ranar tonon asiri.

Koda safiya ta waye zuwaira tayi zuru zuru saboda tsananin fargabar da tashin hankalin da take ciki, har Aunty tazo gidan akan su tafi kotun ko shiryawa bata yi ba, saboda kwance take kamar wadda tayi sati tana jinya, don ko wankan jaririn da take yiwa yaron Amrah a ranar kasawa tayi, dole Amrah'r ce ta lallab'a tayi masa sama sama, sannan ta shiryashi amman fa itama kanta k'arfin hali ne kawai tayi don gaba d'aya bata da wani sauran kuzari a jiki.

Dak'yar Aunty ta shawo kan Zuwaira tayi wanka, sannan ta karb'i yaron Amrah ta goye suka Nufi kotun, wadda megidanta yake jagorancin alkalanci wadda acen ne za'ayi shari'ar su Zuwaira.

Tofa ku garzayo muje kotu kar ayi babu mu😂 na tafi nidai wallah 🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️

Akafta 👍🏻

D/Auta ce🤝🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Ina jin dad'in yanda kuke nuna k'aunarku ga book d'in BAKAN Gizo, ina godiya da addu'o'inku gareni nagode sosai ALLAH ya bar zumunci, kusani D/Auta tana yinku irin sosai d'innan, Alkhairin ALLAH ya kai maku masoyana a duk inda kuke 👍🏻

PAGE 27

Tun kafin su k'araso bakin harabar kotun suka hango Nazir tareda wannnan abokin nashi waton Jamilu, tsaye jikin mota suna magana fuskar Nazir a had'e ba alamun sassauci a cikinta, saboda Jamilu yana bashi baki ne akan yayi hak'uri ayi sulhu ba sai an shiga shari'ar ba, amman ya kafe kai da fata akan shifa dole ne ya tsaya gaban Alkali da Zuwaira domin akwato masa hak'k'inshi, don WALLAHI bazai barsu su ci bulus ba, aiko sai ga Napep ta ajiyesu suka fiffito yana kai kallonshi garesu yaji bak'in cikin dake ranshi ya k'ara k'aruwa, Musamman da suka zo suka wuce ta gabansu Aunty ce kawai tayi masu magana, cikin d'aure fuska ya gayar da ita sannan ya wuce fuuu yayi cikin d'akin shari'ar, inda mutane da dama suka hallara wasu 'yan kallo wasu kuma suma zaman jiran tasu shari'ar suke yi.

Amrah kam tunda ta had'a ido da Nazir taji k'irjinta yana dakan lugude, saboda tsanarsu da ta hango cikin k'wayar idanuwanshi, Musamman dai ita da ta lura har wani banzan kallo yake yimata a wulakance, Zuwaira kam jin take kamar tayi dabo ta b'ace b'at a nemeta a rasa, don tsananin firgicin tashin hankalin da take a ciki.

K'arfe tara dam kotu ta cika mak'il har babu wurin zama, inda adaidai lokacin ne Alkali Yusha'u ya shigo k'aton d'akin shari'ar, gaba d'aya kowa ya mik'e tareda fad'in,

"Kooooooootuuuu"

Ba tareda ya kalli kowa ba ya zauna tareda gyara zaman glashin dake idonshi, sannan duk sauran mutanen suka zauna d'akin yayi tsit baka jin k'arar komi sai k'arar fankokin dake ta wulwulawa a sama suna bada iska, Daga nan wani mai gabatar da k'ara ya mik'e ya fara

gabatar da k'ara ta farko da za'a gabatarda shari'arta a wannan lokaciin waton tasu Zuwaira inda yace

"Nazir Mahmud yana k'arar Zuwaira matar Malam Bukar idan suna nan su fito gaban kuliya Alkali yana son ganinsu."

Nazir ya fito da fuskarshi mai d'auke da tambo tambo na raunin dukan da Zuwaira tasa aka yi masa, ya shiga d'an wurin da ake tsayawa ya tsaya, Zuwaira kam kasa tashi tayi saboda cikinta da yaketa kugin neman taimako,tana jin tsoron tashi zawon ya kunyata agaban dubban jama'ar dake wurin, har sai da taji an k'ara kiran sunanta sannan ta mik'e inda kowa ya kai dubanshi gareta, tana tafe kamar kazar da k'wai ya fashe mata a cikin ciki, aka nuna mata inda zata je ta tsaya ta nufi wurin kanta a sunkuye tana k'ara tsinewa Nazir a cikin zuciyarta.

Bayan sun tsayu ne Mai gabatar da k'ara ya zaunabayan ya mik'awa Alkali wata farar takarda, Alkali Yusha'u ya gyara zaman tabaraunshi ya fara karanto takardar kamar haka,

"Nazir yace yana k'arar Zuwaira akan ta bashi Matarshi da danshi da aka haifa masa, saboda haka ke Zuwaira mi zaki ce a gameda wannan k'ara da Nazir yake yi maki?"

Zuwaira da gabanta yake ta fad'uwa ta d'ago fuskarta ta kai kallonta ga Nazir d'in zuciyarta a cike da tsanarshi tace,

"K'arya yakeyi d'iyata Amrah ba matarshi bace, don yanzu haka da AURE a kanta kuma yaron da ta haifa na mijinta ne da take aure ba nashi bane."

Kan Alkali da sauran mutanen dake wajen ya d'aure sosai duk ko da kasancewarshi na ya san komi, amman hakan bai hanashi jefawa Nazir tambaya ba yace,..

"To kaji MALAM Nazir Zuwaira dai tace sam d'iyarta ba matarka bace, haka ma jikanta da ubanshi ba kaine Ubanshi ba me zaka ce akan hakan"

Nazir ya gyara tsayuwarshi yace

"Amrah matatace tun tsawon shekara goma sha biyu da suka wuce, wadda Babanta da hannunshi tun kafin ya rasu ya d'aura mani aure da ita saboda ganin da yayi nine nafi cancanta da ace na aureta"

Cikin d'aga murya Zuwaira tace,

"K'arya kake yi bak'in Munafuki taya za'ayi a aura maka 'yata ni bansani ba?"

Alkalin ya kalleta yayi shiru saboda sab'a dokar kotu da tayi, wani daga cikin ma'aikatan ya mik'e ya kalleta yace,

"Kotu wuri ne na karb'ar uzurin kowa don haka idan har kika sake fad'in wata magana ba tareda an tambayeki ba,kotu zata ladaftar dake saboda haka ki kiyaye"

Zuwaira ta had'iye wasu hawaye masu daci tana zarar ido Alkali ya kai kallonshi ga Nazir yace,

"Kamar yanda naji ka fad'a da cewa kaine kafi cancanta da ka aureta kamar yaya?haka ma saboda mi Baban yarinyar ya aura maka ita yarinyar ba tareda kowa ya sani ba sai kai dashi kawai, shin baka ganin wannan zance kotu bazata iya karbarshi kai tsaye ba?, matuk'ar ba kayi muna bayanin dalilin da ya saka faruwar hakan ba"

Nazir ya gyara tsayuwarshi cike da confidence yace,

"Amrah da gaske Matata ce kamar yanda na fad'a tun farko, saboda unguwarmu d'aya mu mak'ota ne, tun tana 'yar k'arama ALLAH ya jarrabeni da k'aunarta, ina mata so fiye da komi da na mallaka a duniya, nayi mata kula da tarairaya da gatan da ko k'anwata da muka fito ciki d'aya bata sami irin wannan kulawa agareni ba."

Daga nan yayita fayyace masu anahin labarin tiryan tiryan har zuwa inda su Zuwaira suka bar unguwarsu ba tareda sunyi sallama da kowa ba.

Gaba d'aya kotun ta hautsine kowa da tofin ala tsinen da yake yiwa Zuwaira da 'yarta, wanda shi kanshi Alkalin shiru yayi yana nazarin abun aranshi, Musamman Aunty da ko motsi ta kasa yi saboda tsananin tsoron Allahn da ya kamata aranta tace

"Ni daman nasan banza bata kai zomo kasuwa, ashe Nazir rama cutar da aka yi maka ne kake yi..... ."

Tunaninta ya katse ne lokacin da taji Alkali ya buga gudumarshi ana bada umurni akan kowa yayi shiru, Alkalin ya kalli Nazir d'in yace

"Ka tabbatar da duk abunda ka fad'a gaskiya ne?"'. Nazir ya tabbatarwa da Alkalin iya gaskiyarshi kenan ya fad'a, sannan ya kai kallonshi ga Zuwaira da ta jik'e sharkaf da gumi, inda ta saka gefen hijabinta tana fifita, ya k'are kallonta dakyau tareda nazarin yanayinta yace,

"To Zuwaira me zaki ce dangane labarin da Nazir ya fad'a a yanzu?"

Zuwaira ta fara inda indar rashin Gaskiya saboda k'arya ta k'arewa d'an kada don bazata iya musa duk wannan tonon sililin da yayi mata ita da yarta ba, amman duk haka sai da tace

"Ranka ya dad'e ai ba dole nasa yayi muna ba" daga cen nesa na tsinkayo muryar wani d'an kundunbala yace,

"Macuciyar banza bak'ar mayaudariya"

Kowa ya juya inda sautin maganar yake fitowa, daga nan d'akin kotun ya k'ara hautsinewa wasu suka ci gaba da zaginta wasu kuma suna ALLAH wadai da mai halin cuta irin nata, dak'yar aka natsar da kotun tayi shiru, Alk'alin ya kai kallonshi ga Nazir yace, "Nazir Mahmud ka fad'a muna Amrah matarka ce Amman baka sanar damu ya aka yi aka d'aura auren ba, sannan muna son musan suwa da suwa ne suka sheda wannan aure naka da Amrah da kace Mahaifinta ne ya d'aura da kanshi kafin ya rasu?"

NAZIR ya share k'wallar da ta tsiyayo masa yace,

"Mahaifina shine wanda Baban Amrah ya baiwa auren da hannunshi sai dai ALLAH yayi masa rasuwa, haka ma akwai wani malamin makarantarmu ta allo, sannan akwai limamin masallacin unguwarmu wanda shine ma ya d'aura auren da hannunshi, haka zalika acikin dangin Babansu Amrah Akwai Alhaji Mamman wanda shine ma yayi waliccin auren Amrah'r, sai dai shi ba anan garin yake yake zaune ba, amman duk da hakanan tsawon shekara hud'u ina fafutukar neman inda zan sameshi sai kwanan nan na sami numbarshi don yanzu haka yana tare damu anan wajen"

Aikuwa ba Zuwaira ba har su kansu dangin Baban Amrah sunyi mamakin jin wannan magana, saboda su kansu rabonsu dashi shekara goma sha tun rikicin gado da ya had'asu fad'a dashi yayi Zuciya ya bar garin basu sake sakashi a ido ba, don ko a waya basu tab'a yin magana dashi ba saboda daman cen shi mutum ne mai zafi sosai, aiko suka fara warar idon ta ina zasu hango d'an uwan nasu?.

Alk'ali ya katse masu hanzari akan tambayar da yayiwa Nazir, inda yake cewa dashi

"Idan har wad'annan mutanen da ka fad'a suna kusa to su fito ana buk'atar ganinsu"

Aiko sai gashi suna fitowa d'aya bayan d'aya, Malamin makarantar allonsu Nazir ne a gaba sai limamin masallacin tsohuwar unguwarsu, sai kuma ALHAJI Mamman dake bayansu, wanda tun da ya tashi sauran 'yan uwanshi suka bishi da kallo cikin d'okin ganinshi.

Bayan sun jeru cikin d'an akwatinne aka kawo masu alk'ur'ani dukansu suka dafa, tareda yin rantsuwa akan zasu fad'i gaskiyar abunda suka sani.

Daga nan Alk'ali ya dubesu yace d'aya bayan d'aya yace,

"Ko zaku iya sanar damu sunayenku?"

Daga nan suka fara bayani kamar haka

"Sunana Malam d'an Bala mai almajirai, ni kuma sunana Malam Muttak'a limamin Masallacin

unguwar baraje, Ni kuma sunana Alhaji Mamman yunusa mai hulluna"

Alkali yace, "Masha ALLAH to muna jira kuyi muna bayani shin da gaske ne A gabanku aka d'aura auren Nazir da Amrah tsawon shekara goma sha hud'u da suka wuce, ma'ana tun Amrah tana da shekara tara a duniya idan har akayi yi duba da labarin da Nazir ya bamu a yanzu?"

Ba tareda b'ata lokaci ba suka yi bayaninsu wanda ya zamo iri d'aya, Alhaji Mamman ya gyara tsayuwarshi da kyau yace, "Tabbas da gaske ne nine nayiwa Amrah d'iyar d'an uwana waliccin aurenta da wannan yaro naziru, wanda a lokacin shi Mahaifin yarinyar yana cikin ciyon ajali, ina gida ya kirani a waya yace dani inzo yana son magana dani, lokacin da naje ne na taradda wad'annan bayin ALLAH a d'akinshi, har ma da Mahaifin shi wannan yaron da yanzu baya duniya shima ALLAH yayi masa rasuwa, bayan mun gaggaisa dasu ne yake cewa dani, _"wani abun alkhairi ne yakeso yayi tun kafin ALLAH ya karb'i raina, don bana son inmutu ba tareda na cikawa wannan yaro alk'awalin da nayi masa ba, don haka don ALLAH ku taimakeni ku rikani na tashi, saboda ina son a d'aura wannan aure anan wurin yanzu a tsakaninmu, kuma sannan ina son ko bayan raina duk wanda ALLAH yayiwa tsawon ran ganin girmansu to kuyi jagoranci akan tabbatar da zaman lafiyar wannan aure, saboda haka kusani na baiwa Nazir Auren Amrah Duniya da Lahira"_

"To daga nanne baban Nazir d'in ya fito da Sadaki da dabino na karb'a na rarrabawa kowa, wannan Limamin shine ya d'aura auren a wancen lokacin, sai gashi ko sati biyu ba'ayi ba Mahaifin Amrah yace ga garinku nan."

Gaba d'aya d'akin aka ce "ALLAHU AKBAR" sannan Alkalin yace dasu suje su Zauna, ya kalli Nazir yace

"Kasan matarka ce tun tuni me ya hana ka fito fili ka sanar da yarinyar da Mahaifiyarta gaskiya?, idan har sunki amincewa sai ka kawosu k'ara kamar irin yanda kayi yanzu a k'watar maka hakkinka"

Nazir yayi shiru sannan yace,

Naso tun tana shekara sha biyu a bani matata Mahaifina ne ya haneni da yin hakan, sannan ya gindayaman cewar koda wasa kada inyi yunk'urin tab'a yarinyar Mutane har sai ta mallaki hankalin kanta, a cewarshi ko don halaccin da Mahaifinta yayi mani don har ya komawa ALLAH bai sanar da Mahaifiyarta ba, shiyasa niko nabi Umurninshi nayita juriya har zuwa lokacin da ta kammala secondary, lokacin dana zowa da Mahaifiyarta maganar aurenmu, inda ta nuna gara tayi jami'a kafin in kammala ginin gidana, wanda daga nan na fad'a maku matsala ta kunno kai har muka rabu dasu, inda a sanadin hakan ne ma nasha jinya sosai, bayan naji sauk'i ne mahaifiyata tace dani lalle sai na sauwakewa Amrah, don matuk'ar na sake zuwa inda take dai ta tsine mani, shine a lokacin na rubuta mata takardar saki sai dai lokacin da naje unguwar da suka koma, da nufin bata takardar naji bazan iya ba saboda hangota da nayi cikin motar

wannan saurayin nata, shine na juya abuna na koma gida bayan na yaga takardar nayiwa Mahaifiyata k'aryar cewa na bata takardar, a kokarinsa na son kaucewa fushin mahaifiyata sai na watsar da ita na shiga neman kud'ina gadan gadan bayan karatun da nikeyi, cikin ikon ALLAH ya dafa man na kammala ginin gidana, sannan har ma na gangand'a na auradda k'anwata ga abokina Jamilu, a lokacin ne Mahaifiyata ta saka ni a gaba akan sai nayi aure saboda wata yarinya 'yar makarantarmu dake masifar sona, duk da ni har ga ALLAH sam ba aure a tsarina tunda na rasa Amrah, a yunkurina na son dawo da matata yasa wata zuciya ta bani shawara akan inje wajen Wannan lamamin namu na allo, ya bani taimako naje na sakawa saurayin Amrah wata laya a k'ofar gidanshi, wanda a lokacin naji ance saura kwana uku aurensu, aiko a take ba b'ata lokaci yace ya fasa aurenta ana cikin haka kwatsam sai naji ance wai an d'aura mata aure da abokinshi, cikin tashin hankali na koma na sanar da wannan Malamin nawa, ya bani wata laya yace dani shima in binneta a tsakiyar gidanshi idan nayi haka bazata wuce sati biyu gidanshi ba, aiko cike da jin dad'i shima naje na aiwatar sannan, sannan ya bani wani turaren magani yace dani idan zan shiga gidan in murzashi to zanyi kama da wani abokinshi, haka ko aka yi wani zubin inje har d'akinta in kwana da ita amman bana barin wani abu ya hadamu, sai na dai daici motsin mijin in fito ya bini da kallo yana kiran sunan abokin nashi, sai gashi akan hakan shima auren ya mutu ta dawo gida, na sake jewa da Inna akan zancen Amrah ta rufe idonta tace ko bayan ranta na kawo Amrah gidana bata yafe ba, sannan ta matsa man akan dole sai na fito da mata dole badon naso ba na fito da wannan yarinyar dake sona, saboda na yaba sosai da hankalinta, aka nema mani aurenta na kai lefena da Sadaki, amman duk da haka Zuciyata tana manne da son kasancewa da Matata, sai gashi kwatsam naji labarin zata koma wani auren, shima naje na fad'awa malamina ya rakani muka je wajen wani abokinshi muka turo masa aljanin da ya kwantar masa da gabanshi, dole ya rabu da ita saboda matsin lambar Matanshi, daga nan kuma ta sake wannan auren da takeyi a yanzu".

Alkali ya dakatar dashi saboda duba agogon hannunshi da yayi yaga lokacin tashi kotun yayi, ya dubi Nazir yace "an d'aga wannan shari'ar taku sai kuma gobe idan ALLAH ya kaimu saboda lokacin tashi yayi kotuuuuuu"

Rigijigabji wani kaya sai amale 💃Team Nazir kuzo muje gida musha ruwan sanyi, Team Zuwaira ku ja kayanku ku wanke mata zawo, don nasan da wuya idan bata b'ata zanen ba wanya wari🤭

Akafta 🦹

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Ashe zuma kama takeyi da k'uda BAKAN GIZO ko shine yake shanye ruwa 🐓

Na gaya maku labarin tunda dare ya tsala domin kuwa kalma mai zafi ta zarce bugun bulala, ashe jiya anyi ruwa su BAKAN GIZO na sharar bacci, ku yarda da ALLAH ke komi kada ku yarda da bokanci nama shine kayan kura karya itace sai giwa 🐓🐓🐓🐓

PAGE 28

Daga nan Alkali ya mik'e ya bi wata 'yar k'aramar hanya, mutane kowa ya mik'e wasu suka fara ficewa daga d'akin kotun, yayinda wasu suka tsaya suna 'yan surutansu sama sama, Zuwaira dai kasa motsawa tayi daga inda take saboda gaba d'aya bata da k'arfin matsawa daga wurin , har sai da Aunty tazo ta fito da ita daga inda take, Amrah kam tunda taji an tabbatar da Cewa Nazir Mijinta ne, taji zuciyarta cike da wani sabon k'unci musamman da taji ya fad'a da bakinshi, akan cewa shine yayi ta sakata tashin hankalin da ta shiga a baya, taji tana yimasa wata irin tsana da bata tab'a yiwa kowa irinta ba, jikinta yana rawa ta fito daga inda take zaune tasha gabanshi tareda ciyo kwalarshi, jikinta sai kyarma yakeyi hawaye masu zafi suna kwaranya akan fuskarta tace,

"WALLAHI bazan zauna da igiyar aurenka akaina ba ya zama dole ka sauwak'e mani wannan bak'in auren na cuta" Nazir ya kalleta dakyau sannan yayi murmushin takaici ba tareda dogon nazari ba ya d'aga hannu ya wanke ta da wani bahagon Mari har biyu, sannan ya nunata da d'an yatsa yace,

"Ke wacece da har matsayinki yakai ki saka hannu kici kwalata?to bari kiji WALLAHI ba ke ba ko ita Azzalumar Mahaifiyar taki tace ta tari gabana sai na nuna mata cewa ruwa ba sa'an kwando bane, kuma aure da kike fad'in in sauwak'e maki WALLAHI koda za'a halbeni da bindiga bazan tab'a sakinki ba WALLAHI"

Yana k'are fad'ar maganar ya bangajeta ta fad'i ya wuce abinshi, Aunty tayi saurin zuwa ta tada ita daga kwancen tana lallashinta, Zuwaira ko ba shiri taji wani k'arfi ya zo mata tabi bayanshi tana fad'in,

"WALLAHI duk ubanda ya tsaya maka a garinnan sai ka sakar man 'yata, mugun banza azzalumi sai ALLAH ya saka mata da bak'ar isa akanka"

Aiko fitarsu d'akin kotunnan keda wuya 'yan jarida suka yo masu caaa, aiko ya tsaya yayita amsa masu da duk wata tambaya da suka yi masa,har inda aka ce masa

"Me zakace gameda wannan aure naka a yanzu zaka iya ci gaba da zama da matar da tayi maka irin wannan butulcin??" yayi 'yar dariyar k'eta yace

"zama daram kuma ba gudu ba ja da baya"

Dak'yar ya samu ya sulale masu, aiko suka yo caa wurin Amrah inda wata matashiyar 'yar jarida tace da ita,

"Me zaki ce dangane da wannan Aure da aka yi maki tun kina 'yar shekara tara?zaki ci gaba da zama da mijin ko kuwa zaki nemi ya sauwak'e maki ne ki nemi wanda kike so?" Aunty ta ture 'yan jaridar ta jawo hannunta Amrah ta k'wace hannunta ta dawo jikinta yana rawa tace,

"WALLAHI ko inuwarshi bana fatar zaman aure da ita balle shi, saboda na tsaneshi natsaneshi tsana mafi muni a rayuwa."

Ta k'are maganar cikin kuka Aunty ta fisgota da k'arfi ta sakata Napep d'in da ta taro, Zuwaira ma ta shiga ta zauna wani d'an matashin D'an jarida ya zagayo da gudu yace da ita,

"A matsayinki na uwar wannan Yarinya me zaki ce?" Zuwaira fuska a had'e tace

"Ko da zanyi yawo tsirara WALLAHI bazan tab'a bari yayi zaman aure da 'yata ba" Aunty tace da Mai Napep d'in ya tafi kawai aiko yaja da k'arfi suka bar bakin k'ofar kotun, Amrah sai Kuka take yi gwanin ban tausayi har suka je gida ba wanda yace da wani k'anzil.

Amrah ta shige d'aki sai uban kuka take ci zuciyar Zuwaira ta k'ara farashin bak'in cikin dake ranta, aiko ta dinga zuba ruwan bala'i tana tsinewa Nazir da Inna har ma da Malam Mahmuda waton baban Nazir, Aunty dai shiru tayi kawai tana kallonta saboda bata son tayi magana a

lokacin su sami matsala da Zuwairar, saboda tasan duk abunda zata fad'a a lokacin bazai yiwa Zuwaira dad'i ba, don ita kam tana goyon bayan gaskiya koda ko Zuwaira da Amrah zasu ga laifinta.

Yaron Amrah dake hannunta ta mik'awa Amrah tace, "karb'i Umar ki bashi Nononshi yasha ai yayi k'ok'ari ma da baiyi kuka ba" Zuwaira TAYI hanzarin fad'in, "Asabe da alama kema kin yarda da wannan tatsuniyar tashi ta k'arya kenan?"

Aunty tayi 'yar dariya tace, "Me kika gani Aunty?" Zuwaira ta kara had'e fuska tareda kawar da kanta a gefe tace, "Naji kince Umar bayan kinsan sunanshi Abbakar wanda ubanshi ya saka masa" Aunty ta kalleta dakyau tace

" Eh nasani ai shiyasa ma na fad'i ainahin sunan wanda baban nashi ya saka masan"

Zuwaira ta kalli Aunty tace, "Kada ki maidani wata shashasha Asabe, Malam Nura nake nufi don mu shi muka san ya auri Amrah ba wancen bak'in d'an iskan ba, don WALLAHI Alla Alla nake gobe tayi sai ya sakar man 'yata a gaban kowa."

Aunty tayi 'yar guntuwar dariya tace

"To ai tunda har kike so ya saketa kenan dai kema kin yarda da cewa ashe shi d'in Mijinta ne, don haka dole a kira yaro da sunan da ya rad'a masa, duk da dai mu har yanzu bamu san ta yanda yayi ya zamo uban yaron ba, amman ni dai kam zuciyata ta riga da ta sare da cewa wannan yaron d'anshi ne"

Zuwaira ta mik'e tsaye tareda kakkab'e zanenta ta shige d'akinta tana fad'in,

"ALLAH ya tsine masa daga shi har zuri'arshi duka, don WALLAHI ko wannan yaron in banda kada alhakin hak'k'i ya bibiyeni, WALLAHI da ace zan iya da sai na b'atar dashi ya rasashi, indai har akanshi ne yake yi muna wannnan rashin mutunci, to nikam inyi surukuta da Nazir in tsinci me? yaron da a gaban kowa ya ci man mutunci tun kafin yanzu, balle yanzu da yake ganin kanshi dai dai da kowa to WALLAHI ta hanyar da yabi ya saka mu cikin k'unci nima ta hanyar zanbi in tarwatse masa farin cikin da yake tak'ama dashi don uban da ya haifi ubanshi d'an matsiyaciya"

Sannan ta fito ta d'auki buta tayi bayi tana ta zuba ruwan masifa tareda ci gaba da tsinewa Nazir d'in, Aunty ta kalli Amrah ta sake mik'a mata yaron tace, "Karbarshi nace tun d'azu kin barni dashi a hannu sai mutsuniya yake yi, ko so kike yayi kukan sannan?"

Amrah tana ci gaba da kukanta tace, "WALLAHI Aunty ni bazan sake shayar dashi ba nikam" Aunty ta zaro ido cike da jin tsoron maganarta tace, "Kina hauka kuwa?shi wannan yaron me yasani nikam? ballantana ki fara nuna masa bak'in hali ki karbeshi nace ko"

Amrah ta zura hannu ta karbeshi ta jefar dashi akan gadon, aiko yaro ya canyara kuka saboda firgitar da yayi, Aunty ta kai mata wani duka a baya har sai da ta gantsara, sannan cikin tsananin b'acin rai tace, "WALLAHI idan ba so kike yi in zare hannuna a sha'aninki ba to ki d'auki yaronki ki shayar dashi, kuma ki sani ko bana nan kika cutar dashi ALLAH yana kallonki kuma zai saka masa, ki bar ganin wai ke kika haifeshi to ko tsakanin d'a da mahaifiyarshi akwai hisabi matuk'ar ta zalunceshi"

Sannan Amrah ta d'auki yaron tana sharar k'walla ta fara bashi nonon, yana sha yana sauke ajiyar zuciya ita kanta sai da ya daina kukan sannan hankalinta ya kwanta, don ba k'aramin kai zuciya nesa take YI ba akan kawar da kanta ga yaron, don har ga ALLAH ba k'aramin jinshi take a cikin zuciyarta ba, saboda kama sosai da yake yi da ita don fari ne sol masha ALLAH harma da alama sai ya fita kyau.

Sai ga Zuwaira ta lek'o saboda itama kanta kukan yaron ya dameta cike da masifa tace,

"Kar kiji bak'in cikin shayar da yaronki shayar da shi sosai don idan an k'are tashi shari'ar nima za'a shiga tawa, don wajibi ne sai ya biya mu kud'in haike makin da yayi gidan aurenki, sannan ya biyaki wahalar d'aukar cikinsa da kika yi har ma da wahalar nakudarki da kika sha,da kuma shayarwar da zaki YI wa yaronsa, don WALLAHI bazan tab'a bari yaci bulus ba."

Aunty ta kalleta tayi shiru tana nazarin abunda zata fad'a sannan ta d'ago tana kallon Zuwaira tace, "Haba Aunty ina kika tab'a ganin mutum da matarshi kuma ace sai ya biya wad'annan kud'ad'en?Nazir fa Mijin Amrah ne halas dinsa ce kuma bayada laifi kokadan WALLAHI, koda ko ace shine yayi mata cikin wannan yaron, don idan zaki dubi wannan rikici da kyau zaki fahimci cewa Nazir fa tattalin aurenshi ne yayi sai dai zunubin kaucewa hanya da ya d'aukarwa kansa, wanda wannan kuma tsakaninshi da ubangiji ne,amman kuma mu godewa ALLAH da har wannan yaron ya kasance danshi, don da ace tsautsayi yasa Yaron ya fito ta jikin Malam Nura, da WALLAHI bamu san ta inda zamu jefa kanmu ba akan kunyar da zamuyi a idon mutanen duniya, don ba wanda ya isa ya sauya masa sunanshi na shege marar uba, saboda ba ta hanyar aure aka haifesa ba"

Zuwaira ta maka ma Aunty wata k'atuwar harara saboda jin haushin danganta mata d'an jika da tayi da shege, ranta a jagule tace

"A gaban idanunki fa kika ji yace shine yayi ta kashe mata aurarrakin da tayi a baya, amman wai kice bai yi laifi ba saboda kawai mu bakya goyon bayanmu, ki duba fa Nasir satinta biyu ya sakota haka ma Alhaji Mai AKWAI dududu ko wata biyar ba'a rufa ba ya korota, sannan kice wai baya da laifi ai WALLAHI sai in da k'arfina ya k'are wajen kwatowa 'yata hak'k'inta".

Aunty ta gyara zamanta sannan TAYI d'an gareren murmushi tace,
"Ai Aunty Zuwaira Nazir fa taimakonku yayi da har ya hanaku d'ebowa kanku k'aton zunubin yin zina da Matar aure, saboda musulunci da da kristanci duka babu inda akace ayi aure KAN

aure, dan haka ki sani auren Amrah da Malam Nura haramtaccen aure ne har ma da sauran aure auren da tayi a baya, don ko k'adan babu aurensu a addininmu na musulunci har ma da na kiristancin duka don haka Aunty daga ke har Amrah ku ajiye makamanku ku rungumi k'addarar da ALLAH ya tsara maku, kuyi hak'uri Amrah ta tare gidan mijinta sannan kumatayi hak'uri da duk abunda zata gani, don komai na duniya mai wucewa ne ahankali zata janyo hankalin Mijinta akanta, saboda yana tsananin sonta shawo kanshi gareta bazai yi mata wahala ba har ma ta samu ya hak'ura da komi suyi zaman lafiyarsu, don ko ke kanki hankalinki zai fi kwanciya idan ta koma gidan Nazir d'in.

Zuwaira dake tsaye jikin k'ofa tana yiwa Aunty wani kallo tace,

"WALLAHI ALLAH ya kiyaye da ace ta zauna dashi gara ta tabbata a cikin gidannan tare damu"

Aunty ta Mik'e tsaye tana saka hijabinta tace, "Ni dai na tafi sai goben don naga idan na tsaya rayukanmu ne duka zasu ta b'aci abanza don ni dai kam tantagaryar gaskiya ce nike d'oraku akai, kuma komi daren dad'ewa zaku fahimci abunda nike son ku gane"

Aunty ta saka talkaminta sannan ta kalli Amrah tace,

"Ke kuma kiji tsoron ALLAH ki kula da yaronki" sannan ta fice Zuwaira ta bita da harara tace, "Ai ni na dad'e da fahimtarki daman cen ba sona kike yi ba, ALLAH ya kiyaye dangin Nazir ko ma ince k'anwar uwatai don da ita kika fi dacewa." ta kalli Amrah tace

"Ke kuma ki daina kukannan haka na gaji da jinsa a kunnena, ki barni da shi don ubanshi da an k'are shari'ar nima zan shigar da tawa k'arar."

To fa😸😸😸team Zuwais kuzo ku bata hkr 🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️

Akafta 🏃‍♀️

D/Auta ce👍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Ina jin dad'in comments d'inku NAGODE sosai masoya book d'in BAKAN GIZO mai shanye RUWA😅one LUV 💋

PAGE 29

Amrah tana kallon yaron tace, "Nifa Mama WALLAHI nafiso asakashi ya sauwak'e man, tunda har gaskiya ta fito nasan Salis zai dawo gareni idan yaji komi, kinga shikenan hankalinmu zai kwanta."

Zuwaira tayi shiru tana Nazari sannan tace, "Hakane fa WALLAHI kin kawo shawara lalle azimun haka ma za'ayi, don tun farko in banda yayi muna bak'in ciki da yanzu kina cen gidanshi kina jin dadinki, abinci sai wanda kika ga damar ci sutura sai wadda kike so ki d'aura, amman da yake shi d'in mugu ne gashinan ya maidaki k'aramar bazawara ai WALLAHI sai inda k'arfina ya kare bari goben dai tayi muje muji hukuncin da za'a yanke, don nifa ganin nikeyi kamar Asabe zata iya saka mijinta ya ba Nazir d'in gaskiya fa" Amrah tace "A'a bazata yi haka ba gaskiya Mama saboda Aunty tana sonmu WALLAHI baki ga yanda tayi ta dawainiya dani ba gidan Malam Nura"

Zuwaira tayi wani mere sannan tace

"To ai na dole ne tunda ita tayi jagorancin auren, yanzu ba ga shi shi d'an iskan Malamin ba tunda aka tashi daga kotun ko kallonmu bai sake yi ba, ina gsninshi ya haye acab'a ya tafiyarshi ai bari yakeyi idan an kashe auren naga k'afarshi a k'ofar gidannan sai ya rena kanshi

shima don ubanshi"

Amrah tayi shiru ba tareda tace k'anzil ba don bata jin dad'in yanda Mamarta take aibata shi, don tunda take dashi bai tab'a musguna mata ba kullum gurinshi yasakata farin ciki.

Koda safiya ta waye tun kafin Aunty Asabe tazo suka shirya duka aka yiwa yaro wankanshi tsaf aka shiryashi sai k'amshi yakeyi, Aunty tana zuwa ba b'ata lokaci suka garzaya kotu inda suka taradda mutane tsilla tsilla ko taruwa ma ba'ayi ba sosai saboda sakkon da suka yi, aiko suna nan bakin harabar kotun sai ga Nazir ya danno kan motarshi, sai da yaje daf dasu sannan yayi parking ya fito cikin wata arniyar shadda sai k'yalli takeyi, yana kai kallonshi garesu ya d'age kai sama ya jingina a jikin motarshi tareda fiddo wayarshi da ake ta kiranshi tana k'ara, yana ganin mai kiran ya fad'ad'a fara'arshi yace, "Amaryar Nazir ya dai?" cen yayi shiru yana dariya sannan yace, "Saurin me kikeyi sati d'aya ne rak ya rage muna fa nida ke mu zamo abu d'aya, OK to yayi naji dai yanzu dai sai ki shirya tarbona da na k'are abunda nake yi wurinki zanzo, yawwa tawa ko kefa ki kula man da kanki nagode sai kin jini bye bye muah" ya k'are maganar tareda wani shu'umin murmushi.

Ba Amrah ba harta Zuwaira da Aunty sunji haushinshi sosai saboda yanda ya saki jiki ko kunya baya ji agabansu yana wannan rashin kunya, Amrah kam tun kallon da tayi masa na farko ta kawar da kai gefe saboda zuciyarta da tayi wani bala'in bugawa, don ba k'aramin kyau yayi mata a ido ba haka ma har ga ALLAH ita tasan tayi kad'an tace Nazir baya da abunda take so, kawai dai don tun farko bata yardar wa Zuciyarta cewa zata so shi d'in ba ne shiyasa, sannan abu na biyu gefen zuciyarta cike yake da jin zafin wayar da ya k'are, sai dai tayi k'ok'arin cire abun aranta saboda bata san me yasa ma ta damu kanta abanza ba, don ita dai tasan ba sonshi take yi ba to me zaisa taji wani kishinshi don yayi waya da wata?.

Suna nan wurin Sai ga Jamilu abokin Nazir ya shigo shima, ya nufi inda yake da sauri sai wani annurin farin ciki ke sauka akan fuskarshi, wanda ni dai na kasa gano ko na minene.

Zuwaira kam ta bishi da kallo ta buga wani uban tsaki tace, "Aikin banza wa kare wanka komi dai abun Mutum sai ya sakar muna kurwa yau WALLAHI"

Suna nan har mutane suka fara cika harabar kotun aka bud'e d'akin shari'ar mutane suka yi ta tururuwar shiga suna zaunawa, Su Aunty ma suka sami wurin zaman suka zazzauna, inda zamansu ba wuya Alkalin ya shigo tareda 'yan rakiyarshi masu take masa baya.

Bayan an gabatarda al'adar tsarin kotun ne aka sake kiran Nazir da Zuwaira suka fiffito suka tsaya kamar jiya, Alkali ya fara jawabi kamar haka, "A jiya muna cikin shariarku ne lokaci yayi muna halin nasa, Alhmdllh gashi yau mun sake dawowa a zama na biyu wanda muke fatar ya zama na k'arshe , saboda haka Yanzu kai Nazir jiya mun tsaya inda kake bamu labarin yanda kayi ta bin hanyoyi kana kashewa yarinyar Zuwaira Aure, har inda ka gangaro akan mijinta na yanzu da take aure, wanda kayi ik'irarin cewa yaron da ta haifarwa mijinnata danka ne ba danshi ba,to ko zaka iya yi muna bayanin yanda kayi har kayiwa Yarinyar cikin yaron?tunda dai

naga ba'a gidanka take ba to ta wace hanya kayi mata cikin?????"

Nazir duk da yaji kunyar tambayar amman haka ya cije ba tareda ya kalli kowa ba ya fara bayani dalla dalla kamar haka,

"Kamar yanda na sanar daku cewa akwai turaren da nike shafawa in zama siffar duk wanda akayi aikin akanshi, to haka ne shi na shafa tun tana da kwana d'aya a gidan, bayan mijin bugin ya fito gidan a gabana ya wuce sai da na tabbatar ya shige makarantar da yake karantarwar niko naje nayo cefane sannan na shafa turaren na shiga gidan, inda a gaggauce na karb'i budurcinta nayi wanka sannan na fice, to tun daga ranar na dinga zuwa lokaci bayan lokaci ina kusantarta har lokacin da na had'u da wata k'anwar Nura d'in, ganin kamar ta gano bashi bane yasa na yi mata kwakkwaran gargad'i nace idan ta sake wani yaji maganar sai ta mutu, tun daga ranar ban koma ba sai ranar da ta ke asibiti tana laulayin cikin inda anan ma na sake had'uwa da k'anwar Nura d'in tana yiman wani kallo, sai kuma bayan cikina ya girma ne na yanke shawarar na sanar da Mijin bugin nata akan cewa fa ciki nawa ne shine na rubuta takarda nasa wani yaro ya tsallaka ya ajiye masu a k'ofar d'aki, to daga nan kuma na turo mata text d'in cewa Ranar da duk ta haifu a ranar zanzo karb'ar yarona, sannan akwai wasu pic's d'in da nayi muna nida ita watarana bayan mun k'are raya sunnah da ita tayi kwana, to sai na saka su a envelop na baiwa wani dalibinshi shi mijin bugin nata ya kai masa a makaranta, ina lab'e har aka kaimasa a gabana ya bud'e photunan hankalinshi a tashe yayi gidan Aunty Asabe ya nuna mata, ina nan zaune abuna k'ofar gidan naga an fito da ita Matar tawa jini yana sauka a kafafunta aka sakata Napep, nima nabi bayansu hankali a tashe har asibitin, naji ana neman jinin da za'a saka mata suna barin asibitin nace da wani likita Matata ce adibi nawa jinin yana yi asaka mata, kasancewar rayuwarta tana cikin had'ari a wannan lokacin yasa basu tsaya wani dogon binciken gaskiyar zancena ba ana gwadawa aka gano zaiyi aka d'ibi gora d'aya aka saka mata, haka ma ko ranar da ta haifu dani aka je asibitin saboda a kullum ina unguwarsu ina rangadin jiran ranar da za'a haife mani cikin , aiko bayan naga ta haifunne cikin dare na d'auke yarona kai tsaye na kaiwa Mahaifiyata shi, sannan nayi mata bayanin gaskiyar zancen cewa ban saki Amrah ba, don wannan yaron ma Yarona ne da ta haifa man, Mahaifiyata duk da bata son tarayyata da Amrah amman taji dad'in ganin yaron, tayi man fad'a sosai sannan ta bani umurnin in maida mata da d'anta ta ci gaba da shayar dashi, don na nuna mata nazo dashi kenan zan baiwa Jamila K'anwata shi taci gaba da shayar dashi don itama sabuwar haifuwa tayi da nufina na k'in maidowa Amrah shi, amman kasancewarta Inna Uwa ce tagari yasa ta nuna man hakan bai dace ba in maidashi kuma ta amince in yi duk yanda zanyi in dawo da Matata hannuna,lokacin da na kira Aunty nace suzo ga yaron koda suka zo bayan sun karbeshi ne Zuwaira ta tayi kururuwa ta tara man Jama'a suka yi ta jibgata har suka ji man rauni, saboda tace dasu wai sato yaron nayi niko shiyasa zuciya ta debeni bayan anyi sunan yarona Umar na garzayo kotu DOMIN ta k'watar man hak'k'ina ga Zuwaira, sannan kuma abani Matata da yarona in tafi dasu."

Daga cen nesa naji wani yace, "Agaisheka Namijin Duniya" aiko daganan kotun ta harmutse da hayaniya inda mafi akasarin mutane sai jinjina masa sukeyi don ba k'aramar jarumta yayi ba.

Kuyi manage banda caji😢

Akafta 🏃‍♀️

D/Auta ce 👌

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Ku saki jiki ku dinga zubo ruwan comment's saboda inji dad'in murzo maku typing😝

PAGE 30

Alkali ya buga gudumarshi har sau uku sannan mutane suka shiga taitayinsu, inda ya kalli Nazir yace, "Kana da tabbacin cewa mijin bugin nata da ka kira bai tab'a kusantar ba kenan?" Nazir ya gyara tsayuwarshi yace, "Bai tab'a kusantar ba ranka ya dad'e saboda akwai wata aljana da muka tanadar masa, duk lokacin da yake k'ok'arin saduwa da ita sai ta bugar dashi tazo masa da siffar ita Amrah, yayi ta saduwa da ita shiyasa baya kawo cewa ba ita d'in ce ya ke kusanta ba."

Amrah kam tana jin wannan bayanin zuciyarta ta lula tunanin halin da Malam Nuran yake kasancewa idan har yazo kusantarta, aranta tace

"Lalle kai shu'umi ne WALLAHI don muguntarka akaina tayi yawa, don haka WALLAHI nikam bazan iya rayuwar aure da kai ba, ko ka k'i ko ka so sai ka rabu dani d'an renin hankali"

Alkali ya yayi shiru na d'an lokaci sannan yace, "Na gamsu da jawabinka duka amman duk da haka dole ne mu yi ma yaron da kai awon DNA saboda kowa ya gamsu cewa yaronka ne daga jikinka ya fito, saboda haka za'a d'ibi jininka da na yaron aje a auno su yanzunnan, don haka zamu ci gaba da saurarar wata wata shari'a kafin likitan da zai je awon ya dawo" Aiko Wani babban likitan da aka gayyato yazo ya d'ibi jinin Nazir, sannan Aunty ta kawo Umar shima aka zuki nashi jinin.

Alkali ya basu umurnin suje su zauna sannan aka fara wata shari'ar bayan ank'are ne sai aka sake fito da Nazir da Zuwaira, sannan aka yi umurni da Likitan ya kawo takardun gwajin jinin aka mik'awa Alkalin, Alkali ya d'au lokaci yana nazarin takardun sannan ya d'ago fuskarshi ya kalli mutane tareda d'aga takardun sama yace,

"Takardun gwajin jinin Nazir da Umar sun tabbatar da cewa Nazir shine Ya haifi Umar kuma ta jininshi ya fito, saboda haka kotu ta gamsu da cewa Amrah matar Nazir ce Kuma Umar danshi ne, saboda kwararan shedun da suka gabata akan wanzuwar aurensu har ma da na samuwar d'anshi, saboda haka kotu ta aminta da abaiwa Nazir Matarshi da d'anshi, amman don baiwa kowa hak'k'inshi muna buk'atar ganin Amrah Matar Nazir kuma Mahaifiyar Umar akan ta fito itama muji ra'ayinta" Aiko duk kowa ya baza ido akan suga wannan Yarinya da ake ta rikicin akanta, sai ga Amrah ta fito nan kowa ya fara fad'in albarkacin bakinshi, inda wasu suke cewa _"ba banza ba ashe Uwar tayi ta damfarar d'an bawan ALLAH akanta, saboda taga 'yarta mai kyau ce shiyasa" wasu kuma suka dinga fad'in " dole ka susuce Nazir don wannan matar kadara ce" haka dai kowa yayita tofa albarkacin bakinshi har sai da aka natsar dasu sannan d'akin yayi tsit, Alkali ya kalli Amrah yace, "Kinji duk irin abubuwan da suka wakana a gabanki kinji Nazir shine Mijinki na gaskiya ba Nura ba, haka ma kinji shine Uban d'anki da kika haifa, haka ma kinji kotu ta aminta da ki koma gidanshi tareda danshi, saboda haka ke miye ra'ayinki akan wannan hukuncin da kotu ta yanke, shin kin Aminta da zama da Nazir d'in ko kuwa Aa? Kasancewar anyi maki auren tun baki mallaki hankalin Kanki ba kuma baki san minene auren ba awancen lokaci?"

Amrah ta share hawayen dake zubo mata ta kalli Nazir duk da kwarjinin da yayi mata a ido bai

hanata maka masa wata k'atuwar harara ba, sannan ta duk'ar da kanta tace, "Ni dai gaskiya ina buk'atar ya sauwak'e mani saboda ina da wanda nike son inyi zaman aure dashi ba shi ba"

Aiko tofin ala tsine ya fara tashi abakunan mutanen d'akin duka, yayin da wasu suka goyi bayanta akan yana da kyau ta zab'i wanda take so tunda yanzu ta mallaki hankalin kanta, shi kanshi Alkalin baiji dad'in wannan furuci da Amrah tayi ba, amman duk da haka sai da yace, "To kaji Nazir Matarka bata ra'ayin zama da kai don haka kotu zata yanka mata kud'in da zai isheka yin wani sabon auren ita kuma sai ka sauwak'e mata taje ta auri wanda takeso" Nazir yayi wani gajeren Murmushi yace, "Na amince ranka ya dad'e amman idan har zasu biyani kud'ina da na kashe mata tun tana k'arama har kawo wa yanzu to a shirye nike da in sauwak'e mata inje in auri wata matar"

Ba Zuwaira ba har ita kanta Amrah sai da Cikinta ya kad'a,don sun san idan ba su za'a siyar ba to ko basu da kud'in biyan Nazir, Alkali yayi shiru yana nazari sannan yayi gyaran murya yace, "A tsari irinna shari'a tunda har ka had'a shimfid'a d'aya da ita ka kusanceta, to duk abunda ka kashe mata ta ci su komi yawan dukiyar da ta lak'ume maka ko, sai dai yanzu tunda ita bata ra'ayin zama da kai to dole ne ta biyaka kud'in *huld'i* da zaka je ka yi wani auren matar da zata yi dai dai da ita a tsarin halitta, saboda haka zamuyi estimate tun daga kan Sadaki zuwa suturar da zata saka k'ananan hidimarka da ta Amaryar kafin ayi auren duka zamu had'asu waje d'aya, don haka Amrah tunda kince baki son zama da Nazir to zaki bashi kud'i Nera Miliyan biyu, haka ma Zuwaira sakamakon dukan da kika sa aka yiwa Nazir har yaji raunuka, zaki baiwa Nazir dubu d'ari biyar kud'in maganinshi da jinyar da yasha, don haka daga yau har zuwa ranar da zaku kawo kud'in Amrah Matar Nazir ce, kuma yana da ikonta kamar yanda kowane Namiji yake da iko akan Matarshi, don haka kuyi gaggawar had'o kud'in ku kawo don ku kaucewa duk wata fitina da zata taso daga baya, don ko yau kuka kawo kud'in Nazir kotu zata saka shi ya saketa, saboda haka shari'a ta k'are daga yanzu har zuwa lokacin da zaku hannunta kud'in a hannun kotu Bissalam"

Alkalin ya mik'e ya fice Zuwaira ta aza hannu a kai ta fasa kuka tace, "Ina zan samo miliyan biyu da dubu d'ari biyar yanzunnan?don ALLAH ayi muna sassauci akan wannan hukunci saboda yayi muna tsauri da yawa." Mutane da yawa sunji dad'in hukuncin sai dariyar k'eta suke yi mata, Aunty ta shiga lallashinta dak'yar ta fito da ita d'akin shari'ar, sai kururuwa takeyi akan rok'on atausaya asassafta mata ina zata samo wad'annan kudaden?, bayan sun fito ne Yaron Amrah dake goye abayan Aunty ya fara kuka, Aunty sai warar ido take yi ta ina zata ganin Amrah ta bata shi amman bata ganta ba, cikin rikicewa tace da Zuwaira "Aunty Ina Amrah ban fa ganta ba fa" Zuwaira ta zabura ta fara waige waigen ta ina zata hangota, sai dai kam duk iya bincikensu basu ga Amrah ba, Cikin rud'ewa Auntyn tace da Zuwaira,

"Aunty ko dai Nazir ya tafi da Matarshi?" Zuwaira tayi wani tsalle tace, "Kan Uba ai WALLAHI ko da ya d'ebowa kanshi ruwan dafa kanshi." Aiko ta fito harabar kotun ta tare Napep ta fad'a Aunty ta biyota itama ta shiga ta kai kallonta ga Zuwaira tace, "Ina zamu je kuma Aunty bayan bamu ga Amrah ba?" Zuwaira ta kalli k'eyar mai Napep d'in tace, "Kai ni police station." Aunty ta zaro ido jikinta yana rawa saboda firgici tace, "Me zaki yo acen Aunty bayan duk

hukuncin da kotun ta yanke a yanzu?ni dai gaskiya da kin jira in kira Nazir d'in muji har idan tana hannunshi, sannan ne zakiyi wani abu amman koshi da zaki hak'ura d'in har zuwa lokacin da zaki had'a kud'in da yafi, tunda dai kinji abunda aka ce matarsa ce kuma yana da iko da ita kamar yanda kowane miji yake iko da matarshi."

Zuwaira jikinta yana b'ari saboda masifa tace, "Zaka tafi ko in sauka in taro wani mai Napep d'in?" Sannan Mai Napep d'in yace "Haba Hajiya shawara fa naji kuna yi ina jira ne inji inda kuka kai k'arshen za'a kaiku, ni miye nawa a ciki da zaki taso man kamar zaki hadiyeni" Zuwaira tayi fit ta fito Napep d'in tareda ciyo kwalarshi ta fara zazzaga masa ruwan Masifa, aiko Mutane suka yo kansu ana bata hak'uri shikam da gaskiya tayi masa yawa kasa yimata komi yayi yana kallonta, har aka jata aka sakata wata Napep d'in sunzo zasu wuce ta gabanshi yace, "ALLAH ya had'aki da daidai ke"

Zuwaira har ta yunk'ura zata fito Aunty ta rik'eta suka nufi wata police station d'in ta d'ebo 'yansandan, kasancewar tasan unguwar da yake gini ta nufi unguwar kai tsaye, sai dai tayi ta bulayin neman gidan da 'yan sandan ta kasa ganewa, kasancewarta sabuwar unguwa kuma ta masu abin shiyasa ba kowa yasan sunan d'an uwanshi ba, cikin takaici dole suka juya ga yaron sai kuka yake yi, suna k'ok'arin fitowa unguwar ne sai ga Nazir ya doso da motarshi, yana ganin zuwaira da motar 'yan sandan wata dariya tazo masa ba shiri, aiko yayi parking da sauri ya fito Zuwaira tana hangoshi ta diro Napep d'in tana nunawa 'yansandan shi, cike da Mamaki wani d'an sanda ya fito yace da ita, "Shin ba shi bane aka k'are yi maku shari'a dashi yanzunnan?, ni WALLAHI dama nasan shine bazan zo ba tunda kowa ya sheda matarshi ce, ki jira idan har kin biya kud'in da aka ce ku bada yak'i sakin 'yar taki sai kizo mu zamuyi maki jagora akan gurfanar dashi a gaban kotu ya bata takardar sakinta dole, saboda haka ke kawo yaronnan." yace da Aunty Asabe kai tsaye ta kwanto yaron daga bayanta ta mik'a masa shi, ya karbeshi sai da yayi masa kiss yace,

"Fine boy" sannan ya mik'awa Nazir shi yace "je. Ka kaishi wajen Mamarshi ta bashi abincinsa yunwa yake ji" cike da tsantsar farin ciki Nazir ya zura hannu ya karb'i yaron yace,

"Nagode Sir ALLAH ya k'ara kare muna ku" ya juyo ya kalli Zuwaira yana murmushin mugunta mai cike da cin nasara ya shige motarshi da danshi ya juya motarshi ya fice unguwar aguje.

Cikin tsananin takaici Zuwaira ta cakumo d'an sandan tana surfa masa zagi, aiko ya saki jiki tareda sauran 'yan sandan suka yi ta zabgarta da buloli, sannan suka jefata motarsu suka tafi da ita office d'insu suka jefata bayan sel.

Aunty kam gaba d'aya rud'ewa tayi ta fara kiran Mijinta tana sanar dashi abunda yake faruwa.

Tsuntsun da yaja ruwa..... 😝😝😝😝😝😝

Akafta team Zuwais😸🏃‍♀️

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Masu comment's ina godiya sosai nagode da addu'o'inku gareni Allah ya bar zumunci🤝

PAGE 31

Ta fad'a Napep d'in suka nufi police station d'in wanda koda taje ta taradda megidanta har ya rigata kaiwa, Zuwaira taci albarkacin Alkali yusha'u domin kuwa ba tareda an tsaya wani dogon turanci ba ta samu aka fiddota, ido sunyi zuru zuru saboda tashin hankalin da take ciki, sannan ya kwaso su ya nufi gidan Zuwaira ya ajiyeta, shima ya shigo gidan ya zauna inda a fakaice yayi ta nusar da ita akan abunda tayi bata kyauta ba, ya gargadeta sosai akan hakan ya zamo mata izna gobe idan ta tashi yanke hukunci tayi dogon nazarin tunanin abunda ya dace kafin

tayi, sannan ya k'ara da cewa,

"Idan har kina son Amrah ta dawo hannunki to kiyi k'ok'arin biyan kud'in da aka ce ki bada nan da kwana Uku, don gudun kija lokaci hae shi Nazir d'in ya bijirewa umurnin kotu, ni zan koma saboda akwai aikin da nikeyi na katse shi na fito ALLAH ya kawo sauk'i cikin lamarin"

Sannan ya mik'e ya kalli Aunty yace "ke zo mu je in kin tashi in ajiyeki gida sannan in wuce" Aunty ta kalli fuskar Zuwaira taga yanda fuskarta ta kumbure cikin d'an k'ank'anin lokaci saboda marukan da tasha hannu 'yan sanda, duk da bata goyon bayanta amman abu ga d'an uwa ta tausaya mata sosai, amman tana son ta bata shawara akan matsalar kuma idan ta wuce wannan lokacin Zuciyarta ta bata yanda Zuwaira take komai ma zata iya aikatawa domin k'ok'arinta na ganin 'yarta ta dawo hannunta, shiyasa ta biyoshi jiki a sanyaye suka tsaya corridor'n gidan ta kalleshi a marairaice tace, "Aunty Zuwaira fa tana cikin halin da take so a lallasheta a tausar da zuciyarta, don ALLAH ka barni zuwa dare sai kazo ka daukeni kaji Maigida?" ta k'are maganar cikin marairaicewa Alkali Yusha'u ya kalleta dakyau yace, "A gaskiya bana goyon bayan 'yar uwarki don gaskiya ta fito ko ta ina bata da gaskiya, saboda haka da zaki cire kanki cikin matsalarsu da kin taimaki kanki."

Aunty ta ri'ko hannunshi tace, "Yanzu idan na tafi na barta cikin wannan hali wa kake tsammanin zai zo ya k'ara nusar da ita abunda ya dace?, kana fa gani dangin Baban Amrah tun a kotu ko kallonmu basu sake yi ba suka tafiyarsu abinsu, wanda hakan ya nuna cewa sun zare hannunsu a cikin lamarin, gashi mu ba wasu 'yan uwa ne damu ba agarinnan ballantana su zo mu had'a kai muyi shawarar abunda ya dace plss maigida don ALLAH ka barni in k'arasa samun ladarnan, don ina son in nusar da ita sosai akan ta bar Amrah tayi zaman aurenta."

Dak'yar Aunty ta shawo kanshi ya amince sannan ta rakashi tana ci gaba da yimasa godiya akan hak'uri tareda d'awainiyar da yakeyi da ita akan lamarin 'yar uwar tata da 'yarta.

Sannan ya tafi ta dawo gidan ta taradda Zuwaira zaune inda suka barta har lokacin, don ko motsin kirki ta kasa yi saboda zuciyarta da ta Lula dogon nazarin ta inda zata samo kud'in da zata biya Nazir ta k'wato yarta ta dawo hannunta,har Auntyn ta zauna bata masan ta dawo ba sai da ta kira sunanta har sau biyu sannan ne ta dawo hayyacinta, ta kai kallonta ga Aunty ranta a had'e fuskarta a murtuk'e tace, "Asabe ki tashi kije gida don ALLAH nagode da kulawar da kike yimani, tunda har Mijinki baiji kunyar fad'o mani wad'annan manyan kud'in ba, duk da ganin zumuncin dake tsakanina dake, to banga amfanin zamanki tare da mu ba don haka don ALLAH ki zare hannunki cikin lamarinnan nagode da dawainiyarki, don WALLAHI ko fuskarki na k'alla na tuno irin zuzurutun kud'in da mijinki ya lafta muna don baya goyon bayanmu, sai naji bak'in cikin saninki ma balle ki zauna tareda ni kina yiman kilinbibin banza alhali kuma daga ke har mijin naki nasan baku tare damu, tunda ko baku goyon bayanmu to zaman me zaki zo kiyi man anan?, ki tashi kije kawai nagode bana buk'atar ki sake shiga cikin wannan rigima ki barni inji da kaina da 'yata, kud'i kuma tunda har ya furta in badasu a gaban kowa to ko zan tafi tsirara sai na biya kudinnan cikin kwana biyu rak kafin ma ayi ukun da yake fad'a, don haka sawunki a likkafa ki tashi ki tafi kawai bana son ganinki WALLAHI, kuma ki sanar dashi cewa da ya barni a hannun 'yansandan nafi farin ciki so dubu da wannan hukuncin banza da ya yanke

muna, don haka WALLAHI ban yafewa sanin da yayi mani ba ALLAH sai ya isar man akanshi ke har kema d'in don nasan wannan duk shawararki ce, saboda a ganinki bana iya biyan kud'in shiyasa kika ce ya tsaurara kud'in da yawa haka ko? don kawai kina son Nazir yayi galaba akanmu ya zauna da Amrah kamar yanda kike muradi, to WALLAHI kisani in dai har ina numfashi a doron k'asa Amrah bazata yi zaman aure da Nazir ba, dole ne sai ta auri wanda take so." Aunty kam gaba d'aya notukan kanta kwancewa suka yi da kalaman Zuwaira, shiyasa ta kasa furta komai sai binta take YI da kallo, Zuwaira ta mik'e zata shiga d'aki sai ga Abbaci k'anin Amrah ya shigo, Zuwaira ta kalkeshi tace, "Yawwa Abba je ka samo mani dillalin da zai siyi gidannan yanzunnan"
Abbaci ya kalleta sakato yace, "Haba Mama yanzu kuma wani mataki kike so ki d'auka kenan?, ni dai WALLAHI gaskiya bana son ki raba Yaya Nazir da Aunty Amrah, ki kyalesu don ALLAH suyi zaman aurensu tunda har gaskiya ta fito fil..... " kafin ya k'arasa maganar bakinshi yaji saukar marin Zuwaira a kumatunshi, cike da mamaki ya dafe inda ta mareshin yace, "WALLAHI Mama ko zaki kasheni SAI na fad'a maki gaskiya, ki dubi fa irin wahalar da yaya Nazir yayi damu tamkar shi ya haifemu, tunda gaskiya ta fito kuma kinji da kanki Babanmu fa ya d'aura auren tun daranshi, me zai hana ayi hak'uri da komi a cika masa gurinshi na alkhairi da yayi kafin ya bar duniya?, WALLAHI gaskiya muddin kika raba aurennan baki kyautawa babanmu ba." Yana k'are fad'ar maganganun ya yi hanyar fita yana sharar hawaye saboda har ga ALLAH baya son a hanawa Nazir Amrah, yafi so abarsu suyi aurensu ko don a cikawa Mahaifinsu gurinshi ayi masa biyayya duk da baya raye.

Har ya kai bakin k'ofar fita cikin tsananin fushi Zuwaira ta d'aga murya ta kirashi, ya waigo ba tareda ya juyo ba hawayenshi sai zubowa sukeyi, ba tareda ta damu da kukan da taga yana yi ba tace, "Karb'i wayar nan ka dubo mani sunan Salis?" cike da mamaki cikin kuka yace "Wane Salis?" ta k'ara tsuke fuska kai tsaye tace "Saurayin Amrah" ba Abbaci kawai ba har Aunty dake kallonsu sai da ta zaro ido Abban yace, "Me zakiyi da numbarshi kuma yanzu Mama?"

Cikin tsawa tace. "Ubanka zanyi bazaka dubo man numbar bane don ubanka?" Abba yazo ya karb'i wayar ya lalubo mata numbar ya mik'a mata sannan ya fice ranshi a b'ace zuciyarshi cike da takaici.

Aiko ba b'ata lokaci ta danna masa kira har ta tsinke bai d'auka ba, tayi kira yakai shidda kafin ya d'aga jikinta yana rawa ta fara cewa, "Salis ina kwana nice mamar Amrah ka gane ni ko?"

Daga cen gefenshi cike da jin haushin tada shi daga baccin da akayi yace, "Bangane ki ba" da sauri tace, "Amrah masoyiyarka fa wadda kaso ka aura ALLAH bai nufa ba" sannan yace, "Oh sannu Mama barka da rana dafatar kowa lafiya?"

Cike da jin dad'i Zuwaira tace "Lafiya lau Salis d'an albarka yawwa nace don ALLAH idan ba damuwa ina son ganinka ko ka fad'a man inda zan zo in sameka akwai maganar da zamu yi"

Salis yace "Ok ba damuwa bari ni zan zo in sameki gida" cikin tsantsar farin ciki tace,

"Yawwa yaron kirki sai kazo ina jiranka ALLAH dai ya biyaka da gidan aljannah sannunka kaji sai ka k'araso" sannan suka YI sallama ta kashe wayar cikin tsananin jin dad'i, don jin takeyi tamkar ma gurinta ya cika duk wata damuwa da take ciki ta kau saboda hangowar da takeyi da yazo shikenan ita matsalarsu ta kau.

Ta shigewarta d'aki tana 'yan wak'e wak'enta na murna, Aunty ta bi bayanta da kallo ta yunk'ura jiki ba kuzari ta je k'ofar d'akin ta tsaya tareda yaye labulen tace, "Ni zan wuce Aunty kuma nagode da abunda kika yimani, amman duk da haka banyi k'asa a Gwiwa ba ina baki shawarar kada ki raba Nazir da Amrah, don WALLAHI matuk'ar kika rabasu sai kinyi danasanin abunda kika aikata, komi daren dad'ewa ranar zata zo kuma ina da tabbacin zaki tuno abunda na fad'a maki" ta saki labulen ta fice gidan Zuwaira ta biyota har waje tana jifarta da miyagun kalamai, Aunty tak'i kulata abin hawanta kawai ta tare ta shige ta tafiyarta abinta tareda cin alwashin ba zata sake zuwa gidan ba, balle har ta shiga sabgar Zuwaira ko 'yarta.

***

Amrah Kam tana gidan Jamila kwance akan gadonta tana ta sharar barcinta, saboda tunda Nazir ya mamayeta ya shak'a mata wani hankacif bata koma sanin inda kanta yake ba, har Nazir yazo da jaririn ya baiwa Jamila ya fice gidan, kai tsaye ya nufi gidanshi inda ya mayar da Inna tun lokacin da ya kammala gininshi, don daman cen da sashenta a cikin gidan tun farko, cike da wani farin cikin da ya dad'e bai wanzu akan fuskarshi ba yayi sallama d'akin Inna, tun shigowarshi Inna ta bishi da kallo saboda yanayin da ta ganshi a ciki yasa taji dad'i aranta itama, don bata raba d'ayan biyun akan cewa yayi nasara ga shari'ar da yake yi da su Zuwaira, bayan ya zauna ya tank'washe kafafuwa bakinshi yak'i rufuwa saboda murnar da yake ciki kai tsaye yace da Inna,

"Alhmdllh Inna yau dai komai yazo k'arshe nayi nasara Amrah ta dawo hannuna" Inna ta bishi da kallo cikin jin dad'in da iyakacinshi kan fuskarta tana jan carbinta tace, "Na tayaka murna Ubangiji ALLAH ya baka ikon yin adalci a tsakanin Matanka." Nazir yace "Ameen" sannan ya b'ata fuska yace,

"Inna ni dai WALLAHI in banda Kada Sadiya taga kamar na yaudareta da na fasa aurennan gaskiya, don bana son in had'asu su zo su caja man kai abanza." Inna ta bishi da kallo tayi d'an gajeren Murmushi mai cike da ma'anoni tace, "Nazir!!!!" yace "Na'am Inna" ta sake fad'in "Nazir ka shiga hankalinka ka dawo cikin nutsuwarka kada kayi gangancin barin son Amrahtu ya rufe maka ido ka kasa hango gabanka da bayanka, WALLAHI ka kiyayi k'ara saka kanka a matsala saboda macen da batasan darajarka ba, ka yiwa kanka karatun tanutsu ka fahimci duniya da yanda ake zama cikinta, kada kayi gangancin rabuwa da macen da take sonka tsakani da ALLAH akan wadda kai kanka baka da tabbas akanta, ko bayan raina ina so ka tuno da wannan maganar da nike fad'a maka a yanzu, kada kaga cewa na aminta da ka je ka farauto matarka ka d'auka cewa tunda ka sameta shikenan matsalar ka ta kau, to bari kaji in gaya maka ka fa kashe maciji ne amman baka sare kanshi ba, don kuwa muddin Zuwaira ce ta Haifi Amrahtu matuk'ar bata shiryu ba to bazaka tab'a jin dad'in zama da 'yarta ba, don ina da

tabbacin yanzu haka tana cen cike da jin zafinka saboda rabata da 'yarta da kayi, kuma nasan bazata zura ido tayi kallon zaman aurenku lami lafiya kai da Amrahtu ba, don kuwa sai taga abunda ya turewa buzu nad'i, saboda haka ka shiryawa hukuncin da zai biyo baya daga yanzu zuwa lokacin da zata waiwayo kanka, don haka ka iya takunka ka b'oye son nan da kake yiwa 'yarta kada ka yarda kayi saken da zaisa ka dawo kana cizon hannu, kuma kada ka manta da maganata da nayi ta nanatawa a kullum akan ban yafe maka nonona da kasha ba matuk'ar ka k'ara zuwa wurin wani boka ko malam akan rayuwar Amrahtu, na nanata banyafe maka ba Nazir idan har ka sake kauce hanya akan Amrahtu ko akan wani cen daban ko wata koma minene ka barwa ALLAH shi zai yimaka mafita akan komai, sannan kayita istigfari sosai da sosai akan sab'on da ka tafka a baya saboda soyayyar banza marar tabbas, aurenka da Sadiya kuma yana nan yanda aka saka rana don haka kaje ka ci gaba da shirye shiryenka"

Nazir ya sauke ajiyar zuciya mai k'arfi yace,

"Inna naji dad'in shawrwarinki kuma insha ALLAH zan bisu kamar yanda kike so, kuma nayi maki alk'awali ko bayan ranki bazan tab'a zuwa wajen boka ko wani malami ba, ko wannan da nayi WALLAHI Inna bada son raina ba don dai kawai bani da wata mafita ne kawai shiyasa, amman ki yafe mani WALLAHI bazan koma aikata irin hakan ba insha ALLAHU." Inna cikin jin dad'i tace "Masha ALLAH Ubangiji ALLAH ya k'ara kare mani kai gabanka da bayanka da sharrin mutum da sharrin shed'an da sharrin wani abun k'i komai kankantarshi." cike da jin dad'i Nazir yaketa fad'in "Ameen Ameen Inna" sannan ya nisa yace "Inna saura addu'a d'aya da nike buk'atar kiyi man" ta yi masa kallo mai cike da tambaya tace,

"Kamar wace kenan?" ya d'an sosa kai sannan yace, "Ina son kiyi mani addu'a akan ALLAH ya rage mani son Amrah a raina saboda WALLAHI Inna ni kaina haushin kaina nikeji, don da ace zan iya da na sauwak'e mata gaba d'aya ma na huta." Inna ta girgiza kanta tace,

"Kada kayi wannan ganganci ka jira su da kansu zasu nemi sakin, idan sun nema kada kayi shayin komi kayi masu abunda suke so Insha ALLAHU Allah bazai wofintar da son da kake mata abanza ba, yanzu ina ita Amrahtun?" cikin sanyin jiki yace
"Tana gidan Jamila" tace to ka d'aukota ka kawota gidannan sannan kaje ka nemo mata duk abunda kasan mace tana buk'ata a d'akin mijinta dai dai k'arfinka" sannan ta tashi taje ta d'auko wani k'ullin leda ta bud'e sai ga kud'i 'yan dubu dubu ta mik'a masa tace dashi ya kidanya, cike da mamaki ya lissafasu dubu d'ari da goma sha biyar, tayi d'an gajeren murmushi tace, "Kaje da su ka k'ara ka yo mata siyayyar."

Hmmmm Inna ta sani sanyin jiki😢🤔

Akafta😫

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Wannan page naki ne sukutum k'anwata BALKISU GARKUWA(UMMI)kiyi yanda kike so👍🏻

Specal tanks to u all my fan's💋💋💋 musamman irinsu

My momma Mum 3full H
D'iyata Ummu Muh'd
Daughter Rufaida, Nasmi d'iyata, Najida Aliyu, My Ambash
Ammin Sajida, Mmn ss, Amrah barrister
Ummu Arah (goribatyna), Mmn ibtisan, Aisha Sk, Balkisu kc, Zainab Garba, Sauwanatu, Samira D'anjeka
Hannatu, Mardiyya
Mmn meenat, Murjanatu,
Ummu haidar, Nurse d'inmu fati Ghana,
Saratu Aliyu, Mmn Musaddaq, Ummu Emaan, Aunty Sady, Oum Twinz, Mmn laila, Rahila Abba, Mmn Abdul KO nawa ne dukanku daku nake😹
kai yasin kuna da yawa wadda bata Ji sunanta ba tayi hkr amman dukanku all ina gdy sosai da comments d'inki da addu'o'inku tnx alot my guys👍🏻

PAGE 32

NAZIR cike da mamaki yace, "Inna ni fa bana son mu wahalar da kanmu akan mutanen da basu da godiya ko kad'an, kuma har yanzu fa akwai sauran wata rigimar don haka ki bar kudinki kawai ni zanji da komi" Inna tayi shiru sannan tace

"Bana son ka takura kanka Naziru aure ba wasar yara bane, nasan kana buk'atar kud'i fiye da wad'annan, idan ma zaman na Amrahtu bai yiyu ba ai zaka yi hidimar auren Sadiya, don haka kaje dasu ka k'ara kayi komi a wadace ALLAH ya shige muna gaba" Nazir yace, "Ameen Inna amman dai ki ajiye kud'in a hannunki idan har buk'atarsu ta taso zan yi maki magana" yana k'are maganar ya mik'a mata kud'in ya mik'e, Inna ta bishi da kallo tace,, "Kada ka biyeta kuyi tashin hankali don ALLAH nasanka da saurin fushi, ka bi komi a hankali har muga abunda ALLAH zai yi" ya tabbatar mata bazai biye ta ba sannan ya fice gidan zuwa gidan Jamila zuciyarshi cike da fargabar haduwarshi da ita, don yasan ba k'aramin rikici ne zasu yi ba.

Amrah kam cikin Bacci ta jiyo kukan Umar har tsakiyar kanta, tayi firgigit ta tashi sannan ta fara wara ido tana son ta gano a'ina ne take, sai dai kash ta kasa gane d'akin zuciyarta cike da rud'u ta sauko gadon, tana k'ok'arin fita d'akin ne aka turo k'ofar d'akin za'a shigo dole taja baya domin ta baiwa mai shigowar damar shigowa, aiko sai gashi taga Jamila rungume da Umar d'inta fuska a had'e ba walwala KO kad'an, Amrah ta kasa karb'ar yaron cike da fargaba tabi Jamilar da kallo, tuno abunda ya faru a kotu yasa taji Zuciyarta ta buga Dam! Dam! Domin, kuwa idan har ba zuciyarta k'arya ta raya mata ba to tana zaton ta dawo hannun Nazir, cike da tsananin tashin hankali tace da Jamila,, "Ya akayi nazo nan? wa ya kawoni?" Jamila ta k'ara tsuke fuska tace,

"Karb'i yaron ki bashi abincinsa idan wanda ya kawokin yazo sai kiyi masa wad'annan tambayoyin, don nima ba abunda nasani akan hakan" Amrah tabi Jamila da kallo ranta a matuk'ar b'ace tace, "in yaron kuke buk'atar in barmaku WALLAHI zan baku, don bana son abunda zai k'ara had'ani daku saboda haka ki rik'e yaron idan yazo sai ki bashi, amman nikam WALLAHI bazan tab'a zama dashi ba" tana k'are maganar Jamila ta k'ara rungume yaron a jikinta cikin zafin rai tace, "Muma da anyi shawara damu WALLAHI bazamu tab'a had'a zuri'a daku ba, don gudun muje garin haife haifen mu haifowa kanmu wahala, wannan ma da ALLAH ya bada ya isa saboda muji dad'in biyarshi da addu'ar kariya, daga mugun hali irin na mutane masu butulci a rayuwa." Amrah duk da taji zafin maganar amman tayi banza da ita, ta zagaye ta gefenta ta fito d'akin ta nufi hanyar da take zaton itace zata kaita k'ofar gida, aiko jikinta sai rawa yake taje ta tab'a 'yar k'aramar k'ofar gate d'in gidan tajita a rufe, cikin rud'u ta k'ara kallon k'ofar daga sama aiko ta hango k'aton kwad'o, gaban ya fad'i ba shiri cike da masifa ta juya ta koma cikin gidan, inda ta taradda Jamila tana lallab'a Umar d'in akan yayi bacci, cikin d'aga murya Amrah tace,, "Zo ki bud'e mani k'ofa hajiya tun kafin inyi maki tataccen rashin mutunci WALLAHI." Jamila dake girgiza Umar d'in tayi banza da ita, 'yar Jaririyarta da ta haifa ta fara kuka saboda hargowar da Amrah tayi yasa ta tashi daga baccin da take yi, cikin k'arin takaici taje ta d'auko d'iyar ta zauna tana fara bata Nono, Amrah kam ganin kamar Wulak'anci

Jamilar take yi mata yasa tace, "Wai ku wadannani irin Mutane ne ku da baku da zuciya?, ina gudunku kuna k'ara lik'ewa WALLAHI ki tashi ki bud'e man k'ofa in fita ko in jaza maku masifa a cikin gidannan" Jamila tayi mata wani kallon matsa sakarai tace,

"Idan kin fasa ALLAH ya tsine maki, don kinyi masifa ai ba abun mamaki bane ko ba komi ai kin tsotsa a nono, kin ko ga ko kinyi baki da laifi tunda wuce gado wuya ne dashi." A zabure Amrah tayo kan Jamila zata kai mata mari, Jamila TAYI saurin rik'e hannunta sannan ta ajiye 'yar jaririyarta ta mik'e tsaye, tareda yiwa Amrah kallon tsana tace, "Kada kiyi gangancin da zaki rena kanki yanzunnan WALLAHI, don sai in nad'a maki shegen dukan da zan canza maki kamannu" Amrah tuno wacece Jamila tun suna 'yan yara yasa taji jikinta yayi sanyi, domin kuwa tasan karfinsu ba d'aya ba ko a cen baya don taci wuyar Jamilar sosai don ma Yaya Nazir yana shigar mata fad'an, cikin fushi Amrah ta k'wace hannunta ta nufi k'ofar gidan inda tun kafin ta isa taji ana ta kwankwasa k'ofar, Jamila ta biyo bayanta ta bud'e kwadon tareda bud'e k'ofar, Amrah tayi wuf ta fita ba shiri gabanta ya fad'i saboda Nazir d'in da ta gani tsaye, tayi kamar bata ganshi ba ta d'auke kanta zata wuce ta gabanshi yayi saurin shan gabanta fuska a had'e yace da ita, "Ina zaki je?" Amrah ta k'ara had'e fuska tace, "ina ruwanka da inda zanje?" Nazir yayi guntun murmushi yace, "Ni ko ke da ruwa don sai na baki umurnin kije sannan kije" ta d'ago kai tayi masa wani kallon wulak'anci tace,

"Wai kai wace irin zuciya ce da kai ne?nace bana sonka bana sonka ko ana aure dole ne?" Nazir yayi mata wani mugun kallo mai cike da takaici yace, "To ke halan wa ya fad'a maki cewa saboda ina sonki ne nak'i sakinki?to bari kiji ni kud'ina nike so su zo hannuna ba wai don ina son zaman auren da ke ba, ki jira ki gani idan an kawo man kud'in minti biyu bazan k'ara ba zan cillaki waje, don ni ko yanzu da kika ganni nan daga wajen Amaryata na fito, wadda zan aura kwana shida masu zuwa, wadda tasan so take kuma girmama k'auna don asanadinta nasan kaina, ashe cen baya ma shirmen yarinta ne yasa nasoki yanzu kam ALLAH ya yaye man duhun da ya mamaye man idanuwa, ya bani mace son kowa k'in wanda ya rasa budurwa shar ba irinki tsohuwar bazawara ba wadda mazaje da yawa suka yi ta aure suna sakowa, ni in banda k'addara ma mace irinki mai aure auren maza da yawa me zaisa ma in zauna da irinki?, don haka kada kiyi gangancin yiman rashin kunya yanzu in jibgeki WALLAHI, idan kina son ki tafi gida ki kira gidanku kice yanzu akawo man kud'in sai ki tafi abinki, amman yanzu kam yazama dole kiyi zaman kud'ina kuma kiyi man biyayya ko kina so ko bakya so" Amrah zuciyarta sai bugawa take yi saboda kamalam Nazir sun sun shigeta sosai, don sak'on da yake son isarwa gareta yayi tasiri a zuciyarta da gangar jikinta, nan take wasu hawaye masu zafi suka dingo kwaranyo mata afuska wani bayan wani cikin kuka tace

"Da ka sake ni d'in yanzu ai sannan ne zaka kirani da sunan bazawara, don haka in ka isa ka sauwak'e man yanzunnan in kama gabana, ai ba'a ce da kai ka zauna dani dole ba balle ka dinga jifata da miyagun kalamai, aure kuma idan ka tashi ka aure jaririya haifuwar yau ni ba abunda ya dameni da wani aurenka cen, kai ka auro mata dubu ma in zaka iya nidai kawai ka sallameni in kama gabana" Nazir yayi wata dariyar tura haushi yace da Jamila ta kawo masa Yaron, Amrah tana jin haka tayi wuf zata tsere yayi saurin damk'oota, cikin zafin nama ya turata motar ya shiga yamutsata son ranshi, duk da tirjiyar da takeyi bai hanashi cafko bakinta ba sai

da ya tabbatar da tayi laushi sannan ya k'yaleta, saboda ganin Jamila a tsaye da yaron a hannunta ya fito ya karb'i yaron ya d'ora mata shi akan cinyarta, sannan ya zagaya yaja motar da k'arfi suka bar gidan ya nufi gidanshi da ita.

Akafta 👌🏻

D/Auta ce🤝🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

33

Zuwaira kam sai tsumayin zuwan Salis take zuciyarta cike da d'okin zuwanshi, saboda jin da takeyi tamkar da yazo shikenan matsalarta ta kau, aiko minti sha biyar a tsakanin wayarsu sai ga sallamarshi k'ofar gidan, jikinta yana rawa ta d'auko wata sabuwar tabarma ta shinfid'a sannan tayi waje wurin yi masa iso, cikin mutunta juna suka gaisa sannan tace dashi ya shigo daga ciki, bayan ya sami gefen tabarmar ya zauna ne suka sake wata sabuwar gaisuwa, sannan zuwaira ta gyara zamanta tace,, "Kayi hak'uri na tadoka da rana tsaka Wallahi wani

rikici ne ya kunno muna kai dangane da rayuwar Amrah, ina jin ai bazaka rasa jin shari'ar da mukayi da wani d'an iskan yaro ba?" salis yace "Eh najiya mama dafatar dai komi yayi normal"

Zuwaira tayi wani mere tace, "Hmmm aini cutata akayi Salisu ba shari'ar adalci aka yi muna ba, shiyasa nike son ko ta halin kaka in raba Amrah da auren wannan Matsiyacin, don idan ba haka nayi ba zai ga kamar yaci riba akan cutar da rayuwarta da yayi har ma da taka, yanzu ka duba fa ashe shine yayi maka asiri ka fasa auren Amrah don kawai baya tsoron ALLAH, shiyasa naci alwashin tunda har kana sonta niko bazan bari ta zauna dashi ba dole ne ta dawo hannunka, don kai take so kuma dakai ta dace ba shi ba, haka ma nasan kaima kana sonta don haka nike son mu had'a k'arfi da k'arfe da kai mu biyasu kud'insu ya bata sallamarta ta dawo gida." Salis yayi shiru yana nazari sannan yace,, "Mama da dai kin barta tayi zaman aurenta da yafi sauk'i, saboda ina jin tsoron kuma muzo muyi auren ya k'ara biyomu da wani mugun asirin." Zuwaira tayi saurin fad'in,, "Ai WALLAHI bai isa ba ko wannan da yayi don bansan dashi bane da tuni nayiwa tufkar hanci, indai kana sonta to kada kaji komi ka bar komi a hannuna, ka dai kawo rabin kud'in ni in bada rabi, saboda miliyan biyu ne mugun alkalin ya saka muna sai wata banzar dubu d'ari biyar da yace wai in bada saboda kawai an dake shi akan ya sacewa Amrah jariei."

Salis yayi ajiyar zuciya sannan yace,,, " Kiyi hak'uri Mama zan baki abunda Allah ya horemani ko ba yawa kiyi maneji dasu, saboda WALLAHI ko wata biyu ban rufa da yin aurena ba, gashi na kashi kud'i sosai a auren kuma ma idan har Hajiyata taji bazata bari nayi wani auren yanzu ba, saboda ganin ban dad'e da yin aurena ba."

Zuwaira cike da fad'uwar gaba tace

"Kamar nawa zaka badawa? don insan abunda zan cika" Salis yayi 'yar dariya ya saka hannu aljihu ya ciro bandur na 1k ya ajiye mata sannan yace, "Ga abunda ALLAH ya hore sai kiyi hak'uri dasu ni zan tafi ALLAH yasa mu dace" yana k'are maganar ya mike tsaye yana saka talkaminshi, Zuwaira cike da jin haushinshi ta duk'a ta d'auko kud'in sannan tace,, "Ai ba komi sai in saida gidannan tunda har babu wata hanya da zan sami wasu kud'in" Salis kam da sauri ya kai k'ofar fita tareda yin dariyar yak'e yace., "Na tafi Mama ALLAH ya tabbatar muna da alkhairinmu" tabi bayanshi da harara sannan tace "sauka lafiya amman don ALLAH ina zaka samo man dillalan da zasu sayi gidannan da daraja?" Salis ya d'an waigo yace, "Bari zan turo maki wasu idan kun daidaita shikenan." cikin tsananin fad'uwar gaba tace,, "to yayi sai sunzo ina jira" sannan ya fice ta rakashi da harara tace,

"Tunda kai bakasan arzik'i ba ai ka nemo masu sayar, yanzu duk nuna makan da nake yi akan sai da gidan da zanyi baka fahimci inda na dosa ba, ai kaje kada ALLAH yasa ka biya kud'in don ubanka WALLAHI koda auren aka kashe ka dawo bazan bari ka aureta ba, mutumin banza kawai mara tausayi ni zaka gwadawa kayi aure ka kashe kud'i? To kafi akuri aure in donni bak'in munafuki" sannan ta fara nad'e tabarmar tana ta fad'a kamar taci babu, sai ga Abbati ya shigo ko kallonta baiyi ba ya nufi d'akinshi, cike da masifa tace "ina dillalai d'in da nace ka kira

man?" ba tareda ya waigo ba yace "Nifa ba wani dillali da naje kira kibar Aunty Amrah kawai tayi aurenta" Cike da balbalin Masifa Zuwairar ta yo kanshi da zagi ta uwa ta uba dole ya fita bai shirya ba, kuma ta tabbatar masa matuk'ar baizo da dillalai aka yiwa gidan kud'i ba karma ya dawo don bazai kwana cikinshi ba.

****

Amrah kam tafe suke cikin motar tana ta kuka yaron kanshi kukan yake yi amman tayi banza dashi, ganin haka yasa Nazir cikin fushi ya sami gefen hanya yayi parking, cike da takaici ya d'auki yaron ya fara lallashinshi sannan ya samu yayi shiru, Amrah kam bata daina kukanta ba sai ma ci gaba da kukan da takeyi, ya kalleta cike da tsananin bak'in cikin da yake ji dangane da kukan kiyayyarshi da take yi, ya k'urawa waje d'aya kallo yana nazarin abunda ya dace, cikin muryar tausayin kanshi ya kira sunanta yace, "Amrah!!!!!!" taji saukar muryarshi har tsakiyar kanta, wanda kiran sunanta da yayi ya haifar mata da wata fad'uwar gaba, ba shiri ta tsayar da kukanta ta koma sharar hawayen da ke kwaranya akan fuskarta, cikin wata murya da shi kanshi baisan yana da ita ba yace, "Yanzu duk akan bakya son zama dani ne kike wannan kukan?" ta d'aga masa kai batareda tayi magana ba, ya furzar da wani iska mai zafi a bakinshi yace, "Ki bud'a baki ki sanar dani shin da gaske kikeyi bakya sona? Kuma tunda kike baki tab'a jin sona aranki ba koda k'adan ne?" Amrah taji kirjinta ya buga dam! dam!! ta fara wasa da 'yan yatsunta tace, "eh shiyasa nike son ka sauwak'e mani" Nazir hankalinshi yayi k'ololuwar tashi bakinshi yana rawa yace, "ki kalli cikin idona Amrah ki sanar dani cewa bakya sona." Ya k'are maganar muryarshi tana rawar kuka, Amrah ta k'ara sunne kanta sannan ta kawar dakanta gefe tace, "Ai ba sai na kalli idonka ba nidai nasan ba wata soyayya tsakanina da kai tun fil azal bale yanzu, a kulum ina yimaka kallon d'an uwana na jini ba wai mijina ba, don haka yanzu idan ma nace zan zauna da kai muyi zaman aure zan cutar da kaina ne kaima in cutar da kai, mafita d'aya ce mu sauwak'e ma juna ni da kai yaronka kuma idan kana so ka rik'e abunka ni ba damuwata bace"

Nazir ya sauke ajiyar zuciya sannan yace, "OK ba damuwa kada ki damu insha ALLAH zanyi maki yanda kike so karb'i yaron ki bashi abincinshi" cikin jin dad'i Amrah ta zura hannu ta karb'i yaron inda wajen karbarshi ta damk'o hannunshi, da sauri ta janye saboda abunda taji har tana son sakin yaron ya fad'i, da sauri suka rik'oshi dukansu inda suka sake had'a hannun waje d'aya, sannan suka dago suka k'urawa juna kallo tareda musayar aika sakonninsu cikin k'wayar idanuwansu, Amrah tayi jarumtar kawar da nata idon ta karb'i yaron ta rungume, Nazir ya bita da kallon tsantsar sha'awa yace, "Ki bashi Nonon yasha mana" Amrah tayi saurin kai kallonta gareshi ta d'an harareshi sannan tace, "To daina kallona ni dai" Nazir yayi 'yar dariya yace

"Tukunna dai har yanzu ke halalina ce don haka idan baki bashi ba ni zan fiddo masa da kaina yasha"

Amrah ta maka masa wata harara ta zunb'uro baki sannan ta d'an juya k'adan ta tura yaron cikin riga ta fara bashi nonon, aiko tsotsa d'aya biyu yaron ya sark'e ya fara tari, cikin tsananin

firgici ta fara hura masa mad'iga inda shima ya kawo nashi hannun yana bubbuga bayan yaron, saukar d'imi akan hannunshi yasa yayi saurin kai kallonshi wajen, aiko sai ga ruwan nono sai tsalgi yakeyi ya k'urawa nonon kallo gwanin sha'awa, ya cika fam har wani shek'i yakeyi ga kan nipple d'in bak'i k'irin gwanin burgewa, saboda yanda fatarta take fara tass tasa bak'in nipples d'in ya fito rad'am kamar anyi fenti, yabi wurin da kallo cikin shauk'i ya damk'oshi da sauri ta zabura, bai damu da yanayinta ba ya tara hannu ya duk'a ya fara zuk'ar nonon tamkar yana shan fida, har da su kwandal kwandal yakeyi tamkar wani d'an jariri, zuk'ar da yakeyi har cikin ranta takeji ga wani sabon yanayin da ya ziyarceta, ba shiri ta lumshe ido saboda dad'in da take ji har tsakiyar kanta, shiyasa ta hanashi abunda yake yi, shi kuma da abun yayi masa dad'i sai gashi da kamo d'ayan shima ya fara tsotso zumui zumui,gaba d'aya sun shagala sun manta a ina ne suke Allah ya taimakesu wurin ba yawan mutane masu wulgawa, kukan da yaron ya canyara NE shi ya dawo dasu daga duniyar saman da suka shiga, cikin jin nauyin abunda ya faru tsakaninsu Amrah ta ture masa kai ya d'ago yana lasar baki saboda d'and'anon zakin nonon da ya zuk'a, yana wata shuumar dariya yana kallonta da idanunshi da suka yi jajawur saboda jaraba, ta kasa had'a ido dashi ta kawar da kanta tareda turawa yaron nonon ya fara zuk'a sannan yayi shiru yana sauke ajiyar zuciya.

Nazir ya ri'ko hannunta yace,, "Ki tausayawa kanki kada k'i bari shirmen dake kanki yayi tasiri har ya hanaki abunda kike so, ni nasan kina bukatata a kusa dake saboda haka ki tausayawa kanki kizo ki mori kurciyarki, kada ki bari rudin zuciya ya jaki kije kina cizon yatsa, don ba alfakhari ba ki tara maza goma bazaki samu kamata ba, saboda haka kiyi shawara da zuciyarki ki fiddowa kanki mafita."

Yana k'are maganar ya tada motar suka bar wajen, zuciyarshi cike take fam da soyayyarta uwa uba da mahaukaciyar sha'awarta dake ranshi tun ranar da yasan wacece ita, don duk tsawon watannin da aka yi bai rabeta ba zuciyarsh cike take da kewarta, yana dauriya ne kawai ba don yana so ba.

Amrah dai k'anzil bata ce dashi ba sai shayar da yaronta take yi, amman fa zuciyarta ta lula tuno ranar da ya rabata da budurcinta, sannu a hankali har zuwa lokacin da ya maidata mace da kyau tareda mamayeta da soyayyarshi da yakeyi a lokacin kwanciyar auren nasu, sannan yanzu wannan abun da ya faru yasa ta cikin wani rud'ani, har suka kai gidan bata daina nazarin neman mafita ba. Yayi horn maigadi yazo ya bud'e masa ya shiga da motar d'an wadataccen gidanshi, don baza'a kirashi da k'aramin gida ba, ya sami cikin wata rumfa yayi parking sannan ya fito, yayinda ita kam ko motsi kasa yi tayi saboda zuciyarta da ke ta halbawa da sauri da sauri, har sai da ya zagayo ya bud'e murfin ya zura hannu ya d'auko Umar dake ta barcinshi, sannan ya d'orashi a kafad'a ya yi mata wani sihirtaccen kallo yace

"Welcome to your ne home my wify" Amrah tayi kamar bata ji shi ba ta yunk'ura cikin sanyin jiki ta fito, ta kai kallonta ga gidan ya burgeta sosai amman ta waske ta tsaya jikin motar ta rungume hannuwa tana kallon k'asa, Yayi 'yar dariya sannan ya rik'o hannunta ba shiri ta rumtse ido saboda jin wani shock da ya ziyarci gangar jikinta, ba musu tabishi har zuwa 'yar k'aramar k'ofar da zata sadasu da sashen Inna, gaban Amrah sai fad'uwa yakeyi gaba d'aya jin

kanta takeyi wata iri, saboda sabon yanayin da take jin kanta da gangar jikinta har ma da zuciyarta da ruhi gaba d'aya.

Akafta😆

D/Auta ce

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Comment's d'inki yana sani farin ciki ba kad'an ba Alkhairin ALLAH ya kai maku duk inda kuke, masoyana da masoya book d'ina na BAKAN Gizo dukanku ina maku son so fisabilillah💋👍🏻

Da Sallama Nazir ya shiga d'akin Inna rungume da yaronshi, Inna ta amsa tareda k'ara fad'ad'a fuskarta da fara'a saboda hango d'an jikallenta da tayi, Nazir kai tsaye wurinta ya nufa ya mik'a mata yaron cike da tsantsar farin ciki Inna ta karbeshi tana jin k'aunarshi har cikin ranta.

Amrah kam sai da tayi jim na d'an lokaci sannan ta shigo d'akin da sallamarta, Inna da Nazir d'in duka suka amsa mata sallamar kai tsaye wajen Innar ta nufa tana gayar da ita cike da jin nauyinta, Inna ta amsa faran faram kamar ba wani abu a tsakaninsu sanna ta koma tana gyarawa Umar zaman hularshi, don barcinshi yake yi sharkaf saboda yasha ya k'oshi, Inna ta mik'e ta d'auko zane ta goye yaron ram abayanta, a cewarta yaro yafi jin dad'in bacci in aka goyashi aiko ya lafe abinshi yana ta barcinshi har da su ajiyar zuciya.

Inna ta mik'e ta je ta kawo masu abinci da ruwa sannan ta fice tana ta 'yan k'ananun ayukanta, Nazir ya kalli Amrah da ke rakub'e tamkar wata mai jin tsoronsu, yayi d'an guntun murmushi ya Mik'e tsaye ya cire babbar rigarshi da fula ya ajiye sannan yace, "Ki taso muci abinci" Amrah tayi kamar bata jishi ba ta k'ara gyara zamanta, Nazir ya zuba abincin a plate d'aya ya saka spoons ya zo wurinta ya ajiye sannan yace da ita,

"Bismillah Maman Umar farouk" kanta a sunne tace, "Na k'oshi" ya d'ago kanshi ya kalleta yace "Me kika ci?" tak'i bari su had'a ido tace "Bana jin yunwa ne kawai" kafin yayi magana sai ga Inna ta shigo tana fad'in, "Kici ki k'oshi don maijego bata zama da yunwa, ko don yaronta ai taci abinci don ya sami ruwan nono sosai" Amrah cike da jin nauyin Inna ta d'auki spoon ta fara ci a hankali, Nazir ma ganin Inna yasa yana ta cin abincinshi ba tareda ya sake bi takanta ba, Inna gano kamar tana jin nauyinta yasa ta yi k'uryar d'aki ta bar masu falon, zuciyarta cike da tausayin Nazirunta saboda tunanin Zuwaira bazata barsu suyi zaman aurensu ba, duk da ko ita kanta da zai sahale mata d'in da tafi son hakan tunda bata sonshi, kuma muddin idan suka ci gaba da zama a hakan shine a wahale, ga kuma Auren da zaiyi tana jin tsoron itama tazo ta gano Amrah bata girmamashi itama ta bi sawunta su maida mata da yaro Mijin tace, motsin da yaron yakeyi abayanta yasa ta lallab'a ta saukar dashi a hankali ta kwantar dashi akan gadonta, tana k'are masa kallo zuciyarta cike da tsantsan k'aunarshi, wani gefen kuma tausayinshi take ji saboda tabbacin da take dashi na Zuwaira zata bi duk hanyar da zata bi ta raba auren Iyayenshi.

Amrah da Nazir kam sai aikawa juna sak'onni sukeyi ta ido, saboda idan ya kalleta ta maka masa harara yayi 'yar dariya, haka suka ci gaba da cin abincin har Amrah ta ajiye spoon d'in tace ta k'oshi, Nazir bai kulata ba yaci gaba da cin abincinshi har da su k'ari, Inna ta fito tayi waje tana ci gaba da hidimar had'a mata kunun ganyen da take yi mata, wanda tun kafin su zo ta fara hidimarshi, aiko sai gata ta damo kunun da zafinshi cike da wani k'aramin bokiti ta ajiye mata tana 'yar dariya tace, "Ga kunu nan kiyi k'ok'ari ki shanyeshi kafin Dare."

Gaban Amrah yayi saurin fad'uwa saboda daren da taji ta ambata, saboda ta tuno da Zuwaira da 'yan k'annenta aranta tace,

" waton dai ana nufin anan zan ta ci gaba da zama kenan har sai an kawo kud'in?"

Zuciyarta ta karye sai ga Kuka shaaa akan fuskarta, Inna ta bita da kallo cike da mamakinta tace,, "Bakya son kunun ne ko kuwa?" Amrah ta goge hawayenta ta janyo bokitin kunun gabanta ta fara zubawa tace, "Zan sha Inna"

Inna ta zauna tana nazarin yanayinta, Nazir kam Mik'ewa yayi ya yi sashenshi inda d'akinshi yake, zuciyarshi cike da tsantsar farin cikin zuwan Amrah gidanshi, duk da wani sashe na zuciyarshi yana kokwanton zaman nata ya d'ore.

****

Zuwaira kam ganin Abbati yak'i dawowa da wuri yasa ta sab'a hijabinta ta yi wajen bid'ar dillalin da kanta, ALLAH yasa ta taki sa'a ta iskeshi gida suka rankayo gidan tare, koda suka zo sun taradda wani wanda Abbati ya kira gaba d'aya suka shiga gidan, duba nan lek'a nan ko'ina sai da suka tantance sannan wanda ta kira ya fara yiwa gidan kud'i da miliyan biyu da d'ari takwas, ta nuna rashin amincewarta d'ayan kuma yayi masa kud'i da miliyan Uku saboda shi kanshi yasan gidan ko miliyan biyar aka sayeshi ya sayu, amman saboda ganin ita ke son sayarwar shiyasa, Zuwaira kam duk da taji dad'in cinikin nashi amman ta nuna rashin amincewarta da hakan, tace da su su dai k'ara in har suna so ta sayar masu, dole haka suka rabu akan zasu je suyi shawara har d'ayan ya tafi wanda ta kira, sai ga wanda Abbati ya tafo dashi ya dawo yace ya k'ara mata dubu d'ari akai ta nuna masa idan dai ba miliyan uku da dubu d'ari biyu ba bazata sayar ba, ganin ko a haka ya sayeshi zai ci riba sosai yasa ya amince da hakan, saboda yana jin tsoron abokin cinikinshi ya dawo ya saye gidan, amman ya rok'i alfarmar ta bashi nan da sati d'aya zai zo ya biya kud'in, Zuwaira ta dafe k'irji tace

"Ai WALLAHI idan bazaka biya nan da kwana Uku ba to da naga mai saye zan siyar ni ba ruwana,don ni in ta nice ma yanzu abani kud'in inje inyi abunda ke gabana, saboda ai kai kanka kasan haka kawai bazan d'aga gidan da muke zaune ba ince zan siyar, tunda dai ba bakin Uwa ce dani ba, ka dubi girman gidannan kai kasan idan ba dole WALLAHI nida shi mutu ka raba, to amman dole ka dole ka bani kud'in kawai in kana son mu shirya ni da kai"
Mutumin ya nuna mata shima idan son samu ne ya biya yanzu a wuce wurin, to amma had'a kan kud'in yake so yayi shiyasa, yayi ta rok'onta da ta bashi kwana bakawi d'in kamar yanda ya nemi alfarma tun farko, Zuwaira tace da shi to kawai anman aranta taci alwashin da ta sami mai kud'i hannu karb'a zata yi ta fita iskanshi.

Bayan fitarsu ne Abbati ya kalli Zuwaira yace, "Mama idan kika siyar da gidan to mu kuma ina zamu koma? Tunda ai ko ainahin gidanmu kin sayar dashi shima"

Zuwaira ta maka masa wata k'atuwar harara tace, "Ina ruwanka da inda zamu zauna tunda babu ko kwandalarka a ciki, amman tunda har so kake ka sani to bari in sanar dakai gidan haya zamu Je mu kama mu zauna, sauran kud'in da zasu rage in fama sana'a mu sami abin rufawa KAI asiri, kagin ALLAH ya fitowa da Amrah wani mijin aure"

Abbati yayi saurin kallonta yace, "WALLAHI ina jiye maki raba aurennan Mama, don ko har abada Aunty bazata sami wanda zai sota irin son da Yaya Nazir yayi mata ba, yanzu KO don albarkacin yaronnan da aka haifa bazaki bari ta zauna ba? Duk fa wanda zai aureta yanzu da

sunan bazawara zai aureta ba budurwa ba, sannan yanzu abun duba koda ya saketa ai dole ta jira har sai ta yaye yaron sannan tayi wani auren, don ba mai aurenta da d'an wani ya ajiye cikin gidanshi, to ko in hakane me zai hana ki barta cen har ta yaye yaronta sannan ta dawo, tunda dai mu nan idan ma ta dawo ajiyarta za muyi ba auren zata yi ba yanzu."

Zuwaira ta kalleshi shekeke saboda tama rasa abunda zata fad'a taji sanyi aranta, saboda Abbati ya kunnota da kyau da kyau ta had'e fuska sosai sannan tace, "Abbati!!" ta kirashi da wata kakkausar murya tace,

"WALLAHI na koma jin sunan Matsiyacin yaronnan abakinka sai na ci ubanka munafukin ALLAH, waton dai atak'aice na ganoka bak'in ciki ne kake yiwa 'yar uwarka, saboda baka son taje inda zata huta taji dad'i muma muji, to ahir d'inka in kasan bakinka bazai fad'i alkhairi akanta ba to kada ka sake shiga wannan magana, idan kuma gigi ya jaka ka fad'i wata mummunar kalma akan haka to WALLAHI ban yafe maka ba, idan ba don kana wawa ba ai ci gabanta namu ne duka, yanzu wannan gidan da muke zaune Ubanka ne ya bar muna shi cikin gado muka gada koko arzik'inta ne muke ci?da ana nuna maka hanya kana kaucewa, to ka kiyayeni bana son gutsuri tsoman munafuccinka."

Abbati ya shigewarsh d'aki abunshi ya k'yaleta tana ta zuba ruwan bala'i, har da su cewa ai ta gano ba mai sonta tunda yanzu gashi k'iri k'iri Asabe ta had'a kanta da Mijinta anci Amanarta, sannan su gasu dangin Baban nasu Amrah kowa ya zare jikinshi akan maganar bakinta yana kunfa tace,

"Ai WALLAHI duk nasan zaman da nike yi da kowa, kuma duk bala'in mutum sai ya barni tunda na zo duniya da bisimillahta abaki na shigo."

To fa kunji sai ku rage zagin Zuwai don da shirinta tazo zaman duniyar😹😹😹

Manage plss🤦‍♀️

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 35

Zuwaira kam ranar bata yi kwanan kirki ba saboda masifar da take ta yi ita kad'ai, Abbati da kanenshi ma sai da suka gaji da sauraronta suka yi bacci, sai Alla Alla take akan safiya ta waye ta koma wurin dillalin da ta nemo in yana da kud'in shi ya bata ta sayar masa ta je ta karb'o 'yarta da d'an jikanta da tayi marmarinshi da kewar jin muryarshi koda ta kukanshi ce ko.

**

Gefensu Amrah da Nazir kuwa Inna tace dashi yaje ya siyo masu kayan da zasu saka koda na kwana Uku ne, Nazir yaso ya tafi gidan Zuwaira ya d'auko masu kayan Inna ta hana tace yaje dai ya siyo masu wasu saboda gudun tashin hankali, aiko yaje ya lafto masu kayan sakawa musamman Amrah da nata gaba d'aya ready mate ne sai wasu da ya bada a d'inka mata saboda shigar bikinshi da Sadiya idan har zamanta ya d'ore har lokacin, da wasu abubuwan da zasu buk'ata ita da d'anta cike da jin dad'i Inna tayi ta sanya masa albarka, Amrah kam iyakacinta ido ba baki saboda gaba d'aya daga shi har Innar sun dabaibayeta da karamcinsu, wanda har yasata rasa ta wane gefe zata ajiyesu, shin matsayin abokan adawarsu ita da Mamarta koko matsayin mutanen da suke da wani girma a idonta?.

Da dare ma Nazir ya dad'e d'akin Inna sunata fira yana gyarawa Umar kayanshi cikin wani k'aton riyo, Amrah dai kallone nata don ko godiya ma bakinta nauyi yayi mata tayi tagumi tana faman Nazari, har sai da ta fara jin bacci ne Inna tace dashi ya d'auki danshi suje sashensu su kwanta, Wani fad'uwar gaba ya dirarwa Amrah sai ga hawaye wasu na korar wasu ta kalli Inna tace, "Don ALLAH Inna ki barni nan in kwana dakinki har zuwa lokacin da zan bar gidan" Inna tayi 'yar dariya tace, "Ina kika tab'a ganin haka Amrahtu? Ace mace da Mijinta ta kwana

wani d'akin? Kiyi hak'uri kinji kije kiyi kwanciyarki da safe sai ki zo nan d'in kiyi zamanki, in ma zaki kawo man Megidana ne ya tayani kwanan ki kawoshi sai kije kiyi kwanciyarki acen"

Amrah kam sai kuka takeyi yana rok'on Inna don ALLAH ta barta nan ita bazata je wurinshi ba, dole ba don taso ba tace da ita ta shiga d'akin to ta kwanta ita da yaronta.

Nazir dake rungume da farouk d'in yana 'yar dariyar yak'e don yaso ace Inna ta tilastata sai ta bishi, amman ai duk da hakan ai ana tare kuma kwana k'alilan ne suka rage a kawo masa amaryarshi, don yasan abunda take wa gudu duk bai wuce kada ya sami damar rab'ar jikinta ba, ganin ta nufi k'uryar d'akin Inna yabi bayanta yana 'yar dariyar mugunta da nufinshi na ajiye mata yaron, Inna ma biyarsu tayi da kallo zuciyarta cike da tausayinsu dukansu, saboda a d'an zaman da tayi da su a gabanta ta gano ita kanta Amrah ba wai son Nazir ne bata yi ba, kawai dai akwai k'ullin dake ranta wanda yak'i bari ta gano tana sonshi, shiyasa ta yanke hukunci ta bishi cen koda ALLAH zaisa kafin Zuwaira ta kawo kud'in ya shawo kan Matarshi su daidaita.

Nazir kam yana shiga ya ajiyeshi a gefen gadon sannan ya duk'o daidai sautin fuskarta yace, "Yanzu shikenan haka zakiyi ta cutar da kanki ki cutar dani? K'iri k'iri kina buk'atar mijinki kina nok'ewa?hmmmm!! To yayi ba komi amman kisani kina gaf da yiwa kanki sakiyar da babu ruwa domin kuwa Amaryata tana nan zuwa nan da Kwana hud'u masu takwas masu zuwa, ruwanki ne ki tallafi mijinki ya dawo hannunki ko kuma ki sakarwa wata idan tazo ta ririta maki shi tamkar k'wai, saboda gaskiya zan gaya maki WALLAHI Sadiya tana sona sosai, kuma komai zata iya yi a gaban kowa domin kawai taga farin cikina, don haka kisan ta hanyar da zaki jawo mijinki a jiki kafin wata tazo ta k'wace maki shi." yana k'are fad'ar maganar yayi 'yar dariya saboda yanda yaga ta wani turo baki alamun jin haushi, aiko ya mamayeta ya cafko lips d'in ya shiga tsotsa kamar wanda ya sami wani sweet mai d'an Karen zak'i, ta fara mutsu mutsun k'watar kanta amman ina yayi mata rik'on da komi wayonta bazata zille masa ba, aikuwa sai gashi ya samo lagonta musamman da ya saki leb'en ya koma ga breasts d'inta, aiko sai gata da bankare masa tana nishi a hankali na gushewar tunanin a wace duniyar take, shiko ganin hakan yasa ya baje sosai bisa gadon yana ci gaba da yamutsata son ranshi, yayi k'ok'arin zura harshenshi a bakinta yana tsotsa saboda tsoron Inna ta jisu, daga shi har ita sun lula sosai cikin duniyar sama suna yawo cikin gajimaren masoya, sai ga Umar ya falka cikin firgici yana ta kuka ba shiri suka dawo hayyacinsu, Nazir ya mik'e yayi saurin d'aukarshi yana jijjigashi idonshi sunyi jawur saboda tsananin abunda yake ji dangane da Amrarshi, Ita kam lamo tayi tana saita numfashinta da natsuwarta tareda jin haushin kanta da har take bashi fuska yana tab'ata, ta mik'e jikinta yana rawa ta fad'a toilet d'in Inna ya bi bayanta da kallo yana yi mata dariya, sai ga Muryar Inna ta nufo d'akin tana fad'an an bar Umar yana ta kuka, Nazir yayi k'ok'arin saita Muryarshi yace, "Inna tunda na shigo fa take toilet har yanzu tak'i fitowa gashi ni tafiya ma nike son inyi bacci nike ji" Inna ta karb'i yaron ta goye tana fad'in "je abunka barni da ita ta fito inji dalilin da zata bar yaro yana irin wannan kuka haka"

Nazir ya yi mata sallama ya fice d'akin zuciyarshi cike da begen Matarshi wadda ya fara jin kwakwanton anya zai iya rabuwa da ita kuwa?, don shi fa kam matuk'ar aka rabashi da ita ba

k'aramar cutar da rayuwarshi aka yi ba.

Inna kam sai faman fad'a take yi har Amrah ta fito sai sunne kai takeyi tak'i bari su had'a ido da Inna, Inna ta maka mata harara tace

"Wai ke me kikeson mayar da kanki ne? Shima yaron halin zaki nuna masa? Ina fa kula dake tunda kuka zo ba kya son d'aukarshi, me yayi maki shikam da zaki horashi da laifin da ba nashi ba? To ki bud'a kunnenki da kyau kiji Uwa Uwa ce duk runtsi kada ki bari laifin wani ya shafi d'anki da kika haifi abunki, karb'i ki bashi abincinshi ni bani son sakarcin banza" Amrah ta zura hannu ta karbeshi ta fara shayar dashi duk fad'an da Inna take yi ita zuciyarta tana cen ta lula tunanin Maganganun da Nazir ya fad'a mata, waton dai da gaske auren zaiyi to me yake nufi da kawota gidanshi ya ajiye?, salon kawai matar tazo ta renata a banza idan ta gano zaman wuccin gadi ne yakeyi da ita.

Haka ta kwana zuciyarta cike da wani sabon k'uncin da bazata tantance ainahin KO menene ba, tsakanin kishin Nazir da jin haushin kawota gidan da yayi don a wulakantata, tasa aranta gobe zata rok'i Inna akan ta matsa masa ya maidata gida kafin zuwan Amaryar tadhi da yake fad'a.

Tunda sassafe Inna ta d'ora masu ruwan Zafin wanka ita da yaronta, ta kai mata bayinta na waje ta ajiye mata ta bata Umurnin taje tayi wanka ta gasa jikinta sosai da ruwan Zafi, sannan ta zuba wasu taje da nufin tayiwa Umar wanka, bayan ta aza wasu ruwan zafin domin ta dama mata kunun sabarar da zata dinga sha a hankali saboda ta sami ruwan Nono.

Tana cikin yiwa yaron wankanne Nazir ya shigo sashen da sallamarshi a baki, kai tsaye d'akin Inna ya nufa ganin ana yiwa yaron wanka yasa yayi saurin zaunawa yana yiwa Inna ina kwana, cike farin cikin ganinshi Inna take amsawa saboda yanda taga fuskarshi cike da annuri, Shiyasa itama taji dad'i aranta taci gaba da yiwa yaron wankan har ta k'are tana hure masa kunnensa da idonshi, sannan ta mik'a masa yaron bayan ta nad'eshi cikin zane, ta zo zata d'aukar robar ruwan wankan ne da nufin taje ta zubar, yayi saurin ajiye yaron ya karb'i robar yaje ya zubar da zuwan a makwarara sannan ya dawo, ya d'auki yaron ya rungume a jikinshi har ma yana jin gumin ruwan wanka a kirjinshi, Inna ta shigo da kaskon da ta d'ebo wuta ta ajiye sannan ta kalleshi tace, "To rasa kunya mik'o man yaron ka wani makaleshi sai kace wanda aka ce za'a k'wace masa d'and'an"

Nazir kam duk da yaji 'yar kunya amman ya basar ya mik'a mata yaron yana dariya yace, "Ganin nayi yana jin sanyi Inna shiyasa" Inna ta karbeshi ta fara gasa masa cibin suna fira har Amrah ta fito daga wankan, jin muryarshi yasa taji wata fad'uwar gaba ta ziyarceta ba shiri tuno maganar da yayi mata ta zuwan Amaryarshi yasa ta k'ara jin wata fad'uwar gaban, tayi kicinkicin da fuska ta shigo d'akin da sallamarta, ba tareda ta kalleshi ba tace,

"Ina Kwana?" Nazir ya fakaici idon Inna ya bi bayanta da kallo yace, "Bansan inda kwanan yake ba nima idan kin ganshi yazo ina nemanshi" Amrah ta kai bakin k'ofar shiga d'akin Innar

ta waigo ta maka masa harara ta yi saurin shigewa, Nazir ya gimtse dariyarshi sannan ya maida kallonshi ga yaron da Inna take ta gasashi lungu da sak'o yayi lamo abunshi yana jin dad'in dimin zafin, tana k'arewa ta mik'a masa shi tace sai kaje ka kai mata shi ta shiryashi, Nazir ya karb'eshi yana murmushin jin dad'i yace, "A bani kayan shafanshi in shafa masa man Inna, ki k'yale waccen yarinyar da halinta bata iya komi ba sai shirme" Inna tana dariya tace

"Kai Naziru ka kiyayi Amrahtu don na fahimci kana so ka sakota a gaba, ko gaida kan da tayi sai da ka kushe to idan har taubasai kake so ku koma kai da ita to kaci gaba" Nazir ya mik'e yana dariya ya nufi k'uryar d'akin inda ya taradda ita tana saka Pat, da sauri ta daina abunda take ta a mak'aleta a tsakanin cinyoyinta, Nazir kam ya ajiye yaron yazo gabanta ya tsaya yana dariya yace, "Wa na kama?" Amrah ta murgud'a masa baki tareda maka masa wata jar harara, ya matso kusa da ita ya tura hannunshi ya fisgo abudda take b'oyo, ya janyota jikinshi ya matse sannan ya fara aika mata sak'una masu wuyar fassarawa, Amrah jikinta ya saki gaba d'aya ganin haka yasa ya kwantar da ita kan gadon kamar wata yarinya haka yasaka mata Pat d'in, idonta a rufe saboda tsananin kunyar da ta jiya ya d'an yimata kiss a leb'e yace,, "Sangartacciyar Naziru to tashi ki shirya tun kafin Yarona ya fara kuka" Amrah tayi saurin bud'e idonta tayi zumbur ta mik'e tace,

"Nifa bana son abunda kake yimani ko ka daina ko in had'aka da Inna WALLAHI" Nazir yana dariya ya d'auki Umar ya fara shafa masa mai yace, "Me yasa ke duk abunda zaki fad'a ba har cikin zuciyarki maganar take fitowa ba?, ki zama serious ki gani in zan koma kulaki"

Amrah tayi banza dashi ta fara shiryawa abinta zuciyarta cike da jin haushin kanta,tareda tambayar kanta akan mi ma yasa take biyeshi ne har yake ganin damarta?.

Nazir kam sakin jiki yayi ya shafe yaronshi da mansu na jarirai tas har yana k'yallin maik'o, sannan ya badeshi da farar powder wuya da duwawunshi ya saka masa pampers da kayan sanyinshi, ya nad'e shi cikin towel tareda feshe shi da turarensu na Jarirai marar k'arfi, sannan ya sab'a shi akafad'arshi yana jijjigashi, Amrah da ta dad'e da kammala nata shirin da wata doguwar riga ta mai duwatsu a gaba suna tatasniya, ta yafa d'an kwalin tayi zaune tana kallon yanda yake shirya Umar gwanin burgewa, haka kawai taji wani sashe na zuciyarta yana yaba irin kulawar da yake bata ita da yaronta, sai dai kuma tana tuna cewa Aure zaiyi yayiwa Matarshi da abunda zai haifa da ita irin abunda yake masu taji wani k'unci ya ziyarci zuciyarta.

Ta mik'e ta fito fuska turbune ta baro masa d'akin ya biyota da yaron a hannu, Inna ta kai kallonta garesu duk da taji dad'in ganinsu amman ranta bai mata dad'in ganin Nazir yana biye da ita ba kamar wata jela, ita fuska a had'e shi tashi cike da murmushi.

Yana zuwa ta mik'e ta karb'i yaron tace dasu ga abun break d'insu nan su karya, sannan ta nunawa Amrah zazafen tuwon dawan da tayi tace da ita,

"Kema idan kin k'are gashi ki k'ara dashi amman kuma in son samune ki fara cinshi sannan kisha tea d'in daga baya, don kada cikinki ya cika ki barshi gashi yana da Muhimmanci sosai a

jikinki da yaronki"

Amrah tayi wurin tuwon inda k'amshin manshanu ne kawai ke tashi, Inna ta mik'a mata yajin daddawa tace, "Gashi ki saka sai kiji dad'in cin tuwon" cike da jin dad'i Amrah ta fara cin tuwonta, Nazir ma ya had'a tea mai kabri ya yagi masar kwanshi yana cin abunshi yana kallon Amrah yana dariyar yanda take ta cin tuwonta, saboda daman cen ita tun tana k'arama ALLAH ya yota da son tuwon dawa, gashi Zuwaira bata cika yinshi ba Inna ce dai idan tayi ko bata zo gidan ba sai ta zuba ta aika mata, Jamila tayi ta gunguni in aiketa kai mata tuwon wani zubin ma tun a soron gidan take ajiye tuwon ta dawo gida abinta, saboda Jamila bata son yanda Inna da Nazir suke ta d'awainiya da Amrah, bayan ita kuma Mamar Amrah'r ba wani kulawa take yi da ita ba, hasali ma wani zubin ko abu taga tana ci sai dai ta katsa mata tsawa akan ta daina kallonta har ma ta korota gidan kuma ba tareda ta bata shi ba koda ko d'an kadanne.

Bayan sun k'are karyawar ne Nazir ya baje anata fira dashi, Inna ta kalleshi tace,

"Yau bazaka fita bane halan?" ya sosa keyarshi yace "Yanzu zan fita daman ai, me kuke buk'ata idan zan dawo in wuto maku dashi? " Inna tayi. Masa bayani ya d'an rubuta ga wata guntuwar takarda gudun mantuwa sannan ya mik'e yayi masu sallama, Umar yana hannun Amrah tana bashi Nono ya duk'o yayi masa kiss ya fice, Inna ta bishi da kallo tace, "Naziru??? To ALLAH yasa a raka kai da yaron" ya fice yana dariya Amrah kanta sai da ta dara saboda yanayin yanda Inna tayi maganar.

***

B'angaren Aunty Zuwai kam safiya tana wayewa ta koma wurin dillalinta, tace dashi ya kawo kud'in ta sayar masa yanda ya taya d'in, Dillalin jin banza ta fad'i gasassa yace da ita ta jira nan da zuwa marece zai zo ya kawo mata kud'in, cike da jin dad'i ta dawo gida saboda ganin nesa tazo mata kusa matsalarta zata kau, aiko ta dawo gida tana ta tsumayin jiranshi har bayan magriba sannan sai ga sallamarshi tareda wasu mutane uku saboda su zama shedu, jikinta yana rawa ta sab'a zane ta fito tace dashi su shigo kawai, aiko sai gasu sun shigo sukaa zauna tabarmar da ta shinfid'a masu, Mutumin ya zaro kud'in cikin aljihunshi a wata leda bak'a ya mik'a mata yace da ita ta k'irga ta gani, sai ga Abbati ya shigo tace dashi yazo ya k'irga mata sai jin dad'i takeyi tana murna, Abbati ganin kud'in ranshi ya b'aci sosai amman yak'i nuna hakan akan fuskarshi, ya zauna ya fara liissafa kud'in kwatta kwatta dalla dalla filla filla har suka kama Milayan biyu da d'ari bakwai, Zuwaira ta kalli Mutumin tace

"Ya haka Malam Audu? Nawa muka YI ciniki da kai?" wanda aka kira da Malam Audu ya gyara zamanshi yace,

"WALLAHI nayita k'ok'ari kud'in su cika yanda muka yi ciniki Milayan Biyu da dubu d'ari takwas d'in, to ganin kince yau kikeso yasa nace bari in kawo maki wad'annan nan da kwana Uku sai inzo in bada cikon dubu d'ari d'in, sannan muyi zance ranar da zaku tashi ku bani gidana in zuba 'yan haya nima"

Sannan Zuwaira ta fara 'yar dariya tace, "Yawwa yanzu naji zance Malam Audu" daga nan aka bada takarda kowa yasa hannu Abbati ya saka nashi da na kanenshi da ita kanta zuwairar, sannan suka rabu akan bazata bada takardun gidan ba har sai ya cika mata kud'inta, ba musu ya amince da hakan don yasan ko da wuta take yawo bata isa ta yi masa wayo ba.

Bayan fitarsu ne Zuwaira taja ledar kud'inta tayi d'aki ta b'oye, sannan ta dawo tsakar gida ta zauna tana sambatun zuwan gobe taje ta kai kud'i a bata 'yarta.

Koda safiya ta waye Zuwaira ta sullo wankanta tana ta wake wakenta na jin dad'i taje d'auko kud'in da nufin ta ware na kaiwa Nazir suka ce daukarni inda kika ajiye.

Wata sabuwa😳😹😹😹🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️

Akafta🤣

D/Auta ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Kuyi hak'uri da shiruna abubuwa ne suka sha kaina🤦🏻‍♀️

PAGE 36

Cikin tsananin firgici Zuwaira ta k'wallawa Abbati kira ba k'ak'k'autawa, sai gashi ya shigo d'akin yana mutsutsuke ido alamun daga bacci ya taso, Zuwaira ta share gumin da ya cika mata fuska tace,

"Kud'ina Abbati bangansu ba ko b'arayi sun shigo gidannan ne jiya ina bacci bansani ba?"

Abbati ya fara sosa k'eya yace, "To WALLAHI bansani ba Mama ni dai kamar naji motsi cikin dare na zaci kece kika fito"

Zuwaira ta dafe k'irji cikin rud'ewa tace,, "WALLAHI ni jiya tunda na shiga bacci ko fitsari ban tashi ba, saboda jin dad'in kudinnan sun zo hannuna nasan banda wata damuwa kuma yanzu, ashe ashe ina bacci ne ana yiman Nasari ai WALLAHI ko waye yake da hannu a cikin batar kudinnan ya shiga Uku ya lalace, don kuwa sai yasan bakin rijiya ba wurin wasar Makaho bane."

Ta k'are maganar cikin kuka tazo zata fita d'akin jikinta sai rawa yake saboda tashin hankali, Abbati ya kalleta da kyau yace,

"Ina zaki je?"

Zuwaira ta waigo da jajayen idanunta da suka rine cikin k'ank'anin lokaci saboda tashin hankali, hawaye suna zuba akan fuskarta tace

"Wurin boka zanje don wannan abun da aka yimani yafi k'arfin in zuba ido ina kallo, dole inje wajen bokaye insa a nemo mani wanda ya saci kudinnan, ko ya dawo dasu ko billahillazi insa ayi masa asirin da cikinsa zai kumbure ya fashe 'yan hanjinsa su tarwatse kowa ya huta, me akeyi da b'arawo? b'arawon ma irin wannan gagarumi mai gagarumar sata ai baza'a barshi yaci bulus ba" tana k'are fad'ar maganar ta saka talkami har ta Kai bakin k'ofar fita Abbati ya kirata ta waigo jikinta yana tsuma tace, "Kada ka kuskura kayi man wani guntun wa'azinka don ba saurararka zanyi ba, wajibi ne inbi bokaye adawo man da kud'ina ko ta halin k'ak'a"

Abbati ya b'ata fuska yace, "To kafin ki fita ki dubi takalmin dake k'afarki da kika saka ware

daban daban"

Zuwaira ta kai kallonta ga k'afarta ta dawo cikin sauri ta saka talkamin dai-dai ta fice tana ta sambatunta, Abbati yayi shiru yana nazarin mafita sannan ya d'aga kafad'arshi 'ya shige d'aki yaci gaba da kwanciyarshi.

Zuwaira kam tana fita bata zame ko'ina ba sai wajen wata k'awarta Lantana, ko gaisuwa bata bari sunyi ba tace, "Lantana fad'a man sunan shahararren bokan da kika sani a garinnan, don WALLAHI bazan zura ido a cuceni a banza ba" Lantana tabita da kallo cike da Mamakinta tace,, "Yau Zuwaira da kanki kike bid'ar inda Boka yake? Lalle duk abunda ya koro bera ya fad'a cikin wuta yafi wutar zafi, Meke faruwa ne nikam? da har kika canza shawarar bin bokaye da rana tsaka bayan kece ke yiman Wa'azi akan in daina biyarsu"

Zuwaira ta zauna k'asa dab'as ta fara salatin dole tace, "Rana ce ta batar mani lantana Kud'ina aka sace har Miliyan Biyu da rabi" Lantana ta dafe k'irji tace,, "Miliyan nawa?????" Zuwaira ta kawar da kanta gefe tana jinjina Kai cike da firgici tareda rud'un da ke kwance akan fuskarta, Lantana ta jawo kujera 'yar tsugunno ta zauna ta dafata tace, "Kiyi man bayani yanda zan gane k'awata shin miliyan biyu na wasa ko na gaske? Sannan idan har da gaske an sacesu b'arawo ya sace su koko mak'areki aka yi aka k'wace kud'in ta k'arfi? KO 'yan sane ne suka kwashe kud'in a jikinki ba tareda kin sani ba?"

Zuwaira ta mik'e tana saka talkaminta tace

"Zaki fad'a man inda zanje koko inje in nemi wata ta kaini?"

Lantana ta mik'e tana saka hijabinta tace, "Ai abun bai kai cen ba k'awata, ina son in sani ne don musan hanyar da zamu bi ba sai an kai ga zuwa wurin bokan ba, don ta iya yiyuwa ma ko b'arawon na gida ne kinga gudun azo aji kunya daga baya"

Zuwaira har ta kai bakin k'ofar fita ta waigo ba shiri saboda yanda gabanta ya k'ire ya fad'i, jin furucin Lantana sai lokacin tuhumar Abbati ta fad'o mata a rai, cikin Masifa tace, "Tabbas zai Iya tunda har baya son in kai kud'in dole ne yayi man wannan iskancin, aiko WALLAHI dani yake zancen don kuwa sai ya zubar da hawayenshi kamar yanda na zubar da nawa" Lantana tana kallonta baki bud'e kamar wata sakarya tace, "Wa kike zaton ya d'auki kud'in halan?" Zuwaira ta fice gidan ba tareda tace da ita k'anzil ba kai tsaye ta yi hanyar gidanta, saboda baifi gidaje biyar a tsakaninsu ba, kai tsaye d'akin Abbati ta nufa ganin k'ofar arufe yasa ta yi turus dolenta, jikinta yana tsuma ta d'auko guduma ta shiga dukan kubar d'akin, sai gam! gam!! kake ji yana tashi inda sautin k'arar bugun gudumar ta karad'e gidan duka, saboda iya k'arfinta take ta dukan k'ofar sai ga Lantana ta biyota, ganin abunda take yi yasa Lantana ta k'unshe dariyarta ta k'araso tareda dafe kunnuwanta tace, "Wai! Zuwaira WALLAHI baki ji yanda tun waje ake jin wannan k'arar ba" Zuwaira kam sai tayi tsalle ta daki kubar da k'atuwar gudumarta, sai ga d'akin ya bud'e dolenshi sannan ta ajiye gudumar tana maida Numfashin wahala tayi cikin d'akin, ta shiga watsi da kayansu Abbati Lantana ta shigo tayi tsaye tana kallonta, Zuwaira ta d'ago tana hucin wahala tace, "Taimaka man kud'in nike nema"

Lantana ta cire hijabinta suka yiwa d'akin filla filla suka fito da kayan duka amman basu ga kud'in ba, Zuwaira ta zauna tana hawayen takaici tace, "Ashe dai zato ne kawai nake yiwa Abbati ba shine ya d'auki kudinnan ba, Lantana tashi muje wurin bokan daman abunda yasa na dawo gudun inje in cutar da d'ana da hannuna, amman yanzu kam tunda har ba shi bane WALLAHI sai inda k'arfina ya k'are." Lantana tana saka hijabinta tace,

"Kayan fa anan zamu barsu?" Zuwaira ta fara tafiya tace, "ZO muje idan sun dawo su mayar da kayansu"

Suka fice gidan Zuwaira ta rufe gidan da kwad'o ta soke makullin inda suke ajiyewa, sannan suka tari Napep suka nufi wurin wani Malami mai shiga rigar malantaka yana bokancinshi.

Sunyi sa'a basu taradda mutane da yawa ba layi yana kawo kansu suka shige d'an d'akin suka zazzauna, daga nan Zuwaira ta fara zayyano masa labarin abunda ke tafe da ita, d'an tsukakken Malamin ya d'auko wani tire mai k'asa ya fara zane zane, ya d'au lokaci yana kallon zanen sannan ya d'ago yace, "Kud'inki suna nan cikin d'akinki kije ki duba zaki gansu" Cike da tsantsar farin ciki Zuwaira ta mik'e zata fita Lantana ta yi saurin fad'in, "To ki biyashi jingarshi mana ko?" Sannan ta waigo ta bud'a 'yar post d'in dake hannunta ta fiddo dubu biyu ta mik'a masa ta fice, Lantana ta mik'e tana baiwa Malamin hak'uri tareda nuna masa sabuwa ce a harkar yayi mata Uzuri, Malamin yana sosa gemu yace, "Duk da tayi laifi amman anyi mata Uzuri don mutanenmu sun gani kuma sun yaba sai nazo mu gaisa da ita har gida" Lantana tayi 'yar dariya sannan ta fice tana dariyar wannan rikici da Malamin yake so ya b'allo, don kuwa ko rantsuwa tayi tasan bazata yi kaffara ba Zuwaira bazata amince dashi ba.

Zuwaira kam tana zuwa ta bud'e d'akinta taje ma'ajiyar da ta aje kud'in ta duba bata gansu ba, duba nan lek'a cen amman duk dai bata gansu ba, cikin jin haushin k'aryar da Malamin yayi mata ta zauna gefen gadon tana karanta wasik'ar jaki, Sai ga Lantana ta sjigo da sallamarta tana murna tace, "An gansu?" Zuwaira tayi wani mere ta buga tsaki tace, "Ina fa k'ila dai shima bai k'ware da aikinnashi ba" Lantana ta zauna gefenta cikin sanyin jiki tace, "Kin ko duba ko'ina Zuwaira? Don WALLAHI malaminnan yasan aikinshi, bana shakku akan duk abunda ya fad'a mani kema d'in da zaki tashi cikin natsuwa ki k'ara bincike d'akinki a hankali da kinga kud'inki, don tunda har yace sunanan d'in to ba fashi suna nan d'akin"

Suna cikin maaganar ne Abbati ya shigo ganin kaya a k'ofar d'akinshi ne yayi saurin fad'in, "Kan burgu waya fiddo muna da kaya a waje haka?"

Zuwaira tana jin muryarshi ta fito jikinta yana tsuma saboda bala'i tayo kanshi kamar wata zakanya ta shak'o wuyanshi tace,, "Bani kud'ina don ubanka don nasan kaine ka daukesu ba kowa ba"

Abbati ya fara rantse natsen cewwa ba shi bane, Zuwaira ta saki k'wanji ta fara dukanshi awa wata sabuwar kamun hauka, Lantana tazo dak'yar ta karb'i Abbati a hannunta sai ruwan bala'i take surfawa a k'arshe dai ta bashi Umurnin ko ya fito da kud'in ko ya bar gidan, cikin fushi

Abbati ya fisge a hannun Lantana ya fice yana kukan takaici.

Wasa wasa tun daga ranar Abbati ya bar gidan har tsawon kwana goma sha bai dawo ba, zuwa lokacin Zuwaira ta jigata sosai tabi duk ta rame ido sunyi zuru zuru saboda alhinin rashin kud'inta da takaicin Zaman Amrah gidan Naziru,uwa uba rashin dawowar Abbati ya d'aga mata hankali sosai matuk'a tayi datasanin korarshi gidan, gashi yanzu abin yabi ya dameta saboda ko a unguwar kwata kwata ko wulgawarshi bata gani ba, tayi tambayar abokanshi duk suka ce suma basu san inda yake ba.

Ranar da marece sakaliya tana zaune tana Nazarin abububwan da suka dagula mata lissafi, sai ga sallamar wannan dillalin da sukayi akan idan bai bata kud'i kwana Uku ba ba zata jirashi ba, Jikinta yana rawa ta fita zuwa wurinshi bayan sun gaisa yace

"Malama Zuwaira gani dai yau ALLAH ya nufa na dawo, ga kud'in sai ki kidanya ki gani idan sun cika shikenan sai mu tsayar da zancen cinikin" Zuwaira ta hadiyi wasu miyau da suka rik'e mata wuya, jikinta yana rawa ta karb'i kud'in ta jinjina 'yar jakar tace dashi ya shigo, Bayan ya shigo tareda abokinshi da suka zo tare ne suka zazzauna, ta mik'a masa jakar kud'in tace dashi ya lissafa, Abokin ya karb'a ya kidanyesu tass suka cika cif cif Miliyan Uku da dubu d'ari Biyu, cikin fad'uwar gaba ta damk'e jakar kud'in ta mau ba tareda dogon nazari ba ta mik'e taje ta dauko masa takardun gida ta mik'a masa, sannan tace su jira taje ta kira wasu shedu ta bangarenta,aiko sai gata da wasu makotanta biyu ta dawo, shima ya kira wasu mutum biyu a gefenshi suka zo, suka had'u kowa a bangarenshi shedu uku uku kenan, aka had'u gaba d'aya aka tantance komi kowa ya sheda suka saka hannu akan sun sheda Zuwaira ta siyar masa da gida kuma ya biya kud'i cif cif, sannan ya basu notis akan nan da sati d'aya yake buk'atar su bashi gidanshi.

Bayan fitarsu ne ta kalli kud'in zuciyarta fes da farin ciki saboda rabin Bak'in cikinta ya yaye saboda samuwar kud'in, tayi wata dariyar mugunta tace,

"Zanje in karb'o 'yata kud'in da suka rage in baiwa Malam Audu ya biyoni sauran kudin, ai rikici ba gado ba sai yazo muyi ta karawa nida shi indai har na biya bukatata shikenan gurina ya cika, duk sauran rigingimun da zasu zo masu sauk'i ne."

😝😝😝'YAR Zuwais dai

Akafta 😸

D/Auta ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Idan banga ruwan comment's ba zan d'auki hutun satin biyu😅

PAGE 37

A b'angaren Amrah kuwa bayan fitar Nazir ta kalli Inna ta marairece tace, "Inna don ALLAH ki yi masa magana ya mayar dani gida, ayi komai cikin mutuncin ba tareda ankoma zancen kotunnan ba"

Inna tayi shiru tana kallonta sannan ta danne damuwarta tace, "Amrah wannan magana ba ni a cikinta ki bari ki tunkari Mijinki da zancen idan ya amince shikenan sai ku daidaita kanku cikin ruwan sanyi, ko don yaron dake tsakaninku don koda an raba auren ku bazaku rabu ba saboda albarkar d'an da ya ratsa tsakaninku, amman duk haka ina son ki natsu da kyau ki fahimci inda Nazir ya dosa akanki, saboda ke kanki kinsan ba k'aramin so Nazir yake yi maki ba shiyasa ma har kika ga ya aikata abunda yayi akanki, don haka kiyi masa Uzuri ki karb'i mijinki kuyi zamanku lafiya tun kafin zuwan Amaryar da zai yi kwanannan, don bana son tazo ta fahimci akwai baraka a tsakaninku keda shi."

Amrah tayi shiru tana nazarin maganganun Inna tana kuma aunasu a ma'aunin hankali, sai dai kuma jin zancen zuwan Amaryar Nazir yasa kwakwalwarta ta toshe da kishi ta kasa gano gaskiyar da Inna take nusar da ita, Inna kam shirun da taga Amrah tayi ne yasa ta mik'e zuciyarta ba dad'i zata fita waje ne, Amrah ta kai kallonta gareta ganin fuskarta da damuwa yasa ta kwantar da yaron ta biyo bayanta, ta durk'usa har k'asa hawaye suna zuba akan fuskarta tace, "Don ALLAH Inna kiyi hak'uri ki yafe mani naga kamar ranki ya b'aci" Inna ta kai kallonta gareta tace, "Ni bakiyi man komi ba Amrahtu amman ina son ki natsu ki kula da Mijinki" Amrah tana sharar hawaye tace "Insha ALLAH zan kiyaye Inna" Inna taji dad'i har cikin ranta tace

"ALLAH yayi maku Albarka Allah k'ara had'a kawunanku"

Amrah tace, "Ameen" sannan ta Mik'e ta fara taya Inna aiki jin kukan Umar yasa Inna taje ta daukeshi ta goye suka ci gaba da ayukansu har Nazir ya aiko da cefane, Amrah ta saki jiki ta girka masu abinci gida ya kaure da k'amshi Inna sai jin dad'i takeyi tana saka mata albarka fili da cikin zuciyarta.

Bayan ta kammala girkin ne Inna ta k'ara dama mata kunun ganyenta tasha, sannan ta dafa mata ruwan tsalki mai had'in bagaruwa da sauran abunda ke tsuke gaban mace, a cikin wata babbar butarta ta k'arfe, tace da ita ta yawaita yin tsalki da ruwan saboda kariyar jikinta cike da jin nauyinta tayi mata godiya, koda k'arfe hud'u tayi har sunyi wani wankansu ita da jaririnta sun fito fes fes sai k'yallin jego suke yi, Lokacinda Nazir ya dawo gaba d'aya rud'ewa yayi saboda ganin yanda ta yi masa kyau sosai ita da yaronta, ya daukeshi yana yi masa wasa amman duk rabin hankalinshi yana wurinta, gano hakan yasa Inna tace da ita ta d'auki abincinshi ta kai masa d'akinshi, Amrah ba shiri taji k'irjinta ya buga dam! dam! Amman saboda Inna ta gano Nasiharta ta shigeta yasa ta d'auki tiren abincin ta fita, duk da bata san ina ne d'akin nashi ba, ya biyo bayanta rungume da Umar ya shiga gaba tana bayanshi har cikin sashenshi, sannan ya nufi inda d'akinshi yake ya bud'e suka shiga, sanyin dad'in da ya ziyarceta yasa taja numfashi sannan ta ajiye tiren zata juya yayi saurin ri'ko hannunta, ta juyo ba shiri ido cikin ido suke kallon juna, ya saki jiki yayi ta aika mata sakonninshi wanda yasa ta janye nata idon dolenta saboda yanda take jin wata kasala tana sauko mata Jiki ba kuzari tace, "Kallon na menene?" Nazir ya duk'a ya ajiye Umar akan kujera sannan yazo daf da ita, ya janyo hannunta duka biyu ya sauke masu zazzafan kiss sannan ya rungumota gaba d'aya a jikinshi, ya shiga sunsunar wuyanta yana shak'ar kamshinta yana lumshe ido, saboda yanda yake jin azababben sonta

yana ratsa gabban jikinshi ta ko'ina lungu da sak'o, cikin shauk'in sonta ya laso wuyanta yace, "Haka ake tarbon Miji idan ya dawo aka ce maki?, wa ya fad'a maki da an ajiye abinci juyawa ake yi?" gaba d'aya jikinta ya mutu murus saboda salon soyayyar Nazir daban take, ba k'aramin tasiri take yi a zuciyarta da sassan jikinta ba, shiyasa ta kasa magana saboda gudun tonuwar sirrinta ya gano tarkonshi ya kamota sosai, kawai dai tayi jarumtar k'wace jikinta daga nashi amman ta kasa saboda rumfar da yayi mata sosai, tayi k'ok'arin aza hannuwanta a k'irjinshi tace, "Kada Inna fa taga na dad'e ni dai" Nazir ya tallafo fuskarta yana kallonta, ganin kallon da yake yimata yasa ta yi saurin rufe idonta, Nazir ya sauke k'atuwar ajiyar zuciya ya duk'o kad'an ya sauke mata kiss a fatar idonta duka biyu, sannan ya gangaro akan karen hancinta zuwa bakinta, inda yayi nasarar cafko halshenta ya fara yi mata tsotsar lollipop, Amrah jikinta ya saki gaba d'aya da soyayyarshi, ganin haka yasashi zaunar da ita akan kujera yana 'yar dariya yace,

"Matar Nazir ba dai shiga shauk'i ba" ya k'are maganar tareda cije mata gefen kunne, tayi zumbur tareda bud'e ido ta fara sosa wurin tana kukan shagwab'a, yana 'yar dariya ya kama kunnuwanshi duka biyu alamun ban hak'uri yace, "Sorry My Nuri Hayaty" jin sabon sunan da ya kirata dashi ta maka masa harara tace,

"Amrah ce fa ba sabuwar Amaryarka da zakayi budurwa sharr ba" Nazir ya shafo gefen fuskarta yace, "Nima Ni ne Nazirun Amrah wanda yayi ta d'awainiya da soyayyarta tun bata iya wankewa kanta kashi ba, to miye laifin Naziru anan don ya nuna soyayyarshi ga Amrarshi kuma matarshi uwar yaronshi? Da kuma masu zuwa kwanan nan" Amrah tayi saurin kallonshi bakinta yana rawa tace, "Kwanan nan????bangane ba ko ka manta zaman kud'i nikeyi?" Nazir yayi wata guntuwar dariya yace, "Kenan tunda kina zaman kud'i haramci ne in kusanceki kenan?" ta maka masa wata k'atuwar harara tace

"Ka ma daina wannan tunanin domin kuwa ni ba wannan a tsarina, don macen da tayi aure aure ana sakota me kuma za'a tsinta a jikinta? bayan wasu mazan sun tsotse komai" Nazir ya buge mata baki ya b'ata fuska yace, "Kada ki k'ara gangancin furta wannan kalma a gabana" yana k'are fad'ar maganar ya tashi yaje ya fara bud'a kulolin abincin, Amrah dafe da bakinta da ya doka tace, "Ai kai ka fad'a a bakinka idan ka mance ni ban mance ba" ta k'are maganar cikin murgud'a baki ta mik'e zata fice ya kirata da wata murya kakkausa yace, "Kada ki kuskura ki fita dakinnnan har sai na baki Umurni, Kizo ki zuba man abinci ina jira idan kuma kinji bakya iyawa to ki kwashi kayanki ki fita dasu bana buk'ata"

Amrah jikinta yayi sanyi saboda b'acin ran da ta gani kwance a fuskarshi yasa taji damuwa ta mamaye zuciyarta, ta dawo cikin rashin kuzari ta duk'a ta fara zuba masa abincin, ya zuba mata ido yana ta kallonta zuciyarshi sai yabawa takeyi da kykkyawar halittarta, sai k'ara dulmiyawa yake yi tafkin k'aunarta tareda kogin sonta, har ta kammala zuzzuba abincin bai masan tana yi ba har sai da ta dago fuskarta tace, "Gashinan yanzu zan iya tafiya?" Nazir ya dawo hayyacinshi sannan ya d'an sha mur yace, "ki zauna da kyau ina cin abincin kina bani labari" Amrah ta d'an hareshi ganin baya kallonta ta b'ata fuska tace, "To nikam wani labari na iya da har zan bada?"

Nazir ya fara guma loma yana lumshe ido yace, "Koda na daren farkonmu ne nida ke ai nasan kinsanshi kuma bazaki manta da ranar ba ko?" Amrah taji wani yarr! A jikinta tareda zuwan wata sabuwar kunya ta mik'e, yayi saurin kai kallonshi gareta yace,

"baki ji nace kar ki fita sai na baki umurni ba?"

Amrah ta dawo ta zauna ta sunne kai Nazir ya kalleta yace

"Kunyar ta mi cece nikam?" Amrah ta gimtse tareda shiga natsuwarta tace,, "Kunyar me zanji taka to?" Nazir yayi 'yar dariya yace, "Hakane fa kuma gaskiya kunyar me bayan muhallai biyu sun had'u?" Amrah ta zaro ido ta rufe fuska tace, "ALLAH yaya Nazir zan tafiyata idan baka daina irin wad'annan maganganun ba" Yayi mata wani shegen kallo yace, "Kefa kika ce bakya jin kunyata to kuma zancen tafiya ai bai taso ba, dole ki ware kawai mu ci gaba shanawa abunmu tunda ba kunyata a idonki"

Haka dai suka yi ta firarsu yana tsokanarta har ya kammala, sannan ta matsa ta dawo kar Inna taga ta dad'e badon son ranshi ba suka dawo sashen Inna, inda aka had'e da Innar sunata firarsu duk da Amrah tak'i sakin jikinta da Inna saboda kunyar dadewar da tayi wurin Nazir, batasan ita Inna dad'i ma taji ba tareda addu'ar zaman lafiyarsu ya d'ore kada Zuwaira tayi nasarar rabasu.

***

Satin Amrah d'aya gidan ta mulmule abunta gwanin sha'awa daga ita har yaronta sunyi b'ul b'ul abinsu, saboda kulawar da suke samu ta b'angaren Inna da Nazir d'inta mai mayen sonta kamar ha hadiyeta saboda k'auna, Inda cikin 'yan kwanakin aka fara hidimar bikin Nazir da Sadiya, kasancewar ya hana ayi komi amman duk da haka sai da K'awayen Sadiya suka shirya Event d'in da za'ayi dashi, sannan ayi walima a kawo Amarya gidan angonta, tun daren Ranar da za'a YI event d'in Nazir ya ce da Amrah ta shirya gobe suje tare, tace ita kam ba inda zata je k'arshe ma kuka ta fashe masa dashi ya koma lallashi don izuwa lokacin shi kanshi ya gano Amrah tana kishinshi, haka ya shiririce yana lallashinta har sai da Inna ta gaji da jiran ya fito ta rufe d'aki, tace dashi yaja matarshi suje d'akinshi yaci gaba da lallashin a cen, sannan ya fito ya yi masu sallama yayi nashi d'akin zuciyarshi cike da kewar Amrarshi.

Koda safiya ta waye mutane 'yan uwa na nesa ta b'angaren Inna da Malam Mahmuda Baban Nazir suka fara zuwa zuwa gida ya kacame da firar yaushe, duk wanda yaga Amrah sai yayi tambayar ya aka yi ta dawo gidan, wasu kuma da suke da labarin komi sai dai suyi ta binta da kallon reni mai cike da jin haushinta, ganin haka yasa Inna tace da ita ta koma d'akin Nazir da zama, Sannan ta kira Nazir tace dashi ya k'ok'arta ya had'awa Amrah d'akinta itama kada Sadiya tazo ta renata, sannan uwa Uba a kore tsegumin mutane da k'ananan maganganunsu, aiko jikinshi yana rawa ya je ya had'o mata kayan gado na ji da fad'i da kujerunta da komai da mace take buk'ata, sannan ya karb'o mata dinkinta da ya bada yace tayi shigar biki.

Amrah ta fashe masa da kuka tana rok'arshi akan ya kaita gida don ALLAH, Nazir ya share da ita don yasan kishi ne yake d'awainiya da ita, ya kira Jamila ya mallaka mata hidimar gyarawa Amrah d'aki da ita da wasu kannenshi na 'yan uwa, suka tsaya kai da fata suka gyara d'akin amman fa Amrah tasha tsina a wurin Jamila, saboda ganin dawainiyar da Yayanta yake yi akanta amman ita bak'in halinta yak'i bari ta natsu ta hankalta, Koda zaije event d'in bayan ya fito wanka ta bishi da kallo cike da tsantsar kishinshi da ke huda zuciyarta, ta fashe da wani sabon Kuka nan ya lalace yana ta lallashinta har sai da aka yi ta kiranshi sannan ya shirya a gurguje, ya d'auko turare ya mik'a mata yace, "Shafawa angonki Uban yayanki kece da Nazir duk wadda kika ga ta rab'eshi aro ne kika bata, Zuciyar Nazir cike take da tsantsar kaunarki my Wify ki daina d'aga hankalinki kinji" Amrah tayi jarumtar share hawayenta ta karb'i turaren ta fara fesa masa, tuno inda zaije yasa Kuka yaci k'arfinta ta dunk'ule tana ta gunjin kukanta, ba shiri ya d'agota ya had'ata da jikinshi ya rungume tareda dora kanshi a saman wuyanta yana fad'a mata kalamai masu tsada cikin kunne, aiko sai gata ta fara murmushi tana sunne kai a k'irjinshi, ganin ya ciyo kanta ne ya samu yayi sallama da ita agurguje ya fice, tabi bayanshi da kallo ta fad'a gadonshi tana kukan da ita kanta ta gano yanzu ba k'aramin so take yiwa Nazir d'in ba.

Tana d'akin tak'i fita har dare ko Umar sai da yayi kuka ne aka aiko wata yarinya ta kawo mata shi, tana d'akin cikin k'uncin zuciya abinci ma da Inna tazo da kanta ta kawo mata k'in ci tayi, ganin kukan da takeyi yasa Inna ta zauna tayi ta yimata nasiha tareda nusar da ita akan ta rik'e mijinta gam kada tayi sakacin da wata zata k'wace mata shi, sannan ta fice ta barta tana kukan zuciyarta cike da jin dad'in gano Amrah ba k'aramin so take yiwa Nazirunta ba.

Nazir kam k'arfin hali kawai yakeyi a wurin hidimar yana dariyar yak'e saboda yanda zuciyarshi take cike da tunanin halin da ya baro Amrahrshi, yana samu aka kammala ya d'auki Sadiya ya kaita gida suka yi sallama a gurguje sannan ya juyo zuwa gida, inda kafin ya k'araso sai da ya biya ya yo masu siyayyar gasassun kaji da tsire da dafuwar ruwa kumshi kumshi ya nufo gida, sai da ya ware na Amrah sannan ya kira Jamila da ke gidan har lokacin ya bata na Inna da bakinta, sannan ya nufi sashenshi inda ya taradda Amrah tana kan sallaya tana addu'a, tana jinshi tayi saurin mik'ewa ta cire hijabin ta k'udundune a jikinta, saboda bata so ya gano ta fara sallah ashe bata san ya ganta ba baki har kunne ya k'araso ya ajiye ledodin, sannan ya fice zuwa sashen Inna yana gaggaisawa da mutane, sannan ya nufi kuryar d'akin inda Inna take da Jamila suna rabon naman, Ya shigo ya zauna yana dariya yace

"To a kasa dani D'iyar Inna don naga kin k'ware da iya kason yanda ya kamata" Jamila tana dariya tace " sai dai a baiwa Matarka don kam kai ai sai kaci girma ka bata naka kason" Nazir yayi dariya sannan yace "A'a kuci kayanku na kai mata nata"

Jamila ta d'ago ta kalli Inna Nazir yayi saurin fad'in, "To kanwa uwar gami me zaki ce? Don nasan yanzu k'adan kike jira ki ce nayi laifi?"

Inna tayi dariya tace

"Baka da laifi don ka kula da matarka amman ka rage rawar k'afar da kake akanta yafi don gudun reni"

Nazir ya sosa kanshi ya mik'e yace, " To ni dai na shige Inna sai da safe, ke kuma ki kira mijinki yazo ya kwasheki ku je dare yayi" Jamila ta kalli agogon hannunta tace, "Lalle yaya to ai ko k'arfe tara bata iyar ba" Nazir ya fice yace.

"Kyaji da shi ni dai na shige sai da safe" Inna ta bishi da kallo tana 'yar dariya saboda tuno lokacin da Amrah tana kwana d'akinta sai ya kai k'arfe sha biyu a d'akin bai je ya kwanta ba, amman yau tunda tana wurinshi k'arfe tara ce ta zama dare a wurinshi.

Nazir kam koda ya je ya taradda ita akan gadonshi ta k'udundune da yaronta a mak'ale jikinta yana ta bacci, yayinda ita kam kwancen kawai take amman zuciyarta taki natsuwa balle har ta samu tayi baccin taji sanyi, yazo ya zauna gefen gadon ya fara cire Umar dake saman jikinta ya ajiyeshi gefe sannan ya ri'ko hannunta yace, "Nasan ba bacci kike yi ba don haka ki taso kiji wata magana."

Amrah ta juya masa maya tareda rufe fuskarta saboda zubowar wasu hawaye akan fuskarta, Nazir ya kwanta shima yana facing d'inta ya fara yi mata magana mai kama da rad'a yace, "Wai wannan kuka shi baya k'arewa ne?" Amrah ta fara sheshakar kukanta, hankalin Nazir ya tashi yayi saurin had'a jikinshi da nata yana lallashinta tareda aika masa da sak'una masu wuyar fassarawa, sai ga Amrah muk'us ta fara fita hayyacinta tana sauke numfashi ganin ya kamo tasharta yasa ya tada ita zaune, sannan ya ri'ko hannunta suka sauko k'asan carpet d'in ya fara bubbude ledodin sai ga k'amshi yana bugun hancinta, aiko sai ga tsohuwar yunwarta ta taso yana kai naman bakinta ba musu ta wangale baki ya saka mata ta cenye, sannan ya d'auko wani ya saka a bakinshi ya nufo nata bakin yana mata nuni da ta karb'a, ta hararreshi ta make kafad'a ya kamo kanta da hannushi biyu ya kai naman bakinta ta karb'a dolenta, yak'i saki ta ja yaja haka suka tayi har ya sassauta rik'on naman a haurunshi sai gashi tayi nasarar fisgewa ta lunkumeshi a bakinta tana yi masa gwalo, ya biyeta yana ta tsokanarta suna cin namansu suna fira k'asa kasa suna dariya, bayan sun kammala ne ya mik'ar da ita yace suje suyi wanka, tana noke noke tana komi dole ya sakata suka je yin wankan, tun a cen ya dinga mamayeta da salon soyayyarshi har suka kammala suka fito, da suka zo kwanciya ne har ta kwanta ta mik'e yace ina zaki je ne kuma tace, "kimtsawa zanyi kar inyi staining"

Cikin k'ume dariyarshi yace, "Au ya dawo ne daman?" taji wata fad'uwar gaba ta ziyarceta bakinta yana rawa tace, "ai daman cen bai d'auke ba fa"

Nazir ya mik'e tsaye yace, "OK to yayi muje sai in kimtsa kin da kaina" Amrah ta make tace ita dai ya barta tayi da kanta ganin da gaske bukulu take so tayi masa yasa ya janyota akan gadon da dubara da salonshi ya samu ya dangwalo wurin ya duba ganin ba komai sai farin ruwa mai yauk'i yasa yayi wata shuumar dariya ya fara aika mata da sak'onni, tun tana dauriya har ta baje ta saki jiki tana maida masa martani, soyayya filla filla yayita bida ita mataki mataki

har yazo bakin k'ofar shiga fada, ba tareda wani musu ba ta bud'e masa k'ofa ya fad'a, shi ihu ita kuwwa saboda abunda take ji daga gareshi, saboda Nazir yasan hanyoyin da zai jiyar da mace dad'i har ma ta d'auka daga ita sai shi ne a fad'in duniyar ma'aurata, shiyasa Amrah tayi ta ihunta tana sambatu inda shima kanshi ba'a barshi a baya ba wajen nuna jin dad'inshi a fili, haka suka kwashi lokaci suna gurzar junansu kafin d'an jinjirinsu ya katse masu jin dad'in, ta hanyar kukan da ya canyara dole suka dakata suka daukeshi suna lallashi, Nazir ya dura masa ruwa sai da yasha yayi tatul sannan yayita girgizashi har ya koma baccin, ya lallab'a ya ajiyeshi ya jata zuwa falonshi suka ci gaba da holewarsu a cen, don kam a ranar sunsha Amarcinsu sosai wanda ko a cen baya basu yi irinshi ba, kwana suka yi suna begen juna saboda daga ita har shi suna da k'arfin desire zani ce ta taradda muje awannan fannin.

Koda Asuba tayi ma bayan sunyi SALLAH sai da suka k'ara komawa fagen dagar sannan suka koma bacci, Zuciyoyinsu cike da farin ciki da k'aunar juna inda suke jin duk runtsi bazasu tab'a rabuwa da juna ba.

Tofa ruguntsumi tsuntsayen masoya Maza bisa kanku 😳🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️

Akafta😆

D/Auta ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

Koda safiya ta waye cike da jin nauyi Amrah taje ta gayar da Inna da sauran bak'in, Inna ta karb'i yaron ta yi masa wanka itama tace da ita taje ta d'ibi ruwan zafin taje d'akinta tayi wankan, Amrah kam kasancewar toilet d'in akwai fanfon ruwan zafin taje ta had'a ruwanta masu zafi zau tayi wankanta, Nazir ma d'akinshi yayi wankan ya fito fess angonshi, Ya nufi d'akin Amrah sai gata ta fito daga wankan yin tozali dashi ya fad'ar mata da gaba ba shiri, ta wayance ta nufi bakin madubi ta fara tsane ruwan jikinta, ya tako a hankali ya tsaya bayanta yana kallonta ta madubi suna had'a ido ya kanne mata ido d'aya ya zura hannu ya d'ebo mai ya fara shafa mata a hankali yana murje mata fatar jikinta, daga shi har ita suka tsinci kansu cikin WANI yanayi ba tareda ta hanashi ba ta saki jiki yayi ta lundeta da mai kusufa kusufa, har yazo kan breasts d'inta inda ya fara mulmulesu yana sauke mumfashin jin dad'i, itama kanta ba k'aramin jin dad'i take yi ba ganin ya canza akalar ne yasa ta zare jikinta ta nufi ma'ajiyar kayanta, ya biyota ido jawur ya tsaya a bayanta ya d'an duk'o saitin kunnenta yace

"Ki tausayawa angonki idan ba so kike in fita mutane su gano bana cikin natsuwa ba"

Amrah ta juyo cikin wata sabuwar kasala tace, "Fita fa zakayi Yanzu kuma ace ka b'ata shirinka haka kawai a banza" yayi saurin d'ora hannunshi a bakinta yace,, "Shit! Daina fad'ar banzar nan don duk inda zanje ba baza'a bani abunda zaki bani ba a yanzun, kin ko ga ai yafi k'arfin fad'inshi da sunan banza zo kawai ki karb'i sak'ona ni sauri nikeyi" aiko ya kalallameta ya k'ara jik'a alkalaminshi sosai sannan suka sake sabon wanka ya fita, ita kuma ta tsaya jikin madubi ta tsantsara kwalliyarta masha ALLAH, sannan ta nufi d'akinshi tanata k'amshin turare ta gyare masa d'akin tass, sannan ta dawo sashen Inna tana taimaka masu da 'yan ayuka, don ko da tazo Jamila tazo ta taradda ita tana shirya Umar cikin kayanshi dake d'akin Inna, aiko sai ga masu jere sunzo sun fara aikinsu inda ganinsu ba k'aramin kayar mata da gaba suka yi ba, ta dai daure ne kawai don kar aganota amman duk boyonta Inna ta fahimci halin da take ciki, shiyasa ta kirata gefe tana bata hak'uri har ta samu ta ware sannan ta dawo suka ci gaba ayukansu, wasa wasa gida ya fara cika da 'yan uwa da abokan arzik'i, kafin kace me gida ya cika fam da jama'a Amrah tayi tsuru rsuru ta kasa sakin jikinta saboda kallon da taga wasu suna biyarta dashi, wasu ma har nunata akeyi ana rad'a shiyasa ta tsargu sosai gashi kuma cen

sashen nasu cike yake da dangin Sadiya masu zuwa jere da masu zuwa kallo, dole ta lallab'a ta sulale tayi d'akinta duk da kallonta da akeyi, don dangin Sadiyar har lekenta suke yi ta window kafin ta shige sashenta, wasu da yawa sun yaba da tsarin halittarta yayin da wasu suka shiga kusheta saboda taya 'yar uwarsu kishi.

Misalin k'arfe d'aya Nazir ya dawo gida saboda yayi wankan zuwa d'aurin auren da za'ayi k'arfe biyu, kai tsaye sashen Inna ya nufa don yasan Amrah tana cen, amman duk iya wara idonsh bai hangota ba sai da yakyafato Jamila yace da ita ina Amrah? Ta sanar da ita tana sashensu, ya fito kai tsaye yayi d'akin Sadiya inda ya fara gaisawa da masu jeren sannan ya fito ya nufi wurin Amrah, koda yaje ya taradda ita falo kwance tayi lamo kamar mai bacci, amman a zuciyarta sai kuka take yi tana datasanin da bata karb'i Nazir tun a farko ba, da yanzu shikenan ba ita ba kishiya, yanzu gashi tana tsaka da jin dad'inta za'a wargaza mata farin ciki, aranta sai tambayar kanta take yi tana fad'in,

"Me yasa tun farko ban karb'i Nazir a matsayin Mijina ba? Me yasa idona suka rufe da gano irin soyayyar da Yaya Nazir yake yimani?, Ina ma za'a dawo da hannun agogo baya da na rungumi yaya Nazir a matsayin mijin da nafi kowace mace sa'ar samun irinshi a duniya"

Ta k'ara tambayar kanta tace, " nikam ina zan jefa kaina da rashin masoyin gaskiya Yaya Nazir d'ina?." jin furucin da ya fito bakinta yasa ya k'araso da sassarfa baki harkunne yace,

"Baki rasa ni ba gani kusa dake my habibty"

Amrah tayi saurin waigowa tana ganinshi tayi saurin tashi ta rungumeshi tana kuka gwanin ban tausayi, suka zube kan kujerar ya fara lallashinta ta hanyar bata hot kiss masu zafi ta langabe a jikinshi tana sauke ajiyar zuciya, cikin shesheka tace

"Don ALLAH yaya Nazir kayi hak'uri da abunda NAYI maka a baya, WALLAHI nayi danasanin abunda ya faru don nasan duk shine ya janyo aka dankaro mani kishiya da haifuwa d'aya." ta K'are maganar cikin kuka Nazir ya k'ara rungumeta a jikinshi yana share mata hawaye.

Jamila da ke tsaye da abincinshi a hannu jin abunda Amrah take fad'a yasa taji dad'i a ranta, ta rafka masu sallama Nazir yace da ita ta shigo Jamila ta kalli Amrah jikin Nazir kamar wata 'yar mage tayi dariya, sannan ta ajiye tiren ta fice haka kawai ta tsinci kanta da tausayin Amrah wanda a rayuwarta da Amrah bata tab'a yi mata kallon mutunci ba sai yau, koshi saboda gano itama ta tsunduma son yayan nata da gaske har zucinta.

Nazir ya lallab'a ya zare jikinshi ya d'auko plate ya zuba abincin ya ajiye a tsakaninsu yace, "Ci muci sauri nike yi fita zanyi" Amrah ta d'aga kai tana kallonshi hawayen suna kwaranya tace,, "Yaya Yanzu shikenan yau za'a d'aura aurenka da Amaryarka ka tare a d'akinta ni ka barni"

Nazir ya ajiye spoon d'in ya dafe kai sannan ya had'a hannunshi duka biyu yace, "Am sorry

My hayaty wannan aure mukaddari ne ALLAH ya riga da ya tsara don haka don ALLAH ki daina d'aga hankalinki kina sakani jin auren yana ta fice man arai, don ALLAH ki barni inyi adalci a tsakaninku Kinji, don WALLAHI matuk'ar kina irin wad'annan maganganun zaki sa inji na tsani auren inzo inyi abunda bai dace ba, kiyi hak'uri da duk abunda zaki gani don ALLAH amman kar ki mance sonki a raina bazai tab'a goguwa ba koda ko bama tare balle gaki a kusa dani ina jin diminki kina jin nawa, kiyi hak'uri kinji Mmn Uwar farouk d'ina ?" ta d'aga kanta ta fara share hawayenta ta d'auki spoon ta fara ciyar dashi yana karb'a yana lumshe ido, shima ya dinga bata tana ci cikin k'arfin hali har suka cenye abincin plate d'in, ya k'aro masu suka ci sannan ya jata suka yi d'aki tana turjiya tana komi sai da ya k'ara shiga gonarshi, sannan yayi wanka ya fito zuwa d'akinshi yaci nasarar ba wasu mutane a tsakar gidan, a gurguje ya shirya cikin kayanshi na angwanci sai baza k'amshi yakeyi ya nufi d'akinta, koda yaje ya taradda itama ta shirya cikin jin dad'i ya taimaka mata, sannan ya ri'ko hannunta suka fito ta rakoshi har bakin k'ofar sashensu tayi mashi addu'a ya fice ta dawo d'akinta, inda taga dangin su Sadiya sai lek'ensu suke yi suna mamakin irin wannan k'auna tasu, Amrah dai ko kallonsu bata yi ba ta shige abinta tana nazarin ta wace hanya zata karkato mijinta ta karb'e abunta ita kad'ai?, Tana nan zaune sai ga Jamila da wasu matasan mata na 'yan uwansu suka shigo wurinta, ganin yanda suke ta janta a jiki ne yasa ta ware suka ci gaba da firarsu suna dariya, Jamila tace da Amrah tazo su tafi inda 'yan uwan Sadiya ta gayar dasu, Ba don taso ba ta mik'e suka rakata ta gayar dasu d'aya bayan d'aya, aiko sai gashi sun aje tseguminsu sun karb'eta hannu bibbiyu har wata tana tsokanarta da cewa ai itama Amarya ce don wannan kwalliya duk wanda bai sani ba zai d'auka cewa Amaryar ce suka kawo, da d'an barkwancinsu suka fito zuciyar Amrah kamar ta fashe saboda tuno ana cen ana d'aurawa Nazir aure da wata, idonta suka yi rau rau ta shige k'uryar d'akinta tana ta kukanta, sai ga Jamila tazo tace da ita tazo tayi bak'uwa taje toilet ta wanko fuskarta harda guzurin shafa powder ta fito.

Aikuwa cike da tsantsar farin ciki ta k'araso da gudunta baki har kunne tace

"Aunty Asabe ya akayi kika gane gidan?" Aunty ta bita da kallo saboda ganin yanda ta yi b'ul b'ul abinta haskenta ya k'ara fitowa siririn hancinta ya k'ara tsawo gwanin burgewa, cikin tsantsar farin ciki Aunty tace

"Lalle 'yata masha ALLAH Nazir ya iya kiyo wannan kyau haka masha ALLAH ina mai gidan nawa ne?" Amrah ta kalli Jamila tace,

"Jamila ina yaronku ne? Aunty tana so ta ganshi"

Jamila ta mik'e tace da ita "bani minti biyu Aunty yanzu zaki ganshi tunda har yaronmu ne mu kad'ai banda ita" Aunty tayi dariya tace,

"Kinsan 'yar tawa ba daikawaici ba" Jamila ta fice sauran matan ma duk suka fita suka barta da Auntyn, Aunty sai kallon Amrah takeyi tana jinjina hukuncin ubangiji ranta tace

_" ashe dama daman Nazir ne mai saki natsuwa tun farko wauta ta jaki, ALLAH ya soki akwai

sonki a ranshi da ko kallonki bazai yi ba saboda irin butulcin da kuka yi masa..... "_

Shigowar Jamila ne ya katsewa Aunty tunanin zucinta cike da murna ta karb'i Umar tace, "A'a masha ALLAHU kice dai yaron shima yasan gidan Babanshi yazo, ya baje abinshi masha Allah ya cika bayanshi gwanin burgewa, Lalle Amrah ki godewa ALLAH da ya baki Miji mai sonki tsakani da ALLAH" Amrah ta fara hawaye tace,

"Aunty fa yau ake d'aura masa aure da Amaryatai" cikin kuka ta k'are maganar, Aunty ta bita da kallo cikin tsananin jn dad'i tace,

"Ina sane ai shine ma yaje har gida ya rok'eni inzo in lallasheki in baki hak'uri." Amrah tayi saurin kallonta Aunty tace, "Tabbas shine ya ce inzo in zauna dake don ki kwantar da hankalinki, don in banda shi da banzo gidannan ba saboda nayi alk'awalin bazan sake shiga sabgarku ba tunda Aunty Zuwaira bata san mai sonta ba."

Amrah ta marairece fuska tana kallonta hawaye suna sauka Aunty ta kalleta ido cikin ido tace,, "Shawara d'aya ce zan baki duk runtsi kada ki bari a raba ki da Mijinki, don yanzu haka Aunty Zuwaira ta siyar da gidan da kuke zaune akan ta biya Nazir kud'in da aka nemi ta bashi don ya sauwak'e maki, a sanadiyyar haka ma yanzu haka Abbati yana gidan Dangin Babanku saboda yazo har gida ya sanar dani komi, har kud'in da ya d'auke ya b'oye don kar ta biya ta rabaki da Nazir din, da yaji zata kai abun wurin bokaye ne ya maida mata da kud'inta a d'akinta sai dai yayi masu mugun b'oyon da bazata san inda suke ba, akan hakane ta koreshi gidan tace matuk'ar bai kawo kud'in ba kada ya dawo, to yanzu ni dai shawarata guda biyu ce gareki ta farko ki natsu ki kula da Mijinki da Mahaifiyarshi da 'yan uwanshi har da kishiyar taki, na biyu ki jajirce ki tub'ure akan bazaki rabu da Mijinki ba matuk'ar Zuwaira tazo da zancen rabuwarku, don WALLAHI kika kuskura kika biyeta kece a wahala ba kowa ba, haka duk da ban tara sani ga Ubangiji ba amman ki karad'e duniya kaf bazaki samu mai sonki irin Nazir ba don haka shawara ta ragewa mai shiga rijiya, kimsan dai wahalar da kika sha a baya yanzu kuma ALLAH ya musanya maki da alkhairi duk da butulcin da kuka yi masa a baya, don yanzu kam na tabbata kika kuskura kika saki Nazir bazai bibiyeki ba don ko cen da don baya da wata mata ne, amman yanzu ke sheda ce da Amaryarshi sharr a gida don haka kiyiwa kanki kiyamullaili ki natsu gidan Mijinki ki kula da tarbiyyar yaronki."

Amrah ta sauke k'atuwar ajiyar zuciya tace, "Yanzu Aunty ke bazaki nusar da ita ba ta mayarwa da mai kud'i kud'inshi abar zancen ba?" Asabe ta dafe k'irji tace,

"Ni a suwa? Tufani ki saya WALLAHI alk'awali nayi bazan koma shiga sabgarta ba, kedai da ake abun kanki ki kwaci wuyan hannunki daga raba ki da Mijinki da take so tayi, don ke za'a kai a baro a barki da wahala don na tabbata yanzu kina son Nazir, muddin kuma kika bari kuka rabu WALLAHI sai kin fishi shan wahala wannan karon"

Amrah ta share hawayenta tace, "Kinsan halin Mama sarai Aunty bana son mu maimaita

abunda akayi Ikcn aurena da Malam Nura, kina kallon irin cin zarafin da tayi mani akan auren" Aunty ta maka mata harara tace

"To ki zauna ki zura ido ta kassa maki rayuwa kiyi zamanki wata rana ita da kanta zata gano gaskiya ta dawo hanya"

Haka dai Aunty tayi ta yiwa Amrah famfo har zuwa marece, inda ta ce taje ta k'ara yin wani sabon wanka saboda tarbon Amarya, Aiko taje ta kara canzo wata shigar wadda tafi duk wadda tayi tasha dauri sai k'amshi ke tashi jikinta sai kace itace Amaryar.

Koda dare yayi misalin k'arfe takwas dam aka fara gud'a tareda shewar ga Amarya nan tazo gaban Amrah ya k'ire ya fad'i dam! Dam! Dararam!!!!

Tofa kuyo agaji da k'aton Dutse a danne zuciyar Uwargidan Nazirun Inna.

Akafta 🤣

D/Auta ce👍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Happy Birthday to u Mardiyya D'ahiru wishing u the best life in your world and more money to your account 🤪

KUYI hkr dani plss wayata ce ta zama 'yar k'waya 🤦🏻‍♀️

PAGE 39

Ta mik'e kamar wata zararra tana rabon idanuwa Aunty tayi saurin rik'ota tace, "Sai fa kin natsu kin zama jarumar gaske ne zaki iya cenye wannan jarabawa, koda wasa kada ki bari zuciyarki ta saki aikata abunda mutane zasu je dake a baki, kiyi k'ok'arin danne duk wani abunda kike Ji aranki ko don ki jawa kanki girma wajen dangin Nazir da ita kanta Amaryar, ki zauna dakyau kiyita fad'in *Innalillahi wa'inna ilaihirrajiun* a baki insha Allah zaki ji zuciyarki tayi sanyi k'alau, sannan ki had'a da *hasbunallahu wa ni'imal wakil* itama tana sanya aminci da natsuwa a cikin zuciya" Sannan Amrah ta zauna ta fara fad'ar kalmomin a bakinta tana yi tana nanatawa aranta har taji zuciyarta ta sami natsuwa fiye da tunaninta, sai gashi ta kalli Aunty tayi 'yar dariyar yak'e tace,

"Nagode Aunty ALLAH ya bar man ke kuma kema ya baki yara ko don su yi alfakhari da samun Uwa tagari irinki"

Aunty taji dad'in adduarta daga nan tayi ta janta da fira har ta rage damuwar da take ji.

Firarsu ta katse ne saboda jin sautin gud'ar mutane da hayaniyarsu sun nufo d'akinta, Duk da gabanta sai dakan lugude yakeyi amman tayi jarumtar danne komi har ma ta gayyato natsuwa ta saka a zuciyarta, wata gwaggonsu Nazir ce ta fara shigowa da sallamarta rik'e da Amarya, Aunty ta Amsa tareda taronsu da fara'arta har suka zo suka zazzauna, nan take mutane suka cika falon taf kowa da son ganin k'wak'waf a ranshi, Gwaggon ta kalli Amrah ta fara magana kamar haka,

"Amrah ga kanwarki nan tazo ta gaisheki, ke kuma Amarya ga Auntynki nan sai ku gaisa"

Amrah da ke dariyar yak'e tace "Sannu da zuwa Amarya ina yimaki barka da zuwa ALLAH ya

had'a kawunanmu"

Duka falon akace "Ameen" masu amsawa har zuci sunayi masu mere ma suna hararta suma ba'a barsu a baya ba, Sadiya Amarya kam k'ara sunne kai tayi cikin gyalenta tace,

"Aunty barka da dare" Amrah tana 'yar dariya tareda jin sabuwar fad'uwar gaba tace, "Yawwa Sadiya" sannan ta mik'e ta d'auko rafar 'yan d'ari bibbiyu sababbi kal ta nufi inda Sadiya take zaune da 'yar guntuwar fara'arta, ta duk'a gabanta ta d'ora mata kud'in a cinya sannan ta yaye lullubin tace,

"Na riga Ango sayen bakin Amarya don haka dole ne in rigashi ganin fuskarta"

Gaba d'aya falon aka saka dariya wasu da yawa Amrah ta burgesu, yayin da wasu suke d'aukar hakan da tayi a matsayin wani sabon salon makirci irin nata.

Amrah da Sadiya kam yin tozali da fuskokin juna ya saka su fad'uwar gaba ba kad'an ba, Musamman Sadiya da har sai da 'yan hanjin cikinta suka kad'a saboda ganin zallar kyau da Amrah ta mallaka, aranta tace

"Ashe ba banza ba Hubbyna yake ta faman kiran sunanta akai akai hmmmm!"

Tayi ajiyar zuciya a wahale saboda wani kishin Amrah da taji ya tokare mata a mak'oshi, daga nan aka fara yi masu 'yan nasihohin hak'uri da juna tareda addu'o'in zaman lafiya sannan suka tashi suka nufi d'akin Sadiya.

Suna fita Amrah ta sauke k'atuwar ajiyar zuciya ta kalli Aunty tayi dariyar yak'e tace

" Kinga Amarya masha ALLAH itama da kyaunta Aunty"

Aunty tayi murmushi sannan tace, "amman ai duk kyaunta batayi kyaun 'yata Amrah ba"

Amrah ta rufe idonta zuciyarta cike da jin dad'i tace, "Ni ko sai naga ma kamar ta fini kyau Aunty, sannan naga da alamu zata yi sanyin hali" Aunty tayi 'yar dariya tace

"Wannan kuma Nazir ne zai banbance gaskiyar abunda na fad'a maki, amman ina son kar ki yarda ki bada fuskar da reni zai shiga tsakaninku, ki tsaya matdayinki ba'a shedar halin mutum a ido har sai an zauna dashi, sai kin iya taku sosai WALLAHI saboda zama da kishiya ba k'aramin aiki bane musamman irinki da kuke zaune a gida d'aya dole ne ki kawar da kanki akan duk wani abu da zaki gani, kiyi k'ok'arin kawar da kanki a komi ma nasu da zasu yi kada ki zamo mai yawan saka masu ido saboda gudun ki hanawa kanki zaman lafiya ki tadawa kanki hankali a banza, kiyi jarumtar samarwa kanki da mijinki kwanciyar hankali kada kiyi sakacin da kishi zai hanaki ki farantawa mijinki rai, ki zama jajirtacciya wajen baiwa Mijinki kulawa yanda ya dace domin ki k'ara dasa sonki a kowane lungu da sak'o na zuciyarshi."

Amrah ta sauke k'atuwar ajiyar zuciya tareda gamsuwa da zancen Aunty har cikin ranta, Aunty taci gaba da lurar da ita hanyoyin da suka dace tabi sannan ta bata wata 'yar kwalba tace, "kinga wannan ki rik'eshi dakyau kiyi amfani dashi kafin lokacin da zai dawo gareki INSHA ALLAHU da kanki zaki neme ni har ma kiyi man gdy, sannan ki yawaita shan fruit sosai saboda suna saukar da Ni'ima a jikin mace fiye da duk wani shaye shayen kayan mata da zata yi, kinga had'in SAHARA ko ita kad'ai kika rik'e sha WALLAHI kin kulle..... " zancenta ya katse ne saboda kiran da ya shigo wayarta ta kalli Amrah tace, "Ga Megidana ya zo ni zan wuce ALLAH ya baku hak'uri, kar dai ki manta da duk abunda kika ji na fad'a maki ki ceci kanki da kanki, don rayuwarki ce idan tayi dad'i sai kinfi kowa morewa"

Amrah ta rakota tana ta yi mata godiya tare suka je sashen Inna Aunty tayi masu sallama sannan suka fito har harabar gidan ta rakata sannan suka rabu, Aunty ta wuce Amrah ta dawo da sauri saboda kukan Umar da ta jiyo, aiko juyowar da zatayi suka yi kicib'is da Jamila rik'e dashi tana lallashi, ta karb'eshi tayi d'akinta zuciyarta har lokacin cike take da rud'u ba k'adan ba.

Kuyi manage plsss🤦‍♀️🤦‍♀️

Akafta 😆

D/Auta ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

Misalin k'arfe tara da rabi Nazir ya shigo gidan, sai da yaje wurin Inna yayi mata sai da safe ya bata abunda ya siyo masu sannan ya nufo d'akin Uwargidanshi Amrah, inda ya taradda ita a k'uryar d'akinta kwance sai juye juye take yi akan gado, cike da fargaba ya k'araso cikin d'akin da sallamarshi, tana jin muryarshi tayi saurin tashi taje ta rungumeshi tare da aza masa wani sabon kuka, hankalinshi ya k'ara tashi sosai ya ajiye ledodin da ya shigo da su sannan ya zaunar da ita a bakin gadon yana ta lallashinta har tayi shiru, ya fara kwantar mata da hankali da kalamai masu dadi har ya samu ya ciyo kanta, sannan ya dauko ledodin da suke nata ya ajiye mata ya kalleta da kyau yace,

" tashi ki dauko plate ki juye kici ki koshi kinji?". Amrah ta bata fuska tare da kawar da kanta a gefe tayi jarumtar fadin ,

" In sai tashi muje in raka ka bacci nike ji" Nazir cikin damuwa ya kalli Idanuwanta da suka yi jawur saboda kukan da tasha, haka kawai yake ji a ranshi baya son barinta cikin wannan halin, shiyasa ya mike yaje ya dauko plate da kanshi ya zuba kazar da tsiren da ya siyo masu, cikin dabara ya dinga bata a baki tana ci yana yi mata fira mai dadi har ta kusan tashi da naman duka, sannan ya dauko fresh yoghurt mai sanyi ya mika mata ba musu ta karba ta sha fiye da rabi sannan ta rufe gorar ta ajiye, cike da jin dadi ya mikar da ita tsaye yace

"Zo muje in taimaka maki kiyi wanka don nasan ba kiyi ba ko?"

Ta daga masa kai kamar wata karamar yarinya, aiko da kanshi ya taimaka mata ta tube suka yi toilet , sun d'auki tsawon minti talatin a ciki suna yan wasanninsu na ma'aurata, don shi kanshi a nan yayi wankanshi sannan suka fito dukansu suka kimtsa, ya dauki ledodin da zai kaiwa Amaryarshi ta biyoshi a baya zuciyarta cike da takaicin kwanan da zaiyi a d'akin Sadiya, har sun kai bakin kofar da zata sada mutum da gefen sadiya ta tsaya saboda matsanancin bugun da zuciyarta take yimata, har ya shige kofar ya dawo yace

"Zo muje mana ya kika tsaya kuma?"

Ta rungume hannuwa a kirji ta girgiza kai tace

"Ka je kawai Allah ya tada mu lafiya kasha angwancinka cikin aminci ina yi maku fatar alkhairi kai da Amaryark.....".

Muryarta ta karye saboda kukan da yazo mata ba shiri da sauri ta juya ta shige d'akinta ta dantse, tare da jingina bayanta a jikin kofar tana wani kuka mai cike da tsantsar kishin Mijinta, Nazir ya biyota da sauri ganin ta rufe kofar shima ya jingina a jikin kofar ya dafe kanshi dake tsananin Sara masa saboda jin kukanta da yake yi har tsakiyar zuciyarshi.

Sadiya kam da ta cika ta bak'e saboda rashin zuwan da bai yi ba kuma bayan taji saukar motarshi lokacin da ya dawo, Amman ace har lokacin bai Zo gareta ba gashi har kawayenta sun gaji da jiranshi a siye baki sun tafiyarsu, sai gashi taji motsin shigowarshi bangaren nata, sai dai kuma muryar mace da ta jiyo kasa kasa ya tabbatar mata da cewa matarshi CE, ta kashe kunne da kyau tana sauraren shigowarsu sai kuma taji shiru, cikin damuwa ta yaye lullubinta ta fito tsakar gidan har inda yake tsaye dafe da kanshi, tayi tsaye tareda rike kunkuru tana kare masa kallo tare da nazarinshi yanayin da ta ganshi a ciki, kai tsaye ta gano duk wannan damuwar da yake yi akan matarshi ne, a take ranta yayi kololuwar baci Amman ta yi kokkarin shanye bacin rants ta karaso da faraata ta riko hannunshi tana feshe shi da wani munafukin murmushi ta janyoshi suka nufi d'akinta, ta fara yi masa kalamai masu dadi a kokarinta na son ta mantar dashi damuwarshi, shima ganin yanda take son ganin farin cikinshi ya saki jikinshi ya fara tarairayar amaryarshi,sannu a hankali har ya mamayeta da soyayyarshi, cike da jin dadi Sadiya ta kara dulmiyar dashi akan tafkin soyayyarta, don kuwa sakin jiki yayi ya dinga kwasar ganimarshi yana more aurenshi, inda daga shi har ita sunyi kwanan farin ciki sabanin Amrah da tayi bacci rabi da rabi mai cike da mafalkai kala kala.

A zabure ta tashi zaune saboda wani mummunan mafalki da tayi, inda suna wani lambu suna shakatawa ita da Nazir da dan yaronsu dake ta wasarshi a lambun, sai ga Zuwaira ta nufosu kamar wata zakanya tana zuwa ta fusgo hannunta Nazir ya riketa ta ja ya ja haka sunka dinga yi da ita, a karshe dai Zuwaira ta fisgeta tana janta tana tirjiya ya biyosu da gudu yana Kiran sunanta, ta zura hannu shima ya zuro nashi saura kiris ya rikota sai ga Sadiya tazo ta shiga tsakaninsu, Zuwaira ta fisgeta Sadiya ta fara yi mata murmushin mugunta tana kallo taje ta rungume Nazir, a cikin tsananin tashin hankali ta kwalla masa kira tace,

"Nazirrrrrr!!!!!!!!!!!!!!!!!!"

******

Jiki a sanye ta mike taje toilet ta dauro arwallah ta dukafa nafilfili tana rokon Allah yasa kada Zuwaira tayi nasarar rabata da Mijinta, ta dauki tsawon lokaci tana addua sannan wani bacci

yayi awon gaba da ita.

aAsubar farin Umar ya tada ita daga nannauyan barcin da ya kwasheta, ta mike taje ta daukoshi tana shayar dashi sannan ya koma bacci, ta lallaba ta ajiyeshi taje tayi sabuwar arwallah tazo tayi sallah tareda karatun alkuraninta har gari ya fara haske sannan ta mike ta shiga wanka, bayan ta fito ne tayi wa Umar ta shiryashi sannan ta fito zuwa sashen Inna, zuciyarta cunkushe saboda jin haushin rashin motsin Nazir da bata yi ba har lokacin.

Kasancewar dakin Inna cike yake da bakin nesa da basu tafi ba, haka ta bisu da gaisuwa daya bayan daya har ta isa wurin Inna, ta durkusa ta fara gayar da ita cike da jin dadi Inna ta karbi Umar tana yi masa wasa, sannan ta tambayi Inna abunda zaayi na Karin safen baki duk da taga an dora tukunya, Inna tace taje abunta har an Dora ta nace akan ita dai sai anyi aikin da ita, ta fito tsakar gidan kenan da nufin yin aiki sai ga Nazir ya shigo sashen Innar Sadiya a bayanshi, turus Amrah tayi saboda faduwar gaban da ya ziyarceta ba shiri, Nazir din kanshi sai da taji kirjinshi ya bugs saboda hada idon da yayi da ita yayi jarumtar fesheta da wani kayataccen murmushi, ta dan rabe gefe ta bashi hanya ba tare da ta nuns ta kula da abunda yayi ba, Sadiya ta Dan fadada fuskarta tace

"Aunty INA kwana?"

Amrah ta kawar da kanta gefe tare da wayancewa ta hanyar dukawa ta dauki tsintsiya tace,

"Lafiya lau Amarya ya bakunta?".

Sadiya tana murmushi tace

"Ai mun zama yan gida tun jiya".

Tana kare fadar maganar ta shige dakin Inna, Nazir kam kasa motsi yayi balle ya shiga dakin, saboda lafazin da Sadiya tayi yasa ya ji duk ba dadi, saboda yanayin fuskar Amrah da ya gani Kirjinta ya buga tayi saurin dagowa ta kalli Nazir a fakaice, suna hada ido tayi masa wani kallo sannan ta duka ta fara sharartа, jin sautin wata a bayanshi tana gaidashi yasa shi juyawa suka fara gaisawa.

Amrah kam agurguje ta kammala sharar ta tayi dakinta saboda wani sabon kukan da yazo mata saboda tuno mafalkin da tayi,zuciyarta cike da jin tsoron abunda zai je ya dawo aranta tace

"Da gaskiyarki Sadiya kin zama yar gida nice sai har yanzu bansan matsayina ba".

Taci gaba kukanta gwanin ban tausayi jin an dafa kafadarta yasa tayi saurin dago kanta, gabanta ya buga damm! Saboda wani kyau da taga Nazir din ya kara yi mata,Wanda bata San yana da irin wannan kyaun ba a yan kwanakin da zuciyarta ta tabbatar mata da irin son da take

yi masa, Wanda ko Salis da taso a baya bata ji tana yi masa irin wannan son ba, ya saka hannu yana share mata hawayen da suka wanke mata fuska.

D/Auta ce🤝

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITERS ASSOCIATION

Aisha tana godiya sosai da adduoinku tana alfakhari da samun iyaye irinku masu kaunarta da zuciya daya, nima ina godiya sosai Allah ya bar zumunci 🤝

PAGE 41

Damuwa kwance akan Fuskarshi yace "Kiyi hakuri maman Umar farouk nasan nayi maki laifi sai dai kisani ba'a son raina bane, don bani da wata hanyar da zan bi ne da ban yarda hakan ta faru ba, ina son ki karfafa mani gwiwa wajen daidaita adalci a tsakaninku".

Amrah ta sassauta kukanta tace

"Ka tashi kaje plss kada matarka taga ka shigo wajena ranta ya b'aci, don itace take da tabbas din zama yar gidan ba ni ba da zamana yake k'ila wa k'ala"

Gaban Nazir ya fad'i ba shiri cikin wata sabuwar damuwa ya rik'o hannunta yace,

"Yanzu ke zaki iya bari a raba mu?"

Amrah ta Mike tsaye tare da yin taku d'aya zuwa biyu ta tsaya, yabi bayanta yana karewa kykakkyawar halittarta kallo, Amrah ta rungume hannuwanta a k'irji tace,

"A da ina jin ko na rabu da kai bazan ji komi ba har ma zan sami Wanda ya fika sona, sai dai a d'an zaman da nayi da kai yanzu na gano rabani da kai tamkar rabani da rayuwata ne, haka ma jikina yana bani a duk fad'in duniyarnan babu wani mai sona sama da son da kake yi mani, na gamsu da hakan a jikina da zuciyata har ma da ruhina duka, sai dai kuma yanzu ganin kana da wacce kake so take sonka sai naga ai ba wani abu bane don na matsa na baku waje kuji dad'in shanawa ba takura, amman ina son kasani soyayyar Nazir ta yiwa zuciyata Illar da har abada bazan taba jin sa'ida a cikinta ba matuk'ar ba....."

Ta k'are maganar cikin wani sabon kukan da ya sark'eta, Nazir ya mik'e ya zo bayanta ya tsaya tare da rungumota a jikinshi ya dora kanshi saman kafad'arta murya K'asa k'asa cikin shauk'in sonta da ke fisgarshi yace,

"Nazir naki ne fiye da tunaninki haka ma ki rike a ranki yana maki so irin wanda ko kanshi baya yiwa shi, idan kin barshi wane hali kike tunanin zai shiga? Ina son ki d'auka cewa raba Nazir da Amrah tamkar rabashi da rayuwarshi ne, don kuwa zai zama mutum mutumi ne a tsaye amman baya wani amfani a doron duniya, shiyasa bana fatar zuwan wannan rana da na hak'ik'ance zata zo muna"

Ya k'are maganar tareda juyota ya tallafo fuskarta ido cikin ido yace,

"Ina sonki Amrah ina sonki so wanda bazai kwatantu ba a cikin zuciyata, I love you so much my life and all happiness"

Ya sumbaci idonta sannan ya zaunar da ita akan gadon ya durkusa ya rik'o hannunta duka biyu yace

"Ina son kiyi man alk'awali guda d'aya akan duk runtsi ba zaki tab'a rabuwa dani ba"

Hawaye suna zuba akan fuskarta tace, "bani da wannan hurumin sai dai kai da igiyar auren take a hannunka kana da ikon yin abunda kaga dama da ita kuma a lokacin da ka so".

Nazir ya mik'e cike da tsantsar farin cikin wannan dama da ta bashi yace, "idan ko har haka ne to ba shakka bazan yi wasa da igiyoyin aurena ba, nagode sosai Allah ya bar manke har k'arshen rayuwata kuma ya k'ara hada kanku keda k'anwarki Sadiya"

Sunan Sadiya da taji ya ambata tayi saurin k'wace hannunta dake cikin nashi ,saboda jin da tayi

kamar an watsa mata garwashin wuta tayi saurin mikewa tace,

"Bari inje wajen Inna in taya su aiki".

Nazir yayi saurin rik%o hannunta ya mike tsaye yace, "na manta jiya ban sanar da ke ba akwai komi na bukata da na shigo da su nasa akai maku kitchen idan akwai abunda kike so kije ki girka muna muyi break fast da shi, sai dai kuma yanzu gashi lokaci ya kure amman dai muje in tayaki".

Amrah ta fito ya biyo bayanta har zuwa kitchen din da ke tsakiyarsu ita da Sadiya, yana zuwa ya fara fiddo mata kayan yana nuna mata a gurguje ta har hada abunda take bukata yana tayata suna girkin kafin kace me gidan ya gauraye da kamshi, aiko sai ga Sadiya ta fito daga d'akinta saboda jin muryarsu da take ji kasa kasa suna ta firarsu suna dariya, cike da takaici tazo kofar kitchen d'in ta rik'e kugu tana k'are masu kallon yanda yake bayan Amrah ya rungumeota yana taya ta wankin cups din da take yi suna wankewa tare, tayi saurin komawa d'akinta zuciyarta cike da kishin abunda ta gani taje ta kwanta tana nazarin abun yi don bazata zura ido tana kallo ana yi mata cin kashi ranar girkinta ba, haka kawai a dinga cin amanarta a cikin kwanakin girkinta.

Ko da suka kammala hada girkin falon Nazir aka ajiye komi yace da Amrah taje ta kirata, duk da bata so zuwa ba amman haka ta daure taje d'akinta Inda ta taradda ita ta cika fam kiris take jira ayi wadda za'a yi da ita, ganin yanayinta yasa Amrah tana fada mata ta juyo abinta ta dawo, tsawon lokaci suna jiran ta fito amman suka ji shiru dole shi Nazir d'in be ya mike da kanshi ya je ya kirata, sai gata ta zo tana wani cin magani tana kumbure kumburen fuska, ba tare da Amrah ta kulata ba ta had'a nata ta fara karyawa abunta, ganin yanayin fuskarta yasa Nazir yace da Sadiya ta had'a masa ta sauko ta had'a masa din kamar yanda ya nema ba tare da nata ba ya kalleta yace

"Ke fa?"

Ta yatsina fuska tace

"Na k'oshi"

Ya ajiye cup din yace

"Me kika ci ?"

Ta yi shiru tana wasa da yan yatsunta sai ga kuka shaaaa a fuskar Sadiya, da sauri yace

"Lafiya? Me aka yi maki?"

Sadiya ta fara sharar hawaye tace

"Ni dai gaskiya bana son wata ta dinga yi man girki a barni inyi abuna da kaina tunda nima na iya."

Cike da mamaki Nazir yace, "look Sadiya kada ki fara zo man da matsala cikin gida bana so, ai ni a ganina taimakonki aka yi kafin ki saba da gidan nan da kwana biyu zuwa uku sai a sakar maki aikinki ki ci gaba, amman tunda bakya so shikenan ma kin hutar da ita sai ki shirya yin girkin rana Idan na aiko da cefane"

Sannan Sadiya ta saki jikinta ta fara karyawa tana wani shagwaba tana makale masa, wai duk don ta rama abunda aka yi mata ta turawa Amrah haushi, sai dai gano manufarta yasa Amrah ta nuna ko a jikinta tana karewa ta mike ta fice ta bar masu falon, Nazir ya bita da kallo har ta fice sannan cikin bacin rai ya kira sunan Sadiya yace

"Bana son abunda kike yi don haka ki daina matuk'ar kina son ganin farin cikin,sabida ba wai don bana son matata na aureki ba ke kinsani tun farko na sanar dake irin kaunar da ke tsakanina da ita, don haka ban lamunci duk wani cin fuska ko cin zarafin da zai fito daga gareki zuwa Uwargidana ba, ki kiyaye sake faruwar hakan indai kina son mu shirya ni da ke"

Kasancewar Sadiya mutum ce mai sauk'in kai kuma tana gudun b'acin ranshi sosai saboda masifar son da take yi masa, shiyasa ta bashi hakuri har da d'an guntun hawayenta akan bazata koma ba, sannan ya saki jiki suka ci gaba da cin abincin suna firarsu ta sababbin ma'aurata"

Tun daga ranar Sadiya ta karb'i girkinta amma tana takatsantsan akan abunda zata yiwa Amrah a gabanshi, hasali ma sai ta fara jin shakkun ita Amrah'r saboda ganin ko in kular da take yi da ita bata shiga shirginta, Wanda hakan ya yiwa Nazir dad'i ganin gidanshi ya zama nashi.

Ranar da Sadiya ta yi Kwana hudu a gidan tunda sassafe sai ga kiran Alkali Yusha'u ya shigo a wayarshi, yana ganin kiran nashi yayi zumbur ya tashi zaune cikin wani sabon tashin hankalin da ya ziyarceshi ba shiri, saboda ko baa fad'a ba yasan kwanan zancen, Sadiya ta bishi da kallo zuciyarta cike da mamakinshi, Nazir kam hannunshi yana rawa ya d'aga wayar aikuwa sai gashi Alk'alin yana cewa,

"Nazir ka zo da Amrah ga Mamarta nan ta kawo kud'in kamar yanda aka kai karshe a kotu, a kan da ta kawo maka kud'in huld'inka ka baiwa yarta takardar sallama, to ga ranar ta zo yau ka zo da ita yanzunnan gamu nan zamu je kotun sai mu hadu a cen gaba daya"

Nazir kam Jib'i sai sauko masa ya keyi tun daga saman kanshi har zuwa tafin k'afarshi, cikin rud'ewa ya fara safa da marwa a tsakiyar d'akin yana kiran "Innalilahi wa inna ilaihirrajiun."

Akafta👩‍🦱

D/Auta ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITERS ASSOCIATION

Wannan page naki ne sukutum dungurungum Hajiya Luba my mommah💋 mum 4 ful H har dani😹🤪 ki dade kiyi lasting uwa tagari👍🏻

PAGE 42

Cikin firgici Sadiya ta rikoshi tana tambayarshi "lafiya?" "me ya faru?" Amman ya kasa furta ko kalma daya a gurguje ya fada wanka ya fito yana saka kaya yace da ita fita zai yi, Sadiya dai kam tsure take da shi saboda jikinta ya bata cewa ba lafiya ba, ya saka talkaminshi ya fito ta biyoshi da nufin rakashi taga yayi dakin Amrah, cikin jin haushi ta ja ta tsaya tana ta yatsinar fuska tana fushi, Nazir kam bai ma san tana yi ba kai tsaye ya fada dakin na Amrah ya taradda ita a gaban mirror tana daurin dankwali taci wankanta, ya karaso cikin sanjin jiki ya rungumota

tare da runtse idonshi tare suka sauke ajiyar zuciya, cikin mayen sonta ya fara sunsunar wuyanta da daddan turaren da ta fesa, saboda dan kwanakin da yayi bai kusanceta ba jin yake yi tamkar anyi shekarru, gashi kuma rana tsaka wannan balain ya rufto da su baisan ya zai yi da rayuwarshi ba matukar bai samu ya rabi jikinta ba, sai ga saukar hawaye shaaa a kan fuskarshi saukar hawayen a wuyanta yasa ta yi saurin juyawa suna facing din juna, cikin mamaki tace

"My Real me ke faruwa ne? ko wani abun aka yi maka?"

Ya zagayo hannuwanshi ta bayanta hawayen suna zuba yace, "Amrah ki taimaki rayuwata kada ki bari a raba mu wallahi zamu shiga gararin rayuwa matukar kika bari aka raba mu, saboda kin dace da ni nima na dace da ke zamu fi jin dadin zamanmu idan aurenmu ya dore, saboda yanzu Alkali ya kirani yake sanar dani Mama ta kawo kudin mu kawai ake jira a kotu".

Cikin firgici Amrah ta dafe kirji tace "innalillahi wa inna ilaihirraji'un" ta fada jikinshi tare da kankameshi ta fashe da kuka, shima yayi mata kykkyawan mazauni a kirjinshi rungumeta tsantsan tare da sauke wata nannauyar ajiyar zuciya.

Amrah kam sai kukanta take yi Nazir ya janyota suka zauna bakin gado ya fara lallashinta ta hanyar lashe duk wata kwayar hawanyar dake saukowa idonta, jin laushin halshenshi a fuskarta yasa ta fadawa cikin wata duniyar, a take daga shi har ita suka birkice tare da dimaucewa sai yamutsa juna suke yi cikin mayen so, yana gaf da shiga lambun ne Amrah ta fara girgiza masa kai tare da yin karfin halin fadin, "kada son zuciya ya debemu mu aikata haramci Yaya Nazir, kasan har yanzu baka zama nawa ba kada mu shiga hurumin da ba namu ba". Cikin wata kasala ya mike tare da dafe kanshi yace

"Oh sheet!! Ina ma ban yi wannan auren ba? Ina ma babu wannan katotuwar matsalar dake gabanmu? Ni Nazir ya zanyi da rayuwata ne?". Sai tambayoyi yake ta jerawa kanshi wadanda basu bukatar amsa, cikin tsananin tausayinshi take kallonshi itama nata hawayen sai kwaranya suke yi, don a yanzu ta gano dukansu su biyun ne abin tausayi ba ita kadai ba, cikin dakiya tare da gayyato wata jarumta ta yafa ta mike ta fara gyara jikinta ta sauko hijabi ta saka ta mika masa hannu da nufin ya task su je, yabi hannun da kallo har zuwa fuskarta cikin mamakin jarumtarta yace, "Ina Umar?" Ta share hawayen fuskarta tace, "yana wurin Inna" ya kama hannun nata ya yunkura ya mike tsaye suka fito tare, Sadiya kam tana nan inda ya barta da ta gaji da tsayuwa ma ta tsugunna tare da soke kanta cikin runfar da tayiwa hannunta tana sharar hawaye, ganinsu sun fito rike da hannun juna yasa ta yi saurin mikewa tana kallonsu, kasancewar basu cikin hayyacinsu yasa basu lura da kallon da take yi masu ba, ganin sun nufi har fita ne yasa ta biyo bayansu zuciyarta cike da kishinn Amrah kamar ta shakota take ji, ganin sun nufi wurin Inna yasa itama ta biyo bayansu sai lokacin Amrah ta zare hannunta cikin nashi.

Inna kam yanayin da ta ga fuskokinsu yasa taji faduwar gaba cikin zullumi tace, "lafiya Naziru?". Nazir ya zauna sharaf Amrah ma ta dan durkusa tana gaida Inna sannan ta zauna, Sadiya ma ta shigo ta gaidata itama ta zauna tana jiran taji abunda Nazir zai fada,amman sai gashi taga ya mike ya nufi kuryar dakin Inna yace da ita ta zo taji, Inna tabi bayanshi zuciyarta

cike da fargabar tabbatuwar zarginta, sai gashi Nazir ya fayyace mata komai akan abunda Alkali yace, Inna tayi shiru na dan lokaci sannan tace

"Wannan tafiyar dani zaa yi ta".

Nazir yayi saurin kallonta ta tabbatar masa da hakan wajen jawo hijabi ta saka sannan ta kwanto Umar dake bayanta goye ta rungumeshi suka fito dakin fuskarta a hade, ganin Sadiya yasa ta dan saita kanta tace da ita

"Sadiya bari muje wani wajen mu dawo yanzunnan ki kula da gidan kinji?".

Sadiya ta dan yi murmushin karfin hali tace "to Inna a dawo lafiya" suka fice suka barta tana wasi wasin zuci akan abunda suke yi mata boyo basu son ta sani.

Amrah dai biye da su kawai take har suka shiga motar suka bar gidan, suna tafe kowanensu shiru ba mai cewa komi kowa da tunanin da yake yi a ranshi har suka je kotun, inda tun kafin su isa suka hango kotun makil da dan Adam alamun wata zazzafar shiria CE akeyi, suka firfito suka nufi cikin dakin shari'ar ganin mutane damkam a ciki yasa suka dan raba, suna nan tsaye har aka kare shariar sannan aka kira sunan Zuwaira da yarta Amrah da Nazir akan su hadu a dakin sulhu ana nemansu, Sannan aka tashi hutun gajeren lokaci kafin adawo ayi wata shariar.

Nazir da Inna da Amrah suka nufi inda ake fadar su hadu acen, aiko sai gashi tun daga nesa sun hango Zuwaira da kawarta Lantana zaune suna fira zuwaira tana masifa, Amrah ganin mahaifiyarta yasa ta faduwar gaba ba shiru duk da taji dadin ganinta ba kadan ba, sai dai kuma ramar da taga tayi yasa taji wani tausayinta ya kamata, har suka karaso Zuwaira bata lura dasu ba sai da Amrah tazo gabanta tana yar dariyar jin dadin ganinta tace

"Mama!" Zuwaira tayi saurin kai kallonta kanta ganinta yasa ta yi saurin washe fuskarta tace, "Allahu Akbar 'yata ta dawo hannuna sannu Amrah kinji kin ganni nan kullum ban kwana saboda tunanin halin da kike ciki" Amrah ta riko hannunta cikin jin dadi tace, "nima haka Mama".

Nazir ya karaso wurinsu ya durkusa har kasa ya gayar dasu, cike da mamaki zuwaira ta bishi da kallo a lalace ta kawar da kanta gefe, sai Lantana CE kadai ta amsa Amrah kam kunya tasata fadin "Mama ga Inna fa tare muke da ita". Zuwaira ta yi saurin kai kallonta ga Inna kwarjinin da ta yi mata a ido yasa ta gayar da ita ciki ciki, Inna ta amsa ba yabo ba fallasa Zuwaira ta murguda baki kamar wata karamar yarinya ta mayar da kanta sunata firarsu da Lantana, cikin sagewar gwiwowi Nazir ya mike cikin damuwa ya samu wajen zama ya zauna,yana Nazarin har zuwa yaushe Zuwaira zata saduda ne? Ta girma har da jika amman duk a banza, yana cikin tunane tunanen ne Alkali ya shigo dakin kowa ya gyara zamanshi, aka fara gaggaisawa dashi cikin fara'a yake ta amsawa sannan ya kalli Nazir yace

"Ga kudinka nan Mamar Amrah ta jawo kamar yanda ta nema tana bukatar ka sauwakewa

'yarta"

Nazir ya sunne kai yayi shiru na dan lokaci sannan ya dago fuskarshi mai cike da damuwa yace, "Ranka ya Dade Ina son Matata ban shirya sakinta ba har zuwa nan da shekara hamsin masu zuwa in da rayuwa".

Zuwaira ta yi zumbur tace, "wallahi karya lake yi ba ka is a ba sai ka Dakar man 'yata"

Amrah ta durkusa har kasa gaban Zuwaira tana hawaye race,

"Don Allah Mama kar ki raba mu wallahi ina sonshi"

Zuwaira ta tureta da karfin tace, "ke gudu sakarya ina kika San so bale kice yanzu kina sonshi , tun cen da baki San da son ba sai yanzu da suka je dake suka dibga maki asiri sannan ki zo kina karantawa mutane shirme, to wallahi bazan barki kiyi wannan kaddararren auren ba kudi dai ne aka nema in kawo kuma na kawo dole ne idan har alkalin mai adalci ne to ya cika alkawalin da ya dauka yasa a sauwake maki kawai a raba gardamar kowa ya huta"

Ba alkali ba duk Wanda ke wajen yasan shagube ne take yi a maganarta mai kunshe da harshen damo, don gurinta na son gayawa Alkali magana a fakaice.

Alkali yusha'u yayi yar gajeruwar dariya yace, " a lokacin da muka yanke wannan hukuncin ita Yarinyar da ake rigimar kanta bata sonshi kuma ta furta a Gaban kowa yaji hakan, shiyasa aka nemi ta nashi huldi ya sauwake mata amman yanzu tunda har gashi tana fada da bakinta tana son abunta, to a shawarce ina baki shawara da ki barta da Mijinta ke kanji sai kin fi jin dadi shikenan sai a sasanta juna komi ya wuce a zauna lafiya"

Zuwaira tayi saurin fadin, "ban amince ba wallahi ya dai bats takardarta kawai a wuce wurin".

Alkali yayi murmushi mai cike da takaici yace, "OK tunda haka kika zaba kai Nazir ga takarda da Biro kotu ta baka dama da ka rubuta Amrah takardar sakinta". Aka mikawa Nazir takardar ya dirrice jikinshi yana rawa saboda tashin hankali, ya karbi boron da nufin fara rubutun cikin dimuwa aguje Amrah ta is a wurinshi ta fisge biron hawaye suna zuba ta fara girgiza masa kai tace

"Tunda Kana sona nima ina sonka wallahi banga Wanda ya isa ya raba mu ba a fadin duniyarnan sai mutuwa,nayi alkawalin zama da kai cikin dadi ko wuya bazan taba guje maka ba don nafi kowa Sanin alfanunka a wurina, Kaine Mijina kuma uban yayana na har abada ruwa da iska ba zasu rabani da kai ba".

Ta kare maganar cikin durkushewa tana wani gunjin kuka gwanin ban tausayi, Zuwaira ta nufota kamar wata zakanya ta kai mata wani bahagon mari tareda hada mata da wani urban shuri sai da ta yi balance a kasa, a miliyan Nazir ya iso wurinta zai dagata shima ta wankeshi

da wani lafiyayyen mari, kamar wata mahaukaciya ta saka hannu biyu ta turashi baya da karfi yayi taga taga zai fadi Inna ta zo da sauri ta rikeshi cikin wani fushi mai tsanani ta daga hannu ta wankawa Zuwaira Maruka har biyu sai da taga taurarin wuta suna tartsatsi a idonta, kafin ta tantance inda take taji sautin muryar Inna tsakiyar kanta tana fadin, "ke wace irin mahaukaciyar mata CE da zaki dinga cin zarafin mutane ana kyaleki saboda kawaici amman bakya gani? To buda kunnuwanki da kyau kiji diyarki ko diyar lu'u lu'u CE Wallahi in dai ni na haifi Naziru ba zai zauna da ita ba a yanzu, kije da ita ki jikata ki shanye bama so bama so dan da ke tsakani ma mun bar maku don ko a lahira bana fatar dana ya koma zama da yarki"

Ta juya ga Nazir tace

"Idan har nice na haifeka Nazir to na baka umurnin ka sauwakewa Amrahtu yanzunnan".

Daga Amrah har shi Nazir din sai da gabansu ya fadi, cikin zafin nama Amrah ta tashi ta durkusa ta rike kafafuwan Inna tace, "Inna ke Uwa CE mai adalci kada ki bari fushin zuciya ya debeki ki rabamu tunda har kinsan muna son junanmu, Inna ki tallafi zuciyoyin masoya biyu kada ki bari su shiga cikin gararin rayuwa"

Inna ta duka ta tadota tsaye tana share mata hawayen da ke ta sauka kamar zubar ruwan fanfo tace, "ina jin sonki Amrah a raina tamkar diyar da na haifa da cikina, kiyi hakuri da hukuncin da kika ji na yanke ki rungumi kaddararki ki yiwa Mahaifiyarki biyayya, komi daren dadewa gaskiya zata yi halinta ki barwa Allah komi ki rungumi jarabawarki da sannu Allah zai yaye duhun da ya rufewa Zuwaira ido ta kasa hango gaskiya.".

Ta juya kan Nazir ta hade fuska tace, "kayi abunda nasaka matukar ina da matsayin da ake kirana da sunan Uwa a wurinka"

Nazir ya kawar da kanshi gefe yace, "Na sake ki Amrah saki daya".

Yana kare fadar maganar ya fice dakin cikin sauri saboda kukan da ya zo masa, Inna ta kwanto yaron da ke bayanta yana ta baccinshi ta mikawa Amrah, Zuwaira tazo da sauri ta janyeta tace, "Billahillazi bazata karbeshi ba ki je da shi tunda har baki ji kunyar raba auren ba to kije ki rike yaron an bar maki."

Ta fisgo hannun Amrah da karfin gaske tana turjiya tana kuwwar fadin ta bari ta karbo yaronta amman ta fice da ita a hakan saboda rashin Imani irin na Zuwaira😭.

Akafta😢

Princess Dija D/Auta CE ✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Kiyi hakuri da shiruna na Samu marsalar waya be shiyasa amman yanzu komi normal Insha Allah Ina godiya sosai da kulawarku masu kirana da masu turo man massages duk Ina Gdy har ma da wadanda suka tunani a zuci duka nagode sosai Allah ya bar zumunci🤝

PAGE 43

Zuwaira Kam janta kawai take iya k'arfinta tana tirjiyar kiran ki bari in karb'o yarona don Allah, amman Ina idonta sun rufe zuciyarta ta bushe bata jin komi a kunnuwwnta sai kalaman INNA inda tace,

"D'iyarki ko lu'u lu'u ce Wallahi indai Ni na haifi Naziru ba zai zauna da ita ba kije da ita ki jik'ata ki shanye bama so bama so!!!!!!!"

Maganar Inna sai amsa amon kuwwa take yi mata cikin kunnuwwanta, idonta a rufe bata ganin komai sai gabanta suna fitowa Amrah ta hango Nazir cikin motarshi ya Duke kanshi ga sitiyarin mota yana kuka gwanin ban tausayi, Amrah cikin wani sabon karfin da ya zo mata ta k'wace hannunta cikin na Zuwaira ta nufoshi da gudu tana zuwa ta fad'a jikinshi tana wani irin kuka mai tsuma zuciyar mai sauraro, Nazir Kam mutuwar zaune ce yayi saboda jinta da yayi a jikinshi gaba d'aya zuciyarshi da gangar jikinshi sun daina aiki na wuccin gadi, ya kasa dagowa daga duk'en da yake kunnuwanshi kawai ke sauraren kukanta, amman tuno da yayi yanzu fa ba muharramarshi bace yasa ya d'ago fuskarshi a hankali ya b'anb'areta daga jikinshi, ya kawar da kanshi a gefe bai bari sun had'a ido ba tare da jarumtar furta cewa,

"Kiyi hakuri mu yiwa Iyayenmu Biyayya mu rungumi k'addararmu Allah zai kawo muna mafita"

Amrah tana kallonshi hawayen idonta Basu daina sauka akan fuskarta ba tace, "Kai fa kace kada in bari a rabamu me yasa yanzu ka manta komi ka wofintar da alk'awalinmu??" Yayi shiru ya kasa furta komi saboda kololon bak'in cikin da ya zo ya tokare masa k'ahon zuciya, har Zuwaira ta karaso wurinsu ta cira hannu ta kwad'a mata wani bahagon Mari, ta kalli Nazir tana huci tace

"Allah ya Isa tsakanina da Kai tunda har ka yiwa 'yata asirin da zata so ka Ni ta bijiremani Wallahi ban yafe maka ba mugu azzalumi macuci bak'in Munafuki sai nayi ajalinka na sake ganinka kusa da 'yata".

Nazir ya bita da kallo kamar wani Wawa har suka shige Napep suka bar wajen, a take yaji wani sabon kuka ya zo masa ya fashe da wani kuka mai tsanani Yana ambaton sunan Amrah a fili da cikin Zuciyarshi.

INNA Kam bin k'ofar da Zuwaira ta bi take da kallon mamakin tsagwaron rashin Imani irin nata, saboda k'arfin halin raba Uwa da d'anta da tayi tabbas yanzu ta tabbatar da cewa Zuwaira ta wuce duk inda take tsammaninta, cikin sanyin jiki ta dawo da kallonta ga Alkali Wanda Shima kanshi abun ya tab'a masa zuciya, Amman tunda Basu da yanda zasu yi dole ne su barwa Allah komi shikadai yasan me ya tsara a gaba kuma, yayi jarumtar d'auko kud'in da hannunshi ya zo gaban Inna ya tsaya
sannan ya Mik'a mata kud'in yace,. "Ga kudi'n Nazir sai a bashi Allah ya zab'a masu abunda yafi zama alkhairi"

Inna ta karb'i kud'in tace "An gode sosai da k'ok'arinka Ubangiji Allah ya K'ara kareka da sharrin mutum da aljan kuma ya saka maka da gidan aljannah"

Cikin jin dad'i Alk'alin yake ta fad'in "Ameen Ameen Inna nagode Allah ya rufa asiri ayita hak'uri Allah zai kawo sauk'i cikin lamarin insha Allahu"

Inna tace

"Muna fatar hakan Allah dai yayi muna jagora"

Duk Wanda ke wurin yace ,. "Ameen"

Sannan ta fito da Umar rungume a jikinta dauke da ledar kudin da Zuwaira ta bada,. Hango Nazir da tayi duk'e tun daga nesa ya tabbatar mata da cewa kuka ne yake yi, zuciyarta a jagule ta Isa wurinshi ta Kira sunanshi cikin hadewar fuska, da sauri ya dago fuskarshi Yana share hawayenshi ya tada motar, Inna ta bud'a motar ta shiga suka bar bak'in k'ofar kotun zuciyarta a cunkushe da damuwa musamman idan ta Kai kallonta ga Umar har wasu hawayen tausayinshi take sharewa a fakaice, don bata son Nazir yaga fuskar da zai kawo mata wasa har yace zai yi jayayya akan duk abunda zata gindaya masa, shiyasa har suka isa gida ba wata maganar da ta had'asu shi da ita kowa da zancen zucin da yake yi.

Inna tana fitowa ta Fara goya Umar sannan ta d'auko kud'in zata shiga cikin gidan, ta Kai kallonta ga Nazir da yayi zaune abinshi ko alamar zai fito daga motar bai yi ba, Inna ta Kira sunanshi tace

"Ka sameni a ciki Ina son muyi magana"

Tana k'are maganar ta wuce shikam sai da ya D'an ja lokaci yana tunani sannan ya fito ya rufo motarshi yayi sashen nata,.

Shigarshi d'akin yasa gabanshi ya Kara faduwa saboda ganin yanda Inna ta had'e fuska tamau alamun ba wasa yasan akwai magana, jiki a sanyaye ya zauna Amman ya kasa furta komi sai shiru da yayi yana sauraen abunda zata fad'a, Inna cikin dakiya tace dashi

"Ka taimaki kanka ka cire wannan damuwa da kasa a ranka don wannan hukuncin shine dai-dai da ku ko don ka tsira da mutuncinka da kimarka a wurin Zuwaira da idanun duniya, ka mayar da hankalinka kacokam akan yaronka da tarbiyyarshi kada ka yarda kayi sakacin da zai yi kukan rashin Uwa, ka zamo masa Uwa da Uba aboki, dangi, kanne, da yayu, duk runtsi kada ka waiwayi Amrah matuk'ar ba Zuwaira ce zata nemeka da kanta ba, ga matarka nan a gida kana da ta isheka rayuwa idan ma kana da bukatar wani auren kaje ka Nemo duk Yar da kake so ka zo ka auri abukka, wannan kudin kuma ka cire dubu d'ari biyu kaje gidan Mijin da Amrah ta aura Wanda har ka yi cikin Umar gidanshi, ka Kai masa ladar zuwa gidanshi da kayi har ma ka raya sunnar aurenka a ciki, sannan ka bashi hakuri sosai ka nemi yafiyarshi akan abunda kayi masa, haka ma duk wad'anda kasan ka cutar dasu kaje ka nemi yafiyarsu kuma ka biyasu duk abunda suka kashewa matarka a lokacin."

Nazir ya d'ago fuskarshi cike da damuwa yace,. "Inna Baki ganin kamar akwai matsala idan na tunkaresu da wannan maganar?".

Inna ta sauke ajiyar zuciya tace,. "Gara ka fuskanci kowace irin matsala ce matukar dai zaka Samu su yafe maka abunda kayi masu, don kasani ko wannan abun da ya faru da Kai yanzu Yana cikin sakayyar da Allah ya Fara yi masu akanka, saboda a tabbatar maka da cewa Babu Wanda ya Isa yayi jayayya da hukuncin Ubangiji kuma ya zauna lafiya matukar bai tuba ga Allah ba kuma ya nemi yafiyar duk wad'anda ya zalunta, duk da na fahimceka sosai da kuma dalilin da yasa ka kaucewa hanyar gaskiya zuwa bata, Amman hakan ba zai hanani fad'a maka gaskiya ba don haka kaje ka yi yanda nace maka Umurni ne Nike baka ba shawararka Nike nema ba, sannan yaronka kuma ka Nemo masa Madara a dinga bashi Yana Sha"

Nazir ya zaro ido yace

"Me zai Hana a mayar mata da yaron Inna ? In yaso sai in dinga biyanta kudin shayarwar sai ta ci gaba da shayar man dashi har a yayesa in karb'o abuna".

Inna ta girgiza Kai zuciyarta tana Kuna tace,. "Ba zamu maida shi ba tunda har Zuwaira bata ji kunyar rabashi da mamanshi ba to mu kuma ai bazamu nuna gajiyawarmu ba"

Nazir ya yi tagumi cikin matsananciyar damuwa yace, "To me zai Hana akaiwa Jamila shi ta ci gaba da shayar dashi?"
Inna ta yi saurin fadin

"Ba fa inda zamu kaishi mu zamu rikeshi da hannunmu tunda har hakan ta kasance ba yanda zamu yi dole ne mu rungumi kaddararmu Koda Allah zai ji tsusayinka a sanadiyyar hakan ya yafe maka abunda kayi". Nazir yayi shiru na Dan lokaci sannan yace,. "To Inna ba wata matsala idan aka Fara bashi Madarar yanzu? Saboda naga ko wata biyu ba'a rufa ba"

Inna tayi gajeruwar dariya tace,. "Sau nawa Uwa take faduwa ta mutu ta bar jaririnta da ta haifa wani ko kallonshi bata taba yi ba, Amman a hakan ake shayar dashi Madara kuma ya girma ya zama kamar kowa? Kayi kawai abunda nace da kai insha Allahu Allah zai shiga cikin lamarinmu"

Nazir ya Mik'e cikin jin wani sabon k'arfin da ya zo masa yace,. "Allah ya dafa muna"

Inna tace "Ameen"

Nima dai nace Ameen din😢

Manage plss🤝

Akafta😅

D/AUTA ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

COMMENTS dinku shi ke Kara Mani k'arfin gwiwa idan kunyi likimo Nima zan gwada yin irin nawa😅

Nazir har ya fice Inna tace,. "Ka manta da kud'in". Sannan ya dawo ya bud'e ledar ya Ciro kud'in duka ya Fara lissafawa sai gasu cas cas kamar yanda aka fad'a, zuciyarshi cike da jin k'unci mai tsanani ya d'auki wasu kud'in ya saka aljihu sannan ya k'ulle saura ya ajiye gaban Inna ya fice,. Inna ta bishi da kallo cikin tsananin tausayin D'an nata, sannan ta dawo da kallonta akan D'an guda gudan jikanta da Allah ya bata, a take wasu hawayen masu zafi suka gangaro mata akan fuska ta saka gefen Zane ta share hawayen, Amman duk da hakan Basu daina sauka ba saboda zuciyarta da take k'unshe da bak'in ciki da takaicin halin Zuwaira.

Nazir Kam Yana k'ok'arin fita sashen Inna ne suka yi kicibis da Sadiya zata shigo sashen na Inna, ganin yanayin da fuskarshi ta tona zallar damuwar da ke zuciyarshi yasa taji k'irjinta yayi saurin bugawa, cikin firgici ta Sha gabanshi saboda har ya wuce Yana k'ok'arin fita cikin gidan, ido cikin ido suke kallon juna ita fuskarta d'auke da mamakin halin da yake ciki wanda ya saka shi shiga wannan damuwar har haka, shi kuma kallon tausayin kanshi da ita yake yi don ya tabbatar da cewa daga ranar bazata sake ganin fara'arshi ba, tunda dai har ya rasa mahadin rayuwarshi farin cikin zuciyarshi harsken farin watan ruhinshi, wadda da taurarinta ne yake amfani wajen walwala da annushuwarshi ga kowa.

Cikin tsantsar damuwa Sadiya tace

"Plss hubbyna don Allah ka sanar dani meke faruwa ne wai?Wallahi tunda kuka fita zuciyata take ta sake sake amman na kasa hasko abunda zai saka ka cikin firgicin da na hangoku dashi d'azu, daga Kai har Inna har ita kanta Auntyn"

Auntyn da yaji ta ambata ne yasa shi jin wata muguwar fad'uwar gaba wadda ta janyoshi Kai bakin motarshi ba shiri dafe da zuciyarshi, Sadiya ta biyoshi da sauri hawaye suna zuba ta rikoshi tace,. "Kayi hakuri my hubby idan har na b'ata maka kaji?".

Nazir yayi murmushin yake yace,. "Ba komi je ki ciki idan na dawo za muyi magana". Sadiya ta ja baya cikin sanyin jiki tana tafiya tana waigenshi har ta Kai bakin k'ofar shiga gidan ta tsaya tana yi masa bye bye har ya fice da motarshi.

Nazir Kam Yana fita bai zame ko'ina ba sai wani shopping ya lodowa Umar kaya ta bangaren madarar jarirai ta NAN da nufin a Fara bashi idan ta karbeshi shikenan, sai sutura da duk wani abun bukatarshi sai da ya siyo har ma da ita kanta Inna da Sadiya don ya faranta masu, sannan ya juya yaje gidan ya Kai masu ya K'ara fitowa inda Kai tsaye unguwarsu Malam Nura ya nufa, ganin gidanshi a kulle yasa ya nufi makaranta sai ko gashi yaci sa'ar ganinshi, Sai dai shi Malam ko kadan bai yi murna da ganinshi ba hasali ma shi a ranshi ya nasa da yasan shine da bai fito ba.

Cikin sanyin jiki Nazir ya Mik'a masa hannu da nufin suyi musabaha, Malam Nura ya kawar da kanshi gefe sai dai tuno muhimmancin gaisuwar yasa ya Mik'a masa hannun suka gaisa, Sannan ya had'e fuska tamau kamar an aiko masa da sak'on mutuwa, Nazir yayi Yar dariyar k'arfin hali yace,

"Wurinka nazo Ina bukatar muyi wata magana da Kai"

Malam Nura ya K'ara bata fuska yace

"Ina saurarenka dafatar maganar bazata ja lokaci ba saboda karatu nake yiwa yara aka Kirani"

Nazir yayi dan gajeren Murmushin yace "idan ba damuwa zaka iya bani masauki mu zauna saboda muhimmancin maganar"

Malam yayi saurin cewa,. "Ok to idan zaka iya jira har a tada yaran sai muyi maganar saboda akwai abunda Nike son gabatar masu dashi kafin lokacin tashin yayi" cikin takaici Nazir yace

"Ok ba damuwa bari in jiraka d'in". Ya koma motarshi ya zauna Malam Nura ya koma cikin Makarantar zuciyarshi cike da takaicin b'ata masa lokaci da Nazir yayi, saboda har cikin ranshi yake jin tsanarshi don rabashi da masoyiyarshi da yayi.

Tsawon minti talatin Nazir Yana zaman jiran Nura duk da yaran sun tashi sai da ya gama duk abunda zai yi sannan ya fito ya taraddashi, fuska ba yabo ba fallasa yace da Nazir d'in ya shigo cikin Makarantar ya fito motarshi ya rufeta ya biyo bayanshi har zuwa wani D'an tebur suka zauna.

Nazir yayi shiru Yana tunanin ta Ina ma zai Fara cen dai yayi jarumtar fad'in,. "Nasan zaka yi mamaki akan abunda yasa nayi wannan tattaki zuwa wurinka, to ba wani Abu bane illa dangane da abunda ya faru ne Wanda nasan kasani don kaji komi a kotu sai Dan Karin bayanin da zan yi maka a yanz....."

Kai tsaye Malam Nura ya katseshi da fad'in

"Bana bukatar wani Karin bayaninka kawai ka fito Kai tsaye ka nasar Dani abunda ke tafe da Kai."

Nazir Kam duk da yaji zafin kwatsiyar da yayi masa amman ya basar ya furzar da iska a bakinshi yace,. "Na zo ne akan in baka hakuri dangane da abunda ya faru kayi hakuri ka yafe Mani laifukan da nayi maka, Wanda Ni kaina ba da son Raina nayi ba nayi hakan ne kawai don bani da wata mafita ne a lokacin shiyasa"

Malam jikinshi yayi sanyi saboda yanayin yanda yaji muryar Nazir ta karye sosai, wadda kiris take jira aga kuka akan fuskarshi cikin damuwa Nura ya sauke katuwar ajiyar zuciya yace,. "Koda baka zo ba Nima kaina nayi niyyar zuwa nemanka domin in nemi yafiyarka akan mu'amalar da nayi da matarka a cikin rashin sani, don tun lokacin da naji gaskiyar komi na dukufa neman yafiya wurin Ubangijinmu duk da nasan baya Kama mutum da laifin da baisani ba, Nima ka yafe man don Allah saboda laifin namu ne duka ba Kai kadai ba"

Nazir ya sauke ajiyar zuciya duk da yaji dadin fahimtarshi da Malam Nura yayi, Amman jin furucin da yayi na cewa yayi mu'amala da Amrah yasa yaji wani sabon kunci ya mamaye zuciyarshi, cikin matsananciyar damuwa ya Ciro kud'i daga aljihunshi ya mikawa Nura yace,

"Ga wannan ka rage zafin wahalar da na jefaka a ciki Allah Ubangiji ya yafemu dukanmu"

Nura yabi kud'in da kallo Yana girgiza kanshi yace,. "Aa ka barsu kawai ba komi Allah ya mayar man da alkhairi kawai."

Nazir ya kafe dole sai da ya karba sannan suka yi sallama cikin mutunci ya rakoshi har bakin motarshi suka rabu kowa zuciya ba dadi.

Nazir Kam Yana tafe Yana furzar da iska mai zafi a bakinshi a ranshi yace,.

"Yanzu kuma sai Ina zanje???????"

A take wata zuciyar tace dashi

"Ka je gidan Alhaji Mai Akwai don Shima fa ka shiga hakkinshi da yawa"

A take yabi shawarar zuciyarshi ya nufi ainahin unguwar da yake zaune da Matanshi, kasancewar Yana zuwa Ana magriba yasa ya perker motarshi a gefen masallacin da ke daf da gidanshi, ya fito ya Samu ruwa yayi arwallah yana ta Alla Alla akan Allah yasa ya ganshi din, aiko Yana cikin yin arwallahr ne sai ga Alhaji Mai Akwai ya fito gidanshi da sauri tare da yan yaranshi suka nufi masallacin.
Cike da jin dadin ganinshi Nazir ya kammala arwallahr ya shige masallacin Shima.

Koda aka k'are sallah Nazir Yana cikin doguwar adduarshi ta rokon yafiyar Ubangiji akan laifukanshi Yana hango Alhajin zai fita yayi saurin shafa adduar ya Mik'e ya biyo bayanshi, Amman duk da saurinshi har sai da ya kusa shigewa Gate din gidanshi ne ya cimmasa cikin sauri ya Fara yi masa magana, da sauri Alhajin ya waigo tare da yaranshi da yake rike da hannunsu, Nazir ya Kam cikin faduwar gaba ya Fara Murmushin k'arfin hali yace,. "Don Allah Alhaji tambaya Nike yi".

Alhajin Yana Murmushi yace,. "Allah yasa nasani"

Nazir ya gyara tsayuwarshi tare da fadada fara'arshi ta k'arfin hali yace,. "Alhaji Mai Akwai nake nema ance Mani nanne gidanshi"

Alhaji Mai Akwai cikin mamaki yace,. "Nanne gidan Mai Akwai hasali ma yanzu haka da shi kake magana". Nazir ya Sosa kanshi yace

"Masha Allah an Sara bisa gaba wajenka nazo Alhaji saboda akwai maganar da Nike so muyi da kai"

Cikin tanbaba Alhajin ya saki hannun yaran yace dasu su shiga gida kafin ya zo, har sun tafi Nazir ya kirasu ya fiddo 2k ya Mik'a masu kowa daya d'aya saboda su biyu ne Yana dariya yace dasu susha sweet, aiko da gudu suka shige gidan suna murna suna fadin,. "Mun gode Baba Allah ya K'ara rufa asiri".

Cikin jin dadi Nazir da Alhajin suka ce "Ameen"

Bayan sun wuce ne Alhajin cike da jin dadin kyautar da Nazir yayiwa yaranshi yace dashi,. "Yawwa Ina jinka yaro meke tafe da Kai ne?"

Nazir ya shiga natsuwarshi yace

"Atakaice dai Alhaji Sunana Nazir Nine Mijin Amrah yarinyar da ka taba aure shekara d'aya da watanni da suka wuce"

Da sauri Alhajin ya zaro ido yace,. "Tabbas naso na gano fuskarrka saboda naga firar da aka yi da Kai a mujalla akan shariar da kukayi da ita yarinyar a kotu, Allah sarki to to Ni kuma meke tafe da Kai wurina? Bayan ka yi abunda dole na na bar maka matarka ba shiri". Cikin jin nauyi Nazir yace

"Yafiyarka na zo nema ranka ya Dade don Allah ka yafe Mani abunda nasa aka yi maka"

Cikin jimami Alhajin yace,. "Indai ta bangarena ne to kada kaji komi Wallahi na yafe maka tun lokacin da naga labarin rikicin shariar taku, don ko nine zanyi fiye da abunda kayi akan Matata Amman dai haka dinma na jinjinawa kokarinka, duk kayi wauta tun farko da baka dauki mataki ba don da duk hakan bata kasance ba, don Wallahi inda nine Kai sace zan saceta mu bar garin sai dai aga na dawo da ita da katon cikinta nasan dole a hakura don ba yanda zaa yi dani, Amman ba komi hakan ma da kayi ya nuna cewa Kai ma Namiji ne Ina taya ka murna Allah ya baku zaman lafiya"

Nazir yaji wata sabuwar damuwa ta ziyartoshi ya Duke Kai yace "Ameen sai dai kuma yanzu haka ma bama tare saboda sun biyani Huldi na sauwake mata"

Alhajin ya zaro ido yace

"Ya salam waton dai Basu saduda ba aiko Wallahi zasu janyowa kansu hakki yayita bibiyarsu, kayi hakuri kaji Allah ya musanya maka da mafi alkhairi, duk da nasan kana sonta kayi hakuri insha Allah Kaine zaka yi nasara akansu"

Cikin dariyar k'arfin hali Nazir yace "nagode ranka ya Dade da ka fahimceni"

Yana k'are maganar ya Ciro kud'in da zasu Kai five hundred thousand. Ya Mik'a masa cike da mamaki Alhajin yace

"Na minene?"

Nazir Yana Yar dariya yace ,. "Kudinka ne da ka kashe wajen siyen magungunan da na janyo maka shiga matsalar don Allah ka yafe mani saboda nasan na cutar da kai"

Alhajin ya saka hannu ya dauki dauri d'aya na dubu d'ari ya saka aljihu yace,. "Kaje da sauran ka Kara kayi hidimar sabuwar Amaryar da zaka yi, wadannan ma zan baiwa Matana ne domin inji dadin rokar maka yafiyarsu saboda suma sun cutu sosai a lokacin, Amman Ni ta bangarena ba komi Wallahi na yafe maka koma me na kashe fatanmu kawai Allah ya yafemu gaba daya"

Cikin jin dadi Nazir ya rankwafa yayita yi masa godiya kamar yayi kuka haka suka rabu cikin aminci da mutunta juna Alhajin ya shige gidanshi Nazir ya shige motarshi ya bar unguwar aguje ya nufi hanyar zuwa gida, zuciyarshi cike da jin dadin sauke Rabin nauyin da yayi sai dai Yana hango gidan yaji gabanshi ya fadi saboda tuno da yayi hasken idaniyarshi bata cikin gidan.

*****

Amrah Kam sai gunjin kuka take yi cikin Napep duk da fadan da Zuwaira take cisga bai hanata bare Baki tayita kukanta ba, don izuwa lokacin zuciyarta ta kekashe bata jin shayin Mamar Tata sai dai girman da Allah ya bata na Uwa a wurinta kawai da ya rage a idonta, Amman ko kadan bata tsoron duk wani hukuncin da zata yanke akanta don a ganinta duk wani Abu da zata yi mata bazai taba Kai Rabin abunda tayi mata a yanzu ba, ta rabata da Masoyinta farin cikin zuciyarta Wanda Babu irinshi wajenta a duk fad'in duniyarnan, sannan kuma duk da hakan ta yi rashin Imanin rabata da Dan guda gudan yaronta Wanda ta kanshi ne tasan zafin haifuwa tasan dadin samun d'a, Wanda a tsammaninta Koda mutuwa tayi bazata iya barwa su Inna shi ba, sai gashi da ranta da lafiyarta ta rabata da shi ita kanta, haka Amrah tayi ta zancen zucinta tana kuka har suka je k'ofar gidan, abun mamaki suna zuwa suka taradda k'ofar gidan dank'am da mutane saboda yansandan da Malam Audu ya d'auko mata, sai hurar hanci suke suna Harare Harare sunyi tsaye cirko cirko a k'ofar gidan suna jiran zuwan Zuwairar.

Tofa wani sabon cafke😳

Akafta🤣

D/AUTA ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

AM SORRY MY FANS👰🥰

PAGE 46

Zuwaira ido suka Rena fata saboda ganin 'Yansandan ya sata bafad'uwar gaba mai tsananin gaske, Wanda muddin mutum yace zai kasa kunnenshi ya saurara to tabbas zai ji sautin k'arar bugun zuciyar Zuwaira da ke ta halbawa da sauri da sauri, Nan take wani jib'i ya karye mata a jiki saboda tsananin tashin hankalin da take ciki, gashi sun riga da sun hangota da ba abunda zai hanata neman mafaka ta b'oye don yanayin fuskokinsu ya tabbatar mata da cewa ba d'igon Imani cikin zuciyarsu,.

Cikin sanyin jiki ta fito Napep d'in Wanda saura k'iris ta fad'i saboda rawar da jikinta yake yi,. Kai tsaye ta Miki titi cikin rud'ewa a k'ok'arinta na son ta zille masu don ko Mai Napep din ma Bata sallameshi ba sai lantana ce ta biyashi ya tafi, Malam Audu Kam ganin Zuwaira tana son ta tsere ne yasa yayi saurin cewa da wani dayan D'ansandan,

"Oga ga fa matar cen tana so ta tsere"

Cikin sauri wani D'ansanda Mai jajayen ido ya katsa mata tsawa yace

"Hey you Madam come here where are you going???"

Cikin rud'ewa taji hantar cikinta ta kad'a wani zawo Yana Shirin sub'uce mata, cikin firgici ta Fara inda inda wani D'ansanda yazo ya tasata a gaba har k'ofar gidan sai Rabon ido take yi tana soshe soshen rashin gaskiya, cikin rawar baki ta kalli Malam Audu tace

"Malam Audu ya naganka da wad'annan maaikatan? Me nayi maka?" . Malam Audu ya kara tsuke fuska tamau yace,. "Ai dole ne ki ganni dasu tunda har naji labarin wai kinsayar man da gida"

Zuwaira ta zaro ido waje tare da dafe k'irji tace,. "Waya fad'a maka wannan zancen, don Allah kayi hak'uri Wallahi akasi aka Samu Nima ba haka naso ba"

Malam Audu yace

"Ai Nima shiyasa banyi kasa a gwiwa ba na gayyato maki ma'aikatan da zasu titsiyeki ki bani kud'ina yanzunan, na fasa sayen gidan tunda Ashe daman cen cutata kika shirya yi ba wai sayar man da gidan kika tashi yi ba, don haka Wallahi kwandalata bazata yi ciyon Kai ba, ki shiga ciki yanzu Ina jira ki bani kawai mu sallami juna"

Zuwaira tayi rau rau alamar kuka tace "don Allah Audu kayi hak'uri zuwa gobe kazo ka karb'i kudinka, Wallahi na fad'a maka matsala aka Samu bansan ya akayi ba barayi suka sace kud'in".

Malam Audu da sauran Yan sandan suka zaro ido waje bakin Malam Audu Yana rawa yace,.

"Barayi suka sace kud'i har Miliyan biyu da d'ari takwas cabdi um lalle Zuwaira kin kware da d'ibar albarka ai billahillazi ko ki bani kud'ina ko ki k'are sauran rayuwarki gidan yari matuk'ar Baki fito man da kud'ina ba, nafison aje dake cen ayita gana maki azaba har sai lokacin da kika fito da kud'in ,don Wallahi banci nanin ba nanin bazata cini ba cabd'i jam Lalle Zuwaira kin tarowa kanki bala'in gabas da yamma wanda duk danginku sai sun sheda, ke nifa Wallahi bancin wani Abu ma da tuni na lakad'a maki shegen dukan da za'a kaiki Asibiti ba'a shirya ba"

Ya kalli wani D'ansanda yace

"Officer don Allah kuce da ita ta shiga gida ta d'auko Mani kud'ina yanzunnan tun kafin hawan jinina ya taso tayi sanadina"

Ya Kare maganar cikin zubowar wasu hawayen takaici yace

"Allah ya Isa tsakanina dake Zuwaira Ina zaman zamana kika je har gida kika ce inzo in sayi gida Ashe Ashe yaudarata ce kika shirya kiyi ai narantse da Sarkin da ya busaman numfashi yau Akwai yak'i tsakanina dake matuk'ar Baki bani kud'ina ba"

Ya K'are maganar cikin muryarshi da ta karye Yana zubar da hawayen takaici, Zuciyarshi cike da tsantsar fargaba kada ace da gaske babu kud'in, don shikadai yasan yanda yake jin zuciyarshi saboda hawan jini da yake fama dashi.

Zuwaira Kam tayi tsamo tsamo kamar ruwa sun cita ba Baki sai idanuwa da take rabo tana hadiyar yawun Dole, wani D'ansanda ya yi ball da ita har sai da ta Kai kasa ba shiri Sannan ya katsa mata wata arniyar tsawa yace taje ta fito masa da kud'inshi, a zabure ta Mik'e jikinta Yana rawa ta fad'a cikin gidan dafe da zuciyarta tace

"Wayyo Ni Zuwairiyya tawa ta sameni yau Ina zan samo cikon kud'inshi in bashi?"

Wata zuciyar tace da ita,. _"Ki mayar da Amrah ki karb'o kudinki kawai"_

Tayi saurin girgiza Kai a ranta tace,.

"Ina wannan ba mafita bace don tabbas na yi hakan zann bada kaina kuma in janyo su Rena mani wayo a banza bari dai in d'auko mashi miliyan d'aya din da tayi saura in nemi alfarmarshi akan yayi man lamuni zuwa kwana Uku in gani"

Cikin gamsuwa da shawarar da zuciyarta ta bata ta shiga d'akin taje ta d'auko kud'in zata fito suka yi kicib'is da Amrah zata shigo, ganin yanda ta raba ta gefenta ta wuce yasa tayi kwafa ta fita zuciyarta sai halbawa take yi saboda tsoron abunda za'a yi kuma yanzu,.

Tana zuwa ta mik'awa Malam Audu kud'in cikin marairece fuska tace,. "Ga kudi'n Yaya Audu insha Allahu gobe zan cika maka sauran ko baka zo ba har gida zan je in Kai maka abunka kaji?"

Malam Audu ya bi kud'in da kallo fuska a had'e yace,. "Nawa ne?"

Bakinta Yana rawa jikinta Yana bari tace

"Miliyan d'aya ce Yayana Audu insha Allahu gobe....."

Ya katse mata hanzari wajen k'wace kud'in Yana huci yace da yansandan

"Officer ku tafi da ita har zuwa goben idan ta bada cikon kud'in sai a sakota"

Zuwaira ta zaro ido ba shiri ta Kai k'asa tana rokon Malam Audu akan yayi mata hak'uri har goben zata bashi, Malam Audu ya tura kud'inshi aljihu yace da 'yansandan

"Officer kuyi aikinku"

Aiko wata 'Yarsanda mace ta cakumo k'ugun Zuwaira tana kuka tana tirjiya tana kiran "Yaya Audu ka taimakeni Marainiyar Allah ce ni kasani cutawa maraya haramun ne, ka dubi yanda Nike kuka Kuna kasan Kukan maraya Abu ne babba ko ba komin Ina son kaji tausayin Marayun 'ya'yana kada ka tozarta masu Uwa, ka tuna fa kana da kanwa Ladidi idan aka yi mata haka kai ma ai bazaki ji dad'i ba"

Malam Audu Yana hurar hanci yace

"Ko itace zan bada goyon bayan a tafi da ita indai tayi irin abunda kika aikata man Wanda Allah ma ya haramta yin ciniki a kan ciniki, don haka ba wani sassauci har sai kin fito man da kud'ina WALLAHI"

Cikin fushi Zuwaira tace

"Allah ya tsine maka Audu tunda har baka San halacci ba meye ban yiwa matarka ba? Abinci sutura duk Ina Bata Amman wai yau nice zaka sa akaini mak'argama a kulle saboda kud'i, Shege bak'in Munafuki Mai fuskar shanu sai..... " Saukar marin da Yar sandar tayi mata yasata yin shiru dolenta, aka turata motarsu ta shiga ba biya suka bar k'ofar gidan aguje, Aiko Mutane suka Fara tsegumin abun wasu suna ta Allah ya K'ara yayin da wasu suke ta ganin kamar Malam Audu bai kyauta ba, saboda mutuncin da ke tsakanin matarshi da Zuwaira.

Lantana kawar Zuwaira cikin sanyin jiki ta ja kafafuwanta ta shiga gidan, sai ga sautin kukan Amrah ya tarbeta cikin sauri ta nufi d'akin Amrah ta Fara Bata hak'uri tana cewa,. "Kiyi hak'uri Amrah in kinsan Akwai inda zaki je ki samo kud'in to kije ki samo ki kawo aje a karb'o Mahaifiyarki"

Amrah tayi banza da Lantana sai kukanta take yi dama taga Lantana ta dameta tashi tayi ta turata waje ta rufo d'akinta taci gaba da gunjin kukanta, Aiko ciki fushi Lantana tace

"Ah lalle yanzu ke kina nufin bazaki tashi kije ki fadowa 'yan uwanku ba asami kud'in akai su fito da ita ba ko? Ah Lalle Zuwaira sai hak'uri zama gidan Maza ya kamaki Kinga tafiyata idan kin gama kukan sai kisan yanda zakiyi da ita ke ta haifa ba Ni ba"

Ta fice abunta tana fad'a saboda taji haushin abunda karamar yarinya irin Amrah tayi mata.

****

Nazir Kam jiki ba kuzari ya shiga gidan Kai tsaye d'akin Amrah ya shige, a cen yayi sallahr Magriba har aka yi Isha duk yana ciki bai fito ba, Sadiya tun tana sauraren shigowarshi har ta gaji da jira ta yi sashen Inna domin taga me ya tsayar dashi, sai dai ganin Bata hango talkamanshi a k'ofar d'akin ba yasa zuciyarta ta Bata cewa Yana d'akin Amrah don ta hangoshi k'ofar a bud'e,. Kasancewar Inna ta ganta yasa ta shiga d'akin da fara'arta tace,

"Barka da dare Inna"

Inna tana Murmushi tace ,. "Yawwa Sadiya Barka Ina shi Nazirun??". Sadiya tana fara'a tace

"Yana ciki Inna"

Inna tana yar dariya tace da ita,. "To kice yazo in na nemansa "

Sadiya tace "to Inna bari in kirashi" Sannan ta fice jiki ba kuzari tana nazarin maganar da Inna ta fad'a mata d'azu ko ba gaskiya bane, tunda dai in har da gaske Nazir ya rabu da Amrah to me zai sashi ya je d'akinta yanzu?? Cikin damuwa da jin wani sabon kishin Amrah ta shiga falon da sallamarta Amman taji shiru, cikin jin haushi ta nufi kuryar d'akin da nufinta na ganin koma me suke aikatawa tunda har suka yi banza da ita, ganin Nazir kwance shikadai idanuwanshi a sama yana kallon sealing hawaye suna kwaranya a gefen fuskarshi suna biyar kunnuwanshi tamkar wani burgaggen famfo, Amman baisan ma suna zubowa ba saboda ya fad'a cikin zuzxurfan tunanin rayuwar jin dad'in da yayi da Amrarshi.

Cikin sanyin jiki ta k'araso ta zauna saman gadon ta rik'o hannunshi ta yi masa kiss Sannan ta kwanta saman k'irjinshin tana shafo fuskarshi a hankali, Nazir Kam cikin shauk'in son y Amrah da mayen sonta yake shiyasa yq K'ara rungumota jikinshi ya manneta tsantsan Yana sambatun fad'in

"I love u Amrahtah kece farin cikina kece fitilar dake haskaka Mani zuciya, idan Baki a tare Dani bansan Ina zan jefa rayuwata ba, ke Mai kyau ce don ko a cikin jerin kyawawa ke tadaban ce a wajena, zuciyar Nazir gaba d'aya kece a cikinta sonki ya tunbatsa ya cike kowane lungu da sak'on da ke zuciyata, Nazir naki ne ke tawa ce kiyi yanda kike so dashi Nima haka I love u so much my milk wadda zakinta yafi na kowace 'ya mace a duniya"

Cikin zafin nama Sadiya ta tureshi daga yamutsatan da yake yi a haukace idonshi a rufe saboda wani bala'a'en kukan da ya zo mata na zallar tsagwaron kishin Amrah, jikinta Yana rawa ta Mik'e tsaye tare da nunashi cikin Kuka tace

"Meyasa kasan kana yiwa Matarka irin wannan son ka aureni??? Meyasa ka zab'i da in zo

gidanka inyi zaman boranci a gidan Mijina Wanda nafi so fiye da komi a rayuwata??"

Ta durk'ushe tana wani kuka gwanin ban tausayi Mai had'e da zallar tausayin kanta da kanta, don yanzu ta gano Ashe ita d'in ba kowa bace a wurin Nazir face Bora tunda har ya iya wad'annan kalaman Amman ita bai tab'a yi mata ko Rabin rabinsu ba.

Nazir Kam Wata kasala ta sauko masa ba shiri tare da razani akan jin sautin Muryar Sadiya cikin kunnenshi, saboda kalamanta da kukanta sun sa ya jishi wani iri duk ba dad'i ya runtse idonshi ya K'ara budewa yayi jarumtar mik'ewa zaune ya d'agota ya had'ata da jikinshi ya Fara lallashinta, cikin Kuka ta k'wace daga jikinshi tace

"Kar ka koma tabani kaje wajen Mowar Matarka wadda Babu kamarta a wajenka"

Sannan tana K'are maganar ta zo zata fita tace

"Inna tana nemanka idan ka gama mayen k'aunar"

Ta fice tana kuka ta fad'a d'akinta sai gunjin kukanta take yi tayi datasanin zuwa d'akin Amrah don a ganinta da Bata je ba da Bata jiyowa kanta abunda zai hanata sukuni ba.

Cikin sanyin jiki ya Mik'e Yana tangadi saboda rashin k'arfin jiki ya nufi wurin Inna, tozalin da yayi na ganin Umar yasa yaji wani sanyi ya ratsa zuciyarshi, cikin rashin kuzari ya duk'a ya d'aukeshi Sannan ya zauna Yana yi masa wasa, Inna ta bishi da kallon tausayi tace

"Ka je inda nace kaje?"

Ya gyara zamanshi cikin natsuwa yace

"Na je Inna har ma anyi nasara wajen mutum biyun da naje wajensu". Daga Nan ya kwashe duk yadda yayi dasu ya sanar da ita a dunkule, cikin jin dad'i tace

"Alhmdllh mun godewa Allah gobe idan Allah ya kaimu sai kaje wajen sauran don ka Samu ka sauke nauye nauyen da ke kanka ko da zaka Sami natsuwar Zuciya"

Ya sauke ajiyar zuciya Yana kallon Umar a ranshi yace,

"Ta yaya zan Sami natsuwar zuciyar alhali Amrah Bata tare da ni??? "

A fili kuma yace

"Insha Allah Inna gobe zan je in samesu nagode da kika hankaltar Dani tun da wuri"

Inna tace

"Allah ya kaimu Amman ka sani kar ka manta maganar da nayi da Kai a kwanakin baya, akan cewar da nayi ban yafe maka ba matuk'ar ka sake kauce Hanya akan Amrah da rayuwarta da kowa ma Kai ko da ko bayan k'asa ta shafe idona ne, a kullum Ina son ka tuna da wannan maganar tawa don kayi takatsantsan da koma aikata irin abunda kayi a baya"

Cikin gamsuwa da maganarta yace

"Insha Allahu hakan bazata sake faruwa ba Inna nayi maki wannan alk'awali"

Cikin jin dad'i Inna tace,. "Allah yayi maka albarka kuma ya sawa aurenka da yaronka albarka ya bamu ikon kula dashi dai dai yanda ya kamata, kayi hak'uri da duk halin da zaka tsinci kanka a ciki ka barwa Allah komi da sannu haske zai shigo rayuwarka ya haskaka maka zuciyarka har ma ya yaye duhun da kake ganin kanka a ciki yanzu"

Cikin jin dad'i yace

"Nagode Inna Allah ya barmuna ke muci gaba da dafaki muna jin dad'i"

Tayi Yar dariya tace

"Aiko bazai barni ba komin Daren dadewa zan tafi inda kowa zai je, fatanmu kawai Allah yasa mu cika da kyau da imani"

Yace "Ameen" daga Nan suka ci gaba firarsu har goman dare ya buga, tace dashi "Kawo yaron tashi kaje wajen matarka"

Nazir ya marairece fuska yace,. "Inna ki Bari inje dashi da safe in kawoshi"

Inna ta B'ata fuska tace,. "To Ni badani za'a yi wannan shirmen ba kawoshi kaje sai da safe Allah ya tashemu lafiya"

Nazir ya Mik'ashi yayi mata sallama ya fita Inna tabi bayanshi da kallo tace,. "Ubangiji Allah ya kawo haske cikin rayuwarka Naziru"

Ameen Inna😢

Dangin Xuwai a harhado kudi kuzo muje a karbota tun kafin zarnin fitsari ya kasheta🤦‍♀️🙊

Akafta🤣

Princess Dija D/Auta ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Tun kafin ya Isa d'akin ya Fara jiyo sautin kukanta cikin wata sabuwar damuwa ya shiga d'akin da sallamarshi, Sadiya Kam duk da tajishi sarai amman tayi banza dashi ta ci gaba da rera kukanta wiwi, ya k'araso wajenta ya janyota jikinshi ya Fara lallashinta da fatar Baki har ma da

k'ok'arin nuna mata itama tana da matsayinta a zuciyarshi, kafin kace me sai ga Sadiya ta Ware saboda Nazir yasan ta kan yanda ake sarrafa mace har ma ta manta da inda kanta yake,. Cikin natsuwa ya fara sarrafata a hankali duk da zuciyarshi Bata da natsuwa amman a hakan yayi jarumtar nuna Mata nata kalar matsayin, Bayan komi ya lafa ne wani mayen bacci ya Fara fisgarta ya Kira sunanta yace

"Kiyi hak'uri da Ni kinji insha Allah zanyi k'ok'arin kwatanta maki adalci"

Cikin mayen bacci Sadiya tace,. "Ba komi hubbyna ai komi ya wuce Amman don Allah Ni ma ka soni Koda Rabin son da kake yiwa Amrah ne"

Ya yi saurin runtse idonshi yayi shiru Yana nazarin rayuwar jin dad'in da suka shinfida shi da Amrarshi, fuskarta sai GIZO take yi masa a ido tana d'an murmushinta Mai K'ara mata kyau ya sakashi natsuwa, Sadiya Kam shirun da taji yayi ne yasa itama tayi gum har bacci Mai dad'i yayi awon gaba da ita, Nazir Kam ganin tunanin Amrah bazai barshi yayi kwanan ba yasa ya Mik'e yaje ya d'auro arwallah ya fara jera Nafilfili, Sannan ya duk'ufa rok'on Allah akan ya yafe Masa laifukanshi da ya aikata, Sannan yayi add'ua sosai akan idan har aurenshi da Amrah alkhairi ne to Ubangiji ya dawo masa da ita cikin gaggawa, idan kuma ba alkhairi a zaman nasu to Allah ya bashi dangana akan soyayyarta, ya raba dare Yana Abu d'aya Sannan ya d'an gincira sabida wani bacci Mai dad'i da ya ziyartoshi ba shiri, Aikuwa Nan take baccin yayi awon gaba dashi bai tantance ba.

****

Amrah Kam tana cikin kukan ne taji muryar Abbati Yana k'wank'wasa Mata k'ofa, cikin sauri taje ta bud'e d'akin ganin Abbatin yasa taji wani sabon kuka ya zo mata,. Ta dawo Kan gadon ta zauna tana rera kukanta gwanin ban tausayi saboda izuwa lokacin har fuskarta tayi jawur idanuwanta sun kunbure suntum saboda kukan da tasha, cikin sanyin Jiki Abbati ya shigo d'akin ya zauna damuwa fal ranshi yace,

"D'azu Aunty ta kirani tana sanar da ni abunda ya faru a kotu Ina Shirin zuwa gidanta ne, sai gashi Usama ya Kirani yana sanar da ni abunda yake faruwa wai Malam Audu ya d'aukowa Mama 'Yansanda sun tafi da ita, don Allah kiyi hak'uri kinji tunda har hakan ta faru to ki fawwalawa Allah komi da sannu zai yi maki mafita, ki bari Ni zanje yanzu in karb'o maki yaronki kici gaba da shayar dashi har a yayeshi Sannan a mayar masu dashi, idan ma Allah ya daidaitaku shikenan sai ki koma kici gaba da kula da yaronki cikin natsuwa Bari yanzu inje in basu hak'uri su bamu yaron"

Har ya Mik'e Amrah ta kirashi cikin dusashiyar muryarta tace,. "Share da zancen Abbati na riga da na dangana dashi tunda har Mama Bata ji kunyar rabani da yarona ba, Amman WALLAHI Niko ta daina ganin fara'ata a gidannan"

Abbati ya dawo ya zauna cikin sanyin jiki yace,. "Yanzu to ya kike ganin za'ayi da zancen karbota hannun yansandan? Don fa kud'in suna cikin d'akinta kawai dai don bata San inda suke bane". Amrah cikin Kuka tace

"Kaje ka d'auko kud'in ka Kai masu abunsu tunda har kasan inda suke"

Abbati yayi shiru Yana nazari Sannan yace

"Ni ko a ganina ba karb'o Mama ya Dace muyi da kud'in ba"

Amrah ta tsaida kukanta tana kallonshi da jajayen idonta tace

"Kana nufin a cen zamu barta kuma alhali Akwai kud'in karbotan gaskiya ko da ba'a kyauta Mata ba Abbati don Mama duk lalacewarta ai dai Mahaifiyarmu ce"

Abbatin yayi shiru na d'an lokaci Sannan yayi gajeren Murmushin takaici yace,

"Ke yanzu abunda tayi maki tayi maki adalci? K'iri K'iri ta rabaki da Mijinki Mai yi maki son tsakani da Allah Sannan kuma ta yi k'arfin halin rabaki da Yaronki, to Bari kiji Akwai abunda zamuyi Mai Muhimmanci da kud'in Wanda yafi karb'o Mama hannun 'yansanda"

Cikin rashin fahimtar inda ya dosa tace

"Yanzu Akwai abunda yafi karb'ota alhali muna da abun karbotan?"

Abbati ya Mik'e tsaye tare da saka hannunshi aljihu yace

"Gidannan shine rufin asirinmu don bamu da wata kadara da zamuyi alfakhari da ita face gidannan, ko kin manta gidan Babanmu tuni Mama ta sakashi a kasuwa ta siyar dashi? Yanzu idan Shima wannan aka ce ya fita hannunmu Ina kikeso ku zauna ke da ita?, Don ni da Abdullahi ba abun ji bane tunda ko d'akin abokanmu zamu iya zuwa mu kwana ballantana muna da dangin Babanmu da zamu je wajensu mu zauna to da ke da ita fa? Idan maigida ya bukaci a bashi gidanshi yawon haya fa zaku dinga yi"

Amrah tace "to sai mi? Tunda har itace kaddararmu". Cikin b'acin Rai Abbati yace

 "Kin ko san irin bala'in da ke cikin gidajen haya kuwa? Musamman wad'anda aka tara mace fiye da biyu a gida d'aya, to Bari kiji nidai kawai abunda Naga yafi mu Nemo cikon kud'inshi mu had'a mu bashi mu zauni gidanmu yafi don shine rufin asirinmu ta ko'ina, Amman idan har Kinga mu karb'ota da kud'in shikenan zan je sai dai Ni dai abunda Naga ya dace ayi dasu kenan "

Amrah ta B'ata fuska tace,. "Je ka d'auko kud'in kaje karb'ota tunda itace ta zab'i muyi hakan dole muyi ko bamu so in yaso abunda ya rage mu nemi ko d"an karamin gida Mai d'aki biyu mu siya mu koma ciki kaga shikenan an huta da gidan hayar da kake tsoro"

Abbati ya Sosa kanshi yace,. "Aunty Amrah ki fahimci abunda Nike so ki gane WALLAHI gidannan shine rufin asirinmu muddin muka rasashi shikenan komi ya ruguje muna"

Amrah ta maka masa harara tace,. "Shin wai Kai me kake nufi mu barta acen ko? To idanma mun barta din kana da kud'in da zaka cika a mayar wa da Wanda aka sayarwa da gidan kud'inshi?"

Abbati yayi saurin fad'in,. "Kayan d'akinki fa da ake ajiya miye amfaninsu da baza'a siyar ba sai a had'a da kud'in?"

Amrah ta maka masa wata Katuwar harara tace,. "Ance maka wata daraja zasu yi a kasuwa halan? to bari kaji kwata kwata inma an siya da daraja bazasu wuce dubu d'ari da hamsin ba dukansu har kome ma"

Abbati yayi shiru yana Nazari Sannan yace,. "Shin yanzu dai kin goyi da bayan akai kud'in a karb'ota ko?"

Kai tsaye Amrah tace

"Eh". Yace,. "Ba damuwa Amman kisani ba yau ba sai gobe don nafison sanadiyyar zaman da zatayi acen yasa tayi nadama ta gano kuskurenta"

Amrah ta harareshi tace,. "Tashi ka d'auko kud'in yanzu kaje ka karb'ota nace"

Abbati ya Mik'e cikin damuwa ya nufi d'akinta mintuna a tsakani sai gashi ya fito da ledar kud'in yayi zaune ya fidda kud'in Malam Audu Miliyan d'aya da dubu d'ari takwas, Sannan ya fidda Milyan d'aya ya mik'awa Amrah yace,. "Gasu Ki ajiye mata"

Amrah ta karba cikin sanyin jiki ta ajiye a gefen gadon sannan tace dashi,. "Ka Fara yi muna cuku cukun samo wani d'ankaramin gidan sai mu saya kafin Mama ta salwantar da kud'in"

Abbati ya Mik'e yana saka ledar kud'in aljihu yace,. "Ki dai bata kud'in don ni dai ko k'afata ba zaku sake gani a gidannan ba, Abdullahi ma idan yaji wuya ya iskoni gidan Baba Bello in labashi d'akin da aka bani ina kwana, ke ko gaki ga Mamar Nan da kanki sai kin bid'eni don WALLAHI yanzu bazaki tab'a jin dad'in zama da ita ba Koda ko a k'aton gida balle d'ankaramin gidan da kike fad'a,saboda haka tun kafin aje ko'ina ki tubure mata ki nuna mata cewa ke fa gidan Mijinki kike so ki koma, don yanzu haka gaba d'aya dangin Babanmu fushi suke yi da ke saboda cewar da kikayi sai Nazir ya sakeki a kotu, Baba Mamman ma tun a ranar ya bar garinnan ya komawarshi Kano yace Kuma kada a koma sakashi a cikin duk abunda ya taso

namu tunda har kika nemi saki wurin Yaya Nazir"

Amrah ta fashe da kuka tace,. "WALLAHI Abbati yanzu Ina son Yaya Nazir Ko da don bangano irin son da yake yi mani bane, nayi danasanin wofintar dashi tun farko"

Abbati cikin damuwa da bacin Rai yace,. "Da tun farko kin nuna hakan ai da ba Wanda ya isa ya rabaki da Mijinki yanzu kuma gashi ba'a mayarda hannun agogo baya bale ki dawo ki gyara komi, aure dai Mama ta kashe maki yaro kuma yana hannun Ubanshi yanzu Abu d'aya ne ya rage ki gyara tarayyarki ga Allah Koda Allah zai sa Inna ta sauko ta bashi damar zuwa gareki, don na tabbatar da cewa har gobe Yaya Nazir yana sonki kuma zai yi farin ciki idan har aka ce ya dawo dake"

Amrah ta fad'i Kan gadon tana wani irin kuka gwanin ban tausayi, Abbati ya fice cikin damuwar da ta kasa b'oyuwa akan fuskarshi.

***

Zuwaira Kam tana bayan kanta an ajiyeta sai gana Mata azaba akeyi tayi kuka tun ruwan hawayen suna zuba har suka Kai basu fitowa sai dai kukan zuci da take yi, aranta tana ta K'ara tsinewa Nazir da Inna da Alkali yusha'u har ma da Aunty Asabe don a ganinta duk sune suka ja mata shiga wannan hali, ta tsinewa Nazir yafi cikon kwando tayi alwashin har abada Amrah ba zata koma auren Nazir ba tunda har ta sanadinshi ne ta fad'a wannan rikici, tasan ita da komawa gida kuma shikenan tunda bata da Wanda zai biya mata wad'annan makudan kud'in, wata zuciya tace mata

"Sai dai kuma in garinku zaa je a fad'o halin da kike ciki a gangando a had'a kud'in a kawo masu"

Cikin jin dad'i ta leka kanta da nufin ta kira wani D'ansanda tayi masa bayanin aje a kira d'anta Abbati yaje garinsu ya fad'o masu halin da take ciki, sai dai duk iya Kiran da take yi masu suka yi banza da ita suna ta shaye shayensu suna shewa, da ma ta damesu da Kira wani yazo ya saka belt yayita zabga mata tana ihun neman agaji, yayi Mata gargadi akan duk ya sake jin tayi magana sai ya halbeta dole tayi mukus ko motsin kirki ta kasa yi, haka ta kwana sauro yana cizonta tana soshe soshe har safe.

Misalin k'arfe tara na safe sai gashi wani D'ansanda yazo ya budeta yace ta biyoshi, jikinta yana rawa ta biyoshi tana dingishin wahala don gaba d'aya kafafunta sun sage.

Aikuwa sai gata tayi arba da Abbati cikin jin dad'i tayi saurin fad'in ,. "Nagode Allah Abbati kamar kasan ina nemanka kuwa"

Cikin zubowar wasu Hawayen takaici da tausayin halin da ya ganta yayi shiru yana kallonta, Zuwaira tace dashi

"Ka tafi Zamfara ka fad'o masu halin da Nike ciki Abbati Koda Allah zai sa a Samu kud'in a biya Audu in samu a fito dani"

Abbati yayi k'arfin halin fad'in

"Yanzu zamu je gida ai anbiya kud'in har nasa hannu"

Cikin tsananin farin ciki Zuwaira baki a washe tace "ka biya kud'in fa kace ??"

Ya jinjina mata Kai alamar tabbatarwa cikin tsananin farin ciki tace,. "Duka fa?"

Yace,. "Eh duka" bakinta yana rawa tace,. "Ina ka samo kud'in to?"

Ba shiri yaji gabanshi ya fad'i sai dai wani tunani ya zo masa Kai tsaye yace,. "Yaya Nazir ne ya biya kud'in duka yace a fito dake"

Zuwaira ta zaro ido waje cikin tsananin b'acin Rai tace,. "Naziru fa??"

Abbati yace,. "Eh sh...."

Kafin ya Kai k'arshen zancen ta kwad'a Masa wani gigitaccen Mari ta Fara fad'a bakinta yana kunfa tace,. "Yanzu ka rasa in zaka je neman taimako sai wurin Makiyina? To WALLAHI ban gode ba da dai ace shine ya fito dani gara in tabbata anan din har lokacin mutuwata yayi in mace" haka tayi ta Bala'i har sai da wani D'ansanda ya fito ya katsa mata tsawa yace,. "Idan zaman ne bai isheki ba to ki zo a maidaki kici gaba dazaman tunda haka kike so "

Zuwaira tayi wani tsalle ta fito harabar police station din tana hararar D'ansandan murya k'asa k'asa tace

"Ai WALLAHI idan kaga na koma sai in har bana cikin hayyacina , abunda ma kuka yiwa Marainiyar Allah kuje zaku hadu da fushin Ubangiji Yan iska kawai mugaye"

D'ansandan ganin tana hararashi tana muimui da Baki yasa yace, "Zagina kike yi ko?"

Zuwaira ta zabura ta dafe k'irji tace,. "Wani Nan wa zagin Mai bak'in Kaya irin naka?Salatin da banyi bane da safe nike ranko a yanzu Abbati zo mu tafi tunda dai Allah ya rufa muna asiri mun biya bashi"

D'ansanda ya bita da kallo yana dariya don ya ganota Sarai kyaleta ne yayi kawai.

😂😂Aunty Zuwai hooo😂

Akafta🥴

Princess Dija D/AUTA ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 48

Koda suka fito Abbati ya taro mata Napep ya tarowa kanshi acab'a ya haye ba tare da ya kalleta ba yace da ita,

" Ni na tafi"

Zuwaira ta kalleshi da kyau tace,. "Ina kuma zaka je ?"

Abbati ya b'ata fuska yace,. "Inda ake lab'ani Ina kwana tun lokacin da kika koreni"

Zuwaira ta maka masa harara tace

"Cewa nayi gaba d'aya na koreka halan? To bari kaji kada ka yarda in rigaka kaiwa gida"

Abbati yace da D'an acaban su tafi kawai suka haye titi abinsu suka tafiyarsu, Zuwaira ta bishi da kallon mamaki tace

"Bansan Ina ka gado Wagga bakar zuciya ba Abbati don dai babanka Mai sauk'in Kai ne sai in ga danginshi ka debo bak'in halin don Kam Akwai yan zafin kai birjik cikin zuri'ar taku"

Mai Napep yayi mata oda ta yi saurin zuwa ta shiga suka tafi tana ta tunanin Allah yasa dai Amrah bata save ta koma wajen Nazir ba, aranta tace

"WALLAHI ko da har gidan sai naje na ci ubanta mara zuciya ihhta kuma"

Har aka isa gidan bata daina tunanin zucinta ba, kasancewar bata da ko sisi a jikinta don Yan kudinta da taje dasu duk yansandan sun kwashe, shiyasa ta shiga gidan da nufin ta d'auko ta kawo masa kud'inshi tana shiga taga Amrah durk'ushe makwarara sai kwara amai take yi,. Ba shiri taji gabanta ya kire ya fad'i saboda ganin yanda tabi duk ta rame kwana dayan da bata ganta ba, cikin firgici ta nufi wurinta tana salati tare da kiran sunanta, Amrah ta d'ago Kai a cikin mawuyacin halin da take tana kallonta d'aya tayi saurin kawar da kanta saboda wani amai da ya kara taso mata, cikin damuwa Zuwaira ta debo ruwa ta ajiye mata tace

" Gasu ki wanke jikinki idan kin kare kafin in kaiwa Mai Napep kud'inshi"

Tayi saurin barin wurin tayi d'akinta ta d'auko kud'in ta fita da sauri sai gata ta dawo Koda ta zo ta iske Amrah bata tsakar gidan, Kai tsaye ta nufi d'akin Amrar'r inda ta taradda ita kudundune cikin bargo tana rawar sanyi, Zuwaira ta k'araso d'akin cikin tashin hankali tace,

"Yanzu shikenan don an rabaki da wancen mugun shine zaki d'aga hankalinki kizo ki jazawa kanki ciyo a banza shi yana cen yana ta jin dadinshi yana wacaka da kud'in Haram din da yake ci?ke kinanan kina fama da ciyo da kuncin zuciya?, To bari kiji WALLAHI tun wuri ki Ware ki saki jikinki tun kafin inyi maki tataccen wulakanci a gidannan, don ni bazan lamunci wannan rashin hankalin naki ba da rashin sanin 'yancin kai, ke yanzu ko kishin kanki bakiyi kiji dad'i an zare maki matsalarki a rayuwa? Kin manta duk irin abunda yayi maki k'iri K'iri ya hanaki zaman aure ko d'aya bale kiji dad'i, ya rabaki da masoyinki na gaskiya Salis ya zo ya rabaki da Nasir da Alhaji Mai Akwai Yana sonki amman sai da yasa ya sakeki, to bari kiji tun wuri kiyiwa kanki fad'a ki mayar da hankalinki ki taimaki rayuwarki ki dawo Amrar'r ki ki gyagije ki samo Mijinki na tsara

na nunawa sa'a ki aura kiji dad'i har muma muji, idan ko kika ce wannan kuncin zaki ci gaba da yi to kisani fa daman cen ya haifar maki da ciyon zuciya a baya to ya yanzu sai ya iyar da karasa kasheki a banza kije Lahira ba one ba two ki kare zaman duniyar baki mori komi ba"

Amrah dai iyakacinta ji koshi don ba yanda zata yi ne ta hana kanta da ta toshe kunnuwanta ta huta da jin maganganun da suke kara mata wani lodin bak'in ciki a zuciya.

Zuwaira kam ganin Amrah taki cewa da ita komi duk surutun da take yi yasa ta fita taje ta kawo mata pracetamol da ruwa tace,

"Tashi kisha"

Amrah ta juya kwanciyarta tana share hawayen da ke sirnano mata a cikin ido, Zuwaira ta maka mata wani uban duka a baya tace

"Zaki tashi ko sai naci Ubanki wai"

Amrah ta Mik'e tana Sosa inda ta daketan ta fara gunguni tana magana ciki ciki tace

"Ni fa ba wani magani da zansha ki barni kawai ciyon yayi ajalina idan na mutu shikenan sai kowa ya huta"

Zuwaira ta rik'e kugu tace, "To an fad'a maki idan kin mutun shikenan Ni kinka yiwa bak'in ciki Nima daina rayuwa zanyi? To bari kiji ko kin mutun Ina da wasu 'Yay'a don ba ke kad'ai na haifa ba, Danki kika yiwa asara tunda shi zaki mayar marayan k'arfi da yaji"

Amrah ta share hawayen da suka zubo mata tace,. "Ko yanzu da Nike da ran ai maraya ne tunda har kika rabani da shi ta k'arfin tsiya"

Zuwaira ta Fara sallallami tana tafa hannu tace

"Au yanzu kina nufin nice na rabaki dashi bayan kina kallo Uwar Naziru ta d'aga hannu ta sharara mani mari har sai da naga tartsatsin wuta suna tashi a sama, amman ke ko a jikinki sai kokarin karb'o jikanta kike yi ki kawo muna cikin gida kina yi masu bauta, lalle sai yau na gano albasa bata yi halin ruwa ba haifuwarki kawai nayi amman kinfi son wasu a kaina, to tunda abun haka ne Koda wasa naji ance anganki tare da Naziru sai na tsine maki albarka kinbi duniya kin haukace, don na gano asirin da suka yi maki Mai k'arfi ne to ni zanje insa a walwale maki shi tass don bazan zuba Ido Ina kallonki ba kina wannan shirmen banza ba, karbi maganin kisha Wallahi ko yanzu in kanen ubanki."

Ta kare maganar tare da zaro mata ido Dole ta karb'i maganin tasha sannan ta kwanta tana kuncin zuciya, sai ga Sallamar Lantana Zuwaira ta fita tana amsa mata Sallamar ganinta yasa Lantana ta k'araso da fara'arta tana fad'in,.

"Ashe da gaske da aka cemani anga kin dawo? Shine nace bari inzo ingani Ashe ko da gaske, Allah sarki Malam Audu ya sauko kenan?"

Zuwaira ta maka mata wata jar harara tace

"Wane Audun kuma hmmm aini tsakanina dashi Wallahi sai dai ince Allah ya isana dashi, don har in mutu bazan manta abunda yayi man ba duk da taimakon da Nike yiwa matarshi"

Lantana rik'e da Baki tace,. "To keko Zuwaira Ina kika samo kud'in kika biya ko dai kin gane kudinki da aka sace ne?"

Tayi mere tace,. "Abbati yace wai mugun yaron cen ne Dan tsohuwa shine ya biya sai kace wani yace dashi ya biya"

Lantana ta janyo kujera ta zauna tace

"Wane kike nufi kin sani a duhu?"

Zuwaira ta yi wajen durom din ruwansu ta Fara zuba ruwan a bokiti tace,. "Ni Wallahi ko sunanshi bana son fad'i don Raina baci yake yi"

Lantana tayi Yar dariya tace,. "Daure ki fadaman kawata Nima da wani labari Mai dad'i nazo maki don tun abunda ya faru na Fara tunanin abun a raina"

Zuwaira ta dawo wurin lantana ta shinfida tabarma ta zauna tana fad'in ,. "Har kinsa naji na matsu inji ko minane don da wanka naso inje inyi WALLAHI duk kyamar jikina nikeyi, amman na fasa fadoman inji"

Lantana tayi Yar dariya tace,. "Dole ai gidan maza ba Wasa ba to ko kije kiyi sai in jiraki duk da Akwai inda zanje yanzu"

Zuwaira tace

"Aa kedai Gaya man kawai daga baya nayi wankan"

Lantana ta gyara zamanta tace,. "Kasancewar yarki kyakkyawa ce ajin farko kuma matar manya Shiyasa Naga wani abun alkhairi nace bari in zo in sanar dake inji ta bakinki"

Cikin matsuwa da taji komi Zuwaira tace

"Bani insha kawata har kinsa na fara jin dad'i"

Lantana tana yar dariya tace,. "Dole kiji dad'i ai don wannan abun idan har ya tabbata to daga ke har ita kun warke ke har Ni nan sai na sheda da samunku ke da ita"

Zuwaira ta Fara washe Baki tana jinjina Kai Lantana ta dafa kafad'ar Zuwaira tace,. "Na tab'aki da alkhairi tawajena wani hamshak'in Mai kud'i ne ya bada cigiyar a samo masa zankadediyar mace ya aura amman Fara kyakkyawa Yar matsakaiciya ita ba doguwa kwarai ba ita ba guntuwa ba a jiki ma yace baya son siririya samfarin muciya haka ma kuma baya son mai kiba yar tsaka tsaki dai haka irin Amrah, don Ina jin maganar itace farkon wadda ta fado mani a Rai, amman ke ya kike ganin za'ayi yanzu"

Zuwaira cikin tsananin farin ciki tace,

"Kice anzo wajen kawai"

Lantana ta kyakyalkyale da dariya tace,. "Anzo Kam sai ki tanadi aljihwan zuba kud'i don kuwa Akwai kafurar a k'asa tsattsage"

Zuwaira ta Mik'e tsaye ta Fara rawa tana jin dad'i bakinta a washe tace,. "Kice kwanannan za'a Fara kirana da Hajiya Zuwaira"

Lantana ta kwashe da dariya tace, "had'a da Ni Hajiya Lantana don Ni Kam in ma naje makalewa zanyi acen abuna inki dawowa yasin"

Zuwaira tuno Amrah bazawara ce har da haifuwa yasa taji jikinta yayi sanyi tace,

"To ke lantana budurwa yake so ko bazawara?"

Lantana tayi shiru sannan tace

"Nan gizo ke sakar domin kuwa lalle Budurwa yake nema, to Amman ita Amrah wa zai ganta ma yace ba Budurwa bace? Sai a barta kawai a matsayin budurwar tunda ba wani ganewa zai yi ba"

Zuwaira tace. "Aa Lantana gara dai ayi masa bayani yasani yafi da azo daga baya ya gano yayi muna tijara kinsan fa masu kudinnan ba duka ne suke da mutunci ba"

Lantana tace

"Share kawai yanzu akwai wasu dubaru da ake yi ba za'a tab'a gano ba Budurwa take ba matuk'ar aka had'ata ko kullum yake fasa budarci saboda kwarewa to bazai tab'a gano komi ba"

Zuwaira tayi shewa tace ,. "Bani mu kashe kawata kice arziki yazo muna har gida mu gyara

zama kawai mu fantama cikin nera"

Lantana ta kyakyalkyale da dariya tace,. "Tabbas don ko ance don yayi maki kyautar dubu d'ari daga kun gaisa ba wani Abu bane"

Zuwaira tayi wani zillo tace,. "Sai Ni Uwar Budurwa"

Gaba d'aya suka kara kwashewa da dariya, sai ga Amrah ta fito tana K'are masu kallo sama da kasa tace

"WALLAHI ko da za'a kasheni bazan tab'a aurenshi ba, dama kun Nemo wata don Nikam gidan Mijina Zan koma in rungumi dana da aka rabani dashi ta k'arfin tsiy....."

Kafin ta Kai karshen zancenta taji saukar Mari akan fuskarta, Zuwaira tayo kanta zata rufeta da duka Lantana ta riketa tana fad'in,

"Haba kawata wannan ba mafita bace ki barta taji da abunda ke zuciyarta a hankali asirin da suka yi Mata zai karye, Amman yanzu Kam dole sai kinyi hak'uri don kinji ance tsafi gaskiyar maishi"

Amrah ta maka Mata harara tace,. "Ke kuma Munafuka wa yace ki saka bakinki ki kyaleta ta kasheni in har hakan zai sa ta barni in koma gidan Mijina, don WALLAHI Ni ba wani aure da Zan koma yi idan dai ba shi zan sake aura ba "

Zuwaira zata kara dukanta Lantana ta rik'o hannunta suka yi d'akin Zuwairar, murya k'asa k'asa tace

"Ki kyaleta bata cikin hayyacinta fa kizo muje wajen Malaminnan zai Baki abunda zaisa asirin ya karye ta dawo taci gaba da yi maki biyayya fiye ma da yanda take yi maki a cen baya."

Zuwaira tayi shiru tana Nazari sannan tace ,. "Nifa WALLAHI bana son Ina baiwa kattin banza kud'ina suna cenyewa a banza"

Lantana cikin sigar lallashi tace

"Biyan b'ukata fa yafi dogon buri kawata ki saki jiki kawai ki taimaki yarki ta fito daga duhun da miyagunnan suka jefata a ciki, tun kafin abun yayi tsamari kiji ance dake an kamata dashi Yana yawo da ita Hotel hotel"

Zuwaira ta zaro ido waje ta dafe k'irji tace,. "Bari yi Mani wannan bakar fata Lantana kar ki b'ata man Rai "

Lantana ta rik'o hannunta tace,. "Abunda Naga zai iya faruwa ne shiyasa na fad'a maki

matuk'ar ba'a karye asirin ba , amman tunda baki so bari inyi shiru Allah ya huci zuciyarki ni kinga tafiyata sai na jiki"

Zuwaira tayi saurin fad'in "dawo kawata mu Kai karshen maganar musan inda zamu dosa don wannan da kika ganta idan ba rabata da asirinnan aka yi ba to ita kanta bazata ji dad'in kanta ba balle har mu muji"

Lantana ta dawo ta zauna tace,

"Idan ma bazaki je ba to Ni ki kawo kud'in sai inje in karb'o maki maganin". Cikin jin dad'i Zuwaira tace

"Yawwa kawata kin kawo shawara har naji sanyi bari in kawo maki kud'in sai ki Kai masa Allah yasa mu dace"

Lantana cikin tsantsar farin ciki tace,. "Ameen kawo inyi maza inje in Kai masa domin muji wane kalar asirin ne suka yi mata"

Zuwaira taje cikin sauran kud'in da Salis ya bata ta kirgo dubu biyar ta baiwa Lantana , cikin wani tsantsar murna Ladi ta karba ta Mik'e tana gyara mayafinta suka fito tsakar gidan, Zuwaira ta rakata har soron gidan sannan ta dawo zuciyarta cike tsantsar farin ciki tayi d'akin Amrah da niyyar ta lallabata ta shawo kanta ta amince da abunda zasu zo Mata dashi.

Hmmm Ba girin girin ba dai tayi mai🤔🤔

Akafta🤣

D/Auta Novel✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

AM BACK MY FANS kuyi hakur buki muke shiyasa kuka jini shiru🤦🏻‍♀️

PAGE 49

AMRAH Kam sai cisgar kukanta take yi saboda wannan bak'in hali na Mahaifiyarta ya fara bata tsoro, ace ita kwata kwata bata da tunani mai kyau ada tana biyeta bata ganin laifinta sosai, amman yanzu kam tunda ta gano gaskiya ta fahimci cewa sunyiwa su Inna da Nazir bahaguwar fassara, domin kuwa sune masu sonsu na gaskiya kuma tsakani da ALLAH musamman da ta natsu ta tuno irin fad'i tashin da Mahaifin Nazir yayi dasu kafin ya rasu, uwa uba dawainiyar da Nazir yayi akansu daga ita har k'annenta, amman duk da hakan ace wai Mahaifiyarta duk ta mance da komi ta maida su Inna abokan gabarta, wad'anda ya dace ace ta rik'a a matsayin Yan uwanta na jini kasancewarta ba Yar gari ba, gashi ta rabata da Masoyinta da d'anta kuma duk da hakan bata ganin aibin abunda tayi har ma k'ok'arin take yi ta k'ara koma zurmasu cikin wani sabon Bala'i, to ita Kam taci alwashin ba da ita za'a yi wannan shirmen ba don ya zama wajibi wanann karon ta k'waci yacinta hannun Zuwaira.

Tana Cikin zancen zucinta ne Zuwaira ta shigo ta zauna gefen gadon tana kallon yanda Amrah take ta ruwan hawayen ta sauke k'atuwar ajiyar zuciya tace,

"Amrah ki daina wannan koke koken da kike yi ki zauna ki fahimci cewa duk abunda kika ga ina yi bafa don kowa nike yi ba sai saboda ke kiji dad'i ne, rayuwarki ta inganta ko bayan bani duniyar ba zakiyi kuka ba, ki tallafi kanki ki tallafi Yan k'annenki kwaya biyu da ALLAH ya baki, Kinga wannan mutumin da Lantana tazo muna da zancenshi, ance Mai kud'in gaske ne ya

mallaki dukiyar da shima kanshi baisan iya adadinta ba, kinga ko idan muka yi nasara muka dace ya aureki shikenan mu ALLAH ya rabamu da figar kazar wahala, in don ta yaronki ne cikin ruwan sanyi zaki janyo abunki ya dawo hannunki, don kuwa a lokacin kinyi k'arfin da ko Innar Naziru kike so ta zo ta zama Yar aikin gidanki zata amince ta zo ballantana kince a baki yaronki ya dawo hannunki ai da gudu za'a baki, saboda haka ki kwantar da hankalinki ki ajiye komi da ya faru ki fuskanci rayuwa ko don ki mori kurciyarki tun kafin tsufa ya zo maki baki tsinci komi ba"

Zuwaira ta yi shiru tana son ta ji lafazin bakin Amrah, Amman Amrah kam sai kukanta take yi taki cewa Uffan, Zuwaira ta danne zuciyarta tace

"Yanzu ki duba ko ga rayuwata kawai da kika gani ai Ina jin ta isheki zama ishara, lokacin da Babanku ya fito yana Sona Akwai d'iyan manyan mutane masu kud'i a garinmu ke har ma da d'iyan Sarakuna duk sun fito neman aurena, Amman na buga kaina ga k'asa na tirje na bi soyayya nace sai Mahaifinku zan aura, Akwai wani ma Dan uwana da aka so in aura amman na kafe nace sai dai shi d'in na zo na aureshin,Wanda a sanadiyyar hakan ma iyayena suka yi fushi dani suka ce ba ruwansu dani tunda naki bin umurninsu na auri wanda suke so, to amman kinga yanzu wa gari ya waya? Ni!! tunda kinga na auri babanku har yanzu ina nan cikin bak'in talaucina shiyasa ma har Nazir yaga damarmu don yayi muna hidima ya zo yana goranta muna, don da ace Mahaifinku Mai kud'i ne don ya rasu ba zamu tagayyara ba, saboda ai zai barmuna kud'i muci gaba da rayuwarmu har ma fiye da lokacin da yake raye, to amman yanzu gashi k'arshenta ma a gidan haya zamu k'are kingin rayuwarmu, to haka kike so mu zauna Ni ban mori zaman duniyar ba kema baki mora ba?, Kina kallo duk shegen da zai fito Sona da aure idan zaki k'are masa kallo tsaf zaki gano cewa nima abun hannuna suke hange, su kuma wad'anda ya dace ace su zo da nufin auren ba da wannan manufar suke zuwa ba shashanci ne yake kawosu, shiyasa kika ga na tattara aure na ajiyeshi a gefe na zabi in sadaukar da rayuwata in zauna in kula da ku, gashi saboda ku ma naki komawa Mahaifata na zab'i zama cikin danginku don kawai in faranta maku don gudun inje daku cen kuga abunda zai b'ata maku Rayuka, Amman yanzu ke ga irin sakayyar da kike so kiyi mani ki zab'i zama da wanda ya tozartani a bainar Nasi ya kaini K'ara kotu gaban idonki yana fad'i ina fad'i, WALLAHI AMRAH ki dawo hankalinki tun kafin hak'k'ina ya kama ki"

Zuwaira ta fashe da wani bala'a'en kuka ta Mik'e tayi d'akinta gaba d'aya jikin Amrah yayi sanyi k'alau, zazzabin da take ji ya dawo sabo sai rawar sanyi take yi hak'oranta sai kaf kaf suke yi suna had'uwa da juna, Wani sabon Kuka ya zo mata cikin kukan tace

"Ya ALLAH ka kawo man mafita ALLAH ka fiddani cikin wannan hali da nike ciki, ka fahimtar da Mahaifiyata ta dawo hanyar gaskiya"

Cikin k'arfin hali ta yaye bargon da tayi lullub'i dashi saboda sautin kukan Zuwaira da take ji, ta sauko gadon jikinta yana rawa ta fito d'akin jiri yana kwasarta ta nufi d'akin Zuwaira, ta sami gefen gadon ta zauna gaba d'aya zuciyarta tayi sanyi k'alau saboda kukan da taga tana yi yasa ta ji zata ajiye son zuciyarta ta bi abunda take so Koda ita hakan zai cutar da ita matuk'ar ba

sab'on ALLAH bane,. Cikin sanyin jiki tace

"Don ALLAH Mama kiyi hak'uri kinji? Insha ALLAHu daga yau na daina k'in bin abunda kike so, Amman kisani Ina son Yaya Nazir Kuma Ina kwadayin sake zama dashi, amman duk da haka nayi maki alk'awalin zan auri duk Wanda kike so in aura matuk'ar kina ganin hakan shine zai yi maki dad'i ya saki farin ciki, Amman Ina son Don ALLAH ki daina biye shirmen Lantana don ba wani ilimin kirki gareta ba, zata je ne ta dulmiyar dake har ma tasa ki rasa naki sanin da kike dashi."

Cikin tsananin jin dad'i Zuwaira ta share hawayenta tace,.

"Har na fara tunanin komawa Mahaifata in zauna in barku hannun dangin babanku tunda daman cen kunfi sonsu dani"

Amrah ta girgiza kanta da ke Sara Mata tace "A'a Mama yi zamanki kawai insha ALLAHu komi ya wuce matuk'ar dai zaki rabu da Lantana saboda ba mutuniyar kirki ba ce"

Zuwaira ta washe Baki tace "Idan kinyi man haka Ni Kam ai kin gama man komi a rayuwa don Ina son kiyi auren nunawa sa'a muma mu fantama mu yi hannun riga da talauci, Sai dai kuma Kinga Lantana ce ta zo muna da wannan abun alkhairin ai Kinga ko ba k'ashin yadawa ba ce, don haka bari sai kinyi auren shikenan sai mi watsar da banza mu ci gaba da wandak'armu cikin dukiya"

Amrah ta yamutsa fuska saboda tashin zuciyar da take ji ta dafe goshinta, Zuwaira tayi saurin rik'ota taji jikinta yayi zafi zau! da sauri tace

"Wai har yanzu zazzabin bai sauka bane? Ko dai yunwa kike ji ne?"

Amrah ta k'ara yamutsa fuska tace

"Ni bana sha'awar abincin ma sam tea kawai Nike so idan zan samu insha"

Zuwaira ta sauko daga Kan gadon tace

"Bari inje in d'ora maki ruwan zafi yanzu ai tunda muna da sauran Madara kwanta kawai bari in kawo maki."

Amrah ta rab'a gefen gadon ta kwanta ta dunk'ule waje d'aya tana nazarin ta wace hanya zata samu ta shawo kan Mamarta ta dawo hanya ta fahimci gaskiya?.

Tana Nan kwance tana kyarmar sanyi har Zuwaira ta dawo da kofin tea d'in tana juyashi da spoon tace

"Tashi kisha ko da zaki samu cikin ya Dan warware maki watak'ila ma tun jiya rabon da kici komi".

Amrah ta Mik'e ta karb'i tea d'in ta fara sha a hankali har ta shanye Sannan ta ajiye kofin ta k'ara kwanciya,. Zuwaira ta d'auko wani zanen gado ta lullub'eta dashi tace

"Kwanta abinki nima bari inje inyi wanka wai Ina Abdallahh ne?? Ni tunda na dawo ma fa banganshi ba"

Amrah daga dunk'ulen tace "bai dad'e da fita ba kika shigo"

Zuwaira tace,. "Dama ya lafiyar kura bare taci sarauta? Ai tunda yaga bana gida Daman sai inda Manshi ya k'are ai zai zo ya sameni ne."

Da marece sakaliya sai ga Lantana ta dawo gidan da fara'arta musamman da ta taradda Zuwaira tana zubawa Amrah ruwa tana wanke Aman da tayi, ta Sami kujera ta zauna sai faman wasar Baki take yi, Zuwaira ta rik'o Amrah ta kaita d'aki Lantana ta bisu da kallo har suka shige ta girgiza Kai tayi tagumi, sai ga Zuwaira ta fito tazo ta sami wuri ta zauna cikin damuwa tace

"Ya akayi Lantana dafatar dai kinje?"

Lantana ta washe Baki tace,. "Ai ko da ganin fuskata zaki gano naje har ma anyi nasara, Amman ke sai naga kamar ma cikin damuwar kike har yanzu"

Zuwaira ta B'ata fuska tace,. "Dole ki ganni cikin damuwa Lantana saboda yanda Amrah ta saka kulafucin yaronnan a ranta gashi duk ta gayyatowa kanta ciyo"

Lantana tace

"Kwantar da hankalinki zata Ware ne da zarar asirin ya gama fita daga jikinta, don yanzu haka Malam a gabana yayi ta kakkarya asiran da aka yi mata ko ke baki ga wani canji daga gareta ba ne?"

Zuwaira tayi saurin fad'in ,. "Nagani WALLAHI don ma har tayi man alk'awali akan zata amince da duk mijin da nikeso ta aura"

Lantana tayi wani zullo ta rik'e hanci tace

"Ayyururui Masha ALLAHu duk da dai banda hancin gud'a kice Malam aikinshi ya fara tasiri? To Sai mu gode ALLAH yanzu daman abunda yasa na zo da hanzarina saboda yace sai an bada kud'i anje an siyo wani turare da za'a kore bak'in Aljanin da ke kanta Wanda yake sakata jin son

Nazirun aranta, don da zarar ya tashi kanta shikenan zata dawo Amrarta har ma ta manta da shi kwata kwata ta fuskanci sabuwar rayuwar da zata zo mata a nan gaba"

Zuwaira jikinta yana rawa tace

"Nawa ne kud'in? Ai Akwai sauran kud'in da wani Tsohon saurayinta ya bani sai in bada lafiyarta kama da me? "

Lantana ta gyara zama tace

"Dubu biyu ne kacal zaki bada a siyo turaren da zarar yaji k'amshin a jikinta to zai Kama gabanshi"

Zuwaira ta Mik'e taje ta d'auko kud'in ta Mik'a mata Lantana ta karb'a ta Mik'e tace

"To Ni zan tafi sai kin jini"

Zuwaira tace

"To ALLAH ya tsare nafa gode da dawainiryar da kike muna kawar kirki"

Lantana tace,. "Kada ki damu an zamo d'aya ai fatanmu kawai tayi nasarar cafke zuciyar wannan Babban Alhajin"

Cike da jin dad'i Zuwaira tace

"Ameen Ameen Lantana"

Sannan ta rakata har soron gidan Sannan ta dawo cikin farin cikin wannan nasara da aka fara Samu.

***

Bayan sati biyu jikin Amrah yak'i dad'i wasa wasa dai kullum da zazzab'i take kwana sai dai bata bari Zuwaira ta sani saboda ganin yanda ta damu akan ciyon nata da ta ta'allak'ashi da k'awa zucin d'anta da k'ulafucin son komawa gidan Nazir, don ko Aman da take yi ta daina fitowa tsakar gida toilet d'inta take shigewa tana yin abunta.

Tana tsugunne tana wanke wanke sai ga Lantana ta shigo da fara'arta tana gud'a, Zuwaira tayi saurin fitowa daga d'aki ta tareta itama da tata murnar tace,

"Wannan gud'ar k'awata ta mecece?"

Lantana tace

"Albishirinki". Zuwaira baki Yana rawa tace

"goro fari k'al"

Lantana tace "to Alhmdllh Alhaji dai duk cikin photunan da aka Kai masa yace shi duk cikinsu ya fi son Amrah, don itace tafi dacewa da matar da yake so sai dai inda matsalar take cewar da yayi zai zo ya ganta Ido da Ido"

Zuwaira ta fara rawa tace,. " Kice Shikenan na zama surukar Alhazawa?"

Lantana cikin jin dad'i tace,. "Kin zama Kam ai shiyasa kika ji na dage akan ki matsa sai taje tayo photon yanzu ba gashi ba? Tun kafin aje ko'ina ta sark'o zuciyarshi ina ga ya ganta Ido da Ido, duk da dai ta rame amman ai hakan bazai hanashi ya ga kyawonta ba tunda dai har ya tsallake d'inbin photunan da aka Kai masa ya zab'eta"

Cikin sanyin jiki Zuwaira tace

"To fa kinsan bata gama idda ba ya kenan gashi Kuma yace zai zo?"

Lantana ta B'ata fuska tace,. "Ke ganinta fa kad'ai zai zo ya yi ba wai auren za'a d'aura yanzu ba, kinga idanma an zo saka Rana sai a saka dai dai lokacin da zata kammala iddar, Kinga shikenan bazai fahimci komi ba musha biki mu dagargaje abunmu"

Zuwaira tace

"Ni dai da son samu ne ya jira har ta k'are zaman iddar Sannan ya zo Kinga idan yazo ko sati biyu ba za'a rufa ba sai ayi auren"

Lantana ta hararetа tace. "To ai sai kisa ya zaci neman Kai ake da d'iyar tunda har daga zuwanshi anbashi ita, ai gara a Dan ja lokacin don ya gano cewa ita d'in Mai tsada ce, don ma fa nuna masa za'ayi tana da masoya da yawa har ma an tsayar mata da wani kuma taci abunshi, sai a yanka masa manyan kud'in da zai biya, idan ya bada shikenan sai ayi auren"

Sai tsinkayar muryar Amrah suka yi tana fad'in,. "WALLAHI bazan lamunci ayi irin wannan kwamacalar Dani ba idan dai b har ba za'a bari in yi idda ba kafin ya zo to ni na fasa ma biye maku"

Lantana ta zaro Ido tace,. "Rufamuna asiri yarnan baki ga yanda yake sonki ba ne don haka ai ba za'a yi hakan ba, mafita d'aya ce idan ma ya zo kada ki yi magana fitowa kawai zakiyi da ya ganki ki koma shikenan"

Amrah ta maka mata wata k'atuwar harara tace,. "A cikin wani littafin kika ji ance ana neman mace cikin idda?? To bari kiji haramun ne yin hakan idan zai jira har in kammala to idan kuma yaji bazai iya ba to ya je wajen wata tunda ba Ni kad'ai ce mace ba"

Lantana ranta a bace tace,. "ToZuwaira kin dai ji don haka Ni zan zare hannuna in barki da yarki tunda har rashin kunya take so tayi mani, sai in barki da ita ke kuma sai ki zura mata ido kina hango samu ta kaiki wajen rashi , don na tabbata duk Wanda zai zo neman aurenta a yanzu bazai Kai Alhaji mai runbun kud'i ba"

Ran Zuwaira a had'e ta kalli Amrah da ke wanke wankenta tace

"Ko da Wasa kada in sake jin kin d'agawa Lantana murya, don komi lalacewarta dai ai k'awata ce kin ko ga bazan lamunci ki Renata ba"

Lantana tayi zumbur ta rik'e kugu tace

"Ballema dai ba a lalacen aka ganni ba'"

Ta k'are maganar tana murgud'a Baki Zuwaira ta dafa kafad'arta zata yi magana kenan suka jiyo sallama a k'ofar gida, Gaban Zuwaira ya kire ya fad'i saboda sheda muryar Wanda ta sayarwa da gidan da tayi, jikinta yana rawa ta yi k'ofar gidan ko mayafi babu sai dankwalinta da ta kwance ta rufu dashi.

 Aiko tana lek'awa taga shine tayi saurin washe bakin k'arfin hali tace,. "ALLAH sarki Ashe dai Kaine da gaske? "

Yana yar fara'a yace

"Eh nine Kan zancen gidan ne nazo saboda kwana biyu bana garin nayi wata Yar tafiya saukata kenan nace Bari inzo in sanar daku nan da kwana Uku nike son ku bani gidan saboda Akwai Yan hayar da Nike son in zuba a ciki"

Zuwaira gabanta ya kire ya fad'i cikin rawar murya tace

"Yanzu mu idan muna son a bamu hayar zaka bamu ai ko?"

Ya washe Baki yace

"Eh me zai Hana sai dai matsalar d'aya ce su wadancen din har na ma karb'i kudinsu, amman da yake Akwai dakuna cikin gidan sai ku tattara kayanku ku Basu daki biyu daga ciki sai suma su zauna tunda har Kuna bukata ai ba damuwa bane, Zan je inyi masu bayani sai ku zauna tare"

Zuwaira tayi shiru Sannan tace. "Yanzu idan muna son gidan gaba d'aya nawa zaka bamu hayarshi a shekara?"

Mutumin yayi dariya yace

"Da dai kin ba da wasu dakunan saboda a gaskiya kud'in da yawa don kosu wad'annan yanzu haka dubu d'ari biyu da hamsin suka bani a shekarar, koshi dakyar ma na amince da hakan amman idan kina so duka shikenan sai inje in samo masu wani gidan duk da dai ba wani gida da Nike dashi empty yanzu duk haya ne ake yi a ciki"

Zuwaira tayi shiru tana Nazari tace dashi "Bari in shiga gida in fito". Cikin Yar dariya yace

"Ba damuwa Ina jira"

Ta koma ciki zuciyarta sai halbawa take yi ta taradda Lantana zaune ganin Amrah bata tsakar gidan yasa ta yi d'akinta jinta da tayi a toilet tana ta kakarin amai yasa ta Isa wurinta da sauri ta rik'o hannunta tace

"Wai ke wannan Aman na lafiya ne kuwa? Ina murna kinji sauk'i Ashe shi Aman har yanzu baki dainashi ba wai ko dai ciki ne dake bansani ba?"

Amrah ta yi saurin wanke bakinta tare da zaro Ido tace,. "Ciki a'a Nikam WALLAHI bani da komi"

Zuwaira ta maka mata wata harara tace

"Idan har da gaske baki da komi shi wannan Aman na minene?"

Amrah ta fito toilet d'in gabanta yana ta fad'uwa tace

"WALLAHI bani da komi Mama yanzu haka ma fashin Sallah Nike yi"

Zuwaira ta yi saurin fad'in "yaushe kika Fara rashin sallahr? Ai Naga yau ma kinyi sallahr Asuba, ko kin manta nazo tada ke ki tashi na taradda ke kina karatun Al'Qur'ani ko kin manta?"

Amrah ta daburce tace,. "Eh yanzunnan na ganshi yazo"

Sannan hankalin Zuwaira ya Dan kwanta duk da wani sashe na zuciyarta yana kokwanton akan hakan, kasancewar Akwai abunda ke gabanta yasa ta share zancen tace da ita

"Mai gidannan ne ya zo akan zancen tashi mu bar gidan, to da naji Yan haya zai zuba nace dashi muma zamu biyashi kud'in shekara sai mu zauna Kinga kafin Sannan ma kinyi aurenki da

Alhajin har gidan kanmu ma mun mallka Kinga shikenan sai mu bar Masa gidanshi mu koma namu, to Amman matsalar kud'in da naji ya ambata ne suka yi yawa wai dubu d'ari biyu da hamsim gashi Ni nan ko dubu ashirin cikakku banda su ya kika ga za'ayi? Ko kayan d'akinki zamu je mu siyar ne muga in kud'in zasu Kai sai mu bashi?"

Aiko sai gashi AMRAH kud'in da Abbati ya bata ta ajiye mata sun fad'o mata a Rai don kwata kwata shaf ta mance dasu, ta je ta bude inda ta ajiyesu ta d'auko ledar kud'in ta dawo gaban Zuwaira ta tsaya ta Mik'a mata kud'in tace,

"Ga kudinki da Abbati ya bani yace in ajiye maki tun ranar da ya karb'oki na manta shaf sai yanzu na tuno da kika yi zancen kud'i"

Zuwaira ta rik'o ledar jikinta yana rawa ta bud'e kud'in ta leka ba shiri ta zaro Ido tace

"Kan uban cen waton dai Ashe da gaske Abbati ne ya sace kud'innan, lalle ko zanci Uban Abbati iyyee shine yace dani wai Naziru ya biya kud'in Ashe yasan shine barawon kud'ina? Aiko idona idon Abbati WALLAHI sai na ci mutunshi Dan iska wato Ni yayiwa renin hankali don baya Sona yasa Audu yayi man rashin mutunci yasa aka kaini aka rufe, to ai da ma bai fiddo kud'in ya karboni ba ya barni cen idan na mutu yaje ya karb'o gawata"

Aiko inda take shiga ba Nan take fita ba sai surfa ruwan bala'i take yi, har sai da Lantana ta shigo ta Fara bata hak'uri ta sanar da ita ga Mutumin cen fa yana ta sallama ta barshi k'ofar gida, Sannan ta tuno dashi ta zazzage kud'in a kan gadon Amrah ta Fara lissafasu kasancewar kowace dubu goma daban daban suke shiyasa kirga sauran kud'in da suka rage cif cif da lisaafinta idan aka cire kud'in da aka kaiwa Malam Audu Police station aka karb'ota, cikin rawar jiki ta fidda dubu d'ari biyu da hamsim zata fita Amrah ta rikota tace

"Don Allah ki bar Masa gidanshi ya saka duk Wanda zai saka sai muje mu siyi Dan k'aramin gidanmu mu zauna hankalinmu a kwance yafi da ace mu yi ta zama gidan haya har tsawon shekara d'aya"

Zuwaira ta fisge saboda jin wata katuwar Sallamar da mutumin ya rafka, tace

"Ba wani k'aramin gida da zamu je mu zauna ai kafin kudinmu su k'are ma mun mallaki gidanmu na kanmu, bari in Kai masa kud'in in dawo"

Ta fice cikin sauri Amrah ta Kai zaune ba shiri ta dafe goshi ganin kamar hannun Lantana kusa da wani daurin dubu goma yasa tayi saurin tattara kud'in ta mayar leda ta rungume a jikinta, Lantana ta maka mata wata harara tace

"ALLAH dai yasa ba barauniya kika d'aukeni ba? Nafa fara gajiya da halinki yarinyar nan WALLAHI ki kiyayeni tun bansa aka koya maki hankali ba"

Amrah ta maka mata harara tayi tsaki ta fito waje da ledar kud'in a hannunta, Lantana ta biyota tana fad'in

"Ke yanzu Ni kike yiwa tsaki?"

Amrah tace

"Anyi maki ko kin d'auka bansan karyar da kike laftawa Mama ba? Hadda wani turaren k'arya da kika kawo wai na cire bak'in aljani to Bari kiji WALLAHI ko ki fita cikin sha'aninmu ko in fad'awa Mama gaskiya ta daina yarda da ke tunda cutarta kawai kike yi ba wani Malami da kike kaiwa kud'i ke ke cin abunki"

Lantana ta zaro Ido tace,. "Kutumar babban balasi me kike nufi to ai Nima sai in fad'a mata cewa Ciki ne da ke tunda har ita ta kasa gano hakan"

Amrah ta zaro Ido waje tace

"Eh da yake ke kika man cikin ba ai Dole ki fad'a mata bak'ar Munafuka WALLAHI sai nasa Yaya Nazir ya daureki matuk'ar kika fallasa wannan maganar har ta yarda da zancenki"

Lantana ta zaro Ido ta gyara zaman mayafinta tace

"Ni na tafi Amman ki sani duk kika tona Ni WALLAHI ki kwana da Shirin sai nayi sanadin da aka zubar da shegen cikinnan bak'ar jarabba don masifar jaraba irin taki yaro ko arba'in bai yi ba kin bud'e kafafu an sake dirka maki wani cikin don zalamar tsiya"

Tana K'are maganar ta fice, Amrah ta bita da kallo aranta tace

"An bud'a din sai ki zo ki hana Waton dai Ashe da gaske cutar Mama kike yi ai Ni duk fad'a kawai nake yi don in gano gaskiya Ashe ko da gaske to ko WALLAHI sai na fad'awa Mama gaskiya muguwar Mata kawai azzalumar kawai"

Amrah ko Lantana😂

Akafta🤣

Princess Dija D/ AUTA ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

SPECIAL THANKS TO MY CHILD FRIENDS AMINA HALADU SHINKAFI (AMBASH). RUKAYYA HABIBU TSAFE & SHAFA ABU KAURA🤝

Wannan page naku ne sukutum Kuma kyauta ne agareku kuyi yanda kuke so dashi👍🏻

PAGE 50

Zuwaira tsaye da mutumin suna magana sai ga Lantana zata fito tayi saurin fad'in "A'a ba dai har kin fito ba?"

Lantana tayi Yar dariya tace

"Eh Akwai inda zanje ALLAH dai yasa mu cikin masu dacewa kawai"

Zuwaira tace "Ameen Lantana nagode sai kin dawo mu k'arasa maganar ko?"

Tace "Eh" Sannan sukayi sallama ta wuce Zuwaira ranta a jagule tace da mutumin,. "Don Allah ka nemar masu wani gidan Ni bana son su zo su takura muna a banza"

Mutumin yayi dariya yace,. "Hak'uri dai za'ayi abi yanayi sai ku tattara kayanku ku Basu d'aki biyu zasu zo su fara kawo kayansu, don yanzu haka masu neman gidan ne nace maki suka kirani saboda sun matsu da su dawo gidan Kuma gashi duk sauran gidajena kudi'n hayar da aka bani na shekara basu k'are ba, don yanzu haka ma su kansu basu da ra'ayin zama tare da wasu Dole ce kawai tasa don Bana son kiga ban kyauta maki ba"

Cikin sanyin jiki Zuwaira tace,. "To shikenan ai insha ALLAHu ma kafin a rufa shekarar ma mun mallaki namu gidan"

Mutumin yayi Murmushi yace,. "ALLAH ya nufa ai ana son hakan"

Sannan tayi sallama dashi ya tafi ita ta koma cikin gidan zuciyarta cike da takaicin had'a gida d'aya da zasu yi da wasu.

Amrah zaune kan tabarma tayi tagumi tana nazarin neman hanyar da zata b'oye d'an tayin cikinta kada Zuwaira ta gano, don tasan muddin tasan dashi to ko yanzu d'in tsugunne ba zata k'are ba, don kuwa tasan dole ne tace sai an zubar dashi ita ko bazata zura ido ko yanzu ta rabata da farin cikinta ba.

Tana cikin nazarin ne har Zuwaira ta zo ta zauna tana mitar zaman da wasu zasuyi a gidan, don duk surutun da take yi Amrah bata ma san tana yi ba, har sai da taga bata ce da ita kanzil ba Sannan ta waigo ta kalleta tace

"Wai ke tagumin me ne kike yi haka?nifa bana son irin wad'annan abubuwa ke kullum Ina k'ok'arin Inga na faranta maki amman ke kink'i sakin jiki ko d'an Kumarin arzik'i kiyi"

Amrah ta sauke tagumin da tayi tare da sauke wata ajiyar zuciya tace,

"Ya kuka yi dashi ne?"

Zuwaira ta B'ata fuska tayi mere tace,. "Kayanmu zamu kwashe mu basu d'aki biyu wasu zasu zo mu zauna gidan tare dasu, yanzu haka kinga rabin kud'ina ya maido mani"

Amrah ta nisa ranta a b'ace tace,. "Shiyasa Mama kika ji nace mu basu gidansu kawai muje mu

siyi namu yafi muna duk wannan rab'e rab'en da zamu dinga yi"

Zuwaira tayi shiru Sannan tace,. "Kudinmu duk nawa ne halan? da har kike tsammanin zasu ishemu siyen gidan, to bari kiji duk yanda gida ya lalace wajibi ne sai ya haura miliyan d'aya, Kuma yanzu haka kud'in namu ai ko Milyan dayan ba su Kai ba"

Amrah tayi saurin fad'in ,. "A sayar da kayana mana sai a had'a a siye gidan ai zasu isa Mama"

Zuwaira ta maka mata wata jar harara tace

"Idan an kwashe kud'in an siye gidan k'asa kike so mu dinga ci ko kuwa? Ko kuma muna da wani Wanda muka ajiye da zai dinga bamu abinci ne?"

Amrah tayi shiru dolenta saboda ita kanta ta gano cewa fa yanzu basu da kowa sai ALLAH sai kansu, kuma gashi daga ita har Abbati d'in ba wata sana'a suke yi ba balle har su dinga tallafawa kansu, wata kwalla ta zubo mata cikin damuwa ta saka hannu ta goge tace

"To yanzu Mama ya zamuyi haka za muyi ta zama rayuwarmu ta Kare a gidan haya?"

Zuwaira ta Mik'e cikin tsananin b'acin Rai tace,. "Tunda ALLAH ya had'a mu da miyagun mutane ya zamuyi? Kina kallo Asabe ta had'a Kai da Mijinta sun marawa Nazir baya don kwadayin idan an bada kud'in ya D'an tsakura masu su gyara tukunyar abincinsu, to ai ta ALLAH ba ta kowa ba don WALLAHI ko mutuwa nayi ban yarda ku koma huld'a da Asabe ba, don na riga da na yanke duk wani zumunci dake tsakanina da ita har abada"

Amrah tayi saurin share hawayenta tace

"Don Allah Mama kiyi hak'uri Aunty fa Babu ruwanta fa don Wallah....."

Zuwaira tayi saurin katseta tace,. "Yiman shiru WALLAHI tun kafin in sab'a maki duk wa ya kaini shiga wannan bala'in ba ita ba? Sai da nace ban amince da ki auri matsiyacin yaron cen ba ta hure maki kunne kika bijiremani, dangin Babanku suka k'ara doraki a Hanya kika rufe Ido kika nunawa duniya ban isa ba, to ai kinyi auren Kuma Kinga inda auren ya k'are a tanbade ba tare da kin mori komi ba har sai Karin bak'in ciki da takaicin da kika kwasowa mutane, Ni in Banda Uwa Uwa ce ma ai Wallahi da ko kallo baki isheni ba, sai in barki kije cen kiyi ta kayan matsalarki tunda shi wannan d'ebabben albarkar yaron Babu d'igon Imani a zuciyarshi, ai Ni Wallahi tsakanina dasu sai dai ALLAH ya isa don ko Lahira bana fatar ALLAH ya hadani dasu bale Duniya"

Amrah cikin tsananin bak'in cikin maganganunta ta fashe da kuka, Zuwaira ta mangare mata Kai tace

"Wani kukan munafucci yanzu kuma kike so ki bini dashi ko Yaya? Kina yiman shiru ko sai kinja

na rufeki da dukan tsiya wurinnan?"

Amrah ta Mik'e tayi d'akinta tana ta kukanta, cikin takaici Zuwaira ta lek'o tace

"Ki ajiye wannan kukan iskancin ki tashi ki harhada kayanki ki baiwa mai gida d'akinshi"

Cikin kukan Amrah tace

"Wadancen dakunan fa su me suka yi da ba za'a bada su ba sai wannan?"

Tace

"To Hajiya maigidan anji fito ki kwashe tarkacen ki bada filin d'akunan tunda kaddarar bak'in aurenki ta ja muna zama da Yan haya"

Tana rufe bakinta suka jiyo sallama Zuwaira dake k'ofar d'akin Amrah tayi saurin waigawa ai kuwa sai ga wata mace katotuwa da yanmatan yaranta su biyu sai wara Ido suke suna k'arewa gidan kallo ba tare da sunce da Zuwaira kanzil ba.

Cikin mamaki Zuwaira tace

"Lafiya bayin ALLAH naga kun shigo Kuna k'arewa gidanmu kallo wani Abu kuke nema halan??
"

D'aya daga cikin yanmatan ta kalli Zuwaira sama da k'asa ta zubar, dayar ce ta rik'e kunkuru tace

"Lafiyar ce ta kawo haka gidanmu muka zo dubawa inda abunda zamu gyara mu gyara don gobe muke son tarewa"

Cikin rudu Zuwaira tace,. "Toh sannu masu gida to Kuma nuna ikon na miye tunda dai ba ku kuka ginashi da kanku ba?"

Katotuwar Matar da ita dudduba gidan kawai take yi lungu da sak'o jin abunda Zuwaira tace yasa ta kalleta tayi wani mere Mai had'e da wata guntuwar dariya tace

"ALLAH ma ya rabamu da mallakar gida irin wannan kuma ace mu d'agashi a kasuwa in sayar dashi don kawai in kashewa 'yata aure"

Gaba d'aya suka kwashe da dariya daga 'ya'yan har Matar wadda da alama ma Itace ta haifesu, Zuwaira cikin fad'uwar gaba tace

"Kan Uban cen lalle ko gidannan za'ayi yak'in Basasa na biyu muddin aka ce kune Yan hayan

da Zamu zauna daku"

D'aya daga cikin yanmatan wadda da alamu tafi zama tsagera tace

"Kece sabuwa a fagen yak'in mu ai mun riga da munci dubu sai ceto, don haka ki iya bakinki WALLAHI tun kafin mu lakad'a maki shegen duka a yanzunnan don mu Fara sanar dake mu d'in ko su waye ne mu"

Amrah dake d'aki tana kuka jin sautin maganganunsu na rashin mutunci ga Mamarta yasa ta fito rik'e da k'ugu tana kallonsu d'aya bayan d'aya tace,

"Ku haka ake yi daga zuwa sai tashin hankali? To Bari kuji arzikinmu ne kuka zo kuci gidan don haka Babu Yar iskar da ta isa ta d'aga muna dan yatsa bamu karya shi ba"

Yanmatan biyu suka kalli juna suka fashe da dariya dayar ta k'araso gaban Amrah ta tsaya tana nunata da D'an yatsa tace

"Ke karamar k'waranya a cikin kayan miya wacece ke Kuma miye Matsayinki?"

Ta maida kallonta ga dayar tace

"Wai Aunty Zulfi ko itace ma yarinyar da aka ce tayi shari'a da Mijin da Mahaifinta ya aura mata tun tana Yar shekara Tara?"

Wadda aka Kira da suna Zulfi tace

"Kin canka adaidai ko Hafsa don kuwa ita d'in ce dai a gabanki ALLAH dai ya rabamu da irin wannan bak'in halin Mai cike da abun kunya"

Wadda aka Kira Hafsa ta rufe Baki tana k'unshe dariya tace

"Sannu kinji ALLAH ya baki ladar abunda kika aikata don Wannan shi ake kira da rashin sanin darajar Mahaifi, in wasu suna Biyayya bayan rai ga saurayi to ke rashin Biyayya bayan Rai kika yiwa Mahaifinki tirr WALLAHI kinsha haush...."

Kafin ta Kai k'arshen maganarta ne Zuwaira ta d'auketa da wani bahagon Mari, Yarinyar tayi saurin dafe gefen da ta mareta ta zaro Ido tace

"Ni kika mar...?"

Zuwaira ta k'ara d'aga hannu ta sake sharara mata wani Marin, yarinyar tayi wata kuwwa tayi tsalle ta cakumo Zuwaira da kokawa Aiko itama dayar Yarinyar ta iso wurin aguje ta yo kanta da duka, Mamarsu Kam Zaune tayi tana dariya tace

"Ku daki banza Ni nace Kuma ba za'ayi komi ba"

Amrah kam ganin sun rufu sunata kokawa da Zuwaira yasa tayi kitchen aguje ta d'auko muciya Aiko ta Fara dukansu ta ko'ina iya k'arfinta Hafsa tayi tsalle zata kaiwa Zuwaira duka Amrah ta maka Mata muciya a fuska ta yi saurin fasa k'ara tace

" Wyyo Mummy Ta fasa man Ido wayyo ALLAHna ta kasheni"

Zuwaira ko ta d'aga Zulfi ta jefar a k'asa ta tausheta sai dukanta take yi, Amrah ma tabita da muciya sai dukan Zulfi ta ke ga kafafuwa aguje Mamarsu ta rugo don Daman ta d'auka zasu ci galabarsu ne shiyasa ta kyale Amman tana ganin an bugewa Hafsa Ido tasha d'amara ta yo Kan Zuwaira da duka, Ita ko tana ganin haka ta Mik'e tsaye suka Fara dambacewa tsakaninsu.

Hafsa dafe da Ido d'aya Yana tsiyayar jini tana kuruwar neman agaji, Amrah Kam sai dukan Zulfi take ta ko'ina da muciyar Zulfi ma ta yo Kan Amrah cikin zafin nama ta Fara Kai mata naushi a fuska ta k'wace muciyar ta dinga dukanta da ita Amrah Kam ganin bazata iya da ita ba yasa ta fita gidan aguje wajen neman taimako, Aiko sai gata ta dawo ta taradda sun rufu Kan Zuwaira suna ta duka Zulfi da muciyar Mamarsu da wani guntun icce, duk sun farfasa mata jiki da abun dukan mutane suka zo da sauri suka raba fadan.

K'atuwar matar tana ganin yanda jini ke zuba ga Hafsa cikin rud'ewa ta janyota zata fita ta kalli Zuwaira tana maida Numfashi tace da ita

"Sai na kasheku dukanku a gidannan WALLAHI mutukar kuka nakasawa 'yata Ido"

Ta fita rungume da Hafsar Zulfi ta jefar da muciyar ta bi bayansu sai tsinewa su Zuwaira take yi.

Zuwaira ta kalli Amrah dake tsaye tana kukan saboda ganin yanda suka jiwa Mamarta tace

"Zo muje Asibiti Mama a duba ki duk sun ji maki ciyo"

Zuwaira ta shafo goshinta taga jini cikin tsananin bak'in ciki ta yi k'ofar d'akinta tana wara idon inda ta watsar da kudinta amman ko dubu d'aya bata gani ba, cikin takaici ta kalli mutanen da suka yi cincirindo cikin gidan tace

"Ubanwa ya d'auke Mani kud'i ??"

Aiko mutane suka Fara sulalewa wasu Kuma suka tsaya suna ta sa'insa da ita saboda jin haushin laka masu sata da tayi ,yayinda wasu suke ta rantse rantsen su basu bane wasu Kuma suce su dai basu ma ga kud'in ba.

Wasa farin girki🤣

Akafta 🏃‍♀️

D/Auta ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Wannan page naki ne sukutum d'iyar kirki Murjanutu Sa'idu ki dad'e kiyi lasting tawajena👍🏻😛

51

Cikin tsananin tashin hankali Zuwaira ta dafe k'irji tace da Amrah,. "Cikon kud'in hayarmu ne fa da aka maidomuna WALLAHI duk Wanda yasan ya daukesu ya maidosu tun wuri don duk Wanda ya kuskura ya cisu ya ciwa kanshi bala'i don WALLAHI ba zan barshi ya cisu ta dad'i ba"

Ta k'are maganar tare da zubowar wasu hawayen takaici, don ita duk jibgar da tasha bata ji zafinta irin kudinta da aka wawashe ba, Aiko salun alun mutane suka fice suka barta da takaici goma da ashirin.

Amrah ta share hawayenta ta shiga d'akin Zuwairar ta d'auko mata hijabi ta saka mata sanna tace,. "Muje a duba maki ciyukan Mama tun kafin su fara yi maki tsami a jiki"

Zuwaira ta zura talkaminta ta nufi hanyar fita Amrah ta rufo masu d'akunan suka fita, kasancewar akwai wani chemist a unguwar cen suka nufa aka yiwa Zuwaira dressing d'in raunukan da ta samu, aka hado mata da magungunan da zata sha don su rage mata zafin zugi har ma raunin yayi saurin kamewa, suna Kan hanyar dawowa ne sai ga Lantana a firgice saboda taji labarin abunda ya faru, ganin raunukan da Zuwairar taji yasa ta zaro Ido tace

"Kan uban cen yanzu shikenan a haka za'a barsu su ci bulus?"

Zuwaira tayi Yar dariyar k'arfin hali tace

"Ai muma basu ci bulus ba don kuwa Amrah ta fasawa tsagerar yarinyar Ido d'aya kin ko ga muma mun rama"

Tana Kare maganar ta ci gaba da tafiya don ta matsu ta je gida ta kwanta saboda gaba d'aya jikinta ciyo yake, Lantana ta biyo bayanta tana fad'in

"Gaskiya dai wannan Abu bai yi dad'i ba sai kace daman jiraye suke daku? Kuma ace a hakan zaku zauna dasu?"

Amrah tayi saurin fad'in "bar masu gidan zamuyi mukam don ba zamu iya wannan bala'in ba mukam"

Zuwaira ta waigo ta maka mata harara tace

"Ai WALLAHI ba inda zamu je sai dai in sune zasu bar muna gidan, ai in muka yi haka ganin zasu yi kamar tsoronsu muke yi shiyasa zamu bar masu gida"

Cikin jimami Lantana tace,. "Gaskiya fa maganar Yarinyarnan abun dubawa ce don kuwa gara ace kunji tsoron da suje su yi maku wata illar, don fa naji ana labarin cewa matar tace wai sai ta kasheku"

Kafin Zuwaira ta Sami damar mayarwa da Lantana amsa sai ga motar 'yansanda wiwi ta nufo

unguwar, cike da mamaki duk suka bi motar da kallo har ta tsaya k'ofar gidan, sai ga matar biye dasu Kan acab'a ya ajiyeta tana hangosu tace da wani D'ansanda

"Gasu cen"

Aiko ganin yansandan sun nufosu yasa Lantana zankarawa da gudu, Aiko wani D'ansanda ya bita ya damkota tana fad'in

"Ba Dani aka yi fadan ba Nima yanzu na zo"

Amman hakan bai hana a had'a da ita ba don kuwa tare da su Zuwaira aka turata Motar suka tafi,.

Koda suka je aka kaisu wani d'aki aka fara bincikar abunda yasa suka fasawa Yar mutane Ido d'aya? gashi ankaita Asibiti ance dole sai anyi mata aiki saboda gefen gilashin kwayar idon ya fashe, cikin rud'ewa Amrah ta fara kuka wani D'ansanda ya katsa mata tsawa yace

"Yi muna shiru bayani zakuyi kuje ku kawo kud'in aikin idan ba haka ba WALLAHI yanzu mu turaku cell"

Zuwaira tuno azabar da aka bata yasa ta fara kuka tana fad'in

"Oga kalli jikina Nima gaka irin raunin da suka yi mani yanzu haka likita yace gefen Kwakwalwata Yana gaf da tab'uwa Nima biyana za'a yi kenan?"

Wani D'ansanda ya zarowa Zuwaira Ido yace,. "Wai ke ba ke bace kwanakin baya aka kawo muna case dinki ba akan kin canyewa wani kud'i ko ba ke bace?"

Zuwaira ta marairece tace

"Nice amman ban ci kud'inshi ba b'acewa suka yi"

Yace " Ok Da kin kuskura kin sake shigowa hannunmu zaki gane kinyi kuskure don haka ki biya kud'in aikin Yarinya kawai aje ayi mata aiki sauri ake yi"

Zuwaira zata yi magana Amrah ta kalli D'ansandn tace

"Sir zamu bada nawa ne?"

Zuwaira ta maka mata Harara tace

"Ranka ya dad'e ka tausayamani Nima fa dubi yanda suka ji mani rauni haka kawai fa suka rufemu da duka bamu yi masu komi ba"

Katotuwar Matar tace

"K'arya kike yi Munafuka ke kika Fara dukan yarana Sannan 'yarki ta saka muciya ta bugawa Hafsa a ido don haka ki biya kud'in kawai na baro Yarinya a Asibiti Ni kawai ake jira in kawo kud'in"

Zuwaira ta maka mata Harara tace

"Ni da naje chemist aka dubani nawa nace ku bani? Koko don Ni bansan hanyar wajen yansandan bane?"

Wani babban yansandan da tunda aka Fara rigimar baice kanzil ba, don shi kam tunaninshi kacokam yana Kan Amrah da farad d'aya yaji yana bala'in kaunarta, ranshi a had'e ya Mik'e ya fito waje yace da Zuwaira ta biyoshi.

Gabanta ya kire ya fad'i ba shiri duk da daman cen a tsure take don tasa a ranta kwandala bazata bada ba tunda har suka ja aka sace ata kud'i, cikin firgici ta iskeshi inda yake tsaye ta k'ara marairecewa tace,. "Don ALLAH Oga kayi hak'uri WALLAHI bani da kud'in da Zan basu don ma Ni kud'ina har dubu d'ari da ashirin da biyar suka ja aka sace man lokacin da muke fadan"

Mutumin yayi Yar gajeruwar dariya yace

"Waccen Yarinyar 'yarki ce?"

Zuwaira tayi saurin d'aga Kai tace

"Ni na haifeta da cikina kuwa"

Ya gyara tsayinshi yace

"Wani taimako zanyi maku amman Nima sai in zaki taimakeni ki bani auren yarki"

Zuwaira ta zaro Ido tace

"Ranka ya dad'e ai matar aure ce yanzu haka daga gidan Mijinta take ganina ta zo tayi dace da wannan rigimar"

Cikin jimami yace

"Ok ba damuwa yanzu dai tunda nayi niyarr taimaka maku to zaku bada rabin kud'in aikin yarinyar da aka nema zo muje"

Zuwaira ta biyoshi tana fad'in ,. "Ranka ya dad'e a taimaka muna WALLAHI kud'ina aka sace yanzunnan don ko na abunda zamu ci bamu da"

Mutumin ya juyo yace,

"Kuyi hak'uri kawai ku bada kud'in idan ba haka ba WALLAHI yarana zasu rufeku a banza"

Yayi gaba Zuwaira ta bishi da harara a zuciyarta tace

"Ji wata fuskarshi kamar Namijin Saniya wai har yake zancen auren Amrah a hakan zan baka Yar tawa da wannan cin zanzanar a fuska??? Ai ko ni ban iya aurenka ballantana 'yata"

Har suka koma d'akin bata daina aibatashi ba suna shiga Kai tsaye ya kalli matar yace

"Nawa ne kud'in aikin yarinyar?"

Matar ta kalli Zuwaira ta maka mata Harara Sannan tace,. "Dubu Saba'in ne"

Zuwaira ta zaro Ido tace

"WALLAHI ALLAH bazan baki dubu Saba'in ba kaji munafuka"

Lantana ta D'an rik'o hannunta alamar ta sassafta don bayan fitarsu wani D'ansanda daga cikinsu yace

"Shi yama fi son kar ta biya kud'in a kaisu cell a ajiye sai sun lallasu Sannan a fito da su kuma dole sai anbiya kud'in zasu sake su"

Shiyasa daga Lantana har Amrah cikinsu ya duri ruwa musamman Amrah da sai da taji cikinta ya katsa, aiko Zuwaira ta k'wace hannunta tana hararar matar tace

"Sakeni Lantana ba Zan yi shiru in zura ido wannan Muguwar Matar ta cuceni ba WALLAHI"

Wani D'ansanda ya yo kanta kamar zai daketa yace

"Kada kawo muna shirme anan ki bata kud'in kawai taje wurin yarta da kuka nakasa tun kafin ki jawa kanki in yi maki mummunan duka anan wurin"

Zuwaira tayi mukus dole amman idonta basu daina hararar Matar ba, Babban yansandan ya Kara had'e fuska ya kalli Zuwaira yace

"Ki basu rabin kud'in da aka nema"

Zuwaira ta had'iye miyaun da kyar ta marairece zata fara rantsuwa kenan wannan D'ansandan da yake kufule da ita ya ce

"Bada kud'in kawai bama bukatar maganarki"

Amrah ta kalli D'ansandn tace

"Bari inje gida yanzu in kawo maku?"

Lantana tayi zumut tace

"A'a jira Ina dasu a nan na sak'on wata da ta bani"

Ta ciro kud'in ta kindanya dubu talatin da biyar cur! sannan mik'awa Zuwaira, cikin tsananin jin haushin bada su ta mik'awa Ogan ya karb'a, itama Lantana aka ce sai ta bada dubu biyar haka ta zaresu jiki yana rawa ta mika sannan aka sallamesu tare da gargadin kada wani abu ya koma shiga tsakaninsu, suka saka hannu a wata takarda suka fito.

Manage plss

Akafta

D/Auta ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

GODIYATA A GAREKI BATA LISSAFUWA JAR MASOYIYATA RAHMA LADINGO YAR MUTAN NIGER ALLAH ya bar zumunci ni da ke tawajena🤝

PAGE 52

Koda suka dawo gida Lantana bata bar gidan ba har sai da Zuwaira ta biyata kud'inta cas! sannan ta tafi zuciyarta cike da takaicin zuwa wajensu da tayi, don gashi ya jaza mata asarar dubu biyar bata ji ba bata gani ba tana zaman zamanta rabon fitar kud'in yasa ta nufo gidansu da zummar jaje, aranta tace

"Naje jaje da neman jin gulma gashi ni ma yanzu na zama wadda za'a jajantawa, ai WALLAHI wurin Alhaji mai rumbun kud'in zan je in k'ara turoshi Koda zuwan farko ne yayi nasan zan samu fiye da kud'ina da na rasa, ko da cikin ayi auren ni miye nawa in dai zan sami kud'i cen ta matse masu."

Bayan fitar Lantana Amrah ta kalli Mamarta da ke kwance tana jinyar jikinta tace

"Mama Ina da wata shawara"

Zuwaira ta kalleta ta gefen Ido ta b'ata fuska tace

"Don ALLAH in har kinsan abunda zaki fad'a ba zai yi man dad'i ba to don ALLAH ki bar

maganar kawai ban son jinta"

Amrah ta yi narau narau da Ido wata kwalla ta taru a cikin idonta tace

"Kiyi hak'uri Mama daman cewa nayi me zai hana mu koma Zamfara ne? Ni fa WALLAHI hankalina bai kwanta da mutanennan ba, Ina jin tsoron su cutar damu a banza gashi bamu da kowa Wanda zai tsaya muna a garinnan yanzu"

Zuwaira ta Mik'e zaune da k'yar saboda jinkinta da take ko'ina yana mata ciyo ta kalli Amrah tace

"Ba wai bana son komawa garinmu bane ni Ina hangen kada muje cen ne a takuraku don kinsan Mahaifiyata ta dad'e da rasuwa Matar Babana ce kad'ai a gidan gata masifaffiyar gaske ce kuma kinsan yanzu abunda ya faru tsakanina da Asabe bazai tab'a yiyuwa inje gidan Inna Habi in zauna ba". Cewa da Mahaifiyar Asabe da suke Uwa d'aya Uba d'aya da Mahaifiyarta

Amrah ta share hawayenta tace

"Mu tafi kawai Mama ko da ace da sunan ganin gida ne Kin ga sai mu karb'i kud'in hayarmu da muka bada idan mun dawo sai mu nemi wani gidan"

Zuwaira tayi shiru tana nazari sannan tace,. "Matar Babana fa masifaffiya ce ko kad'an tamu bazata zo d'aya ni da ita ba, don akanta ma Babana yace kada in sake zo masa gida a wani ganin gida da na tab'a zuwa shekarun baya lokacin da kasuwa take gara man idan baki manta ba, don ko abunda na kai masa a lokacin fushi yayi ya watso mani abuna yace baya so dole na tattara na kaiwa Inna Habi sannan na baro garin, to Kinga yanzu idan mun je bamu san me zamu taras ba"

Amrah ta share hawayenta da gefen hijabinta tayi shiru tana wasa da Yan yatsunta, saboda maganar da take cin ranta akan ta fad'a tana jin tsoro amman dai dole ta dake cikin fargaba tace,

"Mamah!"

Zuwaira ta d'ago kanta daga kwancen tace

"Ina saurarenki"

Wasu hawaye masu zafi suka gangaro mata cikin sanyin jiki tace,. "Me zai hana ki hak'ura ki barni in koma gidan Yaya Nazir????"

Zuwaira ta maka mata wata k'atuwar harara ta buga tsaki ta nuna mata k'ofa tace,. "Tashi ki fitar man daga d'aki tun kafin ki janyo in sauke fushina akanki"

Amrah ta mik'e cikin rawar jiki ta nufi k'ofar fita tace,. "Don ALLAH kiyi hakuri Mama akwai dalilin da har yasa kika ji nace haka, saboda bana son muyi ta zama cikin wannan hali da muka fara tsintar kanmu a ciki, yanzu fa kina kallo har an fara yi muna gori wurin mutanen da bamu ma sansu ba amman su suna da labarinmu, me kike tsammani a gaba idan har aka ce a haka zamu ci gaba da rayuwa irin wanan marar 'yanci??? A gaskiya ni dai ina son in koma gidan Mijina in kula da tarbiyyar yarana"

A zabure Zuwaira ta mik'e zaune Amrah ta fita da sauri tayi waje tana kuka saboda jin tsoron kada ta daketa, Zuwaira cikin tsananin mamakin da Amrah ta bata tace,.

"Banga laifinki ba don kin watsa man k'asa a ido saboda Namiji ki zab'i ki tozartani a gaban idon duniya, WALLAHI baki da laifi nice mai laifin tun farko da har na shiga cikin sabgarki, ki je ko yau kike son ki koma gidan Nazir Hanya a bud'e take amman kisani duk abunda kika yi mani sai anyi maki don kema ai kin haifa"

Zuwaira ta k'are maganar cikin kuka saboda takaicin da take ji a zuciyarta na abubuwa da yawa, daman cen k'arfin hali ne kawai take yi amman tana bukatar kukan ko don taji sanyi a zuciyarta.

A ranar haka suka kwana daga ita har Amrar zuciya ba dad'i don shi kanshi Abdallah tun da ya fita da safe sai dare ya dawo ya lallaba ya shige d'akinsu ya kwanta, zuciyarshi cike da tsoron haduwarshi da Zuwaira idan safiya ta waye.

Aiko sai gashi tunda sassafe Zuwaira tana baccin gajiya ko lafiya ma bata isheta ba kwana tayi juyi saboda ciyon jiki gashi zuciya ba dad'i.

Sai ga Sallamar Mai gidan a k'ofar gida Abdallah ne ya fito yana amsa masa sallamar bayan sun gaisa ne ya mika masa kud'i yace

"Ka kaiwa Mamarka kace da ita su tattara kayansu su bar gidannan na fasa bata hayar saboda naji labarin abunda suka yi da wad'anda na baiwa hayar gidan, don haka bazan yarda su je su kashe junansu a jaza man bala'i ba haka kawai, don haka yau yau d'innan ku tattara kayanku ku bar gidan tun kafin in zo insa a fito maku da su in baku bi abunda na fad'a ba cikin ruwan sanyi ba"

Yana kare maganar ya wuce fuuu ya bar Abdallah rik'e da kud'i a hannu, cikin b'acin rai ya shigo d'akin Zuwairar ya ajiye mata kud'in a gefen gadonta yace

"Ga kudinki nan inji wanda ya baku haya yace ya fasa mu tattara kayanmu mu bar masa gidanshi don bazai yarda ayi masa kisan kai a gida ba"

Zuwaira ta rik'o hannun Abdallah ta tashi zaune ta Kai kallonta ga kud'in ta yi shiru tana nazari

sannan tace

"Je ka harhad'a kayanka sannan kaje ka samo muna motar da zata kwasar muna kayanmu"

Abdallah ya fita cikin b'acin rai ta bishi da kallo sannan ta mike ta fara had'a kayanta masu muhimmanci tana fito dasu tsakar gidan.

Amrah ta fito da nufin ta shiga kitchen ta dafa masu abun karin safe ne taga duk sun fiffito da kayansu a tsakar gidan, cikin mamaki ta leka d'akinsu Abbati taga duk Abdallah ya fito da kayansu waje, ta dawo da sauri zuwa k'ofar d'akin Zuwairar ta leka ta hangota sai had'a zufa take tana nishi tana banbare katakon gadonta, cikin mamaki ta shigo daga ciki kad'an ta tsaya don har lokacin tsoron abunda Zuwairar zata yi mata take ji, cikin rawar murya tace

"Mama lafiya naga anata had'a kaya?"

Zuwaira tana k'ok'arin dauke katakon ta jingine tace,. "Au wai kina nan baki tafin ba? Ai ni na d'auka tun jiya kin tafin tunda har kin sami damar hakan to zaman me kike yi anan??"

Amrah ta marairece tace

"Kiyi hak'uri don Allah nasan na bata maki bazan sake ba Ina zamu je yanzu nima inje in hado nawa kayan?? "

Zuwaira a gajarce tace da ita,. "Mai gida ya koremu gidanshi wani gidan hayar zamu je mu nema"

Cikin jin dad'in faruwar hakan aranta tace,. "Bari nima inje in hado nawa kayan"

Ta fice cikin farin ciki a zuciyarta saboda daman ita zaman gidan kamar a kaya take jinta, saboda tsoron lafazin matarnan da tace Idan aka nakasa mata idon 'ya sai ta kashesu, kuma tabbas zata iya aiwatar da abunda ta fad'a saboda kwayar idanunta sun nuna hakan.

Zuwaira sai da ta had'a komi nata ta fito dashi tsakar gidan sannan ta yafo hijabinta ta fito ta nufi gidan Lantana, abun mamaki Lantana ta matse fuska tamau kamar bata tab'a saninta ba, cike da mamakinta ta zauna ta kalli Lantanar tace

"Huta da Shan mur unguwar ma zamu bari yanzu saboda maigida ya koremu yace mu bar masa gidanshi yanzunnan"

Lantana ta dafe k'irji tace

"Ina zaku koma to yanzu??"

Zuwaira tace

"Wani gidan hayar zamu je mu kama ya zancen Alhajin ??"

Lantana cikin ganin samu ta ga rashi tace, "Banda ina jin tsoron ku sake jaza mani abunda zanyi asarar kud'i ban ci ban sha ba ai da kun dawo gidannan mun zauna tare don dai Kinga wancen d'akin ya isheki keda 'yarki Abdullahi kuma ko a soron gidan ai zai dinga kwanciyarshi"

Cikin jin dad'in taimakon da Lantana zata yi masu tace,. "Nagode k'awata ALLAH ya bar zaman tare"

Lantana tayi mere tace,. "Ba fa a kyauta zan baku ba Zuwaira jinga za muyi daku sai mu daidaita da ku ku biya"

Zuwaira ta maka mata Harara tace

"Yanzu ke saboda Allah bazaki ji kunyar karbar kud'ina ba???"

Lantana tayi shewa tace,. "Yo in kinji kunya sata kenan amman nikam Wallahi zuruf zan karbe kud'ina in tura aljihu"

Zuwaira ta rik'e baki tace,. "Nawa zan biyaki a shekara??"

Lantana tayi wata yar dariya tace

"Ai tunda ku na gida ne ku bada d'ari da hamsin kawai"

Zuwaira ta maka mata Harara ta yi wani mere tana k'arewa gidan kallo tace,. "A irin wannan tsukakken gidan kike ambatar wad'annan manyan kud'in??"

Lantana ta b'ata fuska tace,. "Idan kinsan cin fuska zaki yi man ki tashi kije ki sami wani don Allah bana son renin hankali akan abunda ke ko rabin rabinshi baki mallaka ba"

Zuwaira ta karkace ta zura hannu a kwagirinta ta zaro kud'i ta lissafa ta mayar da sauran ta mik'awa Lantana kud'in tace

"Ga abunda naji zan iya baki idan har kinji basu yi maki ba to ki bani kud'ina inje in nemi wani gidan saboda gari da yawa....."

Lantana ta fara lissafa kud'in har ta k'are sannan ta ce

"Naga dubu Hamsin yaushe zaki cika sauran to?"

Cikin b'acin rai Zuwaira ta mik'e tsaye tace,. "Sisi ba zan k'ara maki ba idan ba zaki bar man a haka ba ki bani kud'ina in tafi"

Lantana ta yi shiru Sannann tace

"Don dai kina ke ku kwaso kayan an ci sa'a ma d'akin a sharenshi yake"

Zuwaira ta juya zata fita Lantana ta bi bayanta da harara tace,. "Kinyi da mai ramawa in dai nice"

Aiko aka saka baro tun kafin Abdallah ya dawo aka fara jido kayan ana jifgewa har aka k'are, sannan Zuwaira taje ta zo da dillaliya ta siyi kayan d'akin Amrah suka daidaita ta bada fiye da rabin kud'in aka fara jidar mata kayan zuwa gidanta, da nufin sauran kud'in sai daga baya zata bayar sannan suka tattara suka nufi gidan Lantana.

Ba su zauna ba har sai da suka gyara d'akin da zasu zauna a ciki, Abdallah Kam cewa yayi shi kam bazai kwana a soron gidan ba sai dai in Gidan dangin Babanshi zai koma tare da Abbati, Zuwaira tana kiranshi ya kinkimi jakarshi ya tafiyarshi ya barta da sharar k'wallah.

Kwanansu biyu a gidan Lantana Zuwaira ta gano cikin da Amrah take ta b'oye b'oye bata so ta sani, saboda gaba d'aya gidan toilet guda ne ba damar ta b'oye tayi amai idan ya zo mata, dole dai tsakar gidan zata fito tayi shi idan har ya turnukota dole sai ta yi.

Cikin fad'uwar gaba Zuwaira ta bita da kallon tuhuma sannan ta matso inda take ta tsaya tace

"Yanzu sakayyar da zaki yi man kenan AMRAH??"

Amrah ta fara ja da baya tana bata hak'uri amman duk hakan bai hana ta matso wurinta ta falla mata wani shahararren mari ba, bakinta yana kumfa tace

"Yanzu don kina munafuka kinsan kina da ciki shine kika b'oye man?? To Wallahi bud'e kunnuwanki kiji bazan tab'a yafe maki ba matuk'ar kika haife cikinnan don ya zama dole a zubar da cikinnan ko kina so ko ba kya so, in banda tsabar jaraba ma me ya kaiki sakar masa jiki daga zuwanki har ya dirko maki wani sabon cikin?? Bayan ko mirmijewa baki yi daga haifuwar da kika yi ba? Lalle albasa bata yi halin ruwa ba don ni WALLAHI in shekara zanyi da Namiji bazai d'aga man hankali ba balle har in bashi fuskar da zai dirka man ciki alhali Uwata tana hakilon rabani da alakakai, to ai daga ke har shi din WALLAHI baku isa ba kunyi kad'an don kuwa wannan k'addararren cikin sai na zubar dashi a gidannan"

Amrah ta share hawayenta cikin dakiya tace

"WALLAHI bazan tab'a bari a zubar man da ciki ba tunda dai ba shege bane"

Zuwaira ta zaro Ido waje ranta a matuk'ar bace tace

"Yau akan Namiji Ni kike d'agawa murya Amrah???"

Amrah ta janyo hijabinta ta saka zata fita Lantana da ke zaune tana kallonsu ta yi hanzarin Shan gabanta tace

"Ina zaki je Mahaifiyarki tana yi maki magana?? WALLAHI kiji tsoron ALLAH tun kafin hakkinta ya kama ki"

Amrah ta galla mata wata jar harara ta murgud'a mata baki tace

"Idan zaki cire son rai da kwadayin abun duniya to kema ki fito fili ki nuna mata abunda zata aikata ba dai-dai bane, don nasarar da taci a farko ta rabani da yarona da Mijina yanzu kam WALLAHI bazan tab'a lamuntar hakan ba, yanzu zan je in sanar wa da Yaya Nazir don yaja hakkinshi matuk'ar aka zubar masa da ciki"

Tana k'are maganar ta zagaye Lantana zata fita ta sake riketa aiko ta fisge da k'arfin tsiya ta fice, ta kalli Zuwaira cike mamakin Amrah tace

"Ki hanata ta fita fa kar ta je ta b'aro maki aiki"

Zuwaira ranta a b'ace fuskarta a d'aure tamau tace, "WALLAHI bazan hanata ba ki barta taje duk inda zata je ai zata dawo ne ta sameni don wannan tsinannen cikin Naziru ko da Innarshi yake kwana saboda tsabar rashin mutunci to bai isa ya hana Ni in zubar dashi ba"

Tana k'are maganar ta saka hijabinta ta fito gidan kai tsaye chemist ta nufa tace da mai tsaron shagon ya bata maganin zubar da ciki, ya zaro Ido yace

"ciki!?"

Ta k'ara daure fuska tamau tace

"Ciki ko"

Yayi Yar dariya yace

"Bamu da irin maganin anan shagon sai dai ki matsa gaba ko zaki samu"

Zuwaira ta soka hannu a kwagiri ta kirgo dubu goma ta fito da su ta ajiye masa saman katako a gabanshi tace

"Ko da yafi haka d'in ka d'auki sauran kud'in na baka" ..

Yaron ganin kud'in yaji yana ra'ayin bata maganin sai dai yana jin tsoron wani Abu ya biyo baya ya jawowa kanshi jidali, cikin dakiya ya shiga kuryar shagon ya d'auko wani kwayar magani d'aya ya saka a leda ya Mik'a mata yace

"Gashi zan baki amman kisani duk abunda ya biyo baya babu ruwana"

Zuwaira ta karb'a cikin jin dad'i tace

"Bale ma ba abunda zai biyo baya sai alkhairi"

Ta soke maganin kwagirin zata tafi yace da ita,. "To ai ban fad'a maki yanda zakiyi amfani da maganin ba"

Ta dawo tace..

"Ina saurarenka"

Yaron yace

"Matsashi zata yi a cen cikin jikinta da zarar ya narke zai yi gaggawar fito da koma miye a cikin mara Koda ko ya Kai d'a biyar ba d'aya ko biyu ba fit! za su fito duka a lokaci d'aya"

Cikin tsananin jin dad'i tayi masa godiya ta koma gida zuciyarta cike da jin dad'in nasarar da tayi ta samun maganin.

Akafta🤔

D/Auta ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Jinjinar ban girma gareku masoyana kusani a duk inda kike HADIZA D/AUTA tana alfakhari da ku tsakanina da ku son so fisabilillah💋

PAGE 53

AMRAH kam tana fita kai tsaye Napep ta tara ta sanar dashi sunan unguwarsu Nazir, suna tafe tana kuka har k'ofar gidan sai dai gabanta ya kire ya fad'i saboda hango k'ofar gate d'in gidan da tayi da k'aton kwado, cikin fargabar abunda take tunani ta fito ta nufi k'ofar gidan ta k'ara tabbatar da abunda take zargi waton basu nan masu gidan, ta koma Napep d'in cikin tsananin takaici tace da shi su tafi unguwarsu Jamila Kanwar Nazir domin taji ina zata samu Nazir d'in, gashi ita ko wayarta ma tana hannunshi tun a kotu da ya shaka mata abunda ya somar da ita, ya d'auketa ya saka aljihu tun lokacin bata sake ganinta ba kuma shima a lokacin tsoron Zuwaira ta kirata ta hure mata kunne yasa bai bata ba ya kaita ya b'oye.

Kai tsaye suka nufi unguwarsu Jamila itama abun takaici bata sameta a gidan ba, sai wata tsohuwa da ta iske da yarinyar Jamilar tana yi mata wasa, cike da takaicin rashin isketa tace da tsohuwar don Allah ta bata takarda da biro zata bar mata sak'o, tsohuwar ta kalli Amrah tace

"Nikam Yarinya ina naga wata takarda bale biro? Da dai zaki bar sak'on a baki da na fad'a mata idan sun dawo don sun tafi gaisuwa dangin Maigidan a wani k'auye"

Amrah ta fito tace da Mai Napep d'in ya ara mata biro ko pencil in yana dashi, ya lalaba aljihunshi ya fiddo wani pencil ya bata yace

"Ga dai wannan shima a hannun wani kanena na karb'eshi"

Amrah ta karba cike da jin dad'i ta nufi wani kwali ta yago ta tsugunna ta yi rubutu a jiki ta bashi pencil d'in ta koma cikin gidan ta mik'awa tsohuwar tace

"Idan ta zo ki bata kice inji Amrah na zo bata nan"

Tsohuwar ta karb'a ta mik'awa yarinyar tace "je ki kaiwa Mamarki a d'aki"

Amrah ta yi godiya ta fice ta sake shiga Napep d'in tace su tafi gidan Aunty Asabe, aiko tana sanar dashi sunan unguwar ya cilla Napep dinshi kan titi suka nufi unguwar, cike da jin dad'i ta fito ta nufi cikin Gate d'in saboda hango gidan da tayi a bud'e.

Cikin farin ciki ta shiga gidan aiko sai gashi ta hango Aunty cikin kuka ta nufeta ta fad'a jikinta, cike da fad'uwa gaba ta d'agota tace

"Lafiya Amrah? Me ya faru kuma?"

Amrah ta yi jarumtar share hawayenta tace

"Tare muke da Napep Aunty in kina da kud'in bani in kai masa ko sisi babu a hannuna"

Aunty tace da ita "to zauna bari in d'auko maki kud'in"

Amrah ta kasa zama tace, "Bari in Kai masa kud'in dai kafin in zauna don kar yaga an tsaidashi, saboda munsha yawo dashi sosai"

Aunty ta shiga ta d'auko kud'in ta mika mata ta fita da sauri ta kai masa yabata canji ta dawo ta mik'awa Auntyn sannan ta zauna tana wasa da yan yatsunta hawaye suna zubo mata a fuska tana sharewa tana shan majina, Aunty ta kalleta tace

"Kinsani a gaba kina Kuka Amrah meke faruwa ne??"

Amrah ta share hawayenta cikin muryar kuka tace,. "Ciki ne da Ni Aunty kuma Mama tace sai an zubar"

Aunty ta zaro Ido tare da dafe k'irji tace,. "Ciki ?? Ikon Allah kice dai ke zuri'ar Nazir a jikinki take? to ke meye na tada hankalinki?? Ki ma kwantar da hankalinki don ma wannan abun da zata yi ba mai yiyuwa bane, don kuwa ya zama dole ki sanar da Nazir kina da cikin ko don ya kare cikinshi ya hana Aunty Zuwaira cika wannan bakin nufin nata, don haka ki kirashi a waya yanzunnan ki sanar dashi kawai yafi"

Amrah ta fashe da kuka tace

"Bani da waya a hannuna yanzu Aunty amman yanzu haka daga gidanshi na fito ba kowa a gidan, naje gidan Kanwarshi Jamila itama ta fita na bar mata sak'o dai a bata ta sanar dashi ina da ciki"

Aunty tace ,. "Masha ALLAHU kinyi abunda ya dace amman ya zama wajibi ki je da kafafunki a Zamfara ki fadowa Baba Nuhu halin da ake ciki, don shi kad'ai ne zai hana Zuwaira aiwatar da wannan danyen aikin"

AMRAH ta zaro Ido tace,. "Aunty baki ganin kamar Mama zata ga laifina idan na had'ata da Mahaifinta??"

Aunty ta b'ata fuska tace,. "Koda zata ga laifinki to gara ta gani da dai ace ki zura ido ta zubar maki da ciki akan wani dalilinta na banza, yanzu ki tashi ba sai anjima ba zan baki kud'in mota ki je ki fado masa da kanki don bama zan je ba don kada taga Ni na zuga ki, ta zo ta sake ci man zarafi don wannan karon ba zan kyaleta ba gaskiya"

Aunty cikin takaicin Yar uwar tata ta shiga d'aki ta d'aukowa AMRAH kud'in ta mika mata tace "karb'i ki tafi amman bari in zubo maki abinci ki ci kafin ki tafi"

Amrah ta karb'a jiki a sanyaye tace,. "Aunty ki bar Abincin kawai Ni zan tafi don kada dare Yayi mani a hanya sai dai ina ganin Ni bazan gane gidan ba sosai"

Aunty ta yi mata bayani dalla dalla har ta gane sannan ta rakota har bakin titi ta hau Napep suka nufi Tasha inda kai tsaye ta shiga motar Zamfara, sai tunani take yi a ranta

"Anya Mama bazata ga na munafunceta ba?"

Wata Zuciyar tace

"Gara hakan da ki je ta Kai ki ta halako a banza watak'ila ma garin zubar da cikin ki je ki mutu ko kuma a jaza maki wata matsalar mahaifarki ta lalace ki zo ki kasa samun wata haifuwar a gaba, da ko shikenan ta kassara rayuwarki"

Haka tayi ta tunanin zuci har suka isa Gusau inda kai tsaye ta shiga motar Kaura-Namoda, zuciyarta cike da fargaba da tsoro har suka isa garin.

Mai Napep yana sauketa a k'ofar gidan Kakan nata taji gabanta ya kire ya fad'i saboda tsoron abunda zata je ta ta taras, don labarin da Mamarta ta bata na masifaffiyar Matar Kakan nata yasa ta jin tsoron shiga gidan, don ita bata yi wayon saninta ba don ba wani zuwa Zuwaira ta ke yi garin ba balle har su ta zo dasu su san danginta sosai ba, cikin dar dar ta kutsa kanta cikin gidan da guntuwar sallamarta, sai gashi ta ji an amsa a cikin wani d'aki dake fuskantar Wanda ya shigo gidan, kai tsaye ta isa k'ofar d'akin ta sake yin wata sallamar, sai gashi ko tsohon ya sake amsawa daga cikin d'akin ya bada umurnin ta shigo.

Ta cire talkamanta ta shige ciki bakinta d'auke da wata sabuwar sallamar ta Sami gefen shi ta zauna ta tankwashe kafafuwa ta gaidashi sannan ta sunnen Kai tana wasa da wani dan Kare da ta d'auka, Dittijon tsohon ya kalleta da kyau duk da shekaru sun ja amman kar yake saboda dan jikin fillani da yake dashi, ya kura mata kallo yace

"Ina Uwarki? ko ke kad'ai kika zo ne??"

Amrah tayi saurin d'ago Kai ta kalleshi cike da mamakin saurin ganota da yayi, tayi dan Murmushi tace

"Tana gida amman ya aka yi ka ganoni?"

Tsohon yayi Yar gajeruwar dariya yace, "ai ko cikin duhu mutum yasan ta inda zai zura abinci cikin bakinshi, don haka kamar yanda hannu yake gano Baki a cikin duhu haka Ni ma nake gane zuri'ata duk inda na ganta a fad'in duniya"

Amrah ta yi Yar dariya tace,. "Allah ya bamu ya taku muma idan mun kai shekarunku, ina matar gidan ne naji gidan shiru??"

Dattijon ya yi Yar dariya shima yace,. "Tana ciki yanzu ta fita d'akin bari in kirata"

Amrah gabanta ya fad'i tace,. "A'a bari in je da kaina in gayar da ita itama"

Har ta tashi yace da ita,. "Dawo ki zauna fad'a man me ya kawo ki wurina?? don nasan banza bazata sa zomo ya je kasuwa ba, don fuskarki ta nuna damuwar da zuciyarki ta kunshe da ita"

Amrah ta dawo cikin sanyin jiki tuno abunda ya kawota yasa hawaye suka zubo mata, ta saka hannunta ta share Sannan ta ja majina tace

"Mama ce ta ke so ta zubar man da ciki bayan ta raba Ni da Mijina da Jaririn yarona"

Dattijon nan take b'acin Rai ya bayyana akan fuskarshi yace,

"Yi man bayani dalla dallah yanda zan gane ki saki jikinki da kyau kin zo inda za'a share maki hawayenki in dai akan matsalar Zuwaira ne"

Amrah ta gyara zamanta ta fara bashi labarin duk abunda ya faru tun daga zancen aurenta da Salis har zuwa yanzu da Zuwaira take son zubar da cikin Nazir tana kuka ta kare sanar dashi, tsoho tun yana gincire har ya Kai ya zaune ba shiri cikin tsananin b'acin rai ya share hawayen tausayin Amrah da su suka cika masa idanuwa, ranshi a b'ace ya mike ya fita minti sha biyar a tsakani sai gashi ya dawo tare da wata Mata Sannan ya zauna, itama tana kallon Amrah cike da tausayi ta zauna ta fara lallashinta, cikin matsananciyar damuwa ya sauke ajiyar zuciya yace,

"Kiyi hak'uri Amrahtu insha ALLAHu daga yanzu wannan matsalar ta wuce Ni zan nemo Mijinki da kaina in bashi hak'uri akan abunda aka yi masa ki koma gidan Mijinki ki zauna, ita kuma ki barni da ita gobe tunda safe zan tafi har katsinar in nuna mata cewa ko gaba da gabanta"

Matar da ke rungume da Amrah tana share mata hawayen da take ta yi tace,. "A'a Maigida ka rabu da Zuwaira ka dai sa a nemo maka Mijin Yarinyar ka mayar masa da Matarshi kawai"

Dattijon yayi shiru sannan yace

"Na gaji da matsalar Zuwaira Dije ya zama dole in nuna mata kuskuren da ta aikata, don rashin Imani irin nata ace tayi yajin k'ujen raba Yarinya da Mijinta Kuma duk abun bai isa ba har sai da ta rabata da yaronta da ta haifa ko wata biyu bai yi duniya ba?haba abun yayi yawa sannan yanzu tace wai zata zubar da ciki sai kace wanda aka yo a titi ba cikin Sunnah ba? To WALLAHI wannan karon sai na nunawa Zuwaira cewa ba itace ta haifi kanta ba Haifuwarta aka yi, ALLAH ya jikanki Meramu da har bakayi tsawon ran ganin wannan rashin mutuncin na Zuwaira ba"

Matar da ya kira Dije ta mikar da Amrah da ke ta kuka suka fito d'akin zuwa cikin gidan, Kai tsaye d'akinta ta kaita ta zaunar da ita akan gadon tace

"Zauna in kawo maki abinci kici sai kije kiyi wanka ki yi sallah"

Amrah ta kalleta har zata fita cikin shakakkiyar muryarta da tasha kuka tace

"Bari in fara yin sallahr don bana jin yunwa"

Matar ta mika mata buta cike da ruwa ta nuna mata bayi Sannan ta koma d'akin ta shinfida mata tabarma da carpet a kai ta fito ta nufi d'akin dattijon tsohon.

Bata yi mamakin ganin halin da ta taraddashi ba domin kuwa kuka ta iske yana yi kashirbin na tausayin jikanyarshi Amrah saboda halin da ta tsinci kanta a ciki kuma duk ta sanadiyyar bak'ar Uwa da ALLAH ya bata.

Matar ta zauna cikin sanyin jiki tace

"Don ALLAH kayi hak'uri Malam wannan kukan ba shine mafita ba mafita kawai ka sa a nemo Mijinta ka damka masa ita da hannunshi shikenan anyi maganin matsalar, don in kace ka biye halin Zuwaira sai ta fama maka ciyonka ya tashi ta samu shiga Uku, don ALLAH na tuba ai ko ni da ban haifeta ba ai nasan halinta ballantana kai da ka haifeta da cikinka"

Dattijon ya share hawayenshi yace

"Ni Dije ba komi Nike tunani ba irin halin da yarinyar nan ta shiga da kurciyarta, shin ita Zuwaira ta manta cewa muma irin haka tayi muna lokacin aurenta? K'iri kiri ta ki Auren Sahabi ta fitittike ta ce bata sonshi duk da yake d'anuwanta ta nuna tafi son bare a kanshi, Kuma a hakan muka bata wanda take so d'in ba tare da da mun rabata da shi ba, aka zo ya rasu tun da kurciyarta maimakon ta dawo gida ta nemi yafiyarmu amman bata yi ba, don tunda ta yi aure bata sake tako ma gidannan ba sai da taji Mahaifiyarta ta kwanta ciyon ajali, sannan ta zo ta ganmu ta koma tun daga lokacin bata dawo ba sai da sak'on mutuwar Meramu ya risketa sannan ta zo tana yi muna kukan munafucci, don Mijinta kanshi yayi zuwa yafi uku kafin ya rasu amman ita tunda ta zo gaisuwar Uwar bata dawo ba har sai da ta kwashe shekarru sannan ta zo kuma ta nuna zata ci zarafinki na koreta, to tun daga lokacin Kuma yau za'ayi shekara uku rabonmu da ita, mu bamu takurata ba amman wai ita ta saka yarta a gaba da masiba kala kala karamar Yarinya irin wannan"

Dijen tayi ta bashi baki tana tausarshi har ta samu ya sauko Sannan ya d'auki wayarshi ya kira Babban danshi Wanda suka fito ciki d'aya da Zuwaira yace ya zo yana nemansu duka ya tattaro sauran Yan uwanshi.

Dije ta mike tace

"Bari in baiwa yarinyar nan Abinci in dawo"

Ta fita ta je ta Kai wa Amrah tuwon dawa da miyar danyen yaud'i taji manshanu, aiko Amrah ganin mutuminta yasa ta washe baki ta saki jiki ta ci abunta har ta koshi sannan ta fito da kwanon Dije tana tsarguwarta akan cewa

"Shikenan tunda kin iya cin tuwon gobe sai ki surfa muna dawar ki tuka muna tuwon"

Amrah tayi dariya tace

"Ai har da fura ma duk sai na yi maku kusha ke da Mijinki har sai kunnuwanku sunyi motsi saboda zakin hannuna"

Suna cikin barkwancin ne suka jiyo Sallamar Yan uwan haifuwar Zuwaira maza da mata na

d'akinsu da na Dijen suna shigowa d'aya bayan d'aya.

Don wasu da yawa ma Amrah ta sansu lokacin aurenta na farko da suka zo, mazan dai ne ba duka tasani ba sai dai kamar da suke yi da juna don kusan dukansu Kama da Baba Nuhu suke yi shiyasa kamarsu ta zo d'aya da juna, don ko ita kanta Amrah kama da su take yi saboda gaba d'aya kamar Zuwaira ce ta d'auke sai Karin farin da ta fita wanda sai yanzu ta gano ta d'auko farin ne ga Baba Nuhu don har yanzu farin bafillace ne tas! Duk da tsufa ya fara dusashe farin.

Amrah cike da jin dad'in ganin yanda suke ta faram faram da ita ne yasa ta saki jikinta da su kamar daman cen ta saba dasu, bayan sun gaisa ne duka suka tattara zuwa d'akin Baba Nuhun, kasancewar dare yayi yasa bai b'ata lokaci ba yace da Amrah ta fad'a masu abunda ta sanar dashi, aiko fillah fillah tayi masu bayanin komi da ya faru har irin dawainiyar da Nazir yayi dasu a baya, dukansu jikinsu yayi sanyi da jin labarin cikin b'acin rai Babban wansu duka ya yi gyaran murya yace

"Baba Ni a ganina a nemo mijin yarinyar a mayar da ita gidan Mijinta, amman kafin Nan sai mun tuntubi dangin Baban Yarinyar don muji ta bakinsu"

 Gaba d'aya duka suka yi amanna da shawarar Yaya Harun babban wan nasu, sannan wani dan matashi daga cikinsu yace, "To ita Aunty Zuwairar wani mataki zaa d'aukar mata?"

Baba Nuhu yace

"Ku barni da ita Ni zan yi maganin matsalarta don ko hakkin Yarinyar Nan kawai aka barta dashi ya isheta darasi a rayuwa"

Haka dai kowa yayi ta tattauna abunda ya dace, har suka tsayu akan gobe mutum biyu zasu je Katsinar a binciki abunda yake faruwa wajen dangin Babansu Amrah sannan dukansu suka yi sallama da juna kowa ya nufi gidanshi.

Akafta🥴

D/Auta ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA
Wattpad Princess Dija 246's

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Jinjina a gareki malatyn Wattpad 😹😹😹Ameera Madobi uom Aslam barkarki da k'ok'ari ta wajena👍🏻 ALLAH ya bar zumunci🤝🏻

PAGE 54

Tunda sassafe yayan Zuwaira wanda suke Kira da suna Yaya Harun ya iso gidan tare da wani k'aninshi dan d'akin Inna Dije mai suna Mustapha, suka yi sallama da su Baba Nuhu dangane da tafiyar da za su yi ya basu sak'on su je gidan Zuwaira su ce ta zo yana nemanta, Amrah kam zuciyarta sai bugawa take yi saboda tsoron abunda zai je ya dawo, don tasan Mahaifiyarta sarai da abunda zata iya yi mata idan har ta damk'eta matuk'ar ta gano itace ta kawo k'ararta, sai dai Kuma Dije ta yi ta tausarta tana nuna mata ba wani laifi da tayi hakan da tayi shine dai dai don matuk'ar ba'a yiwa abun tufkar hanci ba ba'a san iya inda abun zai tsaya ba, ta lurar da ita ta kwantar da hankalinta ba abunda Zuwaira ta isa ta yi mata in dai tana gaban Baba Nuhu, amman duk da hakan zuciyarta ta ki natsuwa da hakan.

****

Tun k'arfe takwas suka bar garin kasancewar daga KAURA ba wani nisan zango bane zuwa Katsina, shiyasa koda k'arfe goma tayi masu suna cikin garin kai tsaye gidansu dangin Babansu Amrah suka nufa, Wanda ya kasance big house na familynsu duka sai 'yan d'aid'aikun da suke zama a wasu wuraren daban.

Anyi masu tarba mai kyau sosai cikin mutuntawa da karrama juna kamar daman cen su 'yan'uwan juna ne, bayan komi ya lafa ne suka fara aiwatar da abunda ya kawosu, inda Kai tsaye yaya Harun ya fara tambayar ba'asin abunda ya ke faruwa,cikin natsuwa babban wan Babansu Amrah ya fayyace masu komi da suka sani ya faru tun daga lokacin da Baban Jamilu

Abokin Nazir ya zo akan zancen aurenshi da Amrah har zuwa wannan lokacin da ake ciki da Zuwaira ta kai kud'i aka raba auren, da matakin da suka d'auka saboda jin haushin Sakin da Amrah ta nema a gaban kowa a kotu duk ta ji gaskiya a bakin mutane dan'uwansu Baba Mamman, wanda a sanadiyyar jin haushin hakan ne suka ce sun zare hannunsu akan zancen Auren Amrah da Nazir tunda har ta goyi bayan Zuwaira aka raba aurenta da shi.

Yaya Harun ya sauke ajiyar zuciya Mai k'arfi ya fara basu hak'uri akan duk b'ata masun da aka yi, sunji dad'in halin dattakonsu Yaya Harun suka nuna ba komi komi ya wuce, cikin jin dad'i Baba Harun yace

"Idan har ba zaku ga munyi maku shishigi ba to muna bukatar a mayar da Amrah d'akin Mijinta, saboda har yanzu tana cikin idda tinda Koda ya saketa da cikinshi a jikinta, idan ba damuwa muna son ku rakamu mu had'u da ku muje gidansu yaron mu basu hakuri Kuma mu rok'eshi akan yayi hak'uri ya maida Matarshi d'akinta"

Dukansu suka yi amanna da hakan kuma suka ji dad'in wannan shawara da ya kawo masu, a tare suka mik'e suka nufi Unguwarsu Nazir sai dai ko da suka je sun taradda gidan nashi a dantse da kwad'o wanda alamu duk sun nuna basa garin saboda k'ura da suka hango a harabar gidan sosai da suka leka, cike da takaicin rashin samunshi da basu yi ba Wan Baban Amrah ya ce da su su zo su tafi gidansu Baban Jamilu wanda shine a yanzu yake kallo a matsayin Uba suka d'unguma dukansu suka nufi gidan nashi.

Sai dai shima ko da suka je d'in sun taradda baya nan yana Kasuwa sai dai sun karb'i numbarshi sun kirashi yace da su su jirashi gashi nan zuwa, ya bada umurni aka bud'e masu sittroom d'inshi suka zazzauna zaman jiran zuwan nashi.

Aiko minti Sha biyar a tsakani sai gashi ya iso gidan da fara'arshi ya tarbesu duk da bai wayi su Yaya Harun d'in ba, amman haka suka gaggaisa cikin sakin fuska da mutunta juna sannan Wan Baban Amrah ya fara yi masa bayanin abunda ya kawosu wajenshi.

Cikin tsantsar farin ciki yace,. "Alhmdllh naji dad'in jin wannan maganar Kuma nayi farin ciki sai dai Kuma Nazir baya garinnan yanzu haka an turashi Aiki a garin Gombe, kusan satinsu Uku acen tare da Matarshi da Mahaifiyarshi da d'anshi yaron wajen ita Amrah'r"

Cikin jin dad'in tayashi murnar samun aikin da yayi ne suka yi ta yi masa fatan alkhairi, sannan Baban Jamilu yace

"Amman dai duk da hakan ba wata matsala ba ce bari in kirashi yanzu in sanar dashi abunda yake faruwa, don na tabbata idan har ya ji to ba k'aramin farin ciki zai yi ba kar ki Sha mamaki idan aka ce gobe gobennan zaku ganshi a garinnan ya zo don ba k'aramin so yake yiwa Yarinyar ba"

Aiko kira d'aya biyu har ta tsintse amman ba'a sameshi ba cike da takaicin rashin samunsan da

bai yi ba yace dasu,

"Kada ku damu ko bayan kun tafi ne zan yi ta gwada kirannashi insha ALLAHu zan sanar dashi komi kuma Ina da tabbacin zai zo d'in kamar yanda na fad'a"

Wan Baban Amrah yace,. "Yawwa mun gode da k'ok'arinka idan har ya zo Amrah'r tana Zamfara gidan Mahaifin Mamarta don wad'annan ma daga cen suke asali ma sune ma suka zo muna zancen"

Baban Jamilu ya ce "Allah ya biyasu ya saka masu da Alkhairi kuma ya sa mu dace gaba dayanmu Kuma ya tabbatar muna da alkhairi dukanmu"

Dukansu suka ce "Ameen" Sannan Yaya Harun ya karb'i numbar Baban Jamilu akan zai kirashi ya ji duk abunda aka Kai karshe idan har an Sami wayar Nazir d'in, sannan shima ya karb'i numbar Nazir suka yi sallama da juna suka fito gidan suka yi sallama da juna suka rabu cikin mutunci da mutunta junansu.

Yaya Harun da k'anenshi Mustapha suka nufi Unguwarsu Zuwaira, sai dai gidanta na da suka nufa suka tambayi inda ta koma aka nuna masu gidan Lantana.

Suna zuwa k'ofar gidan su ka aika wani yaro cikin gidan akan ya kira masu Zuwairar, sai gata ta fito da jajayen idonta na kukan rashin ganin Amrah da bata yi ba tun jiya ta sha yawon nemanta gida gida, cikin tashin hankali ta ke har lokacin shiyasa da ta ji ana nemanta ta fito da sauri, don tsammaninta ko zancen Amrahr ne aka zo yi mata, a rude ta fito gidan tana wara idonta aiko sai gashi ta yi Ido biyu da 'yan'uwan nata, tayi saurin dafe k'irji saboda bugawar da zuciyarta ta yi ba shiri, bakinta Yana rawa ta k'araso wajensu fuskarta cike da kuka tace,

"Yaya Harun Mustapha kuma kunji b'atan Amrah ko?"

Ta k'are maganar cikin wani sabon kuka, dukansu suka basar da zance nata kamar ma basu ji me ta fad'a ba saboda haushinta da suke ji, Yaya Harun ya yi mata wani kallon reni yace

"Baba ke nemanki idan kinsan zaki b'ata Muna lokaci mu yi gaba ki biyomu daga baya"
.
Cikin sabon fad'uwar gaba ta zaro Ido tace

"Lafiya???"

Harun ya shige Motarshi yace,. "Idan kin tafi zaki ji daga bakinshi zaki zo mu tafi ko mu wuce?"

Zuwaira cikin kid'imewa ta juya tace

"Bari inyi sallama da mutane to kar su ji ni shiru su zaci ko ba Lafiya ba"

Sannan ta shige sai gata ta fito da 'yan kayanta a wata jaka Lantana a bayanta tana yi mata ALLAH ya tsare hanya, ganinsu Harun yasa Lantana ta fara gaidasu saboda kamar da taga suna yi da Zuwaira sosai hakan yasa ta gano cewa 'yan uwanta ne na jini.

Zuwaira ta shige baya da 'yar Jakar kayanta Lantana tana d'ago mata hannu har suka bar unguwar suka mik'i hanyar zuwa KAURA.

Zuciyarta cike da zullumin abunda yasa Baba Nuhu yake nemanta gashi Kuma su bata ga fuska a wajensu ba balle ta tambaya taji mafarin kiran.

Sannun a hankali har suka isa garin inda ta k'ara tsurewa saboda fad'uwar da gabanta yake k'irjinta sai matsanancin bugawa ya ke da sauri da sauri har suka isa k'ofar gidan ta kasa natsuwar zuciya, kamar wadda kwai ya fashewa a ciki haka ta fito cikin sanyin jiki ta ja 'yar Jakarta tayi cikin gidan.

Cikin fad'uwar gaba ta yi sallama aiko sai gata da datse guntuwar sallamarta saboda hango Mahaifinta da tayi a kwance rumfar bakin k'ofar d'akinshi, cikin dakiya ta nufoshi ta tsugunna ta fara gaidashi, shikam ko kallo bata isheshi ba ita ko ta nace sai gaidashin take yi har sai da ya juyo ya maka mata wani mugun kallo wanda ya sakata tsurewa cikin tsoro taSha jinin jikinta, ya kalli su Yaya Harun yace

"Sannunku da zuwa ya Hanya? dafatar kun dawo lafiya? Allah ya hutar da gajiya ya baku ladar zumunci"

Duk suka ce "Ameen"

Sannan ya kalli Mustapha yace,. "Tafi Kira man 'yar taka"

Mustapha y mik'e cikin sauri ya nufi k'ofar d'akin Inn Dijen ya Kira Amrah, cikin tsananin faduwar gaba ta biyoshi, saboda tunda ta ji muryar Mamarta tasha jinin jikinta tana rab'e rab'en ganin Zuwaira ta yi gefen Baba Nuhu ta rakub'e taki bari ma su had'a Ido da Zuwairar.

Zuwaira kam tunda ta hangota ta zaro Ido waje zuciyarta cike da bakin cikin abunda tayi mata, aranta tace

"waton Ni ina cen ina kukan rashin ganinki ke kina nan kin zo hadani da Mahaifina da Yan uwana"

Ta k'are maganar zucin tana wulla mata wata k'atuwar harara zuciyarta sai hasaso mata irin dukan da zata yi mata take yi.

Baba Nuhu ya tashi zaune ya kalli Zuwaira cikin tsananin b'acin rai ya ce,. "Naji rashin Imanin

da kika yi Zuwaira Anya ko kina son ki mutu Annabin Rahama ya ceceki kuwa? Yanzu a ce ki raba yarki da Mijinta sannan ki yi k'arfin halin rabata da D'an jinjirin yaronta daga nononshi, sannan kuma yanzu ki zo kice shima cikin da ta samu za ki zubar to ko shege ne kika zubar a tunaninki Allah ba zai kamaki da laifin ba halan? Ballantana dan sunna WALLAHI Zuwaira ki fita idona in rufe tun kafin in yi maki tofin alatsine, don haka ki bud'e kunnuwanki da kyau kiji Yarinya dai za mu maidata gidan Mijinta Kuma ko da wasa kika taka kafarki gidan da wata muguwar manufa Allah ya isa ban yafe maki ba"

Zuwaira ta mike tsaye tana nuna AMRAH tace,. "To shikenan gurinki ya nufa anyi maki abunda kike so kin hadani da Mahaifina kinji dad'i amman kisani ni ma daga yau ki manta da cewa kina da uwa ki d'auka cewa ma ta mutu don ko Ni da ke har abada, ko mutuwa nayi ban so ki zo kan gawata na barwa duniya ke tunda har akan Namiji kika zab'i ki watsa man k'asa a ido"

Tana k'are maganar ta juya cikin fushi da nufin ta bar gidan Baba Nuhu cikin zafin nama ya jawo k'atuwar bulalarshi da ke b'oye a jikinshi sai kawai ta ji saukar duka a bayanta, ba shiri ta zabura ya sake sauke mata wani dukan ta yi k'ofar Inna Dije aguje ya bita yana ta dukanta tana ihu har sai da ta lallasu Sannan Inna Dije ta rik'e bulalar tana bashi hak'uri, cikin tsananin fushi ya nunata da hannu yace

"Ke yanzu har kina da bakin da zaki ce wai yarki ta gujeki akan Namiji? Ke duk kin manta irin abunda kika yi muna akan Mahaifinta ko? K'iri k'iri Dan uwanki yana sonki kika rufe idonki kika ki bin umurninmu kika bi zabin ranki, sai yanzu ki zo ki ce itama yarki ba zata bi Wanda take so ba? Ai ke ma kinsan Wannan k'arya ce kike yi don kuwa wajibi ne ta yi maki abunda kika yi muna muma, Kuma WALLAHI ko kallon banza naji kin sake yi mata sai na ci maki mutunci a duk inda kike"

Ya wuce fuu zai shiga d'akinshi ya kalli Amrah da ke rakub'e jikin gini tana ta kuka gwanin ban tausayi yace

"Sai kin jajirce ko da zaki k'waci wuyan hannunki ga waccen mahaukaciyar Uwar taki,don ita Sam Sam bata san miye duniya balle tasan yanda ake zama cikinta, Mijinki kuma da ta zo zai tafi da ke idan yaso ta dad'e bata had'iye zuciya ta mutu ba"

Yana K'are maganar yayi d'akinshi su Yaya Harun da Mustapha suka bi shi suna bashi hak'uri, har suka samu ya sauko sannan suka sanar dashi duk abunda aka yi, cikin jin dad'in maganarsu yace da Harun ya je yayi ta gwada kiran Nazir d'in har ya samu duk yanda suka yi ya zo ya sanar dashi.

Sannan suka yi sallama suka fito Yaya Harun ya kalli Amrah da ke rakub'e ya ce ta zo, ta jawo kafafunta ta iso wurinshi ta dan rankwafa ta fara gaidashi cikin kuka, cike da tausayinta yace

"Kiyi hak'uri kinji insha ALLAHu zaki koma gidan Mijinki ki rungumi yaronki ki kwantar da

hankalinki"

Mustapha ya kalli Harun yace

"Yaya ina son ta biyoni muje gidana don ina jin tsoron Aunty Zuwaira ta daketa don kasan ba hak'uri ne da ita ba,don wannan kukan da ka ji tana yi da wuya idan bata fanshe akanta ba kuma ka ga wani sabon jidali ne zata jawo gashi Baba ba shiru zai yi ba ta je ta tada masa ci yo a banza"

Cikin gamsuwa da zancenshi yace

"To ka sanar da shi to kafin ku tafi..."

Sai ga Zuwaira ta fito sabe da Jakarta ta yi hanyar fita ba tare da ko kallonsu ta yi ba

Amrah ta kallesu hawaye suna zuba tace,. "Bari inje in bata hakuri tunda Ni ce na ja aka daketa"

Yaya Harun yace

"Ki kyaleta ita da kanta zata nemeki watarana idan ta gano gaskiya"

Amrah tana kallonsu kuka yana zuba akan fuskarshi ta bi bayanta aguje tana kiran sunanta.

Akafta🤣

Princess Dija D/Auta ce✍🏻
🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

WHATTPAD PRINCESSDIJA246's

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

MY FAN'S INA YINKU A DUK INDA KUKE ALKHAIRIN ALLAH YA KAI MA KU A KO'INA KU KE KUSANI HADIZA IBRAHIM D/AUTA TANA GODIYA DA KAUNAR DA KUKE NUNA MATA DUKANKU I LOVE YOU ALL💋

55

Amrah ta biyota tana kuka tana fad'in,. "Don Allah Mama kiyi hak'uri banda wani zab'i ne shiyasa har na yi haka amman duk da haka WALLAHI banji dad'in abunda ya faru ba Don Allah ki yafe man"

Ta k'are maganar cikin kuka gwanin ban tausayi ganin Zuwairar ta yi banza da ita sai tafiyarta take yi yasa, ta yi saurin cimmata ta rik'e mata kafafu ta durk'ushe tana kuka tana rokonta akan ta yafe mata, aiko Zuwaira ta ajiye Jakarta ta rufe Amrah da duka har da su shuri da k'afa, ganin su Yaya Harun sun fito ne ta zaci Baba Nuhu ne shi yasa ta kinkimi Jakarta ta fita da saurinta ko waige bata sake yi ba, aiko sai ga Baba Nuhun ya fito saboda Kukan Amrah da ya jiyo, sai dai kasancewar bai ga Zuwairar a gurin ba yasa ya dan rage zafin da ya debo, ya kalli Yay Harun yace

"Ina ita shashar Uwar tata? Ai na zaci itace ta daketa"

Yaya Harun ya gayyato murmushin kore damuwa akan fuskarshi yace,. "A'a Baba ba ita bace ta ga fitarta ne tabiyota tana bata hak'uri don taki kulata ne shine take kuka"

Baba Nuhu ya k'araso wajen Amrah da ke durk'ushe tana kuka gwanin ban tausayi yace,. "Ba nace ki daina wannan kukan ba?? To idan har kina son mu shirya da ke ki ajiye komi ki fuskanci gabanki idan Mijinki ya zo ki je gidan aurenki ki rungumi yaronki, Ina mai tabbatar maki sai wani

lokaci ya zo da zata dinga kuka tana baki hakuri akan zaluncin da ta yi maki, ban ce kar kiyi mata biyayya ba don Uwa Uwa ce komi kaskanciinta kuwa, amman ki rage damuwa akanta don itace tayi maki laife ba ke kika yi mata ba"

Mustapha ya kalli Baban yace,. "Baba zan tafi da ita gidana d'in yanzu don nasan da ta had'u da Fatima zata ware insha ALLAHu"

Baba Nuhu ya ce

"ALLAH ya kiyaye to amman ka kula amana ce ita a hannunka duk da bana shayinka amman dai a kuka sosai Allah ya yi maku albarka dukanku ya baku ladar zumunci"

Suka ce "Ameen"

Sannan ya K'ara da cewa "sai dai Ina son idan har Mijin nata bai zo ba gobe ko jibi ba to a je da ita ta zaga dangi taga 'yan uwa tunda ita mahaukaciyar Uwarta bata bari tun farko aka yi zumuncin ba"

Har suka fita gidan Baba Nuhu bai fasa zabgar fad'a da Zuwaira ba sannan da tirr da miyagun halayenta, har sai da Inna Dije ta yi ta bashi baki sannan ya dan lafa da fadan.

AMRAH Kam kai tsaye Mustapha gidanshi ya nufa da ita inda ta tarar da kyakkywar Matarshi da D'an yaronshi mai kama dashi sak wanda ba zai wuce wata biyar a duniya ba bul bul dashi, ganin yaron yasa ta tuno da nata yaron wanda idonta suke ta yi mata gizo da fuskarshi, cikin jin dad'i ta karb'eshi tana yi masa wasa, ganin haka yasa Mustapha ya ji dad'in yanda ta fara sakin jikinta yayi d'akinshi Fatima ta biyo bayanshi tana yi masa sannu da zuwa, yana cire clips d'inshi yace da ita

"Ga bakuwa nan na kawo maki don ALLAH ki kula da ita sosai zuwa anjima zaku shirya mu je a sissiyo mata kayan da zata sakawa"

Cike da jin dad'i Fatimar tace,. "ALLAH ya bani ikon sauke nauyin da ka d'ora mani bari inje in bata abinci kafin ka fito wankan"

Ta fice Cikin farin ciki saboda tunda ya bata labarin Amrah ta ji tana matuk'ar tausayinta don ta yi ta kwatanta halin da Amrah ta shiga akanta, ta ji lalle ba k'aramin jarumta Amrar'r tayi ba don ita Kam yanda take KAUNAR Mustapha da D'an yaronta ace a rabasu rana tsaka wata kila ma itakam mutuwa zata yi ko ta haukace don bata da k'arfin zuciyar d'aukar matsalolin amman a nata tunani fa.

Kafin kace me ta cika diny table da kayan abinci ta k'araso cikin falon tana yar dariya tace,.

"Amrah ko?"

Amrah da ke yiwa yaron wasa Yana ta dariya ta dago da sauri tace, "Eh"

Fatima tace

"Kawoshi ki je kici abinci to"

Amrah ta fadada fuskarta da fara'a tace

"A'a bar man shi ai ba ma abincin zan iya ci ba"

Fatima ta b'ata fuska tace, "haba dai ai kema dai kinsan baza ki fara ba"

Amrah ta yi yar dariya tace,. "Allah ba komi ai don bana jin yunwa ne shiyasa"

Fatima ta nufi diny tace, "bari dai in sauko maki dashi anan in kinfi jin dad'in zaman nan din"

Ta dauko kular da plate da spoon ta ajiye a gabanta tace

"in ba so kike yi Auncle dinki ya zaci kamar ban iya tarbon baki ba to ki sauko kici abinci don ALLAH"

AMRAH ta sauko tare da yaron ta zauna Fatima ta fara zuba mata abincin har ta kammala sannan ta ce ,. "Kawoshi to yanzu sai kici ko"

AMRAH ta ki bada shi tana dariya tace

"Barman kanena anan Aunty bana son ki rabani dashi ina sonshi sosai don fuskarshi sak Umar sai dai shi wannan ya girmeshi Kinga ma Ni saboda dokin ganinshi ko ma sunanshi ban tambaya ba"

Ta k'are maganar tana dariya Fatima ta zauna Kan kujera tace,

"Lalle waton shi dan farin din ma ko kunyarshi ba kya yi to shi wannan sunanshi baya fad'uwa don sunan Baba ne aka saka masa muna ce masa Amir"

Amrah ta zaro Ido tace,. "Ki ce tsofo an yi masa aboki tun kafin ya gangara"

Fatima ta dafe Baki tace,. "Lalle wannan yarinyar wuyanki yayi kauri to ki kiyaye ba'a tab'a Baba a gabanmu asha da kyau ehe!!"

AMRAH ta d'aga yaron sama tana yi masa tawai tana fad'in

"Kai dan tsoho mai ran k'arfe yaushe zaka wuce ne don mun matsu mu ci gumba fa"

Fatima ta mik'e tsaye tace

"Ki ci abincin don na fahimci cin fuska kike so kiyi muna ni na tafi inji da Auncle dinki"

Amrah ta yi dariya ta dan tsakuri abincin kad'an don bata son ta ci da yawa kada ta yi amai, tana k'arewa ta ajiye Umar kan kujera ta kwashe kayan ta mayar dinyn din sannan ta dawo ta kalli yaron yana son yin bacci ta d'aukeshi ta d'ora a kafada ta fara zagaye falon tana jijjigashi har ya yi baccin, sai ga Fatima da Mustaphan sun fito suna fira k'asa k'asa suna dariya Amrah ta yi saurin kawar da kanta akansu saboda tuno Nazir da tayi, cikin sanyin jiki ta zauna Kan d'aya daga cikin kujerun ta lallaba ta kwantar da Amir d'in, aikuwa sai gashi ya falka zai yi kuka ta yi saurin daukarshi ta d'ora a bayanta ta kalli Fatima tace

"Bani zane in goyashi bacci yake son yi"

Fatima da ke zubawa Mustapha abinci a diny tace

"WALLAHI ba ruwana idan ya nanake maki hancin jariri ko jaririya"

Amrah cike da jin kunyar maganar ta yi shiru saboda ganin Mustapha a wurin, Fatima ta k'are zuba masa ta nufi d'aki ta dauko zane ta mika mata, Mustapha ya kallosu yace

"Fatima ki karb'i yaronnan ki goya kada a takurawa yarinyar nan fa"

Amrah ta b'ata fuska tace, "Zan iya fa Auncle don ALLAH a bari in goyashi"

Ta k'are maganar cikin bata fuska da tunzuro baki, Fatima ta saka hannu zata karbeshi Amrah ta hana ta karbe zanen ta goyashi, Fatima ta rufe bakinta tana kallon Mustapha ya yi kamar bai gansu ba ya ci gaba da cin abincinshi har ya k'are sannan ya mike ya kalli Fatimar yace

"Ni zan fita ku shirya zuwa anjima da na dawo za mu je, ki kaita d'akin da zata zauna tayi wanka ta huta kafin in dawo"

Fatima ta rakashi tana yi masa a dawo lafiya sannan ta dawo ta kalli Amrah tace,

"Zo mu je in rakaki masaukinki"

Amrah ta dauko hijabinta ta biyo bayanta tana bubbuga duwawun Amir don ya ji dad'in baccin har zuwa wani k'aramin d'aki mai d'auke da k'atuwar katifa wadda tasha gyara da zanen gado fes fes dashi, ta nuna mata toilet d'in da ke d'akin tace

"Kinga d'akinki kafin Oganki ya zo ya kwasheki don nasan duk inda yake kina cen cikin

zuciyarshi a makale"

Amrah ta yi dan murmushi ba tare da tace komi ba, Fatima tana yi mata dariya tace

"Bari in je in kawo maki kayan da zaki saka don nasan ko nace ki kawoshi ba badawa zakiyi ba"

Amrah tana dariya tace

"Kamar kinsani ALLAH ganninshi nike yi tamkar Umar dina"

Fatima tace

"Kyaji da shi yarinya amman dai anga kawaici ga dan farin fa"

Amrah ta rufe Ido tana dariyar jin kunya Fatima ta fice itama tana dariya, fitarta yasa ta sauko da Amir ta lallaba a hankali ta ajiyeshi, kasancewar baccin yayi masa nauyi ya baje abunshi har da su ajiyar zuciya.

****

Satin Amrah biyu a gidan Mustapha zuwa lokacin ta saba sosai da Fatima sun shaku matuk'a kasancewar Fatimar mai faram faram da mutane Shiyasa itama Amrah ta saki jikinta da ita sosai, don ta ji rabin damuwar da take ciki ta yaye muradinta d'aya ne a yanzu ta yi Ido biyu da Nazir da D'an yaronta Umar.

Itama Fatimar tsantsar soyayyar da AMRAH ta ke nunawa Amir yasa ta k'ara jin kaunar Amrah aranta, daman ance mai da Wawa ne mutum ko baya sonka ya nuna yana son danka ganin kake yi tamkar Kai yake so, don ko wanka tunda ta zo gidan itace ke yi masa ta shiryashi, tsakaninshi da Fatima shayarwa amman komai AMRAH ke masa, Sannan Uwa Uba Amrah har kitchen suke shiga tare su dafa abunda suke so na k'walam don duk abunda taji tana sha'awarshi tare su ke yi su zo su baje falo suyi ta ci suna tsokanar juna.

Wasa wasa Amrah ta kwashe wata biyu a gidan Mustapha izuwa lokaciin cikinta yana wata na uku amman har lokacin ba'a sami labarin Nazir ba, a lokacin ne Aunty ta zo garin domin suna waya da Amrah akai akai da sabuwar wayar da Mustaphan ya siyo mata.

Sun yiwa Aunty tarba Mai kyau sannan Amrah da Auntyn suka fara firar yaushe gamo, Fatima ta bar masu falon don su ji dad'in tattaunawa, Aunty cike da jin dad'in ganin yanda Amrar'r ta yi kyau abunta Masha ALLAH tace

"Lalle yarinya shikenan kin shige nan abunki kin barmu cen da rigimar Aunty Zuwaira"

Amrah ta zaro Ido tace, "me Kuma ya faru Aunty"

Aunty ta yi shiru sannan tace, "ita da kawarta Lantana ne suke ta rigima wai ta sace mata kudi da abun ma yayi tsamari har police station su ke"

Amrah ta zaro Ido tace, "wai Ni ALLAH WALLAHI tun tuni Nike ta sanar da Mama Lantana ba mutuniyar arzik'i ce ta rabu da ita amman taki ganewa, ai yanzu gashinan ta fara ganowa da kanta"

Ganin damuwar da Amrah ta shiga ne yasa Auntyn tace

"Ke mu ajiye wannan zance ya ake ciki da zancen Nazir??"

Amrah ta marairece tace, "WALLAHI ana Nan dai yanda ake Aunty don har yanzu ba'a samu wayarshi ba, shima kanshi Baban Jamilun ya damu sosai da rashin samun numbar don ko abokinshi Jamilun shima yanzu baida numbarshi"

Ta k'are maganar cikin zubowar wasu kwalla Aunty ta yi shiru sannan tace,.

"Idan na koma zan je gidan kanwar tashi insha ALLAHu inji shin miye mafarin wannan shirun haka? Don ko Ni nayi ta nemanshi da numbar da Nike da ita tashi amman bata zuwa"

Amrah ta ce "nagode Aunty ALLAH ya saka maki da gidan aljannah"

Aunty tace

"Ameen Amrah ai ni tamkar 'ya na d'aukeki ki dai tamani da addu'ar da kika Saba in da rayuwa kuma da rabon nima in samu nawa rabon"

AMRAH tace

"Insha ALLAHu Aunty ALLAH yana sane dake da duk sauran masu nema zaku samu duk tsawon lokacin da aka d'auka in har da rabon to zai zo da yardar Allah"

Aunty tace,. "Allah ya nufa d'iyar kirki bari in tashi inje don gobe tunda sassafe zan kama hanya"

Amrah da Fatima suka rakota har bakin gate tare da abun alkhairin da Fatimar ta yi mata har ma da ita kanta Amrah'r, sannan suka yi sallama da juna tare da yiwa juna sai watarana sannan suka dawo.

Cikin Amrah har yana da wata biyar zuwa lokaciin kowa ya damu da halin da ake ciki, don har Baba Nuhu ya fara zancen a bishi cen Gomben aji ko lafiya, Yaya Harun yace dashi a dai dan sake jira don Baban Jamilu yana iyakacin k'ok'arinshi akan lamarin.

Baba Nuhu ya kyale ne Amman ba don ya so hakan ba don baya son ace har Amrah ta haifu ba tare da Nazir d'in ya zo ya mayar da aurenshi da ita ba.

Wata ranar Asabar Amrah tana d'akinta kwance da cikinta da ya fara fitowa kawai taji Kiran waya da wata sabuwar Number, har ta so ta share don ita duk numbobin da ke wayar duka na Yan uwanta ne ba bare don ko numbar kawarta d'aya babu a ciki sai ta Fatima, shiyasa ta share anyi kira har sau biyu bata d'auka ba sai a na uku ne ta d'auka cikin rashin son yin magana saboda tunanin Mijinta da ya addabeta, sai ga ta da tashi zaune ba shiri tare da dafe gaba tace

"Yaya Nazir!!!!!"

😳😳😳

D/Auta ce✍🏻

"
🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

Wattpad PrincessDija246's

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

56

Ba shiri ta ajiye wayar ta fito da sauri jikinta yana rawa ta taradda Fatima a kitchen bakinta yana rawa tace,. "Aunty Albishirinki"

Fatima cikin zak'uwa da taji abunda zata fad'a tace,. "Goro daughter yi sauri ki fad'a mani don jikina yana bani cewa Baban Umar ne ya kusa bayyana"

Amrah tayi wata Yar kuwwa ta fara rawar jin dad'i tace,. "Aunty Yaya Nazir d'ina yana kan hanyar zuwa garinnan saura k'iris ya k'araso bansan me zan tanadar masa me sauki ba"

Fatima tayi wani tsalen jin dad'i tace

"Wow! Ki ce Muna da babban bak'o yau"

Amrah ta yi wani juyi zuciyarta cike da jin dad'i tace,. "ALLAH ya karb'i addu'ata wayyo! Yaya Nazir d'ina Ina sonka sosai Allah ya kawo man Kai lafiya"

Fatima tana dariya tace,. "Ameen Juliet me kike san yana so a dafa masa shaf shaf kafin ya k'araso?"

Amrah ta yi shiru tana so ta canko abincin da ya fi so tace

"Ummmmmmm! A bangaren abinci dai ya fi son pride Rice da miyar Koda, abinsha Kuma yana bala'in son kunun aya sosai"

Fatima tace

"Ok to je ki yi sauri ki shirya yanzu zan had'a masa don akwai komi a k'asa"

Cike da jin dad'i ta zo zata fita sannan ta dawo ta fara bud'a prizer ta fiddo k'odar ta fara yanyankawa tana Murmushin jin dad'i tace,. "Bari in yi masa miyar da hannuna Aunty zuciyata tafi natsuwa idan har naji ya fara santin abincin"

Fatima ta kalleta ta bud'e baki tace

"Oh ni jikanyar mutum hudu wannan rawar Kai haka! To ki dai dan ja class kad'an don kar ya gano kinfishi shan wuya"

Amrah tana dariya tace, "Daman fa ai haka d'inne Aunty don shi yana da matarshi Ni ko fa? Bani da kowa sai shi na rasashi ai dole in fishi jigatuwa"

Haka suka ci gaba firarsu Fatima tana had'a abincin gida AMRAH tana had'awa Nazir har ta kammala, a gurguje ta je ta fad'a wanka tana wanka ta jiyo Kira a wayarta abuje ta fito ta d'auka jin yana sanar da ita cewa gashi gidan Baba Nuhu yasa tayi dan tsalle ta ce

"Wayyo dad'i"

Ta kashe wayar da sauri ta koma toilet d'in a gurguje ta kammala wankan ta Fara tsantsara kwalliya, don tunda take gidan bata taba zizarawa bakinta jambaki ba sai ranar, kafin ka ce me ta fito sak Amrah'rta gwanin burgewa, don cikin ya kara mata kiba kad'an Kuma ya sata ta k'ara yin haske fatarta ta yi lumui lumui saboda kwanciyar hankalin da ta samu a gidan Mustapha.

Ta k'are shiryawar ta yi tsaye jikin madubi tana kwatanta irin tarbon da zata Masa, da kalar Murmushin da zata yi masa na farko idan sun yi four eyes, tana Murmushi tana rufe fuska a gaban madubi Fatima ta shigo ganin yanda ta cancada ado ne ta kalleta da kyau ta rik'e baki tace

"Lalle wannan mutumin ba k'aramin kamu yayiwa zuciyarki ba, to Alhmdllh yanzu Aucle dinki ya kirani yace gasu nan za su zo gidannan in sanar da ke ki kimtsa"

AMRAH ta dafe zuciyarta tace

"Wayyo Zuciyata Aunty baki ji yanda take ta bugawa ba"

Aunty ta fashe da dariya tace

"To Hajiyata ki Kai masa abincin a falon waje tun kafin su k'araso ko?"
Amrah ta yafa gyale ta kalli jikinta ga madubi tayi Murmushi ta dauko wani turaren ta sake fesawa a jikinta ko'ina sannan ta kalli Fatima tace

"Nayi ko Aunty ??"

Fatima ta yi mata alamar 👌 da hannun tace, "wonderful Abu d'aya ya dan so ya kwabsa maki cikinnan da ya fito"

Amrah ta b'ata fuska ta kalli cikin ta zumburo baki tace

"Bari in saka doguwar riga don bana son yayi saurin ganoni"

Fatima tace,. "A'a kinyi fa Wasa ce nike maki WALLAHI ba makusa ta ko'ina don wannan tsinin shine ma ai ya K'ara fito maki da kyaun"

Amrah ta rufe idonta tace

"WALLAHI Aunty Ina jin kunyar ya ganni da cikinnan"

Fatima ta kyalkyale da dariya tace,. "Au lokacin da kika baje aka yi cikin Baki ji kunya ba sai yanzu zaki ji kunyar ya ganki da shi?"

Amrah zata yi magana suka jiyo sautin Mustapha yana Kiran Fatima zai nufo d'akin, aguje ta fita ta tareshi Yana sanar da ita ga Bakon ya zo Ina Amrah'r ta fito.

Amrah ta fito kanta a sunne ta fara gayar da Mustaphan ya kalleta yayi Yar dariya saboda ganin kwalliyar da ta cab'a yace

"To kije Mijinki yana falon waje yana jiranki"

Amrah ta kalli Fatima tace

"Zo mu je Aunty"

Fatima ta yi dariya tace,. "A'a ki je dai daga baya zan zo mu gaisa"

Amrah ta fara yi mata magiya Mustapha ya katsa mata tsawa Dole ta fice ba shiri sai janyo gyale take yi tana rufe Cikin, tana lek'awa ta gani tare da tambayar kanta tace

"Wai da gaske ana ganin Cikin?"

Koda ta je bakin k'ofar falon ganin talkaminshi yasa taji wani yarr! Ta dan dad'e a bakin k'ofar tana yarfar hannu sannan ta yi jarumtar cire nata talkaman ta rik'e labulen da nufin ta yaye ta sake yin Jim sannan ta bankadeshi ta shiga da yar guntuwar sallamarta.

Nazir da ke latsar waya sallamarta tasa yayi saurin d'ago kanshi sai gashi ko yayi arba da kyakkywar fuskarta, da sauri ya taso zuciyarshi Cike matsanciyar kaunarta ya zo inda take tsaye sunne da Kai tana Wasa da yan yatsunta yace

"Irin tarbar da za'a yiwa Angon kenan??"

Amrah ta rufe fuskarta tana Murmushin jin dad'i sannan ta sami d'aya daga cikin kujerun ta zauna cikin dakewa ta saita kanta tace

"Yaya Nazir sannu da zuwa ya su Inna da Uwargidanka??"

Nazir ya k'araso wurinta ya zaune Kan hannun kujerar da take zaune ya rankwafo ya kalli fuskarta yayi Yar dariya sannan ya sauko yayi durkuso a gabanta yana leken fuskarta yace

"Ina son in kalli da wane idon ne har kike da kwarin gwiwar tambayata wata Uwargidana cen bayan gaki a tare dani, tukunna ma wai akwai wata Uwargidana ne bayan ke halan? Ko kuma har yanzu baki shiryawa Nazir akan ya sake zama da ke bane in koma??"

Amrah ta yi saurin d'ago fuskarta ta kalleshi Ido cikin Ido ta kasa d'auke idonta akanshi Sabida ganin yanda ya K'ara kyau Masha ALLAH kurciyarshi ta k'ara fitowa shar! dashi, ga wata kibar da ya fara azawa da dan gemunshi da ya zagaye kyakkywar fuskarshi gwanin burgewa, a kallo d'aya zaka gano irin hutun da ya ratsa jikinshi don fatarshi har wani sheki takeyi duk da kasancewarshi chaculate color ba fari ba.

Ganin kallon da take masa ne yasa ya hura mata iska a cikin Ido yana dariya yace,. "Idan kika cenye shikenan kin huta wannan kallo haka ai sai ki janyo inyi rashin kunya a gidan surukai"

AMRAH ta rufe fuskarta Cikin jin kunyarshi Aiko sai gashi gyalen da ta tula a gabanta wanda ya b'oye Cikin ya zare Cikin ya fito radam a jikinta, Cikin tsantsar farin ciki Nazir ya Kai hannunshi ya shafo Cikin yace

"Alhmdllh Lalle ALLAH Kaine abun godiya Kai ne gagara misali tabbas ke Alkhairi ce a wurina don wannan ni'ima da yayi man ba kowa yake samu ba sai dan baiwa, to Kam tabbas na yarda nidinnan dai d'an baiwa ne tunda har gashi Umar da wata bakwai na Kara samun wani rabon, sannu kinji ALLAH ya biyaki da gidan aljannah Kuma ki sani tuni ke matatace don na mayar da aurena da ke tun ranar da aka sanar dani kina d'auke da juna biyuna, Lalle na iya buga goal a saiti suruf ta shige cikin raga Allah yayi maki albarka kuma ya saukeki lafiya kinji??."

Amrah ta motsa labbanta Cikin makoshi tace,. "Ameen"

Ya tashi daga durk'uson da ya yi ya zauna a kusa da ita ya rik'o hannunta yace

"Wai yau Ni Nazir ni ake jiwa kunya?? Hmmm dama kin ware Yarinya don Ni Kam da zafina nake tafe yanzu haka da shirina na zo na tafiya da ke gobe gobennan"

AMRAH ta zaro Ido tace,. "Sai na haifu fa idan anyi suna sai ka dawo mu tafi"

Nazir ya zaro Ido yace

"Idan so kike yi in tare maku anan ai shikenan Amman nikam gobe Zan juya Kuma tare da ke zamu tafi na baro yarona kada yayi kewata"

Amrah jin zancen Umar yasa taji zubowar wasu hawaye masu zafi akan fuskarta ta saka hannu ta share saboda tuno rabuwar da tayi da yaronta, Nazir ya fiddo wani hankacif a aljihunshi ya Fara share mata hawayen yace

"Har abada Baki ba kuka lokacin kuka ya wuce yanzu lokacin farin ciki da annushuwa da nunawa junanmu soyayyya ne, don idan ma Baki iya ba ki koya don Wannan karon ba d'aga k'afa don ki sani"

Ya tura hannunshi ta bayanta ya rungumota a jikinshi ya dan duk'o saitin wuyanta idonshi a lumshe ya shako numfashi yace,. "Wow! Wannan daddadan turaren fa yaman dad'i sosai Maman Umar"

Amrah tsikarta ta tashi Yar! Ta yi saurin kalloshi ta yi yar dariya tace,. "Idan kana bukata tamkar ka samu ne"

Nazir ya bud'e idanuwanshi da suka fara canzawa yace

"Ina so amman a jikinki in yi ta shaka ina jin dad'i, shin wai Ni kam me zanyi wanda zan nuna farin cikina da ALLAH ya nuna mani wannan Rana da Nike ta jiran zuwanta yau gashi ta zo gani gaki a matsayin ma'aurata ba wani shamaki a tsakaninmu"

Amrah ta rufe fuskarta tace

"Ka godewa ALLAH don shine abunda ya fi cancanta da ka yi a farko"

Nazir ya sake shako turarenta ya cusa kanshi cikin wuyanta yana k'ok'arin tura hannunshi cikin rigarta, ta rik'e hannun tana yi masa kashedi da Ido tana yar dariya ya yi saurin ci zo kunnenta ta yi yar k'ara da sauri tace,. "Wayyo da zafi fa" kanshi cikin wuyanta yana shakar daddadan turarenta yace

"Dama zafin nike son ki ji don ki gano nima naji zafin hanani abunda nayi niyya"

Sannan ya ciro kanshi ya saita bakinshi a idonta ya yi mata wani kiss a hankali ya bud'e idonshi cikin shaukin sonta ya kalleta da kyau Ido cikin Ido yace, "Nagodewa ALLAH da ya mallaka mani ke a matsayin Uwar 'ya'yana, bansan ta ya zan nuna maki farin cikina akan wannan alkhairin da ke k'unshe cikin cikinki ba, don shine yayi tsani wajen dawo da mu a matsayin ma'aurata ba tare da munyi dogon shako ba, Kuma shine ya janyo aka haramtawa kowa ke sai Ni d'innan don nasan idan ba donshi ba da yanzu ina Kan gadon Asibiti, don na tabbata Dole ne wani yace zai yi wuf! da ke gashi bazan tab'a jurar jin lafazin wai kin auri wani ba har ya shiga inda nake birgimata ba, sai gashi ashe daman Ni kad'ai ne aka mallakawa wurin idan ba Ni ba ba wani Wanda ya isa aiko Dole na k'ara yiwa ALLAH godiyata"

Ya kare maganar tare da Kai mata kiss a goshi ya gangaro a bakinta Cikin mayen sonta ya fara

lasar lebenta har yayi nasarar cafko halshenta, ya b'ata lokaci yana tsotsar bakinta tamkar wanda ya sami wani sweet mai dan Karen dad'i, duk da shi a yanda yake ji a zuciyarshi ya ma fi sweet din dandano.

Sannu a hankali ya zare bakinshi idonshi a lumshe yace

"I can't explain what am loving you in my heart my noory, kece hasken idona mai haska ko'ina a cikin rayuwata, kece farin cikin zuciyata mai sakani nishadi a kowane lungu da sak'o na zuciyata, na godewa ALLAH da ya bani ikon yiwa Inna biyayya tsananin sonki bai sa Ni na take umurnin da ta bani ba, yau gashi na ci nasarar hakurina ga ki a kusa dani kuma ga albarkar da ALLAH ya k'ara yi mani baiwa dashi Kai Alhmdllh for everything"

AMRAH ta fashe da kuka ya yi saurin bud'e idonshi ranshi a b'ace yace,. "Bana son kukan nan fa nasan damuwarki ki kwantar da hankalinki insha ALLAHu Ni Nazir zan zame maki Uwa Uba har ma da dangi gaba d'aya, Ina yi maki albishir ba zaki tab'a yin danasanin aurena ba saboda yanzu zamu fara shinfida rayuwa sabuwa Ni da ke da yayan da Allah ya bani a yanzu da kuma wad'anda suke tafe a gaba, ki godewa ALLAH tunda har ya kashe ya baki Nazirun Inna Abu d'aya ya rage kisan ta yanda zaki tarairayi abunki saboda Ni naki ne ke kad'ai har abada ba wani shamaki da zai sake shifa a tsakaninmu ni da ke."

Hmmmm soyayya dad'i😢

D/AUTA ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

Wattpad PrincessDija246's

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

Ina ganin ruwan comments d'inku ta ko'ina Ina godiya ku sani ina jin dad'in addu'o'inku gareni alkhairin Allah ya kai maku a duk inda kuke a fad'in duniyar nan one luv🤝💋

57

Amrah ta sauke ajiyar zuciya mai k'arfi ta k'ara rik'e hannunshi gam tace,. "Yaya Nazir na gode da soyayyar da kake yi mani a yanzu da kuma wadda kayi mani a cen baya lokacin da bansan kaina ba, hakika kai alkhairi ne a wurina kuma Ina godiya da Allah ya bani kai a matsayin miji kuma uban 'Ya'yana, bansan ta ya zan siffanta maka irin son da nake yi maka ba a zuciyata don bakina yayi kad'an da ya bayyanashi, na dad'e ina jinyar sonka a Raina sai dai ni kaina ban gano gaskiyar abunda zuciyata take nusar dani ba sai daga bayannan, don ALLAH ka yafe mani duk abunda nayi a baya na rashin kyautawar da nayi maka, ina yi maka albishir d'in cewa zuciyata cike take fam! da soyayyarka Yaya Naziruna, na baka amanar kaina da soyayyata duka Hubbyna"

Ta k'are maganar cikin k'ara shigewa jikinshi tana shakar kamshinshi, cikin jin dad'in kalamanta wad'anda sunfi zuma zaki a wurinshi, ya lumshe idonshi ya ja wata doguwar ajiyar zuciya yace

"Alhmdllh ALLAH ko yau na mutu gurina na duniya ya cika daman irin wannan ranar na dad'e ina jira yau gata ta zo muna babu wani shamaki a tsakaninmu"

Amrah ta d'ago fuskarta daga kwancen ta shafo fuskarshi tace, "Shamaki kam akwaishi tunda kana da Matarka a gefe fatana kawai Ubangiji ya bamu zaman lafiya"

Nazir ya sauke Mata wani kiss a goshi sannan yace

"Babu wani shamaki Nazir ke kad'ai ya ke jira"

Amrah ta tashi zaune tace

"Bangane inda zancenka ya dosa ba kayi man gwari gwari yanda zan gane ina ka kai ita Sadiyar??"

Nazir kam nan take ya b'ata fuska ya yi shiru na d'an lokaci sannan yace, "Idan muna tare ki daina sako wata a cikin zancenmu ki d'auka cewa ke kad'ai ce a gabana yanzu ba ni da wata sai ke kuma ke kad'ai ce wadda nike son inyi rayuwa da ita har karshen raina"

Amrah ta goge guntuwar kwallarta ta mik'e tsaye ya rik'o hannunta yace,. "Ina zaki je kuma?"

Tace "bani minti biyu kacal yanzu zan dawo"

Rik'e da hannunta ya mike ya k'araso jikinta ya rungumeta tare da Fara yamutsata yana sauke numfashi a hankali, duk da tana jin dad'in yanayin amman hakan bai hanata rik'e hannunshi ba tace,

"Plss hubbyna minti biyu zaka bani kaji"

Shi ma ya rik'e nata hannun gam yace,. "Ba na son rabuwa da ke Matata ko da ko na second d'aya ne je ki dawo ina jira"

Amrah ta fesheshi da wani tsadadden murmushi sannan ta juya ya bi bayanta da kallo har ta fice, sannan ya dafe Jarumarshi yayi dariya zuciyarshi cike da jin dad'i ya zauna tare da janyo wayarshi ya fara Game kafin ta dawo.

Amrah kam tana tafe zuciyarta cike da tsantsar farin ciki da jin dad'in ganin daga yau shikenan matsalarta ta kau farin cikinta ya dawo gareta, sai faman murmushi take yi ita kad'an ba shiri ta ji ta yi karo da Fatima da sauri ta dawo natsuwarta tace

"Sorry Aunty Fatima"

Ta k'are maganar tana rufe fuska, Fatima ta kyalkyale da dariya tace,. "Ai duk abunda kika yi a yau Dole ayi maki uzuri don soyayya gaskiya ce musamman irin taki da Angonki fatan da muke yi maku kawai shine ALLAH ya k'ara had'a kawunanku ya K'ara kabe shedan a cikin rayuwar aurenku"

Cikin jin dad'i Amrah tace,. "Ameen Aunty kema ALLAH ya bar ki da Auncle Dina ke kad'ai ba kari har mutuwa"

Fatima tana dariya tace, "Ameen d'iyar Auncle ina zaki je haka kika baroshi shi kad'ai??"

"Amrah ta ce Abincin Zan Kai masa tun d'azu sai surutu muke ko ruwa ban bashi ba"

Fatima ta dafe Baki tace,. "Au! Eh lalle su soyayya manya to ki yi sauri ki Kai masa ai Ni na d'auka kin shigar masa da su Shiyasa na jiki lumkum don nima Ina cen ina ji da rigimammen Auncle d'in cen naki je ki dauko bari in je in k'arasa masa aikin kada ya ga na dad'e"

Fatima tayi d'akin Mustaphan Amrah ta d'aga murya tace

"Amir baccin yake sha har yanzu da ba zai zo su gaisa da Hubbyna ba?"

Fatima ta waigo tace

"Je ki ji dashi dai kafin in zo in kawo masa shi su gaisar"

Amrah ta yi kitchen ta je ta dauko k'aton tire za jera kulolin abincin ta bud'e firij ta dauko kunun ayar da ta yi masa ta zuba a cikin wani hadadden jug mai rik'e sanyi ta d'ora cup's da plates da spoons ta kinkimi tiren ta nufi falon da Nazir din ya ke, aiko yana hangota da tiren yayi saurin zuwa ya tareta ya karb'i tiren ya ajiye sannan ya kalleta ranshi a b'ace yace

"Shine baki fad'a man ba in zo in taimaka maki haka kawai salon ki wahalar man da Baby?"

AMRAH ta yi saurin zama dafe da bayanta tana sauke nishi tace

"Bana son ka wahala shiyasa"

Nazir ya kalleta da kyau yayi Yar dariya yace,. "Raguwa ki dai zama jaruma don aikine ja agabanki"

Amrah ta harareshi ta mike ta fara zuba masa abincin tace,. "Ai Kai ma kasan ni ba ta wasa ba ce"

Nazir ya rufe baki yana dariya yace. , "Kika ce?"

Ta d'ago ta d'aga masa kai tace,. "Yes!!"

Ya zauna fuskarshi cike da fara'a yace

"Ok to zamu gani ai don in da ba k'asa nan ake gardamar kokuwa, saboda haka mu gani a kas sannan ne zamu tabbatar da gaskiyar zancen"

Amrah ta rufe fuskarta alamun jin nauyin maganar tashi, ta dauko plate d'in abincin ta saka spoon ta dawo kan kujerar da ya zauna ta ajiye sannan ta mike ta fara kiciniyar cire masa malummalum d'in da ke jikinshi ya taimaka mata ta cire masa ta je kan wata kujera ta baza rigar

don kada tayi squeeze, ta dawo ta d'auki plate d'in ta d'ora akan cinyarta ta debo abincin ta nufo bakinshi, fuskarshi a washe ya bud'a ta zuba masa ya lumshe idonshi yana ci yana Murmushin jin dad'i yace,

"Fantastic wannan abinci daga jinsa zazzakan hannun Matata ne ya hadashi, kai nikam na godewa ALLAH da ya bani ke Ni Naziru"

Ya karbe spoon d'in ya ajiye yace

"Saka hannunki ki bani nafi jin dad'inshi"

Ta yi dariya ta zaro Ido waje ya d'aga mata kai alamar tabbatarwa, Dole ta saka hannun ta dinga bashi haka ta dinga ciyar dashi abincin yana ci yana zuba mata santi har sai da ta tabbatar da yayi kat! Sannan ta tsiyaya masa kunun ayar ta mika masa tace,

"Ga Mutuninka fa"

Ya karb'a tun kafin ya Kai baki kamshin kayan had'in suka fara ziyartar hancinshi, aiko kafin ka ce me ya zuke ta sake zuba masa nan ma ya shanye, sai da yasha cup hudu kasancewar basu da wani girma sosai sannan ya fara shafa cikin yace

",Wayyo cikina zai fashe"

Amrah ta k'arasa cika cup d'in taf tace

"Daure ka dan k'ara kaji Mijina!?"

Nazir ya rik'o hannunta ya ajiye plate d'in sannan ya zuba abincin ya fara Bata itama, tana ci tana b'ata fuska alamar bata so idan taki karb'a ya maka mata harara ta bud'a Baki ya saka mata har ma da yaga da gaske bata so ya zuba a bakinshi ya janyo kanta tana mutsu mutsu ya juye mata shi a Baki haka ya dinga yi mata tana tirjiya har ta koshi itama, sannan ya saka halshe ya lashe mata bakinta da abincin da ya b'ata mata bakin ya kalleta yace

"Saura kunun ayar kema yanzu zanyi maki duren da kika yi mani"

Ta Fara girgiza Kai tace

"Idan nasha amai zanyi"

Yace " ba zaki yi ba don wannan duren soyayya ne Zan yi maki"

Aiko ta zuba kunun ayar a bakinshi ya janyota ya juye mata a baki yana lasar halshenta har suka shanyeshi tare sannan ya tsotse bakin tas sannan ya sake zuba wani, haka yayi ta yi mata

har suka shanye shi tare daga nan salon wasar ya fara canzawa sai saukar numfashinsu ake ji, saboda tsimin soyayyar ya mike sai cakuda juna suke yi.

Motsin shigowar da suka ji ne yasa Amrah ta yi saurin zare kanta daga jikinshi ta dan matsa tana sauke numfashi tare da dawo da natsuwarta a jikinta.

Fatima ta yi tsaye bakin k'ofar ta fara yin sallama duk suka amsa mata sai dai kam shu Nazir tashi muryar a shak'e take, Fatima sai da ta yi sallama Uku sannan tace

"In shigo??"

Amrah tana dariya tace

"Shigo kanki tsaye Aunty Fatima" sannan ta mik'e ta zo ta yaye labulen tana ganin Amir ta yi saurin karb'arshi tace

"Oyoyo my Amir sannu da Shan bacci"

Amrah ta nufo Nazir da Amir ta mika masa shi tana dariya tace

"Da wa ka ga yake Kama??"

Nazir ya dagoshi dakyau ya ga fuskarshi sai gashi ya zaro Ido yace

"Wannan ai photocopyn na Umar ne, Kai Aunty zaki bar muna shi mu tafi dashi ko? Sai mu had'a Yan biyunmu waje d'aya"

Fatima ta k'araso falon ta zauna tana dariya tace,. "Eh me zai hana in har zaka barta ta anan ta haifu ka ga shikenan sai ta bar sabon sai ku tafi da shi ba matsala ba ce"

Nazir ya dafe Baki yace, "Lala la Aunty horon da kike so kiyi man kenan shiyasa kika bullo ta nan?"

Fatima tana dariya tace, "ba wani horo sai gaskiya yanzu ma idan ka tashi ka tafi dashi d'in Ni sai muyi zamanmu da ita shikenan"

Nazir yana dariya yace

"A'a baza'a yi haka ba Aunty tuba nake"

Gaba d'aya suka kyalkyale da dariya, daga nan suka fara gausawa cikin mutunta juna sannan Fatima ta mike tace

"Bani shi mu tafi to tunda kun gaisa"

Nazir ya kalli Amir data wasarshi da key d'in da ya bashi ya ce

"Barshi kawai Aunty bamu gama gaisawa ba"

Fatimar ta fice tana dariya Amrah ta kalleshi tace

"Ni ma ranar da na fara ganinshi baka ji yanda naji ba, banbancinshi da Umar kad'an ne"

Nazir ya sake d'ago Amir din yace

"Don ma baki ganshi yanzu ba ne Shiyasa don yanzu yafi wannan girma sosai kullum sai k'ara girma da wayo yake yi, don har ya fara bin gini yana tafiya"

Amrah ta zaro Ido waje tace

"Watanshi takwas fa??"

Nazir yace "Eh takwas d'in ko don Inna cewa tayi in banda jikin da yake dashi da tuni ya fara saki don kiriniya ce dashi sosai"

AMRAH ta yi shiru saboda tuno ranar da aka rabata dashi da tayi, Nazir ya kalleta ta yi saurin share hawayenta tace

"Yayi saurin girma gaskiya"

Nazir ya b'ata fuska yace, "Ni fa bana son kukan nan fa"

Amrah ta sake share hawayenta tace "Ka yi hakuri na daina"

Daga nan suka ci gaba da firarsu har aka yi sallar magrib suka had'u da Mustapha suka tafi masallaciin da ke unguwar, Amrah da Fatima ko su ka tafi d'akin da Nazir zai kwana suka gyarshi tas suka baza Masa k'atuwar katifar Amrah suka shimfida masa sabon zanen gado suka feshe d'akin da freshner mai shegen dad'in k'amshi, sannan suka rufo masa d'akin kowace ta je ta yi sallah.

Koda Mustapha ya dawo Kai tsaye d'akin da za'a saukar da Nazir suka nufa ya nuna masa komi na d'akin sannan ya fito yayi cikin gidan.

Ya kalli Amrah da ke Kan sallaya falo sun gama sallah kenan ita da Fatima ya Sami gefen d'aya daga cikin kujerun ya zauna, ya jira sai da ta gama addu'ar sannan yace

"To ke an Kai karshe gobe insha ALLAHu tare da Mijinki zaku wuce, fatanmu kawai ki yi biyayya gidan aurenki ki rungumi Mijinki da mahaiyarshi da yaranki da Allah ya baki tsakani da ALLAH, duk da a dan zaman da muka yi dake na gano ba ki da wata matsala amman ko kina da kyau to ki k'ara da wanka, ALLAH ya baku zaman lafiya kuma ya sauke lafiya"

Amrah da Fatima suka ce ,. "Ameen"

Amrah ta share hawayen da suka zu bo mata tace,. "Nagode Auncle ALLAH ya biyaku da gidan Aljannah akan dawainiyar da kuka shayi da ni"

Yace "Ameen ai ba komi yi wa Kai ne ki je ki had'a kayanki ni inje wajenshi kafin ki kammala kada ya ga anbarshi shi kad'ai"

Ya mike ya fice gidan Amrah ta kalli Fatima tace,. "Ni Wallahi Aunty da an bari sai ya sake dawowa sannan mu tafi, amman wannan tafiya kwatsam! haka?"

Fatima ta maka mata wata jar harara tace,. "Amman lalle ke wannan yarinyar baki da kunya, yanzu ke duk wannan zaman da ki ka yi na dakon jiran ya zo kullum cikin damuwa yanzu ALLAH ya kawo maki shi a arha ki kawo wannan zancen banzan, to bari kiji WALLAHI kada ki kuskura ki bari Auncle dinki ya ji wannan zance har ya je kunnen Baba, don zaki janyowa kanki fad'a ne a banza, yanzu ko nisan inda ya fito ba kya kallo kice wai ya sake dawowa? To ki tsaya garin kallon ruwa kwad'o yayi maki k'afa, don na tabbatar yanzu haka Matarshi tana cen tana jin haushin biyokin da yayi, amman ace ki watsa masa k'asa a ido ya koma ba da ke ba ai sai kisa ta yi masa dariya, ki natsu da kyau ki ajiye komi ki bi Mijinki ki je rungumi abunki, in don ta yan uwa ko gobe zaki iya zuwa dashi kafin ku wuce kiyi sallama da kowa kuyi bankwana don kada ki tafi wani yayi korafin ba kiyi masu sallama ba"

Amrah ta mike tana share hawayenta tace

"Nagode Aunty Fatima har abada bazan mantaki cikin rayuwata ba, kin d'aukeni tamkar wata Yar uwarki ta jini ba dangin Miji ba nagode nagode Aunty Fatima Allah ya saka maku da alkhairi"

Tana k'are maganar ta yi d'akinta ta fara harhad'a duk wani abunda take b'ukata ta cika jaka fam da kayanta sannan ta zauna k'asa dirsham tana kukan tuno Zuwaira da tayi.

Akafta

D/Auta ce✍🏻

🌈🌈 BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

Wattpad PrincessDija246's

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

COMMENTERS A GAISHEKU DA K'OK'ARI 👍🏻

58

A zuciyarta sai jin take yi kamar ta rasa wani b'angaren na farin cikinta tunda har ba da son ran Mamarta zata koma gidan Nazir ba, aranta sai ganin take yi kamar idan ta yi hakan bata yiwa Zuwaira adalci ba, gaba d'aya jikinta a mace yake saboda wannan tafiyar da zata yi Uwa duniya ba tare da yardar Mahaifiyarta ba musamman a wannan lokacin da take fushi da ita, Amrah tuno dukan da Baba Nuhu yayi mata a kanta yasa ta fashe da wani kuka mai sauti har sai da Fatima ta shigo d'akin ba shiri tana tambayar ba'asin me ke faruwa?.

Amrah cikin kuka ta sanar da ita Mahaifiyarta take son zuwa wajenta ta roki yafiyata kafin su ta fi, gashi tasan da wuya in har Baba Nuhu zai amince kuma Sannan bata son ta je da Nazir Zuwaira ta yi masa abunda bai dace ba, don tasan wajibi ne sai hakan ta faru kuma ko kad'an

bata fatar ta ci wa Nazir mutunci a gaban idonta.

Fatima ta sauke k'atuwar ajiyar zuciya tace,. "Tabbas Amrah Uwa Uwa ce amman ki sani don kin bi Mijinki ba da saninta ba ai ina ga baki yi laifi ba, don umurnin Mijinki ne zaki bi don yana gaba da na Mahaifiyarki matuk'ar aka dorashi a mahanga ta musulunci, don haka ki hak'ura da zuwa wurinta don a wannan lokacin ko kinje daga ke har shi ba zaku sha da dad'i ba, saboda haka mafita d'aya ce ki bi shi ku tafi na tabbata maki ita da kanta sai ta nemi ki Ido rufe tana neman yafiyarki idan ta gano gaskiyar cewa abubuwan da tayi maki bata kyauta ba"

Amrah ta fara share hawayenta tace

"Ni Aunty bana son in tafi tana fushi dani na fi son ta sawa Aurena Albarka ko da sau d'aya ne a rayuwa"

Fatima ta rik'o hannunta tace,. "Zata saka maki fiye ma da sau dubu matuk'ar kika je kika yi biyayyar aurenki kika kyautatawa Mijinki, tashi ki je ki yi wanka ki je ki yi wanka kafin Auncle dinki ya dawo don nasan wajen Mijinki za ki je ki kwana"

AMRAH ta turo baki tace,. "Ni kam gaskiya Aunty ba a cen zan kwana ba gaskiya"

Fatima ta maka mata harara Sannan tace,. "Ni fa wannan sakacin naki shi yake b'ata man Rai da ke, kina so kuma kina kai kasuwa to ni ba ruwana idan har ya zo ya taradda ke baki shirya ba, kuma kinsan zai ga kamar ba kya jin maganarshi ne don kin ganshi k'aramin Kawu"

Amrah ta yunkura ta mike cikin sanyin jiki tace

"Ai matsayinshi ya wuce duk yanda kike tsammani a cikin zuciyata don ya hanani kukan rashin Uba, bari in shiga wankan yanzunnan in fito"

Fatima tana yi mata yar dariya tace,. "Ki tsaya ki gurji jikinki da kyau don wannan wankan daban yake da sauran wankan da kike yi a kullum"

Amrah ta rufe bakinta ta yi toilet d'in da sauri cike da jin nauyin Fatimar, tana wankan tana jin kanta a wata iri saboda ita har ga ALLAH tana jin nauyin ace ta je su kwana d'aki d'aya, don ko ba'ayi komi ba ganin za su yi kamar anyi d'in.

Cikin dan kankanin lokaci ta yi wankan ta fito sai ga Fatima ta shigo mata da wata hadaddiyar rigar bacci tana dariya ta ajiye mata akan madubin tace

"Ga tawa gudunmuwa yace ki fito ki je Mijinki yana jiranki don mu rufe gidanmu za mu yi yanzu"

Amrah ta zaro Ido tace,. "Au yau korata ma ake yi??"

Fatima tace ,. "Da babbar murya ko shirya kawai jirana yake yi yace dani da kin fita in rufo gidan in sameshi"

Fatima ta fice tana dariya Amrah ta bita da kallo ranta a jagule ta fara shafa mai sama sama sannan ta saka rigar baccin ta fesa turare ta kalli kanta a madubi ta juya ta dafe cikinta da ya fito ta yi yar dariya, Sannan ta dauko dogon Hijabi ta zumbula ta jawo plat d'in talkami ta fito suka ci karo da Fatima tace

"Yawwa ko ke fa mu je in raka ki"

Suka rankaya har suka fito cikin gidan, sannan Fatima ta dawo da sauri ta rik'e k'ofar tace,. "Ki je kawai sai da safe Ni ba zaki sakani zama surukar banza ba"

Tana k'are maganar ta rufo gidan Amrah ta bi k'ofar da kallo cikin sanyin jiki ta ja kafafuwanta ta nufi d'akin, ta shiga da sallamarta sai dai bata ganshi a d'akin ba ta dai jiyo motsin ruwa a toilet, ta sami gefen katifar ta zauna tana wasa da yan yatsunta tana nazarin ta wace hanya zata hilaceshi ya hak'ura da ita har sai sun bar gidan ko kuma ma sun tafi Gomben.

Tunaninta ya katse ne lokacin da taji motsin fitowarshi a toilet, gabanta ya kire ya fad'i ta yi saurin gyara zamanta ta yi kwanciyarta a gefen katifar ta runtse Ido zuciyarta sai bugawa take yi da sauri da sauri.

Ganin haka yasa Nazir yayi dan murmushin gefen Baki zuciyarshi cike da farin cikin ganin wannan rana mai cike da d'inbin tarihi a rayuwarshi.

Ya k'araso daga shi sai trouser yana share ruwa akanshi da dan k'aramin towel wanda da alamu daga wanka ya fito, ya zauna a kasan Carpet d'in yana pacing d'inta yace

"Haka ake tarbon Miji daga kwance??"

Amrah ta rufe fuskarta da hijabin da ke jinkinta tace

"Bacci Nike ji shiyasa"

Nazir ya zaro ido yace, "bacci? a yanzu? tab!!"

Ya mike tsaye ya fara binciken aljihun rigar da ya cire sai gashi ya fiddo wata Yar k'aramar kwalba ya dawo wurinta yana kume dariyarshi ya duk'o saitinta gaf da gaf yace,.

"Karb'i kayanki da na yi ta dakon ajiye maki don nasan zai yi maki rana a irin wannan lokacin"

Amrah ta yaye hijabinta da ta rufe fuskarta dashi ta Kai kallonta ga hannunshi ai kuwa ganin kwalbar yasa ta yi saurin juyawa ta rufe idonta, don ta tuna kwalbar abunda Aunty Asabe ta

bata ne tace ta dinga amfani dashi a duk lokacin da Nazir ya dawo gareta lokacin da ta zo tarbar kawo Amaryar Nazir Sadiya.

Cike da jin kunyar ganin kwalbar da yayi tace

"ba fa tawa bace"

Nazir yana dariya yace

"Ni Kuma a d'akin Amrah na ganshi kuma nasan ba Wanda zai ajiyeshi sai ita shiyasa ma har na yi ta faman ajiyarshi, karbi ki je ki saka ko Ni in saka maki da kaina"

Amrah ta k'ara rufe fuska tace,. "To bana sonshi yanzu ka sake b'oye mani har zuwa lokacin da zan nema"

Nazir ya mike tsaye yace,. "Aiko za ki ga aiki da cikawa domin ko yanzunnan zan saka maki shi da kaina, in jira lokacin da zai fara aiki sai mu fara buga wasar"

Amrah ta yi saurin tashi zaune tace

"Bani kwalbar in saka da kaina amman kasan a wannan stage d'in da nike yanzu bana b'ukatar ire iren wad'annan abubuwan fa"

Nazir ya shafa kanshi yace,. "Na sani amman dai ki dan saka man ko da kad'an ne"

Yana kare maganar ya janyo hannunta ya saka mata kwalbar yana dariyar mugunta ya yi kwanciyarshi a katifar yana fad'in

"Idan kika dad'e zaki ganni tsidik kuma kiji tsoron ALLAH ki d'an dangwala ko da ba yawa"

Amrah ta maka masa harara ta nufi toilet ya bita da kallo yana k'unshe dariyarshi, minti biyar a tsakani ta fito ta jefo masa kwalbar akan kafitar ta yi tsaye tanata bata fuska, Nazir daga kwancen yace

"Au idan an saka tsayuwa ake yi don yafi aiki kenan??"

Amrah ta yi saurin zuwa Kan katifar a bayanshi ta dukunkune cikin zumbulelen hijabinta, Nazir ya juyo da fuskarshi bakinshi cike da dariya yace

"Sanyi kike ji halan?"

Amrah ta sake b'ata fuska ta runtse idonta ta yi lamo kamar mai bacci, ya matsa jikinta ya janyota ya fara zare mata hijabin ta yi shiru ko motsin kirki ta kasa yi, hakan ya bashi damar

k'are mata kallo tun daga saman kanta har zuwa tafin k'afarta, ya sauke k'atuwar ajiyar zuciya yace,

"Rangadi wannan kwalliyar duk Ni kad'ai? Wow! To matso ki karb'i tukuici mai daraja"

Ya janyota jikinshi AMRAH ta fara tureshi amman hakan bai hanashi had'a jikinshi da nata ba, ya Fara shakar kamshinta yana sauke numfashi sama sama a cikin dimaucewa ya fara yamutsata tun tana tirjiya har ta saki jiki dolenta, sannan Suka baje kolin farantawa juna tare da nunawa juna kauna, cikin kwarewa da tsantsar zalama Nazir ya dinga sarrafata son ranshi don ita kanta ta gano ba k'aramin missing d'inshi ta yi ba, haka suka d'auki dogon lokaci suna abu d'aya tun tana juriya har ta kai juriyar ta gagara ta fara neman hanyar zillewa, aiko ta ci nasara don tausayin da ta bashi yasa ya kyaleta ba don ya so ba, haka suka kwana cikin farin ciki da tarairayar juna domin Nazir susucewa yayi akanta, sai faman tarairayarta yake yi tare da riritata kamar wani sabon kwai, tasha Albarka a bakinshi daga ita har su kansu su Baba Nuhun.

Asubar farin bayan sun yi wanka sun yi sallah Amrah ta langabe masa akan ya bari har gobe su tafi don bata jin kuzari ko kad'an a jikinta, ya rungumota jikinshi ya ce

"Ko da a hakan zamu tabbata Ni bazan gaji da wannan zaman ba in dai kina kusa da ni, amman sai dai kinsan cewa ni yanzu ma'aikaci ne ana matuk'ar bukatata a office kuma gashi Inna da my boy duk sun kosa da ki zo su ma su ganki,don haka ki lallaba kawai mu garzaya a hakan idan munje cen ki huta abunki"

Sannan ta yunkura tashi zaune cikin tsamin jiki tace,. "Bari in shiga ciki in k'ara had'a kayana"

Ya janyota a jikinshi yace,. "Ba yanzu ba sai na yiwa Babyna Ina kwana mun gaisa sannan"

Amrah ta b'ata fuska cikin shagwaba ta turo baki tace,. ,"To ai ya fad'a man bacci yake yi kuma ba yanzu zai tashi ba"

Aiko da dubara ya hilaceta har ya sake komawa fadar lambun gefen kogin bahar maliyarta, duk tirjiyarta bai hanashi baje kolin hajarshi a babbar kasuwar tata ba.

Misalin k'arfe bakwai na safe Amrah ta fito d'akin tayi cikin gidan zuciyarta cike da jin kunya da nauyin had'a idonta da su Fatima, cikin sanda ta shige d'akinta da sauri sai dai ta yi shuka a idon makwarwa domin kuwa Fatima ta ganta ba shiri ta tuntsure da dariya don ba k'aramar dariya ta bata ba.

Amrah kam tana shiga ta fad'a toilet ta tsalkake jikinta ta yi sabon wanka ta fito ta fara shiryawa cikin wata doguwar riga baka ta yafo dankwalinta ta fito da nufin ta gayar da su Fatima, Aiko sai gashi tana fitowa falon ta ci karo da Mustaphan zai fita da jakarshi ta zuwa office, ta yi saurin rusunawa ta gayar dashi cikin ladabi da jin nauyinshi, bayan ya amsa ne yace da ita

"To Ni zan tafi ALLAH ya tsare hanya ya kaiku lafiya kuma ya had'a fuskokinmu da alkhairi"

Tace "Ameen na gode sosai da dawainiyarka gareni ALLAH ya kara tsare muna ku da duk wani sharri"

Mustapha ya ce "Ameen yanzu zan je muyi sallama dashi kafin in wuce"

Amrah tace

"ALLAH ya tsare"

Yace "Ameen" Sannan ya wuce Fatima dake tsaye bayanshi tana dariya ta bi bayanshi suka fita, Amrah ta sauke ajiyar zuciya ta shigo falon ta zauna tana jinta duk a wata iri saboda tafiyar da zasu yi, don har cikin ranta tana ji dole ne sai tayi kewar Fatima da karamcin Mustaphan, tana nan zaune Fatima ta dawo cikin sauri tace

"Tashi ki Kai masa abun karinsa naji yace yanzu zaku wuce Auncle dinki ma signing kawai zai je yayi office ya dawo, don yanzu Baba ya kirashi yace dashi shi zai kai Abban Umar wajen Yan uwa ya gabatar dashi garesu"

AMRAH ta ji wata kwallah ta zubo mata tace

"Shikenan zan tafi in barku Aunty Fatima WALLAHI sai nayi kewarku da My Amir"

Fatima ta nufi diny ta d'auko tiren ta mika mata tace, "je ki kai masa sauri fa yake yi"

Amrah ta karb'a cikin ranta tace

"Yanzu ba bayan ya gama holewarshi"

Ta fice ta nufi d'akin tana ajiye masa ta zo taza fita da sauri ya kirata yace, "idan har kinsan ba zaki tsaya mu yi breakfast d'in ba to ki kwashi kayanki ki mayar ki je ki fiddo jakarki mu tafi"

Amrah ta dawo tana sunne kai ta dan durkusa kad'an tace,

"Ina kwana Yaya Nazir"

Nazir dariya ce ta sub'uce masa ya kalleta da kyau yace , "Lafiya Lau Yaya Amrah"

Ta fara had'a masa abun break d'in Sannan ta zauna da kyau ta mika masa cup d'in tea, ya karb'a had'e da hannunta yace

"Thanks mum of twins"

Amrah ta d'ago ta harareshi tace, "au anyi wani sabon cikin tsakanin jiya da yau kenan?"

Ya Fara kurba tea d'in yace

"Kinsan zan iya ai don nafi kowa iya zama Sharp shooters bugu d'aya goal ta shige raga kud'um!"

Ta ki biyeshi Saboda son da take yi su yi saurin gamawa kada Mustaphan ya dawo yaga sun b'ata masa lokaci, aiko sai gashi suna kammalawa ba su yi wani dogon jira ba ya zo, Fatima ta janyo jakar Amrah suka fito har bakin Motar Nazir, aka shigar da jakar Boot sannan Mustaphan ya shiga gaba ya zauna Amrah da Fatima suka shiga baya suna tafe suna Yar fira har gidan Yaya Harun, a gaggauce suka gaisa aka gabatar dashi ga iyalanshi sannan ya cikasu da alkhairi suka bar gidan suka nufi gidan wata yayar Zuwaira, haka suka ta yi ta bi gida gida har zuwa gidan Mahaifiyar Aunty Asabe itama yayi mata alkhairi mai yawa tana ta godiya suka fito, inda Kai tsaye gidan Baba Nuhu suka nufa ba tare da dogon turanci ba Baba Nuhu da su Yaya Harun Suka yi ta yi masu nasihohin hak'urin zaman aure, Amrah tana kuka saboda ta so ace da Zuwaira aka yi wannan zaman itama ta sakawa Auren nata albarka, Nazir kam sai godiya yake yi masu zuciyarshi cike da tsantsar farin ciki saboda ba k'aramin dad'i yaji ba akan karamcin da suka yi masa, Baba Nuhu yace dashi ya Kai Amrah gidan dangin Babanta ta nemi yafiyarsu kafin su tafi, amman yace kada ya kuskura ya taka gidan Zuwaira, cikin gamsuwa da zancensu cikin farin ciki ya yiwa su Baba Nuhu da Inna Dije alkhairi, don shi kanshi Amir sai da ya dunkuli manyan kudi ya bada abashi.

Haka suka rakosu kowa cikin farin ciki da kewar junan da zasu yi, Amrah kam sai sharar hawaye take yi ta makale Amir tana ta Kuka har sai da Yaya Harun ya katsa mata tsawa sannan ta Mik'ashi ta shiga motar tana ta sharar kwallar kuka, suna yi mata bye bye tana yi masu suka bar k'ofar gidan.

Suna tafe sai kuka take yi masa ya barta ta yi abunta don ta rage radadin abunda yake damunta, sai dai ya ci alwashin sai ya kaita wurin Zuwaira ko don zuciyarta ta k'ara samun natsuwa da zamansu, don yasan muddin ta yi masu cin fuskar da ta saba to dole ne ta gano gaskiyar abunda ake nusar da ita ta rungumi aurenta da yaranta.

Akafta😅

D/AUTA ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

Wattpad PrincessDija246's

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

59

Koda suka shiga Katsina Kai tsaye family House na su Babansu Amrah ya nufa da su, kasancewar Yaya Harun ya kirasu ya sanar dasu tun kafin su zo, shiyasa tun kafin su k'araso aka sanarwa duk wanda ya dace ya sani ko da suka iso aka tarbesu da murna kowa fuskarshi d'auke da farin cikin ganin wannan rana, ba tare da jan doguwar magana ba Amrah ta fara neman yafiyarsu akan bata masun da tayi, cikin sakin fuska duk suka nuna mata cewa komi ya wuce tare da yi masu addu'ar zama lafiya da yi mata fatar ALLAH ya sauketa lafiya, Sannan yayi masu godiya akan karamcin da suka yi masa yayi masu alkhairi sannan suka yi sallama da su suka fito zuwa wurin Zuwaira.

Tun a bakin k'ofar gidan Amrah ta ji k'irjinta ya buga saboda jin sautin Zuwaira da Lantana suna cacar Baki, cikin sanyin jiki ta kalli Nazir cike da jin nauyinshi ta fito ta nufi cikin gidan, Nazir wani tunani ya zo masa a Rai aiko ya fito ya bi bayanta, Amrah tana jefa k'afarta ta hangosu suna dambacewa tsakanin Lantana da Zuwaira, da sauri ta Isa wurinsu ta na fad'in

"Don Allah ku yi hakuri wannan abun da kuke ba girmanku bane"

Zuwaira ta yi saurin Kai kallonta ga Amrah ta zaro Ido ta saki Lantana ta nunata da yatsa Cikin fushi tace

"Uban wa ya kawoki wurina? Ba kiji duk kashedin da nayi maki ba Ashe? To bari kiji WALLAHI sawunki a likkafa ki koma inda kika fito tun ban yi wasar kura dake a tsakar gidannan ba"

Amrah ta fashe da kuka Lantana ta yi shewa tace,. "In dai kukane yanzu kika fara tunda har kika had'u da masifaffiyar Uwa gantalalliya wadda ta kasa zama gidan Ubanta ta nemi k'are rayuwarta a gidan haya tana nuna isah da iko a cikin gidan da bata da gado da shi balle wani nata"

Zuwaira ta yo cikin Lantana ta Kai mata duka Lantana ta yi tsalle tace ,. " Ai WALLAHI kinyi kad'an ki dakeni inki ramawa"

Aiko suka k'ara kacamewa da dambensu da sauri Nazir ya yayi ta jera masu sallama amman duk da haka ba su daina damben ba bale su amsa, Amrah ta yi saurin zuwa wurinshi tana kuka tace

"Don ALLAH zo ka rabasu kada su jiwa junansu rauni"

Nazir da sauran mutanen da ke tsaye suna kallon fadan suka k'araso cikin gidan, cikin tsananin takaici Nazir yace

"Haba! haba! don ALLAH ku San me kuke yi wannan abun da kuke yi ko kad'an bai kamace ku ba, don Allah ku yi hakuri ganin sunki bari ne yasa ya yi kokarin shiga tsakaninsu, aiko Zuwaira ta wawuro wani duka zata kaiwa Lantana Nazir ya rik'e hannunta cikin b'acin Rai yace

"Haba Mama ku shiga taitayinku mana ku duba ga yara nan fa duk sun tsaya suna ta kallonku"

Zuwaira ta fisge hannunta ta cira hannu ta wanke Nazir da mari tana huci, aguje Amrah ta k'araso wurinshi ta tsaya gabanshi cikin fushi tace

"Ni ya cancanta ki mara tunda Ni kika haifa ba shi ba, gani a gabanki ki kasheni tunda har bakya son ganin farin cikin...."

Zuwaira ta katse mata maganar saboda a zafafe ta sauke mata wani wawan mari har sau biyu a na uku ne Nazir ya rik'e hannunta yace

"Kin ci darajar da kike Uwa a wurin Matata don ALLAH kada ki bari in yi abunda Ni kaina zan ga ban kyauta ba, don ALLAH ki yi hakuri ki sakawa yarki Albarka don kulafuci irin na diya ga

Uwarta yasa ta kasa biyata na nace akan sai ta zo ta nemi yafiyarki, don Allah ki tausayawa yarki ko don juna biyun da ta ke d'auke dashi ki yafe mata".

Zuwaira tana huci tace, "daga Kai har ita ku fita idona in rufe tun kafin inyi maku abunda zaku fita a kafafun d'aukar masu daukarku su kaiku Asibiti"

Ta k'are maganar tare da tura Amrah da ke gaban Nazir dukansu suka yi baya cikin jarumta Nazir ya rik'ota ta fado jikinshi, Lantana ta yi wata gud'a tace "ayyururui Zuwaira Kinga abunki ganin idonki kuma baki gama gani ba tunda har girman soyayyarsu tayi tsanani haka gara kawai ki d'auki wuka ki cakawa kanki ki mutu ki huta don sunyi maki nisan da bazaki iya ja da ikon Allah ba"

Cike da jin haushin kalaman Lantana da suka tunzurata ta kalli Amrah tace

"ALLAH ya tsine maki daga ke har abunda zaki haifa tare da wannan matsiyacin mara kunya Mai Ido a tsakar kai, Kai kuma ka je kai da ALLAH zai saka mani a kanku Kai da munafukar Uwarka"

Nazir ya dafe goshi saboda miyagun lafuzzan da ke fitowa a bakin Zuwaira da suka ratsa kwakwalwarshiz ya janyo hannun Amrah da nufin su fita ta kafe ta fisge hannunta ta bita da sauri ta rik'o k'afarta tace

"Ni yarki ce Mama idan kin tsine man waye zai saka man albarka ta bini??? Na tuba na bi ALLAH na biki don Allah ki yafe mani Don Allah Mama"

Zuwaira ta juyo ta rufeta da duka ta ko'ina tana fad'in

"Kinsan da haka kika nemi ki tozartani a gaban mutane?? To har abada Ni babu yafiya a tsakanina da ke"

Tana rufe bakinta sai ga Abbati ya shigo cikin zafin Rai ya fisge Zuwaira daga dukan da take yiwa Amrah, ya d'ago Amrah ya jawo hannunta ya fita da ita har zuwa motar Nazir ya bud'e ya sakata a ciki zuciyarshi cike da tsananin b'acin Rai yace da ita

"Sai in kina shegiya zaki k'ara tako kafarki wurinta WALLAHI ko tunota kika sake yi ban yafewa Yan uwantakar da ke tsakanina dake ba, tunda dai ke kin zama uwar naci akanta ita Kuma kullum bata jin kunyar tozartaki da duk Wanda yarabeki,to kije ki bi Mijinki tsinuwarta ba inda zata je balai har ta kamaki,don kowa yasan baki yi Mata abunda ALLAH zai yi tirr da ke ba ballantana har tsinuwarta ta banza ta yi tasiri akanki"

Yana K'are fadar maganar ya kalli Nazir da ke fitowa gidan kamar Wanda kwai ya fashewa a ciki saboda tsantsar tausayin Amrah da ya kamashi,cikin jarumta yace dashi

"Ni Abbati na baka amanar Aunty Amrah ka zame mata Uwa da Uba har ma da mu danginta duka, ALLAH ya kaiku gida Lafiya ka gaida Inna da fine boy dinmu"

Nazir cikin sanyin jiki ya mika masa hannu suka yi musabuha sannan ya karb'i numbarshi suka yi sallama ya ja Motarshi suka tafi.

Abbati Kam sai da ya sake komawa gidan inda ya taradda Lantana sai miyagun maganganu take cab'awa Zuwaira,amman ko ta kanta bai bi ba ya fara balbalawa Zuwaira ruwan fad'a kamar ya daketa yace

"WALLAHI in baki nemi yafiyar Aunty Amrah ba kika mutu a wannan halin naki da kike ciki to da wuya in kina shiga aljannah, kin cutar da rayuwar Yar da kika haifa da cikinki don kinga tana tsoronki, to bari kiji ni Wallahi da nice ita da har abada ba zaki sake jin duriyata ba, na barki har abada don ba halittata kika yi ba haifata kika yi kuma ban zalunceki ba kece kika zalunceni, yanzu ko wannan abun da ya faru bai isheki ishara ba??? Kin sai da gida kin raba aure kuma gashi Allah bai kasheshi ba sun sake mannewa har da karin tukuicin rabon da ya sake shiga a tsakaninsu, don haka ki godewa ALLAH da har rabo bai kasheki ba aka sake baki wata damar domin ki tuba ga ALLAH ki sami tsira, idan kin hankalta kin nemi yafiyar yarki mai tsananin biyayya gareki tom! Idan kuma kince haka zaki ta biye wannan Munafukar matar Kuna rabawa kanku abun fad'i a unguwa to ki ci gaba gata ga ki nan Ni kunga tafiyata"

Ya fice fuu ya bar gidan zuciyarshi sai tafarfasa take yi da takaicin halin Uwarsu, wadda arzik'i bai yi da ita sai anbi ta hanyar tsiya.

Nazir kam kai tsaye gidan Baban Jamilu ya tafi ganin halin da suke ciki da shi da ita yasa ya yi ta basu baki tare da nusar da su amfanin hak'uri, basu bar gidanga har sai da ya tabbatar ya saka masu natsuwa a zuciya sannan suka nufi gidan Jamila, inda suka gaisa da su suka wuce gidansu don a acen za su kwana tunda asuba su kama Hanya.

Nazir ya b'oye damuwarshi yayi ta kwantarwa da Amrah hankali da nuna mata misalai kala kala na masu hakuri wad'anda suka ci ribar hakurinsu a gaba, da hilata da wayo da dabara ya kwana yana morewa aurenshi inda yayi nasarar cusa farin ciki a zuciyarta ta saki ranta suka yi ta shan soyayyarsu.

Asubar farin suka kama hanyar barin garin Katsina suka nufi hanyar zuwa Gombe, sun ci tafiya mai suna tafiya sannan suka isa Gombe cikin dare gaba d'aya duk sun jigata iya jigata, Amrah sai faman narkewa take yi saboda a rayuwarta kaf bata taba tafiya mai nisa irinta ba.

Sannu a hankali yana ratsa unguwanni da tituna aiko sai gasu wata unguwa wadda a duba d'aya zaka gano Quaters ne na ma'aikata, sannu a hankali har yayi parking a k'ofar wani Gida da yasha fenti sabon dal, abun burgewa gidan tsaf tsaf gwanin sha'awa yana rik'e da Jakar kayanta tana biye dashi har cikin gidan.

Shigarsu ke da wuya Inna ta fara fad'in "lale lale marhaban lale da zuwanku mutanen Katsinawan Dikko"

Amrah ta fara sunne kai cike da jin nauyin Innar Sabida cikin da ke jikinta da ya fito kuru kuru ana ganinshi, Inna ta yi saurin k'arasowa ta kamo hannunta Kai tsaye ta nufi d'akinta da ita tace

"Zo muje in kaiki d'akinki don daga ganinki wannan tafiyar ta gajiyar da ke sosai"

Amrah sai sunne Kai take yi tana biye da Inna har zuwa wani falonta madaidaici Wanda yaji kayan karau na gyara muhalli da luntsuma luntsuman kujeru sai tashin k'amshi yake yi kamar na wata sabuwar Amarya, bata tsaya da ita nan ba ta nufi kuryar d'akin da ita inda shima yasha kayan furniture's na alfarma sai kamshin sabunta suke yi, ta zaunar da ita akan gadon tace

"Zauna Kan gadonki ki sa albarka kafin Mijinki ya zo ya ya bani kud'in siyen bakina"

Amrah ta rufe fuskarta Sabida kunyarta da take ji don gaba d'aya Inna ta murje ta zama wata Yar gayu tsufanta ya b'oye saboda riritatan da Nazir yake yi, don ba yanda bata yi ba akan ya barta cen katsinar ta samo mai tamata zama amman yak'i, sai gashi zuwa da ita yayi Rana Saboda matsalolin da suka yi ta afkuwa itace ta yi ta d'ora Nazir a Hanya har komi ya zama tarihi.

Nazir ya shigo da jakar Amrah rungume da Umar a jikinshi Inna ta rik'e baki tace

"Yanzu sai da ka ta da yaronnan yana baccinshi???"

Nazir ya ajiye jakar cikin farin ciki yace

"Gara ya tashi Inna shima ai sai a tarbemu da shi "

Inna ta fice tana cewa

"To ni bari inje in kawo maku abincin anan d'in don nasan gaba dayanku a gajiye kuke"

Nazir ya kalli Inna yace,. "Ina Suwaibar ko tayi baccin itama??"

Inna tace,. "Ai tana gama sallah ta Fara kwana kasanta da nauyin bacci musamman idan ta yini tana aiki"

Nazir yayi dariya yace

"Bamotar ba to Ni dai tunda Matata ta dawo ALLAH ya fansheni daga yau na dena cin jagwalgwalon abincinta"

Inna ta bud'e baki tana dariya tace,. "Yau din ma ka bar mata kayanta ai sai ta d'umama da safe ta ci abunta in don Suwaiba"

Ta fice zuciyarta cike jin dad'in ganin Amrah da cikin dake jikinta sai jinjina girman tsalkin mulkin Ubangiji take yi,Wanda shine ya ke baiwa Wanda ya so a lokacin da ya ga dama.

Nazir ya kalli Amrah da ke ta satar kallon Umar yayi dariya yace

"To kunyar ta me kuma gaki gashi nan kiyi ta kallonshi don daman donki na daukoshi don nasan a k'agauce kike da ki ganshi"

Ya k'are maganar tare da Dora mata shi a saman cinya, Umar da har lokacin mayen baccin bai sakeshi ba ya fashe da kuka yana kallon Babanshi, Amrah ta kalleshi zuciyarta fari sol saboda ganin yanda yaronta ya koma tamkar dan indiyawa, gashi fari jajir da cikar bak'in gashi a nannde matsa ALLAH kamar dan Buzaye, gashi katoton gaske daga ganinshi zaka gano anyi barin gwangwanayen Madara a jikinshi.

Cikin jin dad'i ta d'aukeshi ta sakashi a jikinta tana lallashinshi aiko ya langabe abunshi a jikinta kafin kace me har ya koma baccinshi, ta lallaba ta ajiyeshi inda yayi dai dai da fitowar Nazir da yayo arwallah ya kalleta yace

"To maman biyu kema ki shiga ki yo arwallar ki zo mu Rama sallolinmu"

Ta mike tana waigen Umar ta shiga toilet d'in zuciyarta fes da d'inbin farin cikin da ya ratsa ko'ina na jikinta.

Akafta 💃

D/AUTA ce✍🏻
🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

Wattpad PrincessDija246's

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

60

Bayan sun k'are sallolin ne Nazir yace da ita ta dauko kulolin ta zuba masu abincin, tayi kamar yanda ya umurceta suka ciyar da junansu suna yar firarsu suna dariya har suk k'are cin abincin, Amrah ta kalleshi da kyau tace

"Ina son in yi maka wata tambaya sai dai ban son kaga ban ji kashedin da ka yi mani ba"

Nazir ya kalleta ya yi Yar dariya yace,. "Nasan mi ke cikin zuciyarki ko baki fad'a ba don haka ki adana tambayarki sai gobe wannan lokaciin bacci ne ko ke babu gajiyar tafiyar a jikinki?"

Amrah ta b'ata fuska tace,. "Wai me yasa kake kaucewa ne idan na yi maka maganar Sadiya? Naga banji motsinta ba har yanzu shiyasa na so in tambayeka"

Ya b'ata fuska ranshi a b'ace yace,. "Bana son ko sunanta inji an fad'a shiyasa kika ga bana son maganar tashi ki je ki yi wankan ki zo in maki tausa don nasan a gajiye kike ya fi maki da wannan tonon zancen da kike"

Ya mike ya ya d'auki Umar ya je ya kaiwa Inna shi sannan ya dawo ya taradda ita a inda ya barta ta yi tagumi tana nazarin maganar tashi, ya kalleta ya b'ata fuska yace

"Ki ma cire wannan tagumin ki tashi ki yi abunda ke gabanki in don macen da ta so ta sakamu kuka"

Ya saka hannu ya d'agota ta mike cikin sanyin jiki ya taimaka mata ta cire kayanta suka nufi toilet, tare suka yi wankansu wanda ya d'auki lokaci suna wasanninsu na masoya sannan suka

fito dukansu suka bi lafiyar shimfida makale da juna Amrah sai juye juye take yi saboda tsananin gajiyar da ke jikinta, Nazir sai dariya yake yi mata yace

"Ashe shi Naziru Matarshi raguwa ce"

Ta b'ata fuska ta turo baki tace

"Wannan doguwar tafiya ai dole jiki yayi ciyo ni fa ban tab'a yin irinta ba kaf rayuwata"

Nazir ya lakuce mata hanci yace,. "Sai gashi yanzu kin biyo Mijinki Uwa Duniya"

Amrah ta harareshi ta rufe idonta ta yi shiru kamar mai bacci ya janyota jikinshi yace

"Ki jira ki yi excersice mana ko da zaki ji jikin ya warware makk"

Ta fara tureshi amman duk da hakan bai hanashi neman hakkinshi ba, sai da ya gano dai da gaske bata so ne ya hak'ura ya koma yi mata aikin tausa har tayi bacci Sannan shi ma ya baje suka yi ta baccinsu mai cike kwanciyar hankali da gajiya.

Asubar farin ya tashi ya tada ita ita ta yi toilet shi ya nufi masallacin da ke unguwar ta su , bayan sun k'are sallahr ne ya nufi d'akin Inna ya yi mata ina kwana don ka'ida ne kullum idan ya dawo sai ya biya ya ga kwanansu sannan ya koma d'akinshi.

Ko yau hakan ce takasance suna k'are gaisawa ne ya nufo d'akin Amrah, inda ya taradda ita kwance akan sallayar ta dunk'ule cikin Hijab sai baccinta take yi, ya yi dan murmushi ya janyo filo ya ajiye kasan sannan ya tallabota ya d'ora akan filon shima ya kwanta ya d'ora nashi kan suna fuskantar juna ya fara fesa mata iska a ido, ta yi saurin bud'e idanuwanta suna kallon juna Ido cikin Ido tace

"Barka da safiya Mijina"

Nazir cike da jin dad'in maganarta yace,. "Barka juna Matar Nazir da fatar kin tashi lafiya?"

Ta yi masa wani kallon kauna tace,. "K'alau Kai fa?"

Ya dan b'ata fuska yace,. "Ni dai kam ba lau ba tunda har banji d'imin Babyna ba"

Amrah ta zunburo Baki tace,. "Wai kai me yasa baka gajiya ne kullim dai abu d'aya?"

Ya saka hannu ya fara shafo fuskarta ya janyo siririn hancinta yace,. "Saboda yanzu ne nake yin Angwancin don a cen baya ban karadda komi ba"

Amrah ta zaro Ido tace,. ,"Angwanci da wannan abun?"

Ta k'are maganar tare da d'ora hannunshi akan tulelen cikin nata, ya yi yar dariya yace,. "Ai ko shi ni ban kawo ta yanda ma nayi shi ba saboda fargabar da take cikin zuciyata a lokacin"

Amrah ta kyalkyale da dariya tace

"Au! cikin mayen bacci ka yi shi kenan aikam dai naga alama"

Ya sake janyota yana Murmushi ya fara aika mata da sak'una kafin kace me sun fad'a dausayin soyayya ta ma'auratan da suke tsananin son junansu.

Da k'arfe takwas dukansu sun shirya ya taka mata har d'akin Inna ta gaisheta sannan ta kalli Suwaiba da ke ta faman gyaran d'akin Innar kasancewar taganta babba yasa cikin ladabi tace

"Ina kwana"

Suwaiba tana dariya tace, "lafiya lau Amaryar Naziru"

Nazir ya hararеta yace,

"Uwargida kuma Amarya yau dai sai ki nemo masu cin abincinki don nikam girkin Matata zan ci bazan sake cin jagwalgwalonki ba"

Inna tana dariya tace

"Banda cika baki dai Naziru ka mance irin santin abincinta da ka sha yi sai yanzu ka dawo kana yi mata godiyar maye?"

Suwaiba tana dariya ta ce

"Kyaleshi Inna ina zaunena daga shi har Matar tashi sai sun nemeni"

Nazir ya nufi hanyar fita yace

"Ni dai bata abun karin namu ta shigo Muna da shi idan kin had'a amman ki sani daga shi shikenan ba zamu sake ci ba"

Inna tace, "Au baka tuba ba kenan har yanzu?"

Nazir ya fita yana fad'in, " daga yau ne kawai ai Inna"

Dukansu suka saka dariya Amrah dai iyakacinta murmushi bayan fitarshi ne Inna ta kalli Suwaiba tace,. "Suwaiba yau kinga Mamar Umar ko?"

Suwaiba ta kalli Amrah ta washe Baki tace,. "Naganta Inna Masha ALLAH da ita ALLAH dai ya basu zaman lafiya? Lalle da gaske Umar ita ya dauko sak! da kama"

INNA ta kalli Amrah tace,. "Amrahtu wannan da kika gani diyata ce saboda yar kanena ce Mijinta ya rasu bata tab'a haifuwa ba shiyasa na daukota saboda ta taimaka mani da renonshi tun lokacin da Sadiya ta fita"

Amrah ta ji gabanta ya fad'i amman ta dake tace, "ALLAH sarki sannunmu ALLAH ya jikanshi da Rahama"

Suwaiba da Inna Suka ce "Ameen"

Amrah ta kalli INNA fuskarta cike da son tambayarta gano hakan yasa Inna tace da ita , "Tashi ki je ki sallami Mijinki kada yayi latti a wurin aikin nasu" ta Kalli Suwaibar tace, "D'auki abun karin ki shigar masu da shi"

Amrah ta mike jiki ba kuzari zuciyarta cike da son jin me ya fitar da Sadiya?? Don tasan ko ma minene ba k'aramiin Abu bane tunda har INNA ta amince Nazir ya rabu da ita, zuciyarta cike da mamakin abun har ta isa falonta inda kai tsaye Suwaiba ta nufi tsakiyar falon ta ajiye ta fito, Amrah kam d'akinta ta nufa sai dai bata iske Nazir ciki ba ta fito falon sai gashi ya shigo shima da shirinshi na fita Office yasha suit ta kalleshi tace

"Ba dai fita zaka yi baka karya ba?"

Ya k'araso wurinta ya rungumota da jakarshi a rataye ya sakar mata kiss a goshi yace,. "Na makara fa ko so kike yi a bulaleni?"

Amrah ta zare jikinta ta rikoshi har wajen kayan ta zaunar da shi akan d'aya daga cikin luntsumammin kujerun da aka k'awata falon da su, ta karb'i jakar ta ajiye ba tare da ta ce da shi kanzil ba ta fara had'a masa abun breakfast d'in ta mika masa, ya karb'a a gurguje ya kammala ya sabi jakarshi ya fito yana gaba tana bayanshi har d'akin Inna yayi mata sallama suk fito ta rakoshi har gindin motarshi, tana yi masa ALLAH ya kiyaye har ya fice da tana d'aga masa hannu, Sannan ta koma d'akinta ta fara karyawar itama amman fa zuciyarta cike fam da tunanin mafarin fitar Sadiyar, ta yanke shawarar zata tambayi Inna don ita bazata ki fad'a mata ba kamar yanda shi yake ta shashantar da zancen.

Tana nan zaune tana zancen zucinta sai ga Suwaiba sabe da Umar yasha wankanshi tana hangoshi sai k'amshi yake yi ta washe fuskarta da Murmushin jin dad'in ganinshi don daman cen kawaici ne kawai ta yi lokacin da taje d'akin Inna bata ganshi ba, Suwaiba ta k'araso wurinta ta ajiyeshi gabanta tace da ita

"Ga yarona nan na kawo maki ya tayaki fira"

Amrah tana Murmushi ta rik'o hannunshi tace,. "Nagode dafatar dai ya iya bada labarai ?"

Suwaibar ta kwashi kayan break d'in ta nufi hanyar fita tana dariya tace,. "Kala kala kuwa duk wanda kike so"

Sannan ta fice AMRAH ta janyoshi ta zaunar dashi akan cinyarta tana k'are masa kallo zuciyarta cike da tsantsar farin ciki saboda ganinshi Masha ALLAH dashi gwanin burgewa, ta shafo sumar kanshi da take kwance luf luf da yayi gado irinta fulanin usuli, shi ko sai kallonta kawai yake yi tayi dariya ta lakuce masa hanci tace

"Ka sanni ne? Miye sunanka"

Shi dai kallonta kawai yake yi da ma yaga ta matsa masa da kallo ne ya sauka jikinta ya dafa kujera ya mike ya yi ta biyar jikin kujerun ya nufi wajen remote d'in da hango ya dauka, sannan ya yi zaune yana ta wasa da shi yana ta gwarancinshi shi kad'ai cike da jin dad'i Amrah ta mike ta daga saman carpet d'in da take ta zauna kan kujerar tana ta kallonshi tana jinta cikin farin ciki.

K'arfe goma dam Nazir ya aiko da cefane Kai tsaye Suwaiba ta kawo mata suka had'u kitchen suka fara girkin Abincin, suna yi suna yar firarsu ta rashin sabo da juna har suka k'are ne AMRAH ta je ta yi wanka tayi sallah Sannan ta nufi d'akin Inna da zummar ta yi mata tambayar da ke ta yi mata kaikayi a zuciya.

Aiko bayan sun gaisa ne ta kalli Inna cikin d'ar! d'ar! Tace,
"Wai ni ko Inna tunda na zo banga Sadiya ba sai gashi naji d'azu kince bayan fitarta ne kika dauko Suwaiba, to shine abun yake ta damuna nace Bari in tambayeki inji"

INNA ta yi shiru Sannann tace, "Nazirun bai fad'a maki ba ashe?"

Amrah tace, "ba muyi maganar dashi ba gaskiya har yanzu"

Inna ta sauke ajiyar zuciya tace, "waton ita Sadiya rudin zuciya da sharrin shedan ya jata da kuma miyagun abokai da shawarwarin munafukai Yan zuga wad'anda basa son suga ana zaman lafiya"

Amrah ta yi shiru tana kallon Inna cike da son karin bayani akan zancen nata, gano hakan yasa innar tace,

"Tun ranar da kika bar gidannan Nazir ya sauya gaba d'aya don ba ita da take Matarshi ba har Ni nan Naziru sai da ya sauya man akan rashinki da yayi, ita kuma ganin hakan yasa ta shiga damuwa ta ki barwa zuciyarta ta fara fad'awa kawayenta halin da take ciki, inda wata ta bata shawarar ta fara shan kwayoyin hana d'aukar ciki don muddin ta fara haifuwa bata janyo ra'ayin

Nazir gareta tun da kurciyarta ba to da ta jagwabe ta fara haifuwa shikenan ita tata ta k'are, shine ta amince ta fara shan maganin hana daukai ciki, Sannan ganin yanda Nazir yake ta fad'i tashi akan yaronshi yasa ta fara kishi tana jin haushi, tun bata kulawa har zugar kawaye tasa ta fara zaluntarshi a b'oye ba Wanda ya sani amman a gabanmu ta dinga nuna masa so Kamar ta hadiyeshi, ana cikin yanayin ne muka bar Katsina muka dawo nan to anan d'in ma tana had'uwa da miyagun makotan da ta kulla kawance da su suka k'ara zugata suna nuna mata cewa na takurata haka kawai in kwaso jiki in biyosu don kawai in zo in takura masu, suka nuna mata ta bi duk hanyar da zata bi in bar garinnan in koma inda na fito ko da zata samu Nazir ya dinga bata kulawa fiye da wadda yake nuna Mata, ta biyesu ta fara adawa da zamana har tana k'ok'arin yi mani rashin kunya sai dai ban tab'a sanar da shi ba don bana son rigima ta bullu a tsakaninsu, Sabida baya zama kullum idan ya fita tun safe sai k'arfe hudu zuwa biyar yake dawowa watarana ma har shida ya ke kaiwa kasancewarshi ma'aikacin Banki.

Sai dai shima a dan zaman da yake yi a ranakun hutun mako ya fara korafin shige da ficen da munafukan makotan suke yi wurin Sadiyar, nice nake hanashi idan ya yi kudurin korarsu sai dai Ashe a b'oye yaje yayiwa mazajensu magana akan su daina shigo masa gida, amman duk da hakan ita da taga Nazir ya fita sai ta wanke k'afa ta je wajensu suna k'ara hure mata kunne.

To sai dai shi mutum duk abunda yake yi yau da gobe matuk'ar bai daina ba watarana sai Rana ta batar masa, don kuwa haka ta faru gareta wata rana ya dawo gida ya taradda ita tana yi man rashin kunya akan taci zalin Umar na yi magana, Aiko ya fara dukanta da kyar na tabeta hannunshi na hanashi saboda rantsewar da na yi akan kada ya sake dukanta, to tun daga ranar rashin jituwa ya shiga tsakaninsu nima ta k'ara k'arfin kiyayyarta gareni don a ganinta Ni na sakashi ya daketa, don a lokacin Abu kad'an zai sa ta kama Umar ta yi ta dukanshi har sai na zo na karb'eshi a hannunta, idan na yi magana tace Ni banga barnar da yayi mata ba k'arshe dai dashi zata fake ta yi ta yaba man bakankanun maganganu amman duk da hakan bana sanar dashi, ana cikin hakan watarana Umar ya tafi d'akinta bansan me yayi mata ba sai ganin na yi ta turoshi da k'arfi ya fad'i sai fad'a take yi tana zaginshi ta rufo k'ofar d'akinta da k'arfi, na zo da sauri na d'aukeshi abun mamaki sai Naga yaro ya langabe mani a jiki yana wani mashalo gwanin ban firgita, kafin kace me sai ga kumfa ya fara fita a bakin yaro aguje na tallaboshi na fito na nufi gidan wata Yarinya da ke girmamani sosai a unguwar kasancewarta malamar Asibiti.

Aiko tana dubashi ta karb'eshi da sauri cikin firgici ta ce in biyota, Muka shiga motarta cikin tsananin tashin hankali muka nufi Asibitin da take aiki, cikin gaggawa aka shiga dashi domin a bincikeshi don izuwa lokacin har numfashinshi ya fara yin k'asa, Ina nan tsaye Ina ta sharar kwalla Ina add'ua a raina Sabida gaba d'aya naji tsoro don jikina ya bani kamar yaron ba zai tashi ba.

An d'auki lokaci mai tsawo sannan yarinyar ta fito tana share gumi fuskarta d'auke da tashin hankali, ganin yanayin da ta ganni yasa ta fara lallashina akan inyi hak'uri an samu sa'ar shawo Kan matsalarshi, sai dai cikin tsananin b'acin Rai tace dani

"Inna ya aka yi yaronnan yasha guba???"

Na zaro Ido cikin firgici nace ,. "Guba???"

Ta tabbatar man da lalle guba ce aka bashi yaci Allah ma ya tsare yana da sauran numfashi a duniya da mai aukuwa ta auku, sai dai tace dole sai anyi masa aiki an cire gefen hanjinshi da suka lalace.

Na fasa kuka Ina salati ta nuna mani in kwantar da hankalina sun yi masa wata allura kuma zata kashe duk wata kwayar cutar da ke jikinshi, amman Dole ne sai anyi masa aikin don haka a sanarwa da Mahaifinshi abunda yake faruwa duk da ba'a buk'atar a ja dogon lokaci.

Ina kuka na ce da ita na baro wayar gida shine ta ce in sanar da ita inda wayar take ita zata je ta d'auko man sai a Kira Nazirun, na yi mata bayani ta je ta d'auko wayar don tun a cen ma ta kirashi tana sanar dashi abunda yake faruwa, Aiko sai gashi kusan a tare ma suka iso Asibitin don tana shigowa yana shigowa shima cikin tashin hankali yake tambayar meye mafari, Ina kuka na sanar dashi abunda na sani kai tsaye ya saka hannu akan takardar zuciyarshi kamar ta buga aka shiga da Umar d'akin da za'a yi masa aikin, sai ga Nazir ya kasa dauriya ya fashe da kuka ya nufi motarshi ya fad'a aguje ya bar Asibitin.

 Ashe wai fitowar da yayi dawowa gidan yayi ko da ya zo ya taradda d'akin Sadiyar har lokaciin a dantse cikin hargowa ya fara Kiran sunanta sai gata ta bud'e tana mutsutsuke Ido alamun daga bacci ma ta tashi, ba tare da binciken komi ba ya fara kai mata Mari cike da masifa ya yi mata dukan kawo wuk'a, Sannan ya had'ata da saki har uku kuma ya kira yansanda suka tafi da ita Ni duk ban ma san ya yi ba Ina cen Asibitin ina jiran tsammani har sai da ya dawo ne yake sanar dani.

Sai gashi cikin ikon ALLAH aka fito dashi anyi nasarar aikin satinmu biyu a Asibitin aka sallamomu yaji sauk'i Masha Allah, a lokacin ne nace dashi ya sa a fito da ita ta koma gida hakanan ai ta lallasu, to kinji mafarin fitar Sadiya"

Amrah ta sauke k'atuwar ajiyar zuciya

Akafta😟

D/AUTA ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

Wattpad PrincessDija246's

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 61

Amrah ta sauke k'atuwar ajiyar zuciya tace,. "Gaskiya abun bai yi dad'i ba ALLAH ya kyauta ya k'ara karemu da kariyarsa"

Inna da Suwaiba suka had'a baki wajen fad'in "Ameen"

Inna ta kara da cewa,. "Ke ma kanki sai kinyi hankali da wad'annan mutane don kuwa nasan da sun kyalla Ido sun hangoki za su ce sai sun shiga jikinki, don ba abunda suke yawo dashi a gidajennan sai gulmace gulmace da kananan maganganu don haka kisan yanda zaki zauna da kowaccensu, don idan aka d'auke maki wannan yarinyar ma'aikaciyar Asibiti da wasu cen da ban da basa shiga sabgarsu kusan dukansu haka suke da kananan maganganun"

Amrah cikin jimamin labarin Sadiya da Innah ta bata tace,. "Ni daman cen Inna kinsanni ba ruwana da shirgin kawaye barkatai, yanzu hakan ma ni ko kawayena wad'anda muka shaku da su sosai na dad'e basu ganni ba ban gansu ba balle wad'annan marasa aikin yi"

Cikin jin dad'i INNA tace,. "Ai baza'a ce mutum ba zai yi kawaye ba amman dai kasan su wa ye suka dace kayi huld'a da su?, Don wasu rimi rimi za su nuna suna tare da kai amman idan aka tona sune gaba gaba wajen zama ayi da Kai, su kwashi sirrinka su je su bazawa Mutane sai dai ka ji ana kallonka a d'age ana kus kus ana yi maka kallon banza, wani fa don bala'i sai ya shiga jikinka ya san sirrinka tas abu kad'an zai had'aku fad'a ya je ya dinga fallasa ka mafita d'aya ce a wannan lokacin da muke cikinshi ka koyi b'oye sirrinka ta kowace hanya, don mutane yanzu sun zama abunda suka zama fatanmu kawai ALLAH ya karemu da sharroransu"

Su Amrah suka ce "Ameen"

Suna ta tattauna zancen ne aka kira sallahr la'asar kowacensu ta mike suka nufi wajen arwallah, Amrah Kam d'akinta ta nufa tayi sallah ko da ta k'are ma ta dad'e akan sallaya tana ta adduoin tsari da sharrin mutum da na aljan, ta yiwa Mijinta da dan yaronta da ya tsallake rijiya da baya don bancin da ALLAH ya tsare da yanzu ya zama tarihi.

Ta share yar guntuwar kwallarta sannan ta mike ta nade sallayar ta je ta sake yin wanka domin tarbar Maigidanta, aikuwa sai gashi tana Cikin shirinne ta ji shigowar Motarshi, cikin sauri ta feffesa turaren ta fito sai dai kuma ta ji nauyin yanda zata fita ta tarbeshi a gaban INNA, dole ta ja ta tsaya k'ofar shiga falon tana dakon shigowarshi ai kuwa sai gashi ya shigo kai tsaye wurin Inna ya nufa ya yi mata barka da gida sannan ya dauko Umar suka nufo d'akinta.

Tun kafin ya k'araso ya ji kamshin turarenta da sauri ya shigo falon suka yi arba da juna cike da tsantsar farin ciki suka rungume juna kowanensu cikin shaukin murnar ganin dan'uwanshi, Amrah ta karb'i jakar ta yi gaba ya biyota a baya yana faman murmushi har lokacin yana sabe da Umar a kafadarshi har kuryar d'akinsu, ya ajiye Umar akan gadon ya k'araso wajenta ya rungumota yace

"Sannu da gida Matata?"

Tana dariya tace

"Kai ake wa sannu Mijina kai da ke dawainiya da mu ka je ka samo ka kawo muna mu ci ALLAH dai ya k'ara dafa maka akan al' amurranka na yau da kullum, kuma ya kara budi na alkhairi ya tsare muna kai da dukkan wani sharri ko mi kankantarshi"

Cike tsananin jin dad'i ya ke ta fad'in "Ameen Ameen"

Ta taimaka masa ya je yayi wanka Sannan ya saka kaya zuwa doguwar jallabiyya ya nufi masallaci kasancewar kiran sallar magrib da aka kira a lokacin, itama ta je ta yo arwallar ta fara gabatar da tata.

Bayan ya dawo ne suka nufi diny ta zuba masu abinci cike da jin dad'i yake kallonta har ta k'are

ta zauna tace da shi

"Bismillah Mijina"

Ya kalleta yana murmushin jin dad'i yace,. "Na gode Matata Allah ya yi maki albarka"

Bakinta a washe tace

"Ameen"

Sannan suka fara cin abincin suna yar firarsu suna dariya cike da jin dad'i da annushuwa har suka kammala ta kwashe kwanukan ta fito da su a kitchen ta ajiye, ko da ta dawo ta ganshi a wajen kayan kallo yana had'awa ta Sami d'aya daga cikin kujerun ta zauna tana kallonshi har ya k'are ya dawo ya zauna kusa da ita yana latsa remote yana saita tashoshin ta kalleshi da shaukin sonshi ta langabe a jikinshi ta rik'o hannunshi tace

"Na gode da soyayyarka gareni Yaya Nazir ALLAH ya kara karemu da sharrin mutum da Aljan"

Nazir ya ajiye remote d'in ya kara matseta a jikinshi yana shafar gashin kanta yace,

"Ah yau dai Nazirun Inna ya zama dan gatan maman Umar, to ki adana kalamanki baki ga komi ba indai akan soyayyarki ce"

Amrah ta mike daga jikinshi ta rik'o hannunshi tace

"Yawwa yaya Nazir in tambayeka?"

Ya k'ara damke hannunta cikin nashi yace,. "Tambayarni yanzu a shirye nike da in amsa maki tambayoyin ko da ko sun kai d'ari ba cas'in da tara"

Daga shi har ita suka tuntsure da dariya sannan Amrah ta nutsa tunani na dan lokaci ta b'ata fuska tace, " mi yasa lokacin da na baiwa Jamila sak'o akan ta sanar da kai ina da ciki baka waiwayeni ba? ka kyaleni har tsawon lokaci ina ta dakon zuwanka gareni gashi a lokacin ana ta kiran wayarka kullum ba'a samu ba"

Nazir ya sauke ajiyar zuciya ya sake matse hannunta har ta yi Yar k'ara sannan yace,

"Tabbas Jamila ta sanar da ni daga ni har Inna munyi farin ciki da jin hakan sai dai kuma mun ji tsoron tunkararki ne Saboda halin Mama, shiyasa Inna tace da Ni in d'aga k'afa har ALLAH yasa idan ta fahimci cikin ta sauko da kanta ta amince da aurenmu in ba haka ba ko tsugunne bata k'are ba, don bazata tab'a zubar da makaman yakinta matukar dai ba ita ce ta sauko don kanta ba, to a lokacinne nake yawan kashe wayata don bana son zuciya ta debeni inki bin umurnin Inna duk da a takure nake kullum addu'ata shine ALLAH ya kawo sanadin alkhairin da

zai mallaka man ke ta ruwan sanyi ba tare da fargaba ko tsoron faruwar wani Abu ba, sai ko gashi cikin ikon ALLAH Baba Musa waton Baban Jamilu ya kirani yana sanar dani abunda ke faruwa, sai dai na nuna masa cewa ga abunda ya yi mani shamaki akan kusanto kaina gareki, na hadashi da Inna suka yi magana ta fahimta suka yanke shawarar a dan d'aga k'afa kafin muga nasarar da za'a ci ta bangaren ita Mamar, ana cikin hakan ne zaman Sadiya ya k'are a gidannan ganin hakan yasa Inna ta bani Umurnin in je in dawo dake, cike da jin dad'i na nufi Zamfara sai gashi cikin nasara na had'u da dattijan kirki mutanen arzik'i masu sanin yakamata suka bani ke cikin ruwan sanyi ba tare da nasha wahala ba, to kinji dalilin da yasa baki ganni tun a lokacin da Jamila ta sanar da ni ba"

Amrah ta share hawayenta saboda tuno Zuwaira da tayi cikin sanyin jiki tace,
"Mu godewa Allah tunda har yasa muna da sauran wani zaman"

Nazir ya rungomta jikinshi yana lallashinta yace,. "Insha ALLAHu kuma ba za mu sake rabuwa ba sai mutuwa ce kad'ai ta isa ko ita don tana dole fatanmu kawai ALLAH ya ara muna lokaci ya bamu Rai da lafiya mu mori aurenmu idan lokacinmu yayi yasa mu cika da imani"

Amrah tana kuka tace,. "Ameen"

***

Haka suka ci gaba da gudanar da rayuwar aurensu cikin aminci da kaunar juna, kowane Yana kaffa kaffa da bacin ran dan uwanshi haka ma ta bangaren Inna suna iya kokarinsu wajen kyautata mata.

Watan haifuwar Amrah yana kamawa ta haifo santalelen danta mai kama da Umar sak!, Farin ciki ga Nazir kamar ya take kan jariri Inna kanta ba k'aramin dad'i ta ji ba don wannan haifuwar da Amrah ta yi ya kara sakata kaunar Amrah Uwa Uba yanda take mutuntata kamar ita ce ta Haifa ba Nazir d'in ba, hakan yasa ta ji shaawar ganin ta shirya da Zuwaira ko don hankalinta ya k'ara kwantawa.

Yan Katsina da Zamfara su ma sunyo tattaki har garin Gombe domin tayasu murnar wannan Haifuwar, cikinsu kuwa har da su Aunty Asabe da itama a lokacin take d'auke da cikinta amman duk da hakan sai da ta zo don tsananin dad'in da ta ji, Fatima ma da wasu dangin Zuwaira suma ba'a barsu a baya ba anyi taron suna lafiya aka sakawa yaron sunan Baban Nazir ana kiranshi da sunan Abie.

Anyi taron suna Lafiya an watse lafiya Nazir ya yi masu goma sha tara ta arzik'i sai murna suke yi suna yi masa godiya, lokacin da zasu ta fi ne Aunty ta janyo Amrah gefe ta sanar da ita itama fa tana d'auke da ciki, cike tsantsar farin ciki Amrah ta yi tsalle ta ce

"Alhmdllh Aunty mun godewa ALLAH daman shi ko mi da lokacinshi WALLAHI na yi murna

sosai ALLAH ya wanye Ido lafiya Aunty"

Aunty ta ja mata kunne tace, "to ki dai natsu ki k'ara kula da Mijinki kin dai ga nasara a hankali sai zuwa take yi cikin rayuwarki, Sannan ki yi ta yiwa ALLAH godiya da ya baki Miji irin Nazir, abu d'aya ya rage maki yanzu shine ki shawo kan Mahaifiyarki ta fahimci gaskiya don yanzu haka zancen da Nike maki naji ance tayi aure"

Amrah ta yi narau narau da Ido zata yi kuka Aunty tace

"Kada kiyi kuka ki dai ci gaba da yi mata addu'ar kawai ai ALLAH ma ji rokon bawanshi ne da sannu komi zai wuce har ma ki ga ya zama tarihi"

Amrah ta share hawayenta Fatima ta k'araso tace da Aunty ta zo ita kad'ai ake jira motar da zata kaisu ta zo, kasancewar mota biyu Nazir ya dauko masu yan Katsina dangin Baban Amrah daban ta 'yan Zamfara dangin Zuwaira daban, wad'anda suka zo da motarsu kuma su tafi abunsu amman duk da hakan bai fasa yi masu alkhairi ba.

Aunty ta yi sallama da Amrah ta fice don tuni an saka masu kayansu a motar, Fatima ta kalleta da kyau tace

"Haba tawajena mi ye abun kuka Kuma? Ba akwai waya ba? Sai mu dinga gaisawa ai "

Amrah ta rik'o hannunta tace,. "Aunty Fatima sak'on nan da na baki don ALLAH ki tabbatar ya isa ga Mama na baiwa su Abbati na su wurin Aunty"

Fatima ta yi saurin fad'in,. "Na fa baiwa Aunty Asabe ta Kai mata kuma ta karb'a insha ALLAHu ba za'a sami wata matsala ba, ki kwantar da hankalinki ai Auntyn ba zata biyeta ba"

AMRAH zata yi magana kenan sai gashi an zo kiran Fatimar ta zo motarsu zata tashi ta fita da sauri Amrah ta d'auko mayafinta ta fito har wajen inda Inna da Suwaiba da wata makociyarsu mai kirki suke ta yi masu sai watarana, tare da addu'ar ALLAH ya tsare hanya har motocin suka tafi ba su daina d'aga masu hannu ba.

Sannan Amrah ta dawo tana kukan rabuwa da su, Inna da Suwaiba da Makociyarta mai suna Maryam suka yi bata hakuri.

*****

Zuwaira kam ita da Lantana zama yaki dad'i kullum fad'a kamar kaji, don ita Zuwaira tace bazata bar gidan ba ko da kud'inta sun k'are tunda har Lantana ta sace mata kud'i, ita ko

Lantana ta kafe akan cewa tunda ba ita ta d'auki kud'in ba kud'in da ta bada suna k'arewa zata bar mata gidanta tunda ba da kud'inta aka ginashi ba, gori da habaici kala kala babu wanda Zuwaira bata sha wurin Lantana akan hakan ne ma ta fara jin kamar bata kyautawa Amrah ba, gashi ba damar ta fita sai an yaba mata magana akan abunda ta aikata na sayar da gida don ta kashewa yarta aure kuma gashi yar ta koma gidan Mijinta tayi ba one ba two ba d'iyar hannunta kuma ba gidan Babu kud'in gidan duk sun salwanta.

Ganin bala'in da suke yi kullum ne yasa Lantana ta garzaya wurin Malaminta ta sanar dashi tana so a kori Zuwaira daga gidan, a yi ta hura mata zafin wutar asiri a jiki ya zamto ta ji ta tsani gidan da kanta ta kwashe komatsanta ta barshi ba shiri, Malamin yayi dariya yace

" Kice Sai ta dawo nawa gidan kenan? don wannan karon ba ta isa ta tsallakewa tarkona ba, dole ne sai na aureta ta zauna cikin Gidana na yi yanda nike so da ita"

Cike da jin dad'i Lantana tace

"Masha ALLAHU hakan ma ni yayi man in rabu da masifarta in huta, amman fa danginta da wuya in har zasu yarda ka aureta idan suka ganka"

Malamin ya kyalkyale da wata shegiyar dariya yace, "Ai su ma ba haka za'a barsu ba Dole ne sai an toshe masu bakin aibanta auren Sannan in fito da zafina"

Lantana ta yi shiru tace, "To ya zaka yi da matanka? naga su hudu ne cif!"

Malamin ya yi dariyar gefen Baki yace

"Ke ma kinsan dole d'aya waje zata yi don Wannan ba sabon Abu bane a wurina"

Lantana ta jinjina kai saboda tuno labarinshi da gidanshi akan Matanshi da shirgin yaranshi da ke jibge cikin kuntaccen gidanshi.

Aiko ya harhado mata magungunan da zaa yiwa Zuwaira kala kala nata da na Malamin ta nufo gida aka yi dace Zuwairar tana bayi ta ko fiddo wani ta barbada mata a k'ofar d'akinta, ta yi saurin barin wajen ta shige d'akinta da sauri sai ga Zuwaira ta fito da yar wakarta ta tsallake maganin ta shige d'akinta.

Aiko cikin kwana Uku Lantana ta aiwatar da aikinta sai gashi Zuwaira ta fara tsirar fitowa k'ofar gidan tana zama saboda gaba d'aya zaman gidan kamar a saman kaya take jinshi, sai ta fito take jin dad'in rayuwarta a lokacin ne Malamin yake yi mata wani turaren asiri, wanda yana turarashi a d'akinshi Zuwaira take fara shiga cikin wani yanayin bacewar hankali na dan lokaci da rashin natsuwa har sai ta je wajenshi, shi kuma ya saki jiki ba tsoron ALLAH yayita k'ok'arin keta mata haddi, sai dai duk da bacewar hankalinta bai sa ya ci nasara kanta ba saboda dan

banzan gumurzun da suke sha da ita, gano hakan yasa ya yi mata wani bak'in asiri ya aureta ba tareda ma tasani ba, don kuwa ko su Baba Nuhu basaja yayi masu ya tura wani a matsayin shi sai dai an d'aura auren da sunanshi.

Aiko yasa aka kwashe mata kayanta tsaf daga gidan Lantana aka kai gidanshi cikin wani dan k'aramin d'aki wanda shi kanshi d'akin Uwar Mazan yayanshi ne samari, ya koreta ya sakata aka jera mata kayanta a ciki ba rakiyar kowa ya daukota yakawota gidanshi, inda ba Matanshi biyu ba har su kansu yaran nashi samarin sun tsaneta mugunyar tsana, saboda ganin an kore Mahaifiyasu sanadiyyarta don matarshi d'aya da gidanta daban don ma Hajiya ce daga zuwa wajenshi neman taimako ya danna mata asiri ya aureta.

Aiko tun a daren farko Zuwaira ta fara gano bata da wayo, don kuwa tun ranar samarin yayan suka had'u suka lafta mata dan banzan duka sannan suka bar gidan, Matan gidan da sauran tarkacen yaran gidan suna kallonta suna ta dariya musamman jin da suka yi tana fad'in

"Don Allah ku yi hakuri kar ku kasheni ku taimakeni ku barni haka wayyo Allah ku yi hakuri Wallahi zan bar maku dakinku ku yi hakuri"

Koda Malam ya shigo cikin gidan ya taradda Zuwaira kwance tana nishin wahala saboda duk sunji mata rauni don ma wasu daga cikinsu har bulalar doki suka saka mata wajen yi mata dukan kawo wuk'ar, amman a hakan bai ji tausayinta ba ya bi ya tumurmusheta tana ihu tana neman agaji haka yagama shan shagalinshi ya tsallaketa yana dariyar mugunta, ba tare da ya damu da raukan da ke jikinta ba.

Kasancewar gidan nashi kaf ba Wanda baisan halin bunsurancinshi ba don a wata majiya ma har yaran nashi bai bari ba, shiyasa gidan gaba d'aya ba mai tarbiyya ga diya kamar kuda saboda yawansu amman kaf da wuya a sami biyu nagari, don a kididdiga ma yaranshi zasu kai ashirin da takwas saboda yawan aure auren da yake yi Yana saki, don da ya kyalla Ido ya hango mace ta yi masa ko tana da aure sai ya bi duk hanyar da zai bi ya mallaketa in kuma ya ga ba zai ci nasara ba sai ya yi auren ya kawo mace gidanshi ya ajiye da shi da yayanshi su yita ganawa mutum azaba, to sai gashi yanzu ya tsokanowa Zuwaira rigima tunda Uwargidanshi ce kacakam ya saka ya auro Zuwaira.

Satinta biyu a gidan ta bi ta susuce gaba d'aya ta hargitse ta yamutse saboda ba ta samun wadataccen abinci balle abinsha uwa uba ga masifar Malamin da diyanshi ba kwanciyar hankali ko kad'an kullum safiya da sabuwar masifar da zata gani, don ita har ta samu yana bata kud'in abinci saboda shi bai damu da kula da bada cefane a dafa abinci ba, da safiya ta waye ya mik'awa mai girki d'ari biyu ya fice shikenan sai kuma in lalura ta dawo dashi cikin gidan don yana d'akinshi dake k'ofar gidan na tarbar masu neman taimako wad'anda suka kasa barwa ALLAH zuciyarsu ta mutu suke zuwa wajenshi neman biyan b'ukata, duk da yana samu amman baya kula da gidanshi bale ya tsaya ya basu tarbiyya yanda ake so, kowa ta kanshi yake yi a gidan don wasu da yawan yaranshi matan duk sun lalace saboda rabi duk iyayensu basu gidan matan gidan kuma ba abunda ya shafesu da su kowa abunda yake so yake yi,ga su kamar

beraye saboda tsabar sata ba mazan ba ba matan ba duk Wanda ka yi sakaci da abunka yanzu zai wawasheka tsaf ba tare da ka tantance ba, don ko ita kanta Zuwairar zuwanta gidan duk sun sace mata abubuwa da yawa masu Muhimmanci ciki kuwa har da wayarta da sauran yan canjin da suka rage mata.

Ko da Amrah ta haifu ma da Abbati ya zo da nufin ya sanar da ita kiri kiri yaran Malamin Suka hanashi shiga gidan, Abbati kam zamanshi dan zafin kai yasa suka fara rigima har da su kokawa akan sai ya shiga su ko suka ce bai isa ba, har sai da Malamin ya zo ya raba fadan sai dai jin cewa wajen Zuwaira zai shiga yasa ya bata fuska yace dashi ya bar masa k'ofar gidan ko yasa a lakad'a masa dukan tsiya, Abbati ya yi zuciya yana gaggaya masa magana ya bar gidan zuciyarshi cike da kuna, don tun farko sai da ya so hana ta tarewa gidanshi ammman Zuwaira ta ki jin maganarshi don ko daurin auren sai dai ya jiyo daga sama, a lokacin da ba yanda zai yi sai zura Ido yayi kallon ikon ALLAH.

Ranar da Aunty Asabe ta je Kai mata sak'on Amrah ko da ta je ta taradda wata matashiyar budurwa tana k'arewa Zuwaira zagi ta uwa ta uba har da su dungure mata Kai amman Zuwaira tana zaune k'ofar d'akinta ko kanzil bata ce mata ba illah tagumin da tayi buta a gabanta zuciyarta cike da tunanin 'ya'yanta musamman Amrah da tafi shakuwa da ita fiye da saura.

Aunty tana yi sallama har sau biyu amman ba wanda ya amsa ta kutso Kai ta hango yarinyar tsaye kan Zuwaira ta fara jiyo sautin yarinyar tana fad'in,

"Ai WALLAHI mu a gidannan ba shegiyar macen da ta isa ta zo ta ce zata hanamu abunda muke so mu yi mu da gidanmu, ruwa ne kuma Wallahi tunda ba ke ko wani naki ya debo mana su ba zaki tab'a yin amfani da su ba"

Tana k'are maganar ta fisge butar a hannun Zuwaira ta zube ruwan kaf a jikinta duka ta wurgar da butar a k'asa ta tafiyarta.

Aunty ta k'araso cikin sanyin jiki ta tsaya tana kallon Zuwaira da ke zaune har lokacin da taguminta ta bi yarinyar da kallo, Aunty ta duk'o ta dafa kafad'arta Zuwaira ta yi saurin waigowa cikin fad'uwar gaba don tsammaninta ko wani ko wata ne zasu sake yi mata wani abun sai gashi idonta sun sauka akan fuskar Aunty, ta yi saurin zaro Ido bakinta yana rawa fuskarta a washe tace

"Asabe!!!"

Akafta😟

D/AUTA ce✍🏻

🌈🌈 BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

62

Ta yi saurin mik'ewa tana wasar Baki tace, "Sannunki da zuwa dafatar kin zo lafiya?"

Aunty Asabe cikin sanyin jiki ta kalli yaran da ke tsakiyar gidan sunyi cirko cirko suna kallonsu tace,. "Lafiya Lau Aunty ya gida kin ganmu da rana tsaka ko?"

Zuwaira ta sake washe Baki tace,. "Zo mu shiga daga ciki kin kwaso rana"

Ta yi gaba Aunty ta bi bayanta zuciyarta cike da alhinin halin da ta ga Zuwaira a ciki, ko da ta shiga zata zauna akan kujerar dake d'akin ne Zuwaira ta yi saurin fad'in "jira in d'ora maki wannan zanen saboda fitsari ne aka yi akai kuma gashi ko ruwan da zan sakawa ruwan babu don sallah ma yanzu haka banyi ba saboda rashin ruwan"

Aunty ta kalli Zuwaira da kyau sannan ta rab'a ta gefenta ta dosana duwawunta akan katifar da ke shimfide a tsakiyar d'akin, ta ajiye ledar da ke hannunta da jakarta sannan ta sauke ajiyar

zuciya tace,. "Ashe kinyi Aure Aunty? Shine ba ko sanarwa bale har mu zo mu yi ALLAH ya sanya alkhairi"

Zuwaira ta sosa keyarta tace,. "Ki yi hakuri abun ne ya zo a gaggauce shiyasa, amman ya aka yi kika san gidan? "

Aunty tana k'arewa d'akin kallo tace,. "Abbati ne ya kawoni"

Zuwaira ta zaro Ido tare da dafe k'irji tace,.

"Ina Abbatin ashe yasan gidan shine har yanzu bai zo man ba bale ya kawo Abdallah shima ya ganni"
Ta k'are maganar cikin kuka, Aunty ta yi saurin fad'in

"Ai ya zo fad'a maki Haifuwar Amrah Mai Gidan ya hanashi shigowa"

Zuwaira ta sake zaro ido hawayen da take makalewa suka zu bo mata tace,. "Shi Maigadin ya hanashi shigowar?"

Aunty ta gyad'a Kai tace,. "Tabbas don ma har fad'a yayi da 'ya'yan Gidan akan sai ya shigo amman aka hanashi shigowa"

Zuwaira ta yi shiru hawayenta suna zuba tace,. "Wayyo Abbati Abdallah fa?"

Aunty ta ce

"Lafiyarshi Lau har ma an maidashi Makaranta yanzu don ko yawon da yake yi yanzu duk ya daina daga Makaranta sai Makaranta"

Zuwaira ta share hawayenta tace,. "ALLAH ya raya me ta samu?"

Aunty ta yi Yar dariya tace, "Yaro ne ta Haifa Masha ALLAH da shi Nazir ma yayi mata hidima sosai kuma muma yayi muna goma sha tara ta arzik'i da muka je, saboda aikin Banki yake yi a yanzu yayi kud'i abunshi WALLAHI baki gani ba"

Zuwaira ta yi shiru ruwan hawaye suna sauka akan fuskarta, ganin hakan yasa Auntyn ta miko mata ledar da tazo da ita tace "ga sakonki inji Amrah tace a gaisheki"

Kafin Zuwaira ta karb'a zuruf suka ga an k'wace ledar dukansu suka d'aga Kai sai gashi ko sunga Malamin tsaye a gabansu yana huci ya nuna Aunty da yatsa yace,. "Tashi ki bar man Gidana tunda har Munafucci ya kawoki ba zumunci ba, tashi Wallahi ko insa yara su fita dake ta k'arfin tsiya"

Ledar da ya karb'a ya wullota waje da k'arfi aikuwa sai ga kayan da ke ciki sun watse k'asa tsakanin soyayyen Naman sunan da daugnot da cincin da cake da duk wani Abu da Amrah ta hado mata na bikin duk yaran suka wawashe sunata kuwwa, ba yaran ba har matan Gidan kansu cikin yaran suka shige sunata wawason kayan suna ihun jin dad'i suna murna, kafin kace me duk sun wawashe komi har su kansu ledodin sai da aka yi jayayya ga masu akansu ga masu son ledodin.

Aunty ranta a matuk'ar b'ace ta bi kayan da kallo ta maido da kallonta gareshi tana k'are masa kallo tace,. "Baka da adalci kuma ba ka yi mutunci ba sannan ka ci amanar rigar Malantar da kake shiga kake amfani da ita, ALLAH ya sakawa Aunty Zuwaira don Kai kanka kasan ba ta dace da Kai ba"

Malamin ya nunawa Aunty k'ofa yace,. "Zaki fita ko sai na nuna maki kalar rashin mutuncin nawa?"

Aunty cike da jin haushi tace,. "Na nawa Kuma? Ai sai dai ka k'ara Ni ALLAH na tuba in banda kaddara ma me zai kawoni wannan kuntataccen gidan"

Ta buga tsaki ta janyo Jakarta ta fiddo dunkulen kud'i masu kabri ta mik'awa Zuwaira tace,. "Gashi dubu Hamsin ce Amrah tace a kawo maki"

Zuwaira tana kuka ta zura hannunta zata karb'a Malamin ya yi zuruf ya karbe yana muzurai yace,.

"Tashi ki fice Uwar had'in kilbibi tun kafin in sa ki bar gidannan talkaminki a hannu"

Yana K'are maganar ya fice d'akin, Aunty ta bishi da wata k'atuwar harara ta d'auki Jakarta ta rataya ta kalli Zuwaira da ke zaune mukus ta kasa cewa komi sai ruwan hawayenta da take ta tsiyayowa tana sharewa ta kalleta da kyau tace

"Ni zan tafi Aunty amman ki natsu ki yi nazari zama wannan Gidan bai kamaceki ba, ki tuba ki komawa ALLAH don shi maji rokon bawanshi ne zai yafe maki duk abunda kika yi masa matuk'ar wad'anda kika cutar sunce sun yafe maki, Ni Kinga tafiyata Amman ki sani AMRAH tana cikin amincin ALLAH tana jin dad'in zaman aurenta hankalinta kwance ita da yaranta, don haka ki banbance gaskiya ki zubar da k'arya ki dawo hanya madaidaiciya na barki Lafiya"

Tana Kare fadar maganar ta fice ranta sai kuna yake yi saboda duk yanda ta Kai ga kawar da Kai da dauriya sai da ta share hawayen tausayin Zuwaira, Koda ta zo k'ofar d'akin zata saka talkaminta suka ce d'auki inda kika gansu, ta wara Ido ko'ina na gidan ba talkamin fuskarta a had'e takalli wata Yarinyar da ke tsaye tana kallonta tace

"Uban wa ya d'auke mani talkamina?"

Wata tsagera ta kantare k'ugu tace

"Ubanki ya d'auka ki je gidanku ki karb'o"

Aunty ta zaro Ido tace

"Ubanah??"

Kafin yarinyar ta bada amsa sai ga wata mata ta fito daga d'akinta tana taunar Naman bakinta a cike fam tace

"Shawara d'aya zan baki ki bar gidannan don WALLAHI Malam ya tafi Nemo yaranshi su fiddaki ta k'arfin tsiya kuma idan suka zo WALLAHI ba ruwansu dukanki za su yi don Yan shaye shaye ne dukansu wasu daga cikinsu ma har giya suke sha"

Aunty ta zaro Ido taji tsoro matuk'a amman cikin burga tace, "WALLAHI kuka yarda na fita baku bani talkamina ba sai kunyi nadama"

Ta fice fuuu suka bi bayanta da dariya dukansu d'aya daga cikinsu tace, "Sauka lafiya amman talkami Kam munci bulus"

Cikin dar dar Auntyn ta fito zuciyarta sai bugawa take yi don tsoron Yan dabar Malamin su zo su taradda ita gata da dan cikinta da suke ta tattali ita Maigidanta, don ko wannan zuwan da tayi bai so ba ya so a Aiko sak'on kawai amman ta nace ita zata kawo, Aiko tana cikin tafiya zata fice gidan kenan sai ga zugar yaran Malam maza kowane da abun duka, suna hangota suka nufota da gudu Auntyn ko ta ari na kare za su bita Malam ya dakatar da su suna huci Suka ce

"Da ka Bari mun kaddamar mata ai". Inji wani daga cikinsu Malamin ya hararеshi yace,. "Dad'ina da Kai rashin hankali Ni daman gurina a tsoratar da ita don kada ta sake dawowa kuma gashi ta ji tsoron don nasan gobe sai taji shakkun zuwa gidannan, amman in kuka kaddamar mata ai kun janyo muna bala'i Malami da Ni ace anyi haka a Gidana"

Aunty kam tana tafe tana sauke nishi har ta fito kwarkwadon lungun, sannan ta dafe kunkurunta da ke ta yi mata ciyo tana tafiya tana tsine masu aranta har ta Kai bakin titi ta sami Napep ta haye ta bar unguwar tana sauke numfashin Wahala.

Malam kam kai tsaye Gidan ya shige yanata wasar Baki ya shiga d'akin Zuwaira inda yataradda ita sai kuka take gurza, Yana dariyar keta ya fara kidanyo kud'i yana lissafawa ganin sun cika hamsin dam ya lissafo dubu biyar ya mika mata yace,

"Karb'i ki ajiye kud'in abincinki na wata biyu idan sun kare ki yi man magana in kara maki ko da dubu d'aya ce ki sa yi sabulun wanki"

Ganin taki karba ya ajiye mata akan kujerar da take zaune ya maida saura aljihu ya fice yana dariyar jin dad'in yayi babban kamu.

Har ya futa ya dawo ya lek'o kanshi yace

"Ki adana kudinki idan kika yi sake burgunan gidan suka gani shikenan kin rasa don kanki kika yiwa ba Ni ba, don ni na fita hakkinki"

Zuwaira ta damke kud'in ta k'ara sautin kukanta zuciyarta cike da tsantsar bak'in ciki da nadamar abunda ta yi wa 'yarta Yar guda guda gashi har yanzu bata yi fushi da ita ba.

******

Haka rayuwa ta ci gaba da garawa da Zuwaira a gidan Malamin har tsawon wata biyar, izuwa lokacin ta bi ta fige ta lalace damuwa fal ranta mai cike da tsantsar bak'in ciki da ma abun yayi mata yawa kai tsaye suka haifar mata da ciyon zuciya, a gefe d'aya kuma ta kamu da ciyon sanyi mai tsanani amman duk da hakan ko kwayar magani bata tab'a samu ta sha ba, kasancewar ba'a zuwa Asibiti a gidan Malamin shi yake dan basu yan jike jikenshi na surkulle suke sha a matsayin maganinsu idan anyi ciyo a gidan.

A hankali ciyo yana cinta a tsaye har ya kwantar da ita amman duk da hakan gidan kaf babu mai tausayinta sai Yarinya d'aya, ita din ma da take dan taimaka mata ba k'aramar tsamgwama take sha ba a wurin mutanen Gidan,.

A kowane wata Amrah sai ta yi wa Zuwaira aike ta hanyar Aunty amman Aunty bata zuwa sai dai ta baiwa Abbati ya kawo mata, saboda taji tsoron rashin mutuncin Malam da iyalanshi gashi itama a lokacin tana fama da kanta, saboda cikinta da yake dan bata matsaloli tun ranar da tayi gudun nan har zuwa lokacin da cikin ya tsufa haifuwa yau ko gobe.

Abbati kam tunda ya fahimci idan ya baiwa Malamin kud'in baya shiga ya kai mata saboda labarin da Aunty ta bashi, shiyasa ya ke neman yarinyar nan duk tsawon kwanakin da zai yi ko bai ganta ba, saboda sauk'in halinta da ya gani lokacin da ya fara cin karo da ita a k'ofar gidan har ma ta gaidashi, to ganin hakan yasa yayi mata bayanin matsayinshi ga Zuwaira sannan ya bata sak'on gaisuwa ga Zuwaira ya damka mata kud'in ta kai mata, sai dai kuskuren da ya samu a gaban idon wani yaro dan gidan aiko tun kafin ma ta isa cikin gidan shi har ya kai rahoto, aiko shigowarta ke da wuya yanmatan suka yo caa akanta suka kwakule kud'in a hannunta, ita ko ta ratsa kuka sai ga Malam ya fito yana tambayar ba'asin abinda ya faru, yanmatan suka yi shiru suna mazuran rashin gaskiya yarinyar kam bakinta sake ta yi masa bayanin komi, Malamin ya zaro Ido yace

"Waton shegen yaronnan sai da ya dawo ko? To ku kawo kud'in duka yanzunnan ko inci ubanku dukanku don WALLAHI akan kud'innan sai kunyi wata hudu ba tare da na bada kud'in cefane ko

na wani abu ba a gidannan"

Yaran suka fara fito da kud'in suna mika masa ya karbe yana ta fad'a abunshi ya fice yace da yarinyar ta biyoshi suka wuce, yanmatan suka k'unshe dariyarsu suka yi cikin gidan saboda duk da burarinshi a hakan wasu sun tashi da wani abin cikin kud'in.

Malamin ya ja ya tsaya k'ofar gidan yana waigen ta inda zai hango Abbati amman bai ganshi ba, ganin haka ya kalli yarinyar yace

"Daga yau idan ya baki kud'in Ni zaki kawowa idan ba haka ba WALLAHI na damkeki sai na kusa kasheki"

Haka yayi ta tsoratar da ita har Yarinyar ta tsorata sosai ya mika mata d'ari biyar yace ta d'auki hamsin ta kawo masa canji, sannan ya yi cikin gidan ya taradda Zuwaira kwance tana murkususun ciyo dafe da zuciya da cikinta tanata nishin wahala, amman ko dar baiji tausayinta ba haka ya jefa mata dubu biyu yace

"Ga kud'in abincinki nan na wata d'aya saura inji kin koma tambayata ko wani abin a gidannan bak'ar masifaffiya baki da aiki sai kunci da karyar ciyo kullum to WALLAHI Ni ba zaki sakani asarar kud'i ba idan bakya shan maganina sai dai ki tabbata da ciyonka a jiki Ni babu ruwana kuma ba abunda ya shafeni"

Tun daga ranar Abbati yake baiwa yarinyar sak'on don duk bulayin neman ta inda zai ga Yarinyar a unguwar sai ya ganta yake bada sak'on sai dai kuma yana bata zata kaiwa Malam ya bata nera hamsin ita Zuwairar ya kai mata dubu biyu watarana ma ko kud'in bai bata taushe abunshi yake yi.

Ana cikin haka ciyo yaci k'arfin Zuwaira don ya kai ko tashi bata iya yi saboda tsananin galabaitar da ta yi, yarinyar ce kawai mai tausayinta shiyasa da sace ta d'aukewa wata Budurwa a gidan kud'i ta nufi chemist duk da yake da nisa daga inda suke haka ta tattaka ta je ta siyo mata maganin ciyon ciki da ciyon zuciya ta kawo mata a b'oye, Zuwaira ta kokarta tasha maganin sai ko gashi cikin ikon ALLAH ciyon ya dan lafa mata, ta yi ta yiwa yarinyar godiya ganin hakan yasa tun daga ranar idan ta sami kud'i ta ke bata ta je ta siyo mata maganin a b'oye take kawo mata ta ajiye tana sha tun maganin yana yi mata aiki har ya zo ya daina yi mata saboda yawan shanshi da take yi akai akai, sai gashi wani sabon ciyo ya dawo mata ciki kuwa hadda ciyon ulcer lalura ta dawo mata sabuwa dal don kuwa zawo take fesawa kamar ruwa tun tana iya zuwa bayi har ta kai ko tashi bata iyawa daga nan take sako abunta, gashi bata da kowa a gidan Wanda zai yi mata hidimar zawon haka zata zauna cikinshi sai ciyon ya dan lafa ta yi hidimar abunta, don ko yarinyar Bata taimaka mata ta bangaren hidimar zawon, taimako d'aya ne take yi mata shine ta je ta debo mata ruwa duk da ko su din kafin Zuwaira ta yi amfani da su an kwashe fiye da rabin ruwan.

****

Ana cikin haka Aunty ta haifu ta sami santalelen yaronta Kato Masha ALLAH dashi, murna ta kowane bangare tayata ake ta yi ciki kuwa harda Amrah da daman cen taci alwashin duk ta haifu da ita za'a sha shagalin bikin, don ita izuwa lokacin yaronta da ta haifa yana dan wata shida, duk da Nisan da ke tsakaninsu haka Nazir ya sakosu mota tare da yaransu direbanshi ya kwasosu suka nufo Katsina, zuciyar Amrah cike da k'ulafucin ganin Mamarta da yan uwanta su Abbati.

Akafta😅

D/AUTA ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

63

Shigar dare suka yiwa Garin Katsina shiyasa kai tsaye suka nufi Gidan Nazir inda tun kafin su zo ma Jamila ta sa aka gyare masu gidan tsaf, Amrah cike da zumudin ganin Mamarta tun da sassafe ta shirya ta shirya yaranta ta matsawa Nazir ya kaita Family house na Babansu su gaisa sannan Abbati ya kaita gidan Zuwaira.

Aiko a gurguje ya shirya suka fito gidan kai tsaye Gidan Jamila ya fara kaisu sai da suka gaggaisa sannan suka nufi cen gidan, sunga tarba a wurin mutanen Gidan kowa sai nan nan yakeyi da AMRAH da yaranta da shi kanshi Nazir din saboda alkhairin da yayi masu lokacin da suka je sunan Abie a Gombe, dalilin hakan yasa suka k'ara daraja a idanuwansu sai haba haba ake ta yi da su cikin farin ciki da kuma firar yaushe gamo.

Bayan sun k'are gaisawar ne Amrah ta tambayi Abbati akace da ita yana Makaranta amman tunda yasan da zuwanta ko yaushe zata iya ganinshi, amman ta kasa jira ta d'auki waya ta kirashi yace da ita gashinan k'arasowa, sai ko gashi minti biyar a tsakani ya iso fuskarshi a washe zuciyarshi cike da jin dad'in ganin yanda Amrah ta koma, ta yi kiba abunta a kallo d'aya zaka gano kwanciyar hankalin da ta samu ga yaranta dagwas gwas! gwanin sha'awa farare da su Masha ALLAH kubul kubul wanke hannu ka tab'a da su.

Abbati ya karbe Abie a hannun wata budurwar gidan yana fara'a yace,

"Wow! Yarona sannunka da zuwa mauh!"

Ya sauke masa kiss a kumatu ya dauko Umar duk da yake dan lukuti fuskarshi a washe yace,. "Amman dai Ni za'a barwa su ko Aunty idan na yi aure in rikesu a hannuna"

Dukansu suka yi dariya Amrah tana dariya tace,. " Yanzun ma ai naka ne daman abunda ya rage kawai Ka d'auki abunka Ni na huta da reno"

Abbati ya k'ara rungumesu a jikinshi ya kalli Nazir yace

"Da gaske kun bani Yaya Nazir??"

Nazir yana dariya yace

"Anbaka sai dai zaka ara muna su har zuwa lokacin da zaka yi auren tukunna sai ka karb'a"

Gaba d'aya wurin aka sake kwashewa da dariya, cikin zumudi Amrah ta kalli Abbati tace

"Mu je ka kaini wurin Mama don ko Gidan Aunty banje ba cen nike son in fara zuwa in ganta"

Nan take farin cikin da ke fuskar Abbati ya gushe ranshi a dan jagule yace,. "Da kin fara zuwa wajen Auntyn daga baya sai mu je cen d'in"

AMRAH cikin sanyin jiki tace,. "Kada kaji komi Abbati mu tafi kawai Ni dai na matsu in ganta ne shiyasa"

Abbati ya sauke Umar ya rik'e hannunshi Suka fita Gidan Amrah da Nazir da sauran mutanen gidan suka rakosu har bakin motarsu, Abbati ya bud'e baya zai zauna Nazir yace ya zauna a gaba don yaji dad'in nuna masa hanyar gidan, amman yace

"A'a bari in zauna da yarana anan Aunty shiga mu je kawai"

Amrah tana dariya ta shiga Nazir ya ja ana yi masu bye bye Suka bar unguwar, sai dai tunda suka nufi Gidan Zuwairar Amrah ta dinga jin gabanta yanata fad'uwa har suka kai bakin titi, inda Dole anan suka ajiye motar don ba hanyar shigar da mota har zuwa gidan, don lunguna ne sirara a hanyar shiga zuwa gidan, Dole a k'afa suka tattaka suna ta tsallake kwatami har suka isa k'ofar gidan inda tun kafin su isa Suka hango taro a k'ofar gidan, don da alamu ma kamar fad'a ne ake yi duba da yanda Suka ga ana rirrik'e wani mutum da ke ta k'ok'arin dukan Malam.

kowanensu fuska cike da mamaki suka isa wurin sai ko gashi Malamin yana fad'in, "da Mutuncina a gari zaka zo ka kulla mani sharri to Ni na kawota wurina? Ko Ni nace ta zo ne?"

Mutumin da suke fadan yace, "Duk unguwarnan wa zai ce bai san halin akuyancinka ba dan akuya? don an fad'i cewa ko Yaranka baka bari ba balle wasu bak'in bunsuru kawai to WALLAHI Matata tafi karfinka don da ace tsautsayi yasa ka tabata da sai na kasheka WALLAHI"

Ganin hankalin mutane da yawa ya raja'a akan fadan Abbatin yace da Amrah su shiga kawai ta d'auki jakar kayan tsarabar da ta cikowa Zuwaira a ciki ta bishi a baya rankai rankai har cikin Gidan, sai dai dole suka yi turus saboda rashin sanin d'akin da zasu shiga, shiyasa da suka yi sallama suka tsaya saboda rabin mutanen Gidan duka suna k'ofar gidan wajen kallon fad'an, Aiko sai ga Yarinyarnan ta biyo bayansu tana washe baki tace da Abbati

"Ku zo mu je ga d'akinta cen"

Suka bi bayanta har k'ofar d'akin sai dai bata shiga ba ta tsaya tana toshe hanci don warin da ke fitowa a cikin d'akin, aiko sai gashi suma suna doso kai cikin d'akin suka shako bala'in warin da ke fitowa cikin dauriya suka shiga suna toshe hanci, abun bak'in ciki abun tausayi sai ga Zuwaira sun hango kwance magashiyyan ta yi zawo duk ya bata katifar kaca kaca sai kuda ke biyarta buu.

Amrah da Abbati suka zaro Ido cikin kuka Amrah ta yi kanta taje ta tallabota a jikinta tace,. "Mama!! Kece a wannan kazamin d'akin??"

Zuwaira ta Kai kallonta gareta da zurmammin idanuwanta da Suka yi rame tana mashalo saboda ciyon yayi mata mugun kamu, AMRAH Jinkinta yana rawa ta mike ta cire gyalenta Suka kinkimota suka fito da ita waje, Amrah ta kalli yarinyar tace da ita

"ina bayinku?"

Yarinyar ta nuna mata cikin rawar Baki Amrah tace Kai man ruwa acen yanzunnan, ta tallabeta ta kalli Abbati da ke gyara mata zanenta mai zawon da ya kwance tace

"Ji da d'akin Abbati Ni Bari inje in wanke mata jikinta"

Ta rungumota a jiki suka nufi bayin inda Kai tsaye ta tube mata kayan da ke jinkinta, Yarinyar ta yi ta debo mata ruwa a buta buta tana kawo mata, ta wanke mata jikinta tass da zawon sannan tace da yarinyar ta bata sabulun wanka, yarinyar tace

"Ai mu sabulun wanki ne muke wanka dashi a gidannan"

Amrah ta ce da ita taje wajen Abbati ta ce ya duba kayan da suka zo dasu ya fiddo sabulun wankan ya bata ta kawo mata, aiko dan lokaci a tsakani sai gata ta dawo da sabulun ta karb'a ta koma bayin ta wanke Zuwaira tass da soso da sabulu mai k'amshi, sannan tace da yarinyar ta je ta karb'o mata kala d'aya cikin kayan da ta kawo mata, ta je da sauri ta karb'o ta kawo mata ta amsa ta saka mata Sannan ta rik'ota suka fito bayin, aiko sai gashi ta hango mutanen gidan sun taru anata jibgar Yarinyar akan sai ta biyasu ruwan da ta kwasa ta Kai aka yiwa Zuwaira wanka, yarinyar sai kuka take yi suna ta jibgarta.

AMRAH cikin tashin hankali ta kai Zuwaira gefen iccen dalbejiyar da ke tsakar gidan ta ajiyeta ta jingina bayanta tana maida numfashi, AMRAH ta nufi wajensu da sauri tana fad'in

"Don Allah ku yi mata hakuri ku bari Ni zan biyaku kud'in ruwanku"

Gaba d'aya Suka daina dukan yarinyar tsagerar yarinyar ta kalli Amrah sama da k'asa tace,.
"Shafaffa da mai cikin kayan miya ke a suwa? To biya mu yanzunnan WALLAHI ko kema ki Sha na jakin"

Abbati yana fiddo kayan d'akin Zuwairar a waje ya kallesu ya k'araso wajen cikin masifa yace,.

"Kuka kuskura kuka tab'ata WALLAHI dukanku sai kun k'are rayuwarku a gidan yari don Mijinta ba k'aramin mutum bane akanta zai sa a tada unguwarnan duka WALLAHI, matsiyatan banza nawa ne kudin ruwan naku a biyaku yanzunnan?? "

D'aya Matar gidan ta yi gatsal tace

"Dubu d'aya ne abamu in an isah"

Abbati ya buga uban tsaki ya fiddo dubu biyu a aljihunshi ya jefa masu yace ,.

"Cikakkun matsiyata ga dubu biyu nan kuje ku ji da talaucinku kananun Yan iska kawai, wannan bak'in gida in ba Dole ba ma me zai kawo mutum cikinshi??"

Ya buga tsaki ya koma d'akin ya d'auki tsintsiya ya fara sharar tsakar d'akin, Amrah ta biyoshi tace

"Ina su Abie ne?"

Abbati ya d'ago ya kalleta yace,. " Na turasu wurin Babansu ka da su je su kwashi cuta a banza gara mu mun girma abun bazai yi affecting dinmu sosai ba, ki dubi wannan katifar gaba d'aya warin fitsari da Kashi takeyi don mugunta irinta maigidan da iyalanshi babu mai iya taimaka mata duk a cikinsu"

AMRAH ta share hawayenta tace

"Dama ka daina gyaran dakinnan haka don a gaskiya ba zamu barta a wannan kazamin gidan ba, zan kama mata hayar Gida ta koma cen ta yi zamanta yafi"

Abbati ya kalli AMRAH yace,. "To bari kiji ko yanzun ma sa'a muka ci da har muka sami damar shigowa Gidan, don na tabbatar da ace ba wannan rigimar da kika ga ana yi to bazamu sami damar ganinta ba, don maigidannan ba zai barmu ba mu shigo ba"

Wata tsagerar yarinya tace,. "Yanzunma ba ku tsira ba don kuna murna yan Sanda sun kama Malam ko? to WALLAHI su Bala suka iskoku sai kun yabawa aya zakinta"

Abbati ya d'aga murya yace,. "Su su Balan sunci Ubansu duka ki je ki kirasu yanzu ki ce su zo su kashemu"

AMRAH cikin sanyin jiki tace dashi,.

"To ajiye sharar d'akin Ni dai muje mu kaita Asibiti don jikinnan nata yana da kyau a duba muna ita"

"Abbati yace to Bari in mayar mata da kayanta"

AMRAH ta kalli kayan cikin kyama tace,. "Barsu kawai muje Ni dai baza'a rasa sanin abunyi ba"

Tana k'are fadar maganar ta d'auko turare ta fesawa Zuwaira da ke ta rabon Ido ba baki sai ido saboda ciyo yaci k'arfinta, itama ta fesa turaren saboda kayan jikinta da suke ta tashin warin

zawon Zuwaira, ta d'auki mayafinta ta je ta tallabota ta mikar da ita tsaye ta janyo wani wankakken hijabi da ke shanye saman igiyar shanya ta saka mata, sai ga wata Yarinya aguje ta zo gabansu tana huci ta rik'e hijabin tace

"WALLAHI sai anbani Hijabina na sallah Kam!"

Abbati ya fito d'akin yana fad'in,. "Ke matsiyaciya kema nawa ne kud'in Hijabin naki?? "

Ta murgud'a baki tace,

"Dubu d'aya da d'ari biyar"

Abbati ya fiddo dubu biyu yace

"Karb'i bace man daga nan WALLAHI kar in baraddake"

Ta karbe tana murna ta wuce suka rik'o Zuwairar suka fito Gidan sai gashi sunci karo da wasu yaran Malam sunata sauri su shiga don anje an sanar dasu, aiko suna ganinsu rik'e da Zuwaira zasu fita suka ce

"Ku saketa ta koma tun kafin mu fara gwadin iko akanku?"

Abbati yana ganin haka ya fice da sauri
Amrah ta k'ara rungumeta a jiki tana kuka tace

"WALLAHI sai dai ku kashemu a tare amman bazan bar Uwata cikin wannan hali a wannan kazamin gidan ba"

Wani mai bille a gefen fuskarshi ya zoro wuk'a a jikinshi yana muzurai yace,. "Zaki saketa ko kuwa?"

Amrah ta k'ara rungumeta tana kuka ya d'aga wuk'ar da nufin ya yanko mata hannun da ta rik'e Zuwairar ne yaji saukar naushi a fuskarshi cikin sauri ya Kai suka a gefen da aka nausheshin yaji an buge masa hannu cikin zafin nama, da sauri ya waiga Sai gashi ya yi ido biyu da Nazir da bai tsaya iya nan ba sai da ya sake wanka masa wani Marin wahala yayi masa wani mugun rik'o Wanda k'iris ya rage ya karya masa hannun.

 Bala ya fara mutsu mursu yana fad'in

"To sakeni nace tunda ka yi muna yawa"

Nazir ya K'ara rik'e hannun da k'arfi Baka saki wata k'arar masifa Nazir ya kalleshi cikin idanuwanshi yace,

"Babban gangancin da zaka yi a rayuwa shine ka tab'a mani Mata don WALLAHI zuriarku kaf sai na karadda ita akanta"

Ya kalli AMRAH yace "je ki kaita mota" Amrah ta ja Zuwaira suka fita sai dai mamakinta bata ga Abbati ba, ta shigar da ita cikin motar ta zaunar sannan ta koma gidan Umar ya biyota daga baya tana zuwa ta taradda Wani d'aya daga cikinsu ya yana huci ya fisge wuk'ar da ke hannun Bala ya kawowa Nazir yanka aiko yayi zillo ya kauce, ya sake kai masa wani yanka ya kauce ya bugi hannunshi da k'arfi hannun yace KAS wuk'ar ta yi tsalle Umar yana isowa ta fad'i saman k'afarshi, ya fasa k'ara Amrah tayi kanshi da gudu ta d'aukeshi tana kokarin cire masa kambas d'in da ke k'afarshi sai ko ga safar ta fara nashewa da jini da sauri ta cire safar sai ga wuk'ar ta yankashi, cikin rawar jiki da tashin hankali ta d'aukeshi ta saka safar ta d'aure masa wajen da sauri ta kawoshi motar ta ajiye inda Abie yake ta wasarshi ta dantse k'ofar ta koma, sai dai ganin sun rufarwa Nazir dukansu da duka yasa ta fasa k'ara mai k'arfi, kafin kace me mutane sun taru anata k'ok'arin raba fadan ne suka jiyo jiniyar yansanda tun daga nesa kowa ya fara darewa, amman ganin zasu tsere ne Nazir yace da mutanen su rike masa su, aiko caraf aka rirrikesu saboda daman cen ko yan unguwar sun addabesu suma, sai ko ga Abbati da yansandan yana gaba suna bayanshi sun nufo Gidan, suka cafkesu duka suka tasa keyarsu suka tafi dasu Nazir ya nufo motar cikin kunan Rai ya d'auki Umar yana duba k'afarshi duk da wuk'ar bata yankashi sosai ba amman ya ji kamar ya je ya shakesu duka su mutu, AMRAH ta zagayo wajen Zuwaira ta bud'a gefen da take zaune ganin ta langabe yasa ta fasa wata kuwwar Abbati da Nazir da sauran yan kallo Suka nufo wajen, tana kuka tace

"Mama ta mutu Abbati mun shiga Uku Uwarmu ta mutu ta barmu"

Nazir ya ajiye Umar cikin tashin hankali ya d'auko ruwan gorar ya watsa mata sai gata da sauke siririyar ajiyar zuciya, gano bata rasu ba ashe suma ne ta yi yasa suka shishiga motar cikin firgici suka nufi wata babbar Asibitin da ke Garin Katsina da ita, inda kai tsaye aka shiga da ita d'akin taimakon gaggawa Umar ma aka je aka yi masa dressing d'in kafar.

Kai tsaye bincikensu ya basu Zuwaira tana d'auke da ciyon sanyin Mara tare da Ulcer da ciyon Zuciya, a gaggauce aka fara treatment d'inta ta kowane bangare AMRAH sai kuka take yi su Abbati suna Lallashinta, Umar kam ma ganin tana kuka yasa shima ya fara kukan yana gwarancin fad'in

"Aunty k'afana zafi"

Sai da Abbati ya fita dashi da wayo da dabara har samu yayi shiru, AMRAH ta kalli Nazir tace,. "Abban Umar me zai hana mu Kira su Baba Nuhu mu sanar dasu halin da take ciki?"

Nazir ya furzar da iska a bakinshi yace

"Kin kawo shawara bari in Kira Mustapha in sanar dashi"

Aiko kira d'aya biyu yadauka bayan sun gaisa ne yake sanar dasu abunda yake faruwa, sannan suka yi sallama akan zai sanarwa Baba Nuhu da sauran Yan uwansu duk shawarar da suka yanke zai kirashi.

Aiko suna k'are wayar ne Aunty ta kirashi tana cewa dashi ta yi ta kiran wayar Amrah ba'a d'auka lafiya, ya mika mata wayar tun daga sautinta da ta ji yo Auntyn ta gano akwai matsala, Amrah ta fashe da kuka tana sanar da ita abunda yake faruwa, cikin sanyin jiki Auntyn ta fara bata hak'uri tace da ita Abbati ya je ya karb'o masu Abinci sannan suka yi sallama.

Kasancewar akwai yan uwansu Auntyn da suka zo daga cen Zamfarar biyu daga ciki suka biyo Abbati domin su ga jikin Zuwairar, ganin halin da take ciki ne yasa suka tausaya mata matuk'a duk da su tuni ma ta yanke zumunci da su amman hakan bai hana suka ji ba dad'i ba.

Koda dare yayi ma d'aya anan ta kwana tare da Amrah Nazir ko ya kai Umar gidan Jamila ya kwana saboda ya rage kukan da yake yi da rigimar da yake ta yi idan ya kalli bandejin da aka nade masa kafar dashi.

Akafta🧕

D/AUTA ce✍🏻

🌈🌈BAKAN GIZO🌈🌈

NA HADIZA D/AUTA

TAURARI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 64

Kwanan Zuwaira Uku a Asibiti aka yi sunan Aunty don dakyar ma Amrah ta samu ta je ta gano yaron wanda yaci sunan Usman, saboda hidimar Zuwaira duk da a lokacin ta fara samun kanta don duk da Likitocin sun hanata shiga damuwa saboda ciyon zuciyarta, amman hakan bai hana ta yin kukan nadamar abunda ta yiwa Nazir da Amrah ba, musamman idan ta kalli yanda daga shi har ita suke ta faman dawainiya da ita, ga kuma Yan yaransu masu burge kowa tana kallonsu tana share hawayen takaicin abunda ta yi masu a baya,.

Kwananta bakwai a Asibitin aka sallamota direct Nazir ya wuce da ita tsohon gidansu Amrah inda suka yi zaman makotaka a lokacin tare da su Nazir, mamaki fal ran Amrah da Zuwaira da Abbati da kuma Matar da take kula da ita wazon Yar uwarta.

Saboda tun daga wajen gidan yasha gyara Kuma yasha fenti ta ko'ina sai kamshin sabunta yake tashi, Koda suka shiga haka cikin gidan ma yasha gyara da wasu sauye sauye da ya K'ara fito da gidan dai dai da zamani, Zuwaira ta kalli Nazir cikin son karin bayani Nazir ya bud'e wani d'aki yace su shiga aiko dukansu suka shiga sai gashi d'akin sai kamshin dad'i yake yi Zuwaira cikin sanyin jiki ta kai zaune saman d'aya daga cikin kujerun tace

"Naziru ka man bayani zuciyata sai fargaba take yi ina jin tsoron nadamar da abin kunyar da nayi su zamo ajalina ba tare da na nemi yafiyarka ba"

Nazir yace kowa ya zauna sannan duk Suka sami wajen zama suka zazzauna, yana Yar dariya yayi Gyaran murya yace

"Gidanku ne Mama ya dawo gareku don tun tuni na sayi gidan a hannun wanda kika sayarwa dashi, sai yanzu nasa aka gyarashi fatanmu kawai a yanzu ALLAH Ubangiji ya baki lafiya sai ki yi zamanki anan don ki ci gaba rayuwarki cikin aminci kamar cen baya"

Zuwaira da Amrah suka fashe da Kuka Abbati ya je ya rik'o hannunshi yace,. "Mun gode mun gode yaya Nazir ALLAH ya jikan Mahaifa ALLAH yasa ka gama da duniya lafiya"

Kowa yace

"Ameen" Zuwaira ta k'ara sautin kukanta tace,. "Kaico Ni Zuwaira nayi wauta kuma nayi wa ALLAH shishigi gashi yau abin kunyar da na yi ya dawo kaina ka yafe man Naziru ka yafeman don ALLAH ka yafeman na cutar da kai ba bisa hakkinka ba yau gashi na fara tsintar kaina cikin tsantsar nadama da jin kunyarka, Ina ma zan ga Inna in bata hak'urin abunda nayi mata don ALLAH ka ce dani ta yafeman, Amrah ki yafeman kema na zalunci rayuwarki gashi ke har yau baki kullaceni ba,lalle kinyi gadon zuciya mai kyau a wurin Mahaifinku mutum mai tausayi da mutunta kowa mai sauk'in kai da sauk'in mu'amala, yau gani Allah ya jarrabeni da had'uwa da mugun Miji ko ta nan ALLAH ya nunaman sakayyar abunda na yi maku don Allah ku yafe mani"

Ta sake fashewa da wani sabon kukan AMRAH ta taso ta zo gabanta ta rungumeta tana share mata hawayenta tace

"Ni Daman cen tuni na yafe maki mama fatanmu kawai ALLAH ya yafemu gaba d'aya"

Ta waigo ta kalli Nazir tace,. "Mun gode sosai da karamcinka garemu Yaya Nazir Ubangiji ya saka maka da gidan Aljannah ko Aljannar ta kololuwa da Kai da Inna duka da zuriarku gaba d'aya"

Sai Ameen kawai kakeji ana fad'i Nazir ya mike yace

"Ni zan je in dawo"

Amrah tana share hawayenta tace

"ALLAH ya tsare hanya"

Zuwaira da hawayenta a fuska tace,. "Tashi kije ki rakashi ki k'ara yi masa godiya"

Cike da jin dad'i Amrah ta biyoshi suka tsaya corridorn gidan tana share hawayenta tace,. "Yaya Nazir ka yi man halacci a rayuwa bansan da me zan saka maka dashi ba a duniyarnan"

Nazir ya rungumota jikinshi yace,. "Ai Ni tuni kin saka man tunda har Umar da Abie suka ratso jikinki suka fito, fatana kawai ALLAH ya bamu Rai da lafiya Inga kin cika man Gidana da yaran da zaki yi ta haifo mani ina alfakhari da zamanki matata"

AMRAH ta fad'a jikinshi tana kukan kaunarshi saboda a rayuwar duniyar kaf ganin take yi babu wata macen da ta fita yin dace da Miji, don ko a ina zata tsaya ta yi tutiya da hakan har ma ta yi alfakhari ta bugi k'irji tace tafi kowace mace sa'a a duniyar.

Ya d'auki lokaci Yana lallashinta sannan ta rakashi ya shiga Motarshi ya tafi ta dawo cikin gidan, inda ta taradda sai hak'uri ake baiwa Zuwaira tanata kuka gwanin ban tausayi tana fadin

"Na cuci kaina na cuci 'yata yau gashi Wanda nayiwa butulci shine ya tallafi rayuwata nagodewa

Allah da har ban mutu ba sai da na nemi yafiyarshi"

Amrah ta zauna gefenta tana bata baki Zuwaira ta rik'o hannunta tace,. "Ki yafeman cutar da nayi maki Amrah naji dad'i kuma na godewa ALLAH da baki biyo bak'in halina ba ALLAHu yayi maki Albarka ya yiwa zuri'arku duka keda su Abbati gaba d'aya"

Ta karb'i Abie dake hannun matarnan tace,. "Duk Wanda yayi jayayya da hukuncin ALLAH tabbas shine zai Sha k'asa don abunda duk ya nufa sai ya tabbata ko ana so ko ba'a so don gashi yau gani zaune d'auke da yaron da na so zubar da cikinshi ta k'arfin tsiya, Ina jin sonshi a jikina ba kad'an ba"

Ta janyo hannun Umar ta daroshi akan kujerar ta rungumeshi jikinta tace,. "Zo ka rabi jikin Kakarka ka ji sanyi sanadina an ji maka ciyo kaima ka yafeni mani ka ji? na tafka abun kunya ya dawo Kaina amman Kai da Uwayenka baku gujeni ba"

Tana maganar tana kuka Kamar wata zararriya haka suka kasance har dare Zuwaira bata daina sambatun nadama ba, Ko da Nazir ya dawo da nufin yayi masu sai da safe Zuwaira tace ya tafi da Matarshi da Abie amman abar mata Umar anan ya kwana, haka ko aka yi AMRAH da Nazir Suka zille suka tafiyarsu.

Zuwaira sai k'ara jaddada godiyarta ga ALLAH take yi akan fahimtar da ita gaskiyar da yayi tun da wuri,.

Ko da safiya ta waye sai ga su Yaya Harun sun kira Amrah sunce da ita gasu akan hanyar Katsina, a gaggauce Amrah ta yi Gidan Zuwairar Nazir ya kawo cefane aka girka masu abinci, k'arfe d'aya dam suka iso gidan bayan sun ci sunsha sun yi sallah ne aka fara gudanar da abunda ya kawosu, suka fara yi mata ya jiki don da kyar Baba Nuhu ya amince suka zo, sannan Zuwaira tana kuka tana basu hakurin abunda ta sha yi masu acen baya, duk suka yafi juna sai dai sunce ta sami lokaci ta je ta baiwa Baba Nuhu Hakuri tana kuka tace daman tana da niyyar zuwa wajenshi don banda k'addararren aurenta ma ai da cen ma zata koma gaba d'aya, sai dai ta rokesu da suje wajem Malamin su nemar mata takardar sakinta gareshi sun nuna mata cewa ta yi hak'uri tunda dai har an riga da an d'auketa daga gidan.

Naziru ya zo suka yi masa godiyar dawainiyar da yayi da Zuwaira da gidansu da ya mayar masu, ya nuna masu ba komi yiwa Kaine ai, suka nemi gidan Aunty suka yo mata barka da arzik'i suka yi mata alkhairi don Amrah tun zaman da tayi acen wajensu ta Basu labarin irin hidimar da take yi da su, sannan Nazir yayi masu jagora zuwa gidan Malam Mijin Zuwaira saboda an sakoshi amman har lokacin bai je ya gano Zuwaira ba, yace Duk gidan Ubanda ta je sai ta dawo da kafafunta.

Aiko bayan sun fara gaisawa yagano Yan uwanta ne ya Fara kumfar Baki yanata bala'in fad'a akan cewa WALLAHI ba Ubanda ya isa yasa ya saketa tunda aka rufe Masa 'ya'ya akanta, ganin ba za'a kwashe ta dad'i ba yasa suka baro gidan dolensu saboda miyagun alkaba'in da

yake ta sauke mata ita da su, ya bururuce gaba d'aya sai bala'i yake zubawa ana rirrikarshi yana hauka.

Haka suka hak'ura suka dawo gidan Zuwaira suka yi mata sallama sannan suka ce da ita ta tashi tsaye da addu'a don saboda sun ga alamun rashin Imani a tattare dashi.

Haka suka rabu tana kuka tana basu sak'on yafiya wajen Baba Nuhu kafin ta zo, suka tafi suna mai tausayawa mata akan bala'in da ta ruzga na fad'awa hannun mugun Malamin.

Su Amrah suka fara shirin komawa don hutun da Nazir ya d'auka a office dinsu ya k'are tun da sassafe Nazir ya kwashi Zuwaira suka da su Abbati da yaransu Umar da Abi suka nufi Zamfara gidan Baba Nuhu, Zuwaira tana kuka ta rokeshi ya yafe mata abunda ta yi masa shi da INNA Dije, Baba Nuhu yaji dad'in ganin shiryuwar Zuwaira ganin tana nanuke da Abie alamu duk sun nuna nadamarta karara Kai tsaye ya yafe mata duk abunda ta dad'e tana aikatawa na rashin kirki garesu, cike da jin dad'i Zuwaira ta dinga godiya tana k'ara jinjinawa Nazir da yayi silar shiryuwarta da Mahaifinta da danginta, don kwanansu d'aya amman duk zumuncin da ta yanke sai da ta dawo dashi, marece sakaliya suka baro garin saboda su Nazir zasu wuce gobe tun asubanci,.

Ko da suka shigo katsinar sai da Nazir ya je ya lafto ma Zuwaira kayan abinci sannan ya roki dangin Babansu Amrah suka bata Abdallah ya dawo hannunta, sannan ya d'auketa duk da ba wani k'arfin jiki ne da ita ba har lokacin ya kaita wajen Aunty ta yi mata barka sannan ta nemi yafiyarta akan abunda ta yi mata, kasancewar Aunty mai sauk'in hali ce ba bata lokaci suka fahimci juna, Zuwaira ta yi ta yimata godiyar irin fad'i tashin da ta yi dasu musamman ga rayuwar Amrah, Mijinta ya dawo shima ta roki yafiyarshi Amrah da Nazir Kam sallama suka yi da su duka bayan sunyi mata goma sha tara ta arzik'i sanan Suka baro gidan.

Nazir bai bar gidan ba har sai da ya had'a Zuwaira da Inna ta nemi yafiyarta ita ma, sannan suka bar gidan cikin kewar juna da alhini rabuwa.

Sai dai Nazir ya je ya kai report d'in halin da Malamin yake barin Zuwaira aka ja mata layi da tsagerun yaran Gidan Malam akan kada su kuskura su taka gidanta, sannan ya bada Umurnin aka sako yaran.

Amman Zuwaira ta roki alfarmar yarinyar nan mai taimakonta da ta dawo gidanta da zama don daman cen ita kadaice Uwarta ta Haifa ta bar gidan, duk da gutsiri tsoman yan gidan bai hana Malamin ya amince ya bada yarinyar ba don dakanshi ya d'auketa da kayanta suka nufi gidan Zuwairar, saboda kud'in da Nazir ya bashi ya danne masa baki da su Dole yayi mukus.

*****

Bayan shekara biyu abubuwa da yawa sun faru na farin ciki da akasinshi ciki kuwa har da rasuwar mutum biyu Inna da Baba Nuhu, da zuwan Amrah da Nazir Makkah da Zuwaira da

Baban Jamilu da shi Jamilun da Jamila Kanwar Nazir, da kuma sake haifuwar da Amrah ta yi aka saka wa yarinyar da ta haifa sunan Innar ana kiranta da sunan Mimi, itama Aunty ta yi rurrutsa ta sake haifo mace taci sunan Amina Zuwaira kam duk da ba wani dad'in auren take ji ba amman ta sakawa kanta hak'uri da zama da Malamin hakanan, sai gashi kwatsam ba'a San mafari ba yana d'akinshi na tsibbo aka ga wuta ta tashi bal bal don ko mi ba'a fita dashi ba har shi kanshi ya kone kurmus sai tokarshi aka gani.

Iyalan gidan kowa jikinshi yayi sanyi duk da ta wani gefen sunyi murna da rayuwarshi don ya tare masu abubuwa da yawa a gidan, Zuwaira ma bayan fita ruwa ne ta mayar da yarinyar da take rik'o gaban Mahaifiyarta ta tattara inata inata ta koma Zamfara cikin Yan uwanta da gatanta.

Wani tsohon Mai sonta Dan uwansu Wanda aka so had'asu aure tun a farkon aurenta ya dawo suka yi aurensu cikin yardar yanuwanta.

A kullum Zuwaira sai sakawa Amrah da Naziru albarka take yi saboda sun d'auke mata hidimar komi a rayuwa don ko Yan uwanta ma suna rabar alkhairiinsu saboda ita, don ta ajiye komi ta d'auki Inna Dije Uwa ta riki Yan uwanta da zuciya d'aya.

Abbati ma ya k'are karatunshi ya Sami aiki ya auri d'aya daga cikin yayan kanen Babanshi da yake gidanshi zaune, Zuwaira da danginta na Uwa da Uba duk sun yi mata Kara sun zo bikin itama Amrah da yaranta hudu Namiji uku mace d'aya duk sun zo, da Suwaiba da ta yi aure a acen Gombe da yaranta biyu itama ta tako masu bikin, duk da yanzu su Amrah suna Abuja don acen aka mayar da Nazir da aiki Babban Bankin CBN dake cen.

An Kashi kudi anyi wacaka a bikin Abbatin don a lokacin shima ya fara zama da kafafunshi ga Nazir da Amrah da kafafunsu Suka dire sun dafa masa baya, don Abdallah ma yana cen hannunsu yana karatu, don Jamila kanta da Mijinta Jamilu da Mahaifinshi ba k'aramar damawa suke yi ba ta dalilin Nazir,don ganin yake yi komai yayi masu bai fad'i ba don tunda ya rasa Inna bayan Matarshi da Yaranshi bai da wasu dangi da suka kai masa su Shiyasa ya saki hannu ya sake kerawa Baban Jamilu wani k'aton gida na alfarma.

Suna cikin hidimar bikin ne suka Amrah ta hango wata almajira tana har had'a abincin da aka ci aka raga tana juyewa a leda jikinta sai rawa yake yi kar kar Kamar mazari,. Amrah ta k'araso wajenta tace

"Inna ki yi a hankali kada ki je ki ji ciyo"

Almajirar ta d'ago har lokacin jikinta yanata kyarma tace

"Wa nake gani kamar fuskar da na sani?"

Amrah ta zaro Ido tace "Ina kika sanni Inna?"

Matar ta fashe da Kuka tace,. "Ina Zuwaira in nemi yafiyarta Amrah don nasan na cutar da rayuwarta a baya"

Amrah ta zaro Ido tace,. "Ina kika sanmu ne? Wai ko dai Lantana ce naga kamar ita"

Lantana ta na kuka jikinta Yana rawa tace

"Ni ce Amrah Kinga yanda ALLAH ya maidoni saboda bak'in halina ciyo yaci k'arfina ba Ni da kowa sai Allah balle a tallafa Mani"

Sai ga Zuwaira ta k'araso wajen hauren makkarta sai kyalli yake yi a bakinta dafe da k'irji tace,. "Lantana ?? ALLAHu Akbar rayuwa haka kika koma me ya kawoki gidannan?"

Lantana ta fashe da Kuka tace,. "Ki yafe Mani Zuwaira don Allah hakkinki yana cikin abunda ya maidani haka a yanzu, na rasa komi na rasa lafiyata yanzu haka ciyon sugar ne Dani Banda kowa banda komi abincin ci ma yanzu banda mai bani haka nake ta yawo dakyar Nike samo abunda na jefawa bakina, duk da Likita ya haneni da cin abincin amman dole take sakani Ina ci tunda banda wanda zai d'auke mani nauyin kalar abincin masu ciyon sugar yanzu haka Ni kad'ai nasan me nake ji a jikina ki yafe man Zuwaira zaluncin da nayi maki a baya don ALLAH"

Duk Wanda ke wajen ya tausayawa Lantana don Amrah har da guntun kwallarta, haka mutane suka yi ta tattara mata kud'i suka bata Amrah ta nemi izini ga Zuwaira akan ta tallafa mata, Kai tsaye ta amince Amrah ta d'auketa ta kaita Asibiti aka rubuto mata magunguna da anincin da zata ci ta sissiyo mata komi ta kaita har gidan hayar da take zama, ta damkawa wata abokiyar zamanta komi tace ta dinga kula da ita zata biyata duk wata, sannan ta biya mata kud'in hayar har na shekara biyu sannan ta barota sai albarka take saka mata tare da addu'ar gamawa Lafiya.

Tammat bi hamdullah

Na godewa ALLAH da nuna mani k'arshen book din BAKAN GIZO mai shanye ruwa inda muka yi dai dai ALLAH Ubangiji ya bani lada, inda na yi kuskure ALLAHu ya yafe mani da ku gaba d'aya sai mun had'u a sababbin books dina masu sunan...

GIDAN AURE

da

JIKI DA JINI

DUKANSU ALKHAIRIN ALLAH YA KAI MAKU DUK INDA KUKE D/AUTA TANA KAUNARKU ALL🤝

muna inda na yi kuskure A